□ANA BARIN HALAL.....□

STORY AND WRITTING BY AUNTY NICE✍

®GASKIYA WRITER'S ASSOCIATION

(Gaskiya Dokin Kˊarfe□□Burin Mu Faɗakar Da Al’umma Domin Ribatar Duniya Da Lahira.)

BISMILLAHIR RAHMANIN RAHIM

PAGE 1

A hankali Hajiya Ayshaa ta miƙe daga tsakiyan gadon ta jiki duk a sanyaye tayi hanyar window ɗakinta dake kallon haraban gidan ta saka hannun ta wanda yasha jan lalle mai bala'in kyau ta ɗan yaye labulen ɗakinta, idon ta cike da hawaye take leƙen haraban gidanta, inda yake cike maƙil da yˊan kai amaryah, duk da tsiyar da ƙawayenta da suke zaune a ɗakin suke mata na rashin dauriyar da tayi na tafiyan yˊar na ta ƙwaya ɗaya dal kaman rai gidan mijinta, ita dai bata bi ta kansu ba hankalinta yana ga kallon jama'an da ke ta shiga motoci don zuwa kai amaryar gidan mijinta, a hankali ta sauƙe ajiyar zuciya ta juyo tana kallon ƙawarta data dafa Kafaɗanta, cikin ƙasa-ƙasa da murya ta furta, "*Aunty Nice* ban san yayah zanyi na jure tafiyan Maamah ba", lokaci ɗaya kuma idon ta yana ƙara cikowa da hawaye.

Cike da tausayawa na irin soyayyan dana gani a fuskan ta na dafa kafaɗanta nace, "ƙawata ae aure ba mutuwa bace, ba kuma rabuwa bace, ae abun kiyi farin ciki ne ki ƙara godewa ubangiji daya nuna mana auren Maamah, wanda ko wacce uwa take fata da burin taga ta aurar da yˊarta lafiya, mudai fatan mu Allah ya basu zaman lafiya, Allah kuma ya fitowa na baya da mazaje nagari, yadda Maamah ta samu," batare dana bar inda take ba na sake riƙo hannunta nace mata, "haƙuri zakiyi ƙawata, haka aure yake, kuma idan an kwana biyu zakiji sauƙin abun, banda abunki ƙawata ae dama dole mu rabu da yˊayˊan mu watarana," jijjiga kai tayi alaman hakane ta riƙo hannu na tace, "Aunty Nice na shaƙu da Maamah sosai, sai kuma ina ganin kaman bayan zu bane lokacin daya kamata tayi aure".

Hararanta nayi cikin wasa, na juya ina duban yˊar'uwarta da suka fito ciki ɗaya, wanda ta shigo tana kallon Aysha tana tambayanta kowa ya fita a ƙawayenta masu zuwa kai amaryar? Ayshaa ta juya ta kalli ƙawayen ta da suke zaune a kan gado

wasu a kan kujeru wasu a ƙasa, ta sake juyawa ga yar'uwarta tace, " masu zuwan duk sun fita, sune a cikin motan Hajiya Hadiza, dama mutum Uku ne zasuje",

Cikin hanzarin sister nata ta juya da fita daga ɗakin tana cewa, "Dama Goggo ce ta ce na tambayeki"

Haka dai muka cigaba da wunin mu har zuwa magrib, inda dayawa aka fara haraman watsewa, inda kowa ka ganni a cikin ƙawayenta hajiyoyin kansu ne, daga wanda driver ke jiranta sai wanda ita da kanta ta tuƙo kanta, biki ne dai irin bikin yan boko masu ji da naira, wanda komai kushewan ka kaje wurin wannan wunin sai ya burgeka, ga shi komai cikin burgewa da ilimi akayi shi, wanda duk wadata ta ɗaukaka irin na Hajiya Aysha batayi wani events masu yawa a bukin nan ba, liyafa kawai tayi haɗaɗɗe jiya jumma'a a Event Center na Bauchi, mai matuƙar ƙayatarwa, sai yau da aka haɗa ɗaurin aure da wunin bikin ɗiyarta, *NANA KHADIJAH (MAAMAH)*

Har zuwa gate ɗin gidan Hajiya Ayshaa ta rako mu, tana ƙara godiya wa bakinta da suka zo, a haka kowa zakaga ta buɗe motanta ta shiga, ko kuma drivern ta ya tuƙata, fuska ɗauke da murmushi ta juyo tana ƙara riƙe hannu na tana cewa, "Aunty Nice gaskiya nagode da ƙoƙarin da kika mun, nagode da zumunci Aunty Nice, Allah ya nuna mana auren Nabeelah da rai da lafiya", nima fuska cike da murmushi na dubeta cikin farin ciki nace, "Ameen ya rabbi Ƙawata, fatan mu Allah ya basu zaman lafiya da zuri'a mai albarka, Allah yasa baɗi mudawo taron suna",

Cikin rausaya da yanga wanda na lura halittan Hajiya Ayshaa ne, ta amsa mun da "Ameen ya rabbi ƙawata", sannan nace "tou yanzu ƙawata zan baki sati biyu ki huta, gajjiya ya bar jikinki, sai ki bani labarin da kika mun alƙawari, duk da dai nace nadai na rubutu yanzu" na faɗa fuska na cike da murmushi ina dubanta, Hjy Ayshaa cike da rausayar daya bi jikinta, ta lumshe kyawawan idonta a hankali kuma ta buɗe tana duba na, itama fuskanta cike da murmushi tace, "Aunty nice tawa, ae ko bai kai 2weeks bama zaki ganni, da zaran jama'a sun mun sauƙi xaki ganni har gida insha Allahu, idan kin koma gida ki gaida mun da Ɗana *BAPPAH NUHU, da yata NABEELAH* ki kuma miƙa mun saƙo a jama'an mu na *MUYI NISHAƊI DA NOVEL 2, har ma jama'an mu na TABITAL PULAKO* kice musu saura idan sunji labarin suyita zagina", tafaɗa tana ƙara murmushin fuskanta zuwa dariya, nima dariyar nayi nace, "insha Allahu zan ja kunnen su, duk da ma kina group ɗin kina kallon komai da jin komai", mukayi sallama na fito daga gate ɗin gidan, ita kuma ta juya zuwa wurin wasu ƙawayenta cike da rausaya, ni kuma hannu na cike da kayan tsaraban bikin da ta haɗani dasu, dayake ba mota bane gare ni balle driver, sai danayi ɗan tafiya mai ɗan nisa zuwa bakin titi, sbd unguwar tasu ta *G.R.A* wurin babu cikar abun hawa, ina isowa bakin titi na tsaya ina ɗan gyara zaman glashin fuskan na, na duba ƙafana ina kallon takalmina mai kyau na sallan bana da saura kaɗan wata taja

mun asara ta sace mun shi, daga ganin jama'anta da suka zo daga cikin gari ne, wanda sukayi maƙil ata can boys quaters, wata taso ta samfe mun shi ta fallashe ni, don ni banyi niyan sayan takalmi a bana ba, atoh yana yin rayuwar nan ae sai kanayi kana tattali, na kalli dogon riga na danaje Hanco ta zizaramun wani haɗaɗɗen ɗinki, zanina dana saya a wurin *JUWAIRI* itama a *MUYI NISHAƊI* take, matar badai iya zaɓawa mutum kalan zani mai kyau ba, ajiyar zuciya nayi na ƙara duban kaina nace, "oh mace har mace amma babu mota", dariya nabawa kaina naƙara gaba kaɗan na tari adaidaita, mun ɗanyi jayayyah da shi akan ina neman ya kaini a ɗari uku, amma firr yaƙi wai sai ɗari bakwai, kaman zanyi kuka haka na shiga, sbd wasu wurin an fara sallan magrib, ina iso gida na zazzage jakan da aka haɗani da shi, cike da farin ciki nace, "shiyasa nake son bikin masu kuɗi yan boko, komai nasu a tsare, wato komai dai da kika sani an zuba a ciki, su turmin zani ne sallaya ne, hijab ne, kai komai dai dakika sani an zuba aciki, kuma dama tun ana saura 1week biki ta aiko mun da bocket ɗin su cincin da sauran tarkacen kayan buki, kai matar nan Hajiya Ayshaa babu laifi, dama haka wasu Allah yake haɗaka da su, sai kudawo kaman yan'uwa, yanzu sanin da nayi wa Hajiya Ayshaa tun lokacin da nake rubuta *BADARIYYAH* amma ji nake kaman mun shekara 40 tare, Allah kabar mana zumunci Ameen.

Ringing ɗin waya nane ya farkar dani a bacci, wurin ƙarfe 9:46am na safe, narasa dalilin dayasa ban saka shi a silent ba, haka raina bai soba na jawo wayan zan kashe, sai naga *ƘAWATA* ɓalo-ɓalo yana yawo akan screen ɗin wayata, tashi nayi zaune na ɗauki wayan, cike da yangan ta naji muryan ta tana mun sallama, "Aunty nice barka da safiya", nima cikin fara'ar da ta wadata fuskata lokaci ɗaya na maida mata da gaisuwan ta, bayan mun gaisa take cemun yau insha Allahu wajen 11am zata zo idan ina gida, babu ɓata lokaci na dirƙo a gado na nayi toilet, a gaggauce na shiryah mukayi breakfast, a take kuma na ɗaura abincin rana bamai wuya ba saboda na samu daman zama da baƙuwa ta Hajiya Ayshaa, domin hiran da zamuyi da ita yau na musamman ne, duk da wataran takan ɗan tsakura mun kaɗan daga labarinta, muyi shawara a kan wasu abun, nima nagaya mata wasu daga cikin labarina, amma yau na musamman ne, tunda tace mun tun daga ranan haihuwar ta zata bani labarin kanta, har zuwa yau ɗin nan, Rice and stew nayi, sbd ta taɓa cemun favourite ɗinta kenan.

Ayshaa matar arziki matar kirki mai alƙawari mai gaskiya, wuraren 11:00am ɗin kuwa ta tuƙo kanta zuwa gidana, cikin farin ciki na tarbeta har parlor na ta zauna, cike da fara'ar da kullum yake kan fuskanta ta dubeni tace, "Aunty Nice kinsan haka kawai kike burgeni? har wataran nakanji dama ciki ɗaya muka fito, ina son ƙamshi, ina son gayu, gashi Aunty Nice kullum cikin ƙamshi da gayu kike, ni ba gidanki ba

kuma ba jikin ki ba, kin san kullum kikaje gida na sai Maamah tace kinzo," ina dariya nace "haba ƙawata ina ƙamshin yake, duk kawu na Tinubu ya takura mu ɗan turaren ma nakasa sayan dayawa yanzu, manage kawai ake ƙawata",

Kallo take bin ko ina a falo na takeyi da idon ta, " Aunty Nice kedai ki gode Allah da yayi ki yɘar gayu da son ƙamshi, kinsan ƙamshi rahma ne," "hakane na faɗa ina tashi don zuwa kitchen kawo mata abun sha,"

"Aunty nice don Allah ga wannan tou ki shiga da shi babu yawa" naji tana faɗa,

Bucket ne ɗan madaidaici, wanda yake ɗauke da dambun nama a ciki, ɗauka nayi na buɗe ina nuna mamaki fal a fuskata ina cewa "ƙawata wannan uban naman fa daga ina? Ke baki gajjiyawa ne kam"? "Wallahi wanda nasaka akayi ne wa Maamah na manta ban ɗiba miki ba, kinsan ban nutsuba wallahi sai cikin kwanakin nan nagani, tou dama nayi niyyan keda su Hajiya Hadiza da Zainab zan ɗiba muku, babu yawa ae", inji hajiya Ayshaa, godiya na mata na ɗauka nakai kitchen na adana, bayan na kawo mata abun sha, na nemi wuri a ɗayan kujeran da yake kallonta na zauna, "Ranki ya daɗe ina labari? Na furta ina kallonta fuskana cike da murmushi.

Juya idonta tayi cike da yanga da ruba, a hankali ta maida kallon ta ƙasa, kaman wanda take nazarin wani abu akan carpet ɗin, har zuwa wani lokaci kuma sai tayi dogon ajiyan zuciya, ta ɗago ta kalle ni.

Alhaji Usman Umar shine sunan mahaifin mu, Bafulatanine haifaffen garin *TAFAWA ƁALEWA* da yake garin bauchi, mahaifina cikakken ɗan boko ne kuma ɗan kasuwa ne, wanda yake da matan aure guda uku.

Uwargida Hajiya Khadija itace mahaifiyar mu, itama bafulatana ce, wanda sun fito gari ɗaya da mahaifina, wanda takeda yara guda biyar, Babban ɗanta mai suna Mohd, sai mai bi mishi Ahmad, na ukun su Umar, wanda yaci sunan kakan mu, daga kanshi sai da ta shekara takwai tukun Allah ya bata ni Ayshaa, a lokacin ta cire rai da sake wani haihuwan, sai Allah ya kawo ni, bayan shekara biyu kuma Allah ya bata ƙanwata Hafsat, wanda itace autar mu.

Hajiya Zainab itace matar mahaifin mu ta biyu, ita kuma bafulatanar toro ce, ita kuma Allah bai taɓa bata haihuwa ba, amma tana riƙon yɘar ɗan'uwanta mai suna Adda, takwarar tace amma ana ce mata Adda, ita kuma zata kai sa'ar Yayah Umar.

Hajiya Halima itace matar mahaifin mu ta uku, ita kuma yar garin *DARAZO* ne, na jihar bauchi, Hajiya Halima yaranta biyu ne duka mata, babbar sunanta Habibah ita sa'o'i muke da ita, amma ta bani wata uku, sai mai bi mata Raliya ita kuma sa'o'i suke da Hafsat, wacce dayawa muke cemata Hafsy.

Mahaifiyar mu muna ƙiranta Ummi, macece mai haƙuri da kawar da kai akomai, duk abunka da wuya kaji faɗa ko tashin hankali a wurinta, shiyasa abubuwa dayawa zaka ga kaman ana ƙwaranta sbd haƙurinta, acikin yayanta Yayah mohd da Yaya Ahmad da ni muka ɗauko halinta sak, inda Yayah Umar da Hafsy kuma bansan inda suka ɗauko zafin rai ba, don ko shi mahaifin mu zafin shi ba irin nasu ba, duk da shima mutum ne mai zafi da tsauri, amma ya kanyi wasa da dariya da iyalanshi, amma Yayah Umar kam zan iya cewa hatta matan gidan ma shakkan sa suke ji, ita kuma Hafsy kwata-kwata haƙuri ne bata da shi, ga tsaurin ido da rashin tsoro, don ita hatta Yayah Umar ya mata abu zata yi gaba ta ɗan taɓa gunaguni.

Hajiya Zainab kuma mukan ƙirata da Mama, ita kuma macece mai ɗan fushi, itama bata da faɗa amma abu kaɗan zai tunzurata ta yi fushi, gashi itama bata ɗaukan raini ko kaɗan, shiyasa duk rashin mutuncin Mami, wato Hajiya Halima ta kan ɗan ragar mata, don ita bata ɗaukan rashin mutunci ko kaɗan, don ko Baban mune ya mata abu atake zaka ga fuskanta ya canja, kuma zata fito ta gaya maka gaskiya, macece da bata yadda da wai wata ta fita ba a wurin mijinta, ko dan ganin ita bata haihu ba, tou bai taɓa sakawa taji ita koma baya bace, kuma ɗan kowa nata ne, saidai ita bata cika son taga yara suna raɓanta ba, dayawan lokaci idan jikokinta na wurin Adda sunzo zaka ga tana yawan kora su waje wasa, dayake Adda tayi aure har tana da yara uku, na farinta twins ne, sai yanzu da take goyon namiji.

Mamie kuma wato Hajiya Halima mafaɗaciyace na nunawa a gari, domin ita kullum garin Allah ya waye sai ta nemi faɗa, ba mijinba ba matan ba, ba kuma yaran gidan ba, duk da Yayah mohd da Yayah Ahmad sun girma, amma bata bar su ba, Yaya Umar ne kawai zai shigo gidan kaji ta ɓata shiru, har zuwa yanzu da muka fara zama yan mata fitinan ya dawo kammu.

Habiba itama muna kusan yanayi da ita, itama ko kaɗan bata da fitina, idan ka ganta zaka ɗauka Ummin muce ta haifeta, gata ita ma tayi farin mahaifinmu, ga ruwanta na fulani, bazaka taɓa cewa Mamie bace ta haifeta, babu garin Allan da zai waye baka ji faɗan su da Mamie ba, saboda Habiba ita tana da sanyin jiki aiki kaɗan

zaka ga ta ɗauki lokaci, wanda hakan zakaji muryan Mamie kaman zata ta yar da gidan don faɗa.

Raliya kuma wayo ne kaman zai kashe ta, kuma ita ta hannun daman Mamie ce, sannan duk wani rahoto ita ke kaiwa Mamie, babu abinda takeso irin taga ana tashin hankali, nan zaka ganta tana fara'a, kaman wata shaiɗan, shiyasa wataran tana shigowa wurin mu, zakiga Ummi tana mata nasiha, kaman gaske zata rusuna, amma bata wani lokacin zata koma halinta, ita da Hafsy ko kaɗan basu zama inuwa ɗaya da Yaya Umar, suma sanin halinsu baida kyau suna ganin yazo hutu zasu rage shigowa parlon Ummi,

Raliya munafurci da neman tsokana, hafsy rashin kunya, gashi kullum suna tare, amma baki mintuna kaɗan zakji sun kacame da dambe, akansu kullum sai Mamie ta shigo tayiwa Ummin mu rashin kunya da rashin mutunci.

Gidan mu gida ne mai girman gaske a G.R.A, Sakashim road, kina shigowa gidan filine mai girman gaske, wanda idan nace zai ɗauki mota guda ishirin tou banyi ƙarya ba, don idan ana hidiman biki a sake akeyin komai, duk wani programm a wurin ake yin shi, gidan sama ne side ɗin Baban mu, a side ɗin shi kuma idan kin sauƙo ƙasa akwai wani dogon korido, wanda zai kaiki side ɗin ko wacce mace a cikin su, wanda tanan wurin kowa take shigowa side ɗin Baban mu.

Ta waje kuma agefen dama flat ne guda mai ɗauke da parlor da ɗakunan bacci guda uku, wanda anan ne ɗakun su Yaya mohd yake kafin yayi aure, wanda yanzu daga Yaya Ahmad ne sai Yaya Umar.

Gefen hagu kuma shima kaman na su Yayah Ahmad yake, shima parlo ne da ɗakunan bacci guda uku, shi kuma Kakar mu ce Hajiya Ummah ce a zaune a wurin, amma bata daɗe da dawowa wurin ba, don da tana garin jos ne tana aure, rasuwan mijinta wanda bayan rasuwar kakanmu ta aure shi, bata haihu a garin jos ba, shiyasa yana rasuwa Baban mu ya dawo da ita gidan shi, tunda yanzu *TAFAWA ƁALEWAN* Baffanun mune guda biyu a gidan, wanda suke uba ɗaya da mahaifin mu, shima gidan Baban mu ya gama gyara shi, idan kinje zakiji kaman a bauchi kike, domin bai rasa komai na jin daɗin rayuwa ba.

Baban mu su uku ne a wurin mahaifiyar su, shine Babban cikin su kuma shine namiji a cikin su, sai mai bi mishi ita ce mai sunana, tun tana ƙarama Allah ya mata rasuwa, sai ta ukun su Aunty Rakiya, Mijinta babban mai kuɗine, wanda ya riƙe manyan muƙamai, da suna zaune a lagos ne, amma zuwa yanzu yayi ritire ya dawo bch da zama, inda suka ƙera babban gida a Fadaman mada, Aunty Rakiya akwai kaman ceceniyar hali tsakanin ta da Yaya Umar, gashi dama ɗan gidan tane, domin ɗanta na 2 Ishaq abokin shine, itama babbar yarta mace ce, Nana Asma'u, itama ta daɗe da aure a yanzu, sai dai itama ɗanta guda ɗaya dal,

Aunty asma'u ma'aikaciyace a CBN, tana zaune a garin Abuja.

Aunty Rakiya mutumiyar Ummin mu ce sosai, domin ita duk wannan aure-auren da Baban mu yayi takaici ta ke ji, domin ita macece mai tsananin kishi, ko kaɗan babu fuska a wurinta idan tazo gidan mu, ko wacce mace kuma Allah yasa suna shakkan ta, domin ita ɗin favourite ɗin Baban mu ne da kuma Hajiya Umma.

A gidan mu akwai parlo guda ɗaya mai girman gaske, wanda yake saman site ɗin Baban mu, parlo ne mai ɗauke da dining section mai girma, shima yana ɗauke da dining table mai girma, mai ɗaukan mutane 12, sannan doka ne a wajen Bban mu duk lokacin cin abincin dare dole ne a haɗu a wannan wajen, aci abinci tare kuma ayi hira tare, wanda rana ɗaɗɗayane mamie baza tayi faɗa da mutane a wajen ba, ƙarshe mama tashi take suyi barambaram ta bar wurin, shi kuma Yaya Umar duk ranan da yazama yana gidan mu tou tabbas idan ranshi ya ɓaci da faɗan su ƙarshe akan Raliya da Hafsy yake sauƙewa, daga nan kuma ya bar wurin ya koma side din Hajiya Ummah, akasarin lokuta shi da Yayah ishaq sun fi zama a side ɗin kakarmu.

Mamie bayan masifah ita macece mai yawon asiri, wanda kowa na gidan yasan da wannan ɗabi'an nata, amma Baban mu kuma baya yarda, don shi yace bai yadda da asiri ba, shiyasa take tsula tsiyar ta yadda taga dama, gashi ko kaɗan Aunty Rakiya basu shiri, inda Allah yayi taimako kuma tsoro da shakkan Aunty Rakiya ta keji.

Yaya mohd muna tsananin shiri da shi, domin komai nashi ni yake nema, muna jss 3 nida Habiba aka fara maganan auren shi da wata budurwar shi yar maiduguri,

ƙanwar abokin shine, tazo service bch sai ta zauna a gidan mu, sunan ta Bintu, gaskiya zan iya cewa na daƌe banga mace mai kyau da tsarinta ba, gata yar gayu na nuwa, naji daƌi da farin ciki danaji Yayah na danafi so zai auri Aunty Bintu, a site ƌin Ummin mu ta zauna, gashi tana bala'in kyautata mana, kullum da safe idan tana shirin fita inda take service bana gajjiya da ganinta, ga wani ƙamshinta kaman nayi yaya nakeji.

"Aunty nice ranan dana fara ganin ki naji kaman da Aunty Bintu na haƌu, saboda ƙamshin kanuri da naji kinayi, sai naji kema ina ƙaunar ki kwatan kwacin yadda naso ta" Ayshaa ta faƌa tana kallo na, nima cikin ƙara walwala fara'ar fuskata nace, "Aysha kina koƌani dayawa fa, yanzu matan *MUYI NISHAƊI* idan sunji ki sai su ƌauka haka nake fa da ƙamshi, har naje mrs Al'ameen Da takwararki Aisha jewal, da maman fodio sukawo mun ziyarar bazata" na faƌa ina ƙara murmushin fuskata.

Itama Aysha cike da fara'a a fuskarta tace, '"gaskiya ne ae Aunty nice, nidai haka kawai kina burgeni kuma ƙamshin ki yayi daƌi, dole ma ki haƌani da wacce kike sayan turarenki a wurinta, duk da dai Aunty Bintu bata rageni da turare ba har yanzu.

lokacin da maganan auren Yayah mohd da Aunty Bintu ya taso gadan-gadan, lokacin tagama Service har ta koma Maiduguri, Ummin mu ta wakilta Adda yar gaban Mama da wata ƙanwar Ummin mu wacce ake ce mata Goggo, itama anan bauchi take aure, suka wuce lagos domin acan Aunty Rakiya take aure lokacin, acan suka haƌu aka haƌo kayan aure na garari, kinsan auren yan maiduguri da ƙaryan kaya dai Aunty nice?

Girgiza kaina nayi alaman hakane,ina ƙara saurarenta, domin ni gaskiya bana gajjiya da kallon Ayshaan nan, don ni mace mai yanga burgeni takeyi sosai, ido na zura mata ina sauraranta.

Kaman tasan abinda yake raina, sai ta sake juya kyawawan idon ta cike da rausaya ta kalleni tana ƙara gyara zaman ta, "kina ji ko Aunty Nice, lokacin da suka dawo daga haƌa kayan auren ranan anyi tashin hankali agidan mu da Mamie, domin dama tana cike da bala'in tafiya da Adda da akayi lagos ƌinnan, tana jin haushi ba'aje da ita ba, ganin kayan kuma ta tada wani bala'in kan wai ana so duk kuƌin

Baba ya ƙare, don ita bata yadda Yaya bane ya haɗa wannan uban kayan, ta manta Yaya Mohd a NNPC yake aiki, kuma mutumin nan yakai 5years yana aiki a wurin, gashi darajan Baban mu yasamu wuri mai maiƙo, Yaya Ahmad Barrister ne, shima yana Abuja da zama, Yaya Umar ne kawai ɗalibi, don shi kam da saura.

Duk yadda mamie ta kai da son ta raba tsakanin ƙawancen mu da Habibah abin ya gagara, don rana ɗaɗɗayane bata shigowa side ɗinmu tayi masifa wa Ummi, akan dole idan mun shigo Ummi ta kora Habiba, sbd ni babu yadda za'ayi naje side ɗinsu sai mamie ta kore ni, har nadawo ma bana son zuwa, saidai ita Habibah tazo wurina, amma ko sau ɗaya Ummi bata kula ta, watarana ne ma Yaya Umar yazo suna zaune da Yayah ishaq a parlon mu sai ga Mamie cikin bala'inta ta shigo neman Habibah, inda ta shiga batanan ta ke fita ba, gashi bata san Yayah Umar yana ciki ba.

Ranan na tabbatar Yayah Umar gwarzo ne, don tsabar masifah da ƙyar Hajiya Ummah ta shigo da Mamah suka fitar da shi, don rantsuwa yayi akan idan Mamie ta sake shigowa tayi rashin kunya wa Ummin mu ko ta nemi shiga tsakanina da Habiba wlh sai ya mata dokan tsiya, jikin shi har wani rawa yakeyi kaman wani ɗan gunda.

Ita dai mamie jiki a sanyaye taja tsumman ƙafarta ta juya tayi side ɗinta, ƙasa-ƙasa ta ke magana akan yajira dawowan Abban mu, wlh bazata yadda ba, aiko batayi nisa ba, ya biyo bayanta idon shi kaman zasu zazzago yana zare su yace, "wlh ummi na rantse miki da Allah idan baki gayawa Abba baki cika mai sharri ba, kuma ni da kaina zan gaya mishi, ya kuma ja miki kunne akan zuwa gefen mahaifiyata, don wlh idan kowa bai ɗauki mataki ba ni nan".... Yana buga ƙirjin shi da hannu yana nuna kanshi yace "zan ɗauki mataki mai tsauri akan ki da shegiyar munafukar yar ki mai kai miki rahoto".. Ya juya da sauri yana neman Raliya.

Ganin haka Ummie ta ƙaeaso wurin ta kama shi, "Umar na baka umurnin ka fita kada ka taɓa yarinyar nan," daga nan ta haɗa hannun shi da Ishaq tace sufita zuwa wurin Hajiya Ummah su zauna, bata son fitina.

Tsaki Mamah taja tana hararan Ummie tace, "amman ummin su ke ina ruwanki ne? Ki bar shi ya chasa mana munafukar yarinyar nan mana, itama uwar munafukan ae shine daidai ita", tana gama faɗa ta juya ta tafi side ɗinta, aka barni nida Habiba muna tsilli-tsilli da idanu, don Allah yana gani muna son junan mu sosai, kuma

kullum Abban mu yana nuna muna musu junan mu, yana jin daɗin yadda muke tafiyar da rayuwar mu, haka ma Ummie da Yayah mohd, gashi ko sch class ɗin mu ɗaya sit ɗinmu ma yana bayan nasu Habibah.

Maƙwaftan mu muna da wata ƙawar mu mai suna Maryam, maryam itace sit ɗin mu ɗaya da ita, ita kuma Habiba suna zaune da wata friend ɗinmu Jamilah, ita jamila a fadamar mada suke, maryam kuma unguwar mu ɗaya da ita, wato G.R.A, gida ɗaya ne tsakanin mu da su, kuma tun shigan mu primary class ɗinmu ɗaya sit ɗinmu ɗaya, har zuwa yanzu da muke shirin rubuta junior weac.

Ana gama watsewa a wurin muka haɗa ido da Habiba, kaman wasu dolaye muka kwashe da dariya, Habiba ta matso kusa dani tana zare ido tace, "sis yau kam zanci na jaki a wurin Ummie babu mai karɓa na, yau kam jikina zaiyi yakuwa", tana gama faɗa muka sake kwashewa da dariya, nima cikin zare ido na sunkuya dai-dai fuskar ta, don nafita tsayi sosai, Habiba guntuwa ce kaman Mamanta, ni kuma daga Abba har Ummie dogaye ne, sai yazama gaba ɗaya ɗakin mu muna da tsayi, kuma dukkanmu farare ne sol, su kuma kasancewar maman su guntuwa ne sai Habibah ta ɗauko guntancin maman ta, amma farin Abba ta ɗauko, sbd haka banbancin mu babu yawa a haske, don ita har taso ta fini, don ni na sirka da ɗan jaja haka, amma Raliya baƙa ce, ta ɗauko kalan fatar Mamie da kamannin mamie, sai dai ita doguwa ce, don tsayin su ɗaya da hafsy, "Sis kawai mu gudu wurin hajiya ummah, har sai Abba yadawo munga abun da hali yayi, idan ba haka ba ina tsorata miki na jaki da zaki sha yau", na faɗa ina kama hannun ta mukayi wurin kakarmu.

Ana daf za'ayi sallan magrib Abba ya dawo daga tafiyan da yayi zuwa Abuja, ta window muka leƙo nida Habibah muna ganin masu aiki dasu hafsy da suke masa sannu da dawowa, inda ya rungume hafsy da Raliya a jikin shi, Abba yana son mu, wani irin son da ko iyayen mu mata basa nuna mana, da gudu muka fito mukayi wurin shi, fuskar shi cike da fara'a yana, "oyoyo yan biyu na," mukaje ya rungume mu, muma muna mishi oyoyo Abba, Yayan Ahmed ne ya fito a motan shima fuskar shi cike da farin ciki yana kallon mu, hannun shi riƙe da hannun hafsy da raliya, don tare suka dawo da Abba, farin ciki kaman zanyi yaya ganin an fito da kwakwa daga boot ɗin Abba, ina kallon Habiba nace, "sis gobe akwai kwakumeti a gidan nan", Abba ma yana dariya yace, "ae saboda ku na ce dole a sayo kwakwa a gidan nan, yan biyu na zasu mun kwakumeti naci,"

"Abba mu kuma fah"? Cewar raliya da ta zunɓuru baki gaba, tana sake hannun yayah Ahmed ta taho wurin Abba, "ku kan ae baku da tsaraba sbd yawan masifar ku da faɗan ku, shiyasa ma ku bana ganin ku kaman yan biyu," Abba ya faɗa yana wuce side ɗin Hajiya Ummah, sannan yacewa Yayah Ahmed yayi alwala bari yagaida jatumar sa sai su wuce masallaci.

Yayah mohd da Yayah Ahmed basu da hayaniya, amma na Yayah Ahmed har ya ɓaci, sbd shi komai kukeyi baya tankawa, maganar ma da ƙyar yake iya buɗe baki yakeyi, don kullum ina jin Ummie tana cewa yayah yake iya magana a kotu?

Wucewar Abba kaɗan raliya ta juyo ta zabga mana harara, sannan taja tsaki tace, "wallahi duk iya munafurcin ku kwakwan nan namu ne mu duka, tare za'ayi kwakumetin, ko kuma kunayi na faɗawa Ummie ta ƙwace ta raba mana dai-dai wa dai-dai, kunga ku da shan wahala mu kuma da morewa"' ta faɗa tana murguɗa mana baki kaman sa'o'inta.

Mari hafsy ta kai mata a bakinta tana, "mumafuka mai zubin shaiɗanu, shiyasa kikayi baƙi ke kaɗai a gidan nan sbd baƙin zuciyar ki" aiko raliya ta juyo zasu kama dambe da masifar su, Yayah Umar ya daka musu tsawa wanda lokacin fitowar shi kenan daga side ɗinsu, marasa kunyan banza da gudu sukayi cikin gida, amma bakin Raliya bai rufa ba tana cewa, "wallahi sai na haɗaki da ummie, kince a wurinta na ɗauko baƙi da baƙin hali", mudai kallon mamaki kawai muke musu nida habibah.

Kama hannu mukayi muka wucce side ɗin hajiya ummah, dai dai lokacin kuma yayah umar suna gaisawa da yaya Ahmed, hannun su riƙe da na juna, sbd gaskiya yayuna ukun nan akwai ƙauna mai girma a tsakanin su, idan ka gansu kaman abokaina, muma wucewa mukayi side ɗin Hajiya Ummah inda muka haɗu da Abban mu yana shirin fitowa.

Bayan anyi sallan ishaa an haɗu a dinning wurin cin abinci, ido na nida Habiba zuru-zuru muna jiran ko mamie zatayi wani magana akan faɗan ɗazu amma shiru bata ce komai ba, sai dai hararan mu da takeyi a kaikace nida Habiba.

Ana gama cin abinci Yayah Umar ya dubi Abban mu da ke shirin tashi ya wuce cikin parlon yace, "Abba ina son magana da kai" da ɗaurarren fuskan shi kaman shine maigidan ba yaron gida ba, da sauri Mamie ta ɗago tana duban shi, ita kuwa Ummi baki ta buɗe tana, "Ubanah bana son dogon magana fah" babu ɓata lokaci Abba ya ɗaga mata hannu, da nufin ta mishi shiru, yana bada hankalin shi gaba ɗaya kan Yayah Umar.

Girgiza kai Mamah tayi irin alaman Abba ya mata dai-dai, tana hararan Ummie.

"Abba dama alfarma nake nema a wurinka, ina so kayiwa mamie magana akan duk wani abu a gidan nan da ya faro ko akan yara ko na cikin gidan nan, kada ta sake zuwa kan ummie da faɗa, idan ba haka ba wlh Abba wataran labarin da za'aji bazaiyi daɗi ba, don gsky ni haƙurina yana gazawa," ya faɗa yana hararan Raliya ƙasa-ƙasa.

Kaman Abbah bazaice komai ba, har zuwa wani lokaci idon shi yana kan Yayah Umar, zuwa wani lokaci kuma ya maida kan ita mamin, gyaran muryah yayi sannan yace, "Baba nah kafin kagaya mun kai Ummah ta gaya mun, kuma insha Allahu zamu zauna da iyayenkan, kuma zanyi maganin komai, zan kuma kawo ƙarshen komai insha Allahu, kaima ina son ka dinga haƙuri da wani abun, kana kuma kawar da kanka akan su", da sauri mamah ta buɗe baki cikin ɓacin rai tace, " sai an kai uwarshi ƙasa tukun zaiyi magana? Wannan ae ba shari'a bane, shiyasa kullum Hauwa takeji a ranta abun da takeyi dai-dai ne, don ba tsawatar mata akeyi ba" ta faɗa tana miƙewa tsaye da niyyan barin wurin, Abba ya dakatar da ita, "Zainab bawai bana lura da abinda yake faruwa bane ko bazan ɗauki wani mataki akai bane, nan ae ku da yaranku ne zaune, kuma naji ƙorafin Baba na, insha Allahu zan zauna daku muyi magana, ba lallai sai a gaban su ba", ya faɗa yana mai da kallon shi kan mamie da ta wani tura baki gaba kaman zata zunduma ashar, sai dai babu dama, don daga Mamah har Yayah umar tana shakkan su, haka kowa ya tashi yayi side ɗin shi, amma Yayah mohd, yayah Ahmad, Yayah Umar, Hafsy duk miƙewa sukayi suka wuce side ɗin Ummin mu, mu kuma ganin Abba zai tashi da wurin mukayi hanyar

Hajiya Ummah, don gaskiya yau babu mafaka a wurin Habiba sai chan, munafukar kuma Raliya muna shirin fita tana hararan mu, mudai bamuyi takanta ba muka wuce.

Hajiya Ummah tana ganinmu ta harare mu, cikin hararan mu tace, "nice rumfah sha shirginku ko? Idan ana zaman Allah da annabi ne ina binku kuzo mu kwana sai kuƙi, ku masu iyaye sai ku gudu chan, idan sun gallabe ku kuma sai ku kwaso mun ƙazamin jikinku kuzo ku takurani ni da gidan ɗana," ta faɗa tana maida kanta da hankalinta kan T.V, dariya muke mata Habiba ta faɗa jikinta tana dariya, ni kuma na zauna wurin ƙafanta ina nawa dariyan, Habiba tana neman tsokano mana ita tace, " hajiyar mu maganin kukanmu, idan bamu zo wurinki ba wurin wa zamuje? Kinyi na Abban mu kina namu, ae kin muri duniya da abunda yake cikin duniyan, yʻayʻanki su miki jikoki su miki", nima ina dariya na chabke da "gashi muna haihuwa yʻayʻanmu na fari masu sunanta zamu saka".

Buɗe baki tayi tana kallon mu cikin mamaki tace, "amma Allah yayi manyan maƙaryata a nan, ae idan na samu kuka cigaba da zumunci dani ma ae nayi sa'a, da shegen bakin ƙaryanku ae kuna haihuwa kowa wa uwarta zatayi wa mai suna, babu ma ya wayʻennan gardawan Umar da Ishaq, duk sun lotsa mun gado da kujeru na, amma nasan sunayin na kansu bazasu taimakeni ba, ballantana mai suna, sai gatan kashe mun kujeru da yawan zamansu" ta faɗa fuskanta a murtuƙe, dukkan mu dariya muka kwashe da shi, habiba tana ƙara ingiza magana da cewa tun ba ma Yayah Umar ba, don naga ya sakoki a gaba da labcecen jikin shi, juyawan da zanyi kawai sai na ganshi a tsaye a bakin ƙofan parlon, ae banbi takan Habiba ba na rantama ɗakin Hajiya ummah da gudu na murɗa key, ina jin dariyar Hajiya Ummah don babu abinda takeso irin taga yayah umar yana labtan mu, ina jingine da ƙofan ina dariyar Habiba ko ita ina tayi, don naji ihun ta da gudun ta.

Muna shiga SS 1, first term ɗin mu aka fara shirin biki Yaya mohd, wanda bai wuce 2weeks ba ayi,

Wani farin ciki nakeji sbd bikin da za'ayi a gidanmu, gashi Yayah Ahmad ya mana ɗinkuna kusan kala biyar-biyar mu da su Raliya, abun daɗin ma har da Maryam friend ɗinmu, mudai shagali babu kama hannun yaro, gashi dodon mu baya nan, don sai ana satin ɗaurin auren naji ance zaizo, kuma fah Yaya Umar duk zafin shinnan yana mana so na ban mamaki, shidai daga mamie tayi wani rashin hankali ne zaki ga ya wargaza hankalin kowa a gidan, don ni gaskiya bansan wani irin so yakeyi wa Ummie ba.

Biki ya kankama Aunty Asma'u tazo haka ma Adda ta iso, abun farin cikin ma nida Habiba an bar mu zuwa maiduguri wurin event ɗin amaryah, wanda tafiyan mu da Aunty Asma'u ne.

Aunty Asma'u , Adda, da goggo ƙanwar ummin mu duk zasuje, sai kuma wata yar ƙawar ummin mu, sai ni da Habiba za'ayi tafiyan, mota biyu zai ɗauke mu, Yayah ishaq zai ja motan Aunty Asmau, Yayah Umar zaija motan Adda, sai kuma gayyan motan abokan ango da zasu ɗauko amare, Yayah Ahmad dai da Abba zasu haɗa hanya, su kuma ana gobe ɗaurin aure zasuje da tawagar Abba.

Maiduguri munga karamci munga kara, an mana karɓa na ban girma, munga shagulgula na har kan arziki da mutunci, a mutunce akayi komai aka gama, ranan ɗaurin aure muka kama hanyar Bauchi cike da farin ciki, ga kyakkyawar amaryar mu Aunty Bintu.

Mun iso bauchi wuraren ƙarfe uku na yamma, haka kuma a gurguje aka shiryah domin buɗan kai da za'ayi a gidan mu.

Aunty Rakiya ne ƙirjin biki, sai kai kawo takeyi a filin gidan mu, inda ake decorating wurin saboda buɗan kai, ana sallan la'asar wurin ƙarfe biyar aka fito wurin buɗan kai, ranan naga washe baki a wurin Yayah Mohd, ashe yana fara'a haka? Mudai muyi nan muyi nan, gaba ɗaya farin ciki cike da zuciyar mu, anyi taro lpy an gama lpy, inda amaryah da ango sunga karamci, su kansu yan maidugurin sun yaba da karɓan da aka musu.

Bayan sallan ishaa akayi rakiyar amarya gidan ta dake *TAMBARI ESTATE* Gida ne mai ɗauke da flat guda uku, ko wanne yana ɗauke da three bedroom da parlor 2, Abba ne ya gina musu su uku yan samarin shi, wanda ansha artabu da mamie lokacin da Abbah ya ɗauke su sukaje ganin gidan, don ko gaya musu yana ginin baiyi ba, sai da aka saura 1month bikin ya kaisu, ya kuma shaida musu halak malak

ya damƙa su, amma na yayah mohd ne kawai akayi penti, sauran biyun yace kowa ya tashi auren shi ya fente.

Mamie kasa daurewa tayi a lokacin, zuciyar ta kaman zai fashe tana huci tacewa Abba, "amma dai Abban su duk wani dukiyarka anan ka ƙarar ko? haba jama'a idan mutum yace ba'a mishi adalci ace ba haka ba, yanzu namu yaran idan sun tashi aure sai ace komai ya ƙare, kuma ana magana ace kishi ne", ta faɗa kaman zata fashe da kuka.

Tana rufe bakinta, mamah tayi charaf tace," wa na zaice kishi? Sai da ace hassada da jahilci, idan bake kanki baya saiti ba mutum da yʻayʻan shi har kina da bakin cewa wani abu idan ya musu har kan arziki? Wannan hassada naki akanki zai ƙare, naki yara matan cewa akayi ya basu wurin zama idan zasuyi aure ko me?"

Harara mamie tayiwa Mamah ƙasa-ƙasa don tana shakkanta kuma tana tsoronta,

Abba ne duk ya dakatar da su idon shi akan mamie yace, "matsala ta da ke baki da wayo, baki da dabara, huruminane ko kuma dole nane akan yʻayʻana mata? Kinga anyi auren su sun wofinta ne? Don Allah Halima bana son rashin hankalin ki, shiyasa abu dayawa bana son sanar dake sbd ƙorafinki da nuna kishinki akai". Ya faɗa yana barin wurin ya wuce wurin motan shi.

Ummin mu batace komai ba sai murmushi dake sauƙe akan kyakkyawar fuskanta, haka zalika daga Yaya mohd, Ahmad, umar, ni da sauran yʻan'uwa na mata babu wanda tace wani abu, sai duk muka juya mukabi wurin mototi guda biyu da mukazo a ciki, Raliya ce kawai cikin mu take ta wani harare hararenta na banza da wofi, mudai cike da farin ciki.

Bayan ankai amaryah gidan ta, ana ta saka albarka, a gidan da musu fatan zama lpy, kaii Aunty nice gidan yayi kyau, ranan na ƙara tabbatar da yʻan maiduguri ƙarshe ne a wurin ƙyale, gidan nan kaman kada mu tafi ga wani ƙamshi kaman babu gobe, inda muke tsaye nida Habiba da maryam wata yar Aunty Bintu ce tsaye,

suna ce mata yah falmata, nidai matsawa da hanci nakeyi ina shinshina laffayanta Aunty nice, tafaɗa fuskanta ɗauke da dariya, nima ina dariyan nake ƙara maida hankalina kanta, sannan nace mata ae Hajjajo ƙamshi rahma ne, tana dariya tace rahma ɗaya ko biyu, ae nidai tun ranan naji babu abinda nake so irin ƙamshi, muna ji muna gani Yayah umar ya tiso ƙeyar mu muka dawo gida, wanda har ga Allah bamu so ba, a wautar mu bamu ƙi kwana a chan ba.

Da safe kuwa bayan sun karya sun shiryah suka biyo gidan mu domin yin sallah ma da mutanen gidan mu, saboda ranan duk zasu juya maiduguri, wurin 11:00am duk sun kama hanya cike da karamci irin namu na yan bauchi da iyayen mu suka shiryah musu.

Bayan biki da sati biyu yayah mohd ya kawo Aunty Bintu gidan mu ta gaishe da iyayenmu, murna kaman babu gobe, don muna dawowa gida daga school muka ganta a parlon Ummin mu tana zaune, a gefe ɗaya kuma ummin ce zaune suna ɗan taɓa hira kaɗan kaɗan, tunda dama akwai sabo a tsakanin su, da gudu naje na mata oyoyo baki na kaman zai tsage don murna, itama fuskan ta cike da farin ciki tace, "ae nayi fushi daku Aysha, daga ke har habiba babu wanda ya leƙoni"? Ina dariya nace zamuzo Aunty Bintu, mun koma school ne ga kuma Haddan mu an matsa mana zamuyi sauƙa this year.

"Masha Allah" Aunty Bintu tace, sannan na miƙe nayi ɗakin mu domin na chanja kaya.

Har sao wurin nine na dare tukun yayah mohd ya ɗauke ta suka tafi, nida hafsy da habiba har wurin mota muka rakata, muna mata alƙawarin ɗin zuwa mata ranan friday.

Motan su bai gama fita ba motan yayah Ahmad ya shigo gidan ,muma fasa wucewa mukayi cikin gida domin mun jiran ƙarasowan shi, don yamana alƙawari bai cika ba, gara kafin ya bar garin a san nayi.

Bayan sun gaisa da yayah mohd ya ƙaraso ciki da motan shi, yana buɗewa muka ganshi bashi kaɗai bane ashe, tare da wasu abokanshi muka gansu.

"kaiiii" naji muryan Habiba tana faɗin, sisto juyo kiga wasu farare tare da yayah Ahmad kaman wasu halfcast, da sauri na juyo ina duban su, nace "hala twins ne, ina Yayah Ahmad ya samo fararen mutane haka? Har sun fishi fari" muka haɗa ido nida Habiba, sbd kowani magana ɗaya tayi tou ɗaya tasan ina maganar ɗayan ya dosa, riƙo hannu na habiba tayi muka ƙarasa wurin Yayah Ahmad, hafsy na binmu abaya tana cewa, "inaga fah inyamure ne, don farin su yayi yawa, ko kyau basu mun ba sbd farin su yayi bauu, amma kukuma nasan sun burgeku, mayun farare kaman ku ba fararen bane", babu wacce ta kula ta muka ƙarasa wurin yaya Ahmad.

Hannu ya miƙo mana yana "yʻan biyu Abba yyh kuke? Fuskan mu ciki da farin ciki muka miƙa mishi hannun mu mukayi musabaha, ranƙwashi ya kaiwa hafsy yana cewa, "jerry ina tom"? Baki ta turo tana "Allah sarki yayah Ahmad niƙan a gidan nan kaman kowa bai damu dani ba wlh, kowa Sai yʻan biyun Abbah"? Ta faɗa tana hararan mu nida habiba, mudai dariya mukeyi muda Yayah Ahmad, juyawa yayi yana duban abokanshi cikin shiru-shirun shi da rashin son sakewa da dogon magana yace, M.G, da A.G ga sisters ɗina, yana nuna mu yace wayʻan nan sune favourite sister ɗina, suɗin kaman twins suke ga hankali, wannan kuma yana nuna hafsy yace autar mu kenan, ita kuma twin sister nata halin su ɗaya basuji, yadda kasan tom and jerry haka suke, basujin magana basu son zaman lpy", ya faɗa yana riƙo hannun hafsy data turo baki tana hararan mu.

Wanda naji yayan mu ya ƙira da M.G da AG ɗin muka juya muna gaishe su, suma cike da murmushi a fuskansu suka amsa mana, inda ɗayan bayan gaisuwan bai sake cewa komai ba, saidai fuskanshi ɗauke da murmushi yana duban mu, shima ɗayan fuskanshi cike da murmushi yake ƙara mana tambaya akan ajin mu nawa? Habiba ce ta gaya mishi ajin mu da sunan mu, bayan ya sake tambayanta, sannan ya dubi hafsy yace ke kuma kece tom ɗin ko jerryn?

Dukkan mu dariya muka kwashe da shi, banda ita da tasake turo baki gaba tana cewa, "wallahi sunana hafsy ne"

Kawai dai kowa a gidan yafi son sune shiyasa ba'a ganin laifin su, amma wlh manyan yan tawayen gidan mu kenan, kuma basu ji ga iya haɗa munafurci," ta faɗa tana ture hannu na da nakawo kusa da ita, yana dariya yace, "tou nidai banga alama ba, nima ina ga sune favourite sisters ɗina, ke kuma inaga friend ɗina zaki zama" still dai fuskan shi cike da fara'a, daga gani shi yana da ɗan surutu, amma ɗayan tunda ya amsa gaisuwan mu bai sake cewa komai ba, saidai yana bin dukkan mu da kallo, shima kuma fuskan shi cike da murmushin, amma dai bai sake tankawa ba.

Wucewa side ɗin su Yayah Ahmad sukayi, bayan muma mun juya side ɗin Hajiya Ummah, hafsy ko hararan mu tayi ta wuce cikin gida, kaman wasu munafukai, muna shiga parlon hajiya umma muka zauna a kujeranta two sitter muka haɗa kanmu wuri ɗaya domin tattaunawa, kallo ta bimu baki a buɗe tace, "wannan munafurcin da baya sakin ku kuma fah" kudai yaran nan kullum aka ganku cikin nuƙu-nuƙu na gulmah kuke, nidai duk wacce tayi gulma na nabarta da Allah, domin duk abun mutum da gulmanshi nan gidan ɗanane, iko nane, idan ma hassada kukeyi ya kawo ni nan sai kuyi tayi" ta ƙara faɗa tana hararan mu.

Mu dai dariya muka kwashe da shi muna kallonta, habiba ce ta bata amsa da, "in banda ke hajiya ummah gorin na menene? Muma idan muna raye zamu haifi yaran da zasu mana gida gidan sama ma mu wataya, bake da aka miki ɗan akurki ba," ta faɗa tana taɓa ƙafa na, don mun san yau zamusha gori iri-da kala, don hajiya ummah ji takeyi mu kishiyoyinta ne a wurin Abban mu, don ko shigowa mukayi tare da shi ta dinga hararan mu ƙasa-ƙasa, watar tace amma dai kai kan jakin yayа nane, baka kama gabanka suma su kama gaban su? Amma kullum kana naniƙe da su, su hanaka yin abun kanka?

Aiko kaman habiba ta jefa mata ƙarfe a tsakarka ta zabura tana nuna mu da yatsa, "ahir ɗinku wlh, don babu wacce zata haifi ɗa irin wanda na haifah, don ni ɗana ɗaya ne tamkar da dubu,don ko gwabna bai kai shi kuɗi ba, gwamne me a kusa da a kusa da usmanu nah? Ae inaga idan gwamnaty ta kasa biyan albashi usmanuna zai iya bawa gwamna bashi yayi albashi na wata ɗaya kam, kuma arzikin shi bai taɓu ba, don kaf Tafawa ɓalewa ba'a taɓa haihuwa irin nawa ba, kawai dai ya haɗu da jarabawan tara mata marasa abinyi ne sai abun da ya musu", ta faɗa tana mana kallon banza.

Dariya muka kwashe dashi, habiba tana cewa, "a tafawa mahaifiyar Ɗangoten bauchi" bakuyi gatse ba marasa kunya ni nan da kuke gani nafi uwar ɗangote farin cikin haihuwar ɗa mai albarka,

Hajiya Aysha tana duba na cike da dariya tace, "Aunty nice kinsan kakarmu irin mutane ne masu son nasu, kuma har cikin zuciyarta ji take duk ƙasan nan babu wanda yakai Abban mu sukuni, shiyasa muke manna mata hauka akan Abban mu yafi gwamna kuɗi, kuma ta hau ta zauna," Dariya nayi ina ƙara maida hankalina wurin Hajiya Aysha, ina kuma ƙara jinjina irin baiwar kyau da Allah ya mata, domin murmushi fuskanta ba ƙaramin kyau yake ƙara mata ba

Tun ranan da mukaga abokan Yaya Ahmad bamu sake ganin su ba, kasancewar shima ba a gari yake zama ba, amma rana ɗaɗɗaya ne bamu hiran su nida Habiba, wanda har ta kai mun bawa Maryam labarin su da irin farin su, cikin zolaya maryam ta kalle ni tana dariya, "amma dai Ayshaa ke kike koyawa habiba ganin kyaun farin mutum? Kuma daga dukkan alamu kin ƙyasa? Inaga gara a sanar da yayah Ahmad"'

Hararan ta nayi nace, "ban dake maryam yaushe ma na girma da har zanga wani nace ina so? Soyayyan ma ae bamu kai ba, kuma bani da class ne zan ce ina son su? Kawai ni fararen mutanene bana gajjiya da ganin su, kin san bana son baƙin fata", dukan da habiba ta kai mun ne na hankalta da kwafsin da nayi, don mantawa nakeyi mamie baƙace, haɗa ido mukayi muka kwashe da dariya dukkan mu.

Babu wasa rayuwar tana wani irin gudu, a haka yau muke kammala waec ɗin mu, kowa a cikin mu cike da farin ciki da burika kala-kala a zuciyar mu, ranan dukkan mu huɗun, ni, habiba, maryam, jamilah muna zaune kafin driver yazo ya ɗauke mu, a yanayin mu bamu da hayaniyah dukkanmu, sai dai nida habiba da maryam idan mun haɗu mukan taɓa surutu sosai a tsakanin mu, amma idan wanda bai sani bane bazai taɓa yadda muna da surutu ba, amma ita jamila da wuya kaji maganan ta, sai dai kawai ta biku da ido, jamilah bata da matsala ko kaɗan, shirunta yayi yawa, amma akwai azaban kai, domin kanta yana mugun ja sosai.

Maryam ce ta dubi jamilah tace, "yanzu besty da gaske auren za'a miki? Tou karatun naki fah"? Ta faɗa fuskanta cike da jimami, domin duk munyi shawaran karatu zamuyi a wuri ɗaya, wato ATBU, don ko jamb ɗin mu shine first choice ɗin ko wacce a cikin mu.

"Besty tou an yanke muyi auren saboda na bishi chan na fara karatuna, nima kuma gaskiya hakan yafi mun, don ina tsoron yana tafiyan nan wata ta mun wuff da shi", dukkan mu dariya muka kwashe da shi, ni kuma na zabga tagumi ina duban Jamilah cike da mamakin wai zatayi aure, cousin ɗinta ne, kaman wasu zamu shiga SS 3 yace yana sonta, kuma cikin hukuncin ubangiji yagama masters ɗin shi a London kawai ya samu aiki achan, shine iyayen su suka yanke kawai ayi auren su tafi tare, idan yaso karatun sai tayi achan.

"ikon Allah" kawai na furta ina kallon ta, sannan nace, "jamilah kuma zaki iya rayuwar auren da ɗan ƙaramin shekarunki?" kallo na tayi tana murmushi tace "me zai ban tsoro, yayah nane fah, kuma zai ɗaga mun ƙafa sai na ƙara girma yace mun".

Dariya dukkanmu muka kwashe da shi, habiba ta dubeni tana ɗaga kai cikin salon mu idan zamu zolayi mutum tace, "dogon magana" kwashewa muka sakeyi da dariya, maryam da jamilah na taya mu.

Maryam ce ta dube mu tace tou yanzu me zamuyi na event? Kun san muma yanzu bebs ne, don mun girma ta faɗa tana wani juya idanunta, shiru mukayi na zuwa wani lokaci, sai jamila ta gyara zama tace, "mummy na zasuyi liyafa ne kawai, nima bana son wani event sosai, tunda angon yace shi babu wani event da zaiyi bayan recieption da zasuyi, saboda haka ya kamata mu gwangwaje adon mu a liyafar nan.

Da yake nima bana son wani damuwa sosai sai kawai na bada ƙarfin ayi hakan, babu yadda habiba da maryam suka iya kowa sai ta amince, a haka drivern su yazo ya ɗauke ta, muma babu daɗewa aka zo aka ɗauke mu.

Bikin jamila ya gabato sai shirye-shiryen ashobi mukeyi, inda muka haɗu da wasu friends ɗinta guda 6, sai cousins ɗinta guda 2, muka zama mu 11, muke ta shiri da tsare-tsaren mu, ranan da mukaje sallon a *SHAGARI SHOOPING COMPLEX* Yayanta Aliyu ne yazo ɗaukan mu, shima yadda kika ga jamila da kyau da shiru tou shima haka yake, sai dai ba fari bane, kuma baza'a ƙirashi baƙi ba, saboda yana da haske wanda wasu zasu iya kwatanta shi da fari, amma a wurin wanda basu ganin fari sosai, lecturer ne a Federal polytechnic bauchi, yana Computer depertment, ɗan gayu ne na nuwa, kuma daga ganin shi mai tsafta ne, don motan shi wani irin azaban ƙamsh yakeyi, ga kuma sanyin A.C

Gidan mu aka fara wucewa ya sauƙe mu, sannan suka wuce tare da jamila da wata cousin ɗinta Ummitah, daga kaduna suka zo, kuma sun shaƙu sosai da jamilah, saboda kullum hiranta Ummitah ne.

Muna shigowa gate ɗin gidan mu Habiba ta juyo tana kallona, fuskan ta cike da gulmah tace mun, "sisto naga daga dukkan alamu Yayan jamilan nan hankalin shi yana kanki, duk wani nutsuwar shi ina hankalce da shi, sai kallonki yakeyi, ita kuma ummitan nan inaga sai wani rawan kai take mishi, har da wucewa gaban mota ta wani zauna, bayan duk hankalin shi baya tare da ita,"

Hararanta nayi nace, "ke kuma cutar gulmar ki ta motsa duk kin kafe shi da ido, saidai in kece ya miki har ya birge ki, don ni wnn ba layi na bane, fari nake jira", ina faɗan haka na juyo ina kallon habiba na kama haɓa na, "habiba niko ina dai labarin fararen abokanan yayah Ahmad ɗinnan? Kullum yazo ina hankalce ko zan sake ganin su amma shiru, ko dai aljanune?" na faɗa ina ɗan zare ido.

Dariya ta kwashe da shi tana cewa, "inaga wannan karon idan yayah Ahmad yazo dole ayi cikiyar su, kada naje sun kama kurwar ƙanwata," hararanta nayi nace, "me kike nufi? Kina tunanin sun shiga raina ne? Kuma waye ƙanwarkin?" Allah sarki habiba na, wato Aunty nice kullum kika ga faɗan mu tou akan shekaru ne, kowa

bata so ace itace ƙarama, a haka ma habiba da tasan ta ɗan fini da kaɗan wataran ta kance ta bar mun girman, ta ƙara mun shekara uku ma bayan wata ukun, ni kuma na dinga tsokananta ae tunda na fita tsayi tou na rigata zuwa duniya, a haka muke kullum cikin soyayyar junan mu, donni son da nake yiwa habiba ko hafsy da muke ciki ɗaya bana mata.

Washe gari tun safe muka tafi gidan su jamila, saboda wacce zata mana make-up da wuri zata zo.

EVENT CENTRE a wurin aka shirya yin liyafan, masha Allah amaryah tayi musulmin kyau ita da ƙawayenta, sai wani jin falli mukeyi irin muma mun girman nan, har mun fara aure, da yake shine biki na farko da muka farayi na ƙawayen mu sai abun ya ƙayatar da mu sosai, sai wanni basarwa mukeyi muna wani rangwaɗa irin ƙawayen nan, Aysha ta faɗa fuskar ta kaman alokacin ake hidiman, ga kuma wani rangwaɗa kanta da takeyi, kaii ni Aunty nice ina ga mata mai yanga kam, don ƙuri na mata ina kallon yatsun hannunta yadda take watsa su kaman wata ɗawisu, ga magana ɗaya tana juya idon nan kaman ka sace ta ka gudu, gaskiya macen da bata da yauƙi ta rako mata duniya ne, na faɗa a cikin zuciyata.

Aunty nice ina baki labari, maganan habiba kuma sai ya tabbata, domin Aliyu yayan jamilah gaba ɗaya ya takura ni, duk inda nayi idon shi yana kaina, tun lokacin da muka fito za'a tafi wurin liyafan yakasa ya tsare dole sai na shiga motan shi, haka ya aiko Fatie ƙanwar su mai bin jamilah ta ƙirani, gashi ba mai son magana ba, ina fitowa yace na shiga motar shi, ido na zuba mishi ina ɗan kame-kame da riƙe gyalen jikina, a haka na daure nace mishi zan bi motan amaryah ne, ya kallo ya bini da shi cikin nutsuwa da kwantar da kai yace, "amaryah ma da angon ta zasu tafi, kema kibi naki angon kawai ku wuce tare", ya faɗa bada wani damuwa ba kaman dama muna tare.

A razane na kalle shi nace, "ni kuma? Ni ae banida aure, yana duba na ido cikin ido yace, "ehh kema ae zakiyi tunda ba tabbata xakiyi ba, babu yadda na iya da shi, dole naje na jawo habiba da maryam akan mutafi tare, kafin kuma kiyi haka ummitah ta fito tayi jikin motan Aliyun tana wani rangwaɗa, gata kaman zata ɓalle don rama, "Bro bari nazo mutafi, tun da kaima chan kanufa.

Dubanta yayi kai tsaye yace, " bana son takura ki wuce ki nemi wani motan, akwai wanda zan tafi dasu", kuma bai wani ɓata lokaci ba ya buɗe mun gaban motan fuska a ɗaure ya mun alaman da na shige, sannan ya dubi habiba da maryam ya musu alaman su shige bayan motan, ko takan ummitah da ta buɗe baki tana kallon mu bai bi ba.

Ummin mu da maman maryam da mamie duk sunzo wurin liyafan, mamah kawai aka bari a gids, duk inda mukayi idon ummi yana kanmu.

Bayan an buɗe fili da addu'a an fara programm babu daɗewa ango ya iso da rakiyar abokan shi guda uku, bayan sun zauna babu daɗewa D.J ya basu umurnin fitowa filin, aka saka musu waƙan aure, haba zokiga iyayen zamani, ba uwar amaryah ba bana ango ba, duk ɓarin kuɗi sukeyi, damu abu duk ɗaya, kai ranan naga matan manyan bauchi, kowa ɓarin naira kawai takeyi don ace ita ce tafi burgewa, bayan fili ya ɗan lafah amaryah sun koma sun zauna, sai D.J ya sake bada daman ƙawayen amaryah su fito fili.

Da ƙyar maryam ta riƙo hannu na muka fito, domin ita da habiba suna da son rawa a rayuwar su, ni dai haka na fito na tsaya na ɗan riƙe handbag ɗina ina kallon su, batare da nayi rawan ba, sai dai ina ɗan juya jikina kaɗan, wanda wani zaiyi tunanin nice amaryah, a haka Aliyu ya fito yana mun liƙi kaman bai san daɗin kuɗin ba, ganin haka duk inda na kauce yana biye dani sai mummyn su ta fito tare da wata ƙawarta suka shiga liƙa mun kuɗi daga ni har Aliyun, fuskan mummyn sun cike da fara'a, wanda alamu ya nuna mata Aliyunta yayi kamu, wanda ta daɗe tana fata da kuma burin ganin wannan lokacin.

Daga gefen su ummin mu kuma mamie ta wani matse fuska tana bin mu da harara, a haka bakin ta ya suɓuce taja wani dogon tsaki, babu kunya tace, "shishigi a wurin

yaran nan yayi yawa, abu gaba ɗaya babu armashi? Sai wani shishshige musu Aysha ta keyi, ae idan yaro mai rawan kaine idan zaije wuri sai a ja mishi kunnen kamun kai, bawai yaje wuri yana nuna halin rashin kamun kai ba", daga maman maryam har ummin mu babu wacce ta bi ta kanta, a haka aka cigaba da progrmm har magrib tayi, sannan aka fara haraman tashi.

Ummi ana ƙiran sallah sukayiwa mummy sallama suka tafi, sannan ta riƙo hannuna tace ana idar da sallan ishaa Umar zaizo ya ɗauke, sbd haka akula da kai ko". Insha Allahu na amsa mata, ina son umminah Aunty nice, sbd matace mai zuciya mai kyau, bawai yabon kai ba, ban taɓa ganin mai irin zuciyar ummi na ba, tafaɗa tana saka hannun ta tana ɗaukan bottle na ruwa, ni kuma na ƙara gyara zamana ina kallon ta da sauraranta da dukkan hankali na, zuciyata tana son jin yayah labarin fararen abokan yayan ta ya nufa, amma bana so na mata gaggawa.

Bayan gama bikin Jamila da 1week suka bar ƙasan da mijinta zuwa london, Allah sarki har gidanmu tazo ta mana sallama da yammah ita da mijinta, lokacin da muka fito rakata wurin motan ta riƙo hannu na muka ɗan tsaya tana dubana, "Besty kim san yayah Aliyu ya birkece akan ki kuwa? Duk tsare gidan shi amma sai da ya sake ya sameni da maganan, yana ta tambaya na akwai wanda yake neman kine ko yayah ake ciki? Ni dai nace mishi for now babu kowa sai burin fara karatu da kikeyi, nagaya miki mummy sai farin ciki ta ke tayi, yanzu haka ma ya koma lagos kin san achan yake aiki, ya tambayeni number wayanki nace har yanzu de baku fara riƙewa ba", ta sake damƙe hannu na fuskanta cike da jimami tace, "Besty gashi zan tafi na bar ƙasan ban san yayah zanyi da ke ba, nasan hala idan baki ganin ido na kiƙi amsa yayah na, don nafi kowa sanin baki son baƙi, Besty yayah na fa bawai baƙin har chan bane, gashi mai ilimi da class", ta faɗa kaman zata mun kuka.

Juya ido nayi ina kallon ta, "Besty nifa bawai baƙine bana so ba, nifa ban kai aure ba, karatu nake son yi, kuma.... Sai nakasa ƙarasa faɗin abun da zan faɗa na ƙura mata ido.

"kada ki damu besty insha Allahu komai zai tafi daidai indai har muna tare" maryam ta faɗa tana dafa kafaɗan jamila, ni dai ido na bisu ban sake cewa komai akan maganan yayan ta ba, bayan sun tafi muka wuce raka maryam gidan su.

Maryam sai bayani takeyi akan haɗuwan Aliyun, amma ita tsoronta jujuna, nidai ko kulata banyi ba.

Wannan dawowan Abban mu daga Abuja ya taho mana da waya masu shegen kyau da tsada, murna nida habiba kaman babu gobe, a lokacin hafsy take turo baki gaba tana, "Abba mu fah? Muma fah muna son wayan Abba", Abba yace, "Yayanku Ahmad ne ya bayar aka wo musu, dama ya musu alƙawarin idan sun gama school result ɗinsu yayi kyau zai saya musu waya, kuma Alhamdulillahi abu yayi kyau, kuma ku dage ku maida hankali akan karatunku, idan kun gama za'a saya muku".

Mudai sai murna mukeyi muka miƙawa su ummi domin su saka mana albarka, murmushi ummi tayi tace angode wa yayan su Allah ya bar zumunci, sannan ta mana nasiha akan riƙe waya da muka jin tsoron Allah, mamah ma nasihan ta mana, sannan ta mana murnan wayan, sannan ta maida hankalinta kan su Raliya tana musu faɗa akan komai aka mana sai sunyi mita, mu sa'o'in su ne?

Mamie cikin ɓata rai tace "tou ae suma su Raliyan sun kai su riƙe wayan, ae da sai suma a saya musu".

"Babu wanda zai saya musu waya sai sun gama makarantan suma, kuma sai anga result ɗinsu yayi kyau irin nasu Ayshaa, yaran da SS 1 zasu shiga gaggawan me akeyi"? Yayah Umar daya ke shigowa parlon shi da yayah ishaq ya faɗa, ganin haka mamie bata sake tankawa ba, sai tsaki da taja ƙasa-ƙasa.

Gaishe da kowa sukayi sannan suka nemi wuri suka zauna, Yayah ishaq yana duban hafsy data ɗano baki sama kaman zatayi kuka yace, "jerry kada ki damu, nine nan zan saya muku haɗaɗɗe keda tom, amma da sharaɗin babu sim, don kada ki addabe ni da flashing," yana zolayanta ya faɗa, don babu hali taga wayan ummi sai tayi flashing ɗinshi ya ƙira, idan ummi tayi magana tace shine fa kawai ya ƙira, dama tun tana ƙarama Aunty Rakiya da Aunty Asma'u suke zolayanta haɗin gidan shi, gashi babu dama taga yana wasa da Raliya zata zunɓura baki gaba, kowa saidai yayi dariya don yadda ko mu mukayi wasa da shi sai tayi fushi.

Mamah tace tou Allah ya nuna mana lokacin ishaq, amma flashin kam zaka sha shi a wurin wannan ɣar fitinan.

Babu wuya wurin ubangiji yadda lokaci yake ta tafiya har abun tsoro, a haka admission ɗinmu ya fito, ATBU ta bamu gurbin karatu, ranan da mukaje registration sai da muka tuna jamila, Allah sarki jammy besty, tayi burin shiga ATBU amma Allah yayi achan zatayi karatunta.

Course ɗaya muka samu nida jamilah wato *BUSINESS ADMIN* ita kuma habiba *COMPUTER SCIENCE* dama ita da jammy shi suka zaɓa tun lokacin jamb ɗin mu, sai Allah yayi ita bada ita za'ayi ba, kuma zuwa wannan lokacin Yayah Aliyu ya samu number nah ta wurin jammy waya mukeyi har lokacin ban bashi daman zuwa gida ba, don gaskiya ni tsoro nakeji, a haka kuma habiba tayi wani saurayi yana da wurin sai da mota, tana kula shi amma banga alaman zuciyar ta na kanshi ba, sbd da na mata magana sai tace mun yana da rawan kai da yawan surutu, ita bata son mai irin ɗabi'an shi, dama irin Aliyu ne tou bata da damuwa.

Tana faɗan haka na dube ta nace, "sisto tou ko na haɗaku da Aliyun ne? Don ni kinga gaskiya bai mun ba, fari nake so",

Hmmm, "sisto kenan ina kika taɓa ganin anyi haka? Shima ae bazai yadda ba, tunda ae ya ganni amma bai ce ni yake so ba sai ke, kawai dai akwai lokaci sisto,yanzu ne fah muke cika 17yrs, me ma mukayi?" ta faɗa tana maida hankalinta kan wayanta, nidai tsura mata ido nayi ina kallon ta, chan na sake cewa "amma dai sisto idan an mana aure sumul zamu zauna, kuma har mu haihu, kinga ae jamilah har ciki fah take dashi, kuma gashi maryam ma ta samu saurayi ɗan abokin Baban ta, kuma ita ma muna shiga level 2 kinji aure zatayi, kawai na haɗaku nima sai na jira nawa rabon, kinga december this year auren Yayah Ahmed, mu kuma kawai irin next december sai a miƙa mu", na faɗa ina dariya, itama dariyan tayi tana "wayaga Aysha da habiba a ɗakin aure", gaba ɗaya muka kwashe da dariya, " sisto kin san me yake burgeni da aure"? Tana kallo na ta jijjiga kanta alaman a'a, na rausayar da kaina ina fari da ido nace, "na tashi da safe nayi breakfast wa miji na da yaya ana, shi zai tafi office su kuma school, ni kuma ina busy a kitchen", dariys muka sake kwashewa, habiba ta riƙo hannu na tace, "sisto ni kuma na ganni da ciki ina irin laulayin nan, nayi amai na dawo yana ta mun sorry wife, ni kuma ina ta shagwaɓa ina ni abu kaza zanci", dariya muka sake tun tsirewa da shi, cikin dariya nace, "Allah yasa muyi aure rana ɗaya sisto" Ameen mukaji hajiya ummah ta amsa, tana ƙara shigowa cikin ɗakin.

Zaro ido nayi ina kallonta cike da mamaki, wato tsohuwar nan laɓe ta fara mana ko mai?

"yakamata nayi zama da ɗana, domin na shaidah masa inda yaran da yake yabo suka dosa, don alama ya fara nuna kun ƙosa, kun ƙosa mana tunda har lissafin ciki ku ka fara, Allah ya nufa ma baku kai da lissafin kwanciya ba, kafin aje a haka gara ya samu labari" ta faɗa tana ɗirkawa habiba dundo a baya tana, "babu ma yake, domin na lura jaraba irin na uwarki duk kin haddace, sai dai Allah ya rufa asiri.

Tana cikin sababinta Yayah mohd ya turo ƙofan ɗakin ya shigo, yana "kefa tsohuwar nan fitina ne da ke, mutum yana ta sallama ke kuma kina ta sababi ba bazaki saurara ba, kuma kizo kina cewa ba'a miki sallama ba,

Ina zan saurareka yai nakama yaran nan da ake musu kallon sallah -sallah amma ashe ko alwala basu iya ba, dama ina cike dasu yadda ɗana kullum bakin shi yabon shi akan sune, don koni da nayi namijin ƙoƙari wurin haihuwar shi baya gani ballantana kaji ya yabeni, sai wayannan masu kai kaman na zabuwa",

Dariya yayah mohd yayi yana miƙo mana hannu yana faɗin , "kuzo muje parlor kumun bayanin yayah karatun ATBU yake"?

Hararan mu hajiya ummah tayi, tana ya mutsa fuska tace, "ae ni shirme ma nayi da na gaya maka me sukayi, don babu wani mataki da zaka iya ɗauka, dama Ummaru ne, na sanshi aiki ne da cikawa", mudai babu wanda ya kulata don sanin halinta yanzu zata zageka, idan wani kuma ya taɓa ka sai inda ƙarfin ta kuma ya ƙare.

A haka watan azumi ya shigo, kowa ka ganshi sai shirin shiga watan Ramadan akeyi, ko ina sai sayayyah ake, haka yan'uwa na Yayah mohd da yayah Ahmad suka haɗo kayan azumi wa Abba, don yanzu komai sun tsaya akai, basu wani jiran Abba yayi, yayah umar kuma suna shirin tafiya service, shi Kaduna a ka cillashi, yayah ishaq kuma Benin, haka suka shirya suka tafi, azumi nada kwana uku mummyn jamila tazo gidan mu, abin mamaki boot ɗin mutanta shaƙe da kayan Azumi, doya ne dankali ne fruit ne, wai duk toshi ta kawo, sai farin ciki kawai zaka gani a saman fuskanta, ummi da mamah ne suka karɓeta cikin mutunci, suna tambayanta labarin jamilah a chan inda ta ke, nidai bayan nagaishe ta guduwa side ɗin hjy ummah nayi, rai na duk a ɓace, bayan nagayawa Aliyu kada ya fara saka mama tazo, donni tsoro nakeji a sani a gida, amma nayi imani yau kowa sai ya sani, raina a ɓace haabiba ta isoni, kallo ne takeyi cike da damuwa tace, "Sisto tou meye laifin Aliyun nan ne? Nifa banga makusa fah a tare da shi, kawai ki amince, inaga auren farin mutum wani abu ne?" hararanta nayi nace mata ni bani da ra'ayi akan shi, kawai ya rabu dani, tana kallo na tace tou ki gaya mishi mana kafin komai yayi nisa.

Zuwa dare ummi ta ƙirani, tambaya na tayi game da alaƙan dake tsakanin mu da Aliyu wanda ban taɓa gaya mata ba, rai na a jagule na dubeta nace, " ummi nifa bana son shi, nace mishi ma fah ya nemi habiba saboda ita ya mata, amma shine yakama ya gayawa mummy, nidai ummi bana son shi".

Kallo kawai ta bini da shi, sannan tace, "a wani gari kika taɓa ganin anyi haka? Ina ke yagani yake so? Meya kawo maganan habiba kuma, ko yace miki yama sonta ne?"

"Nidai kawai ummi bana son shi, ita kuma ya mata gara kawai ya nemeta," "Allah ya kyauta, Allah ya muku zaɓi na alkhairi inji ummi.

Ganin yadda nayi ummi sai ta ɓoye bata gayawa Abba zuwan mummy ba, kuma ta kwaɓi mamah mah,

A haka satin sallah ya shigo, gaba ɗayan mu ranan mun karɓo ɗin kunan mu, sai murna muketayi gaskiya *JAMILAH HANCO* ta chanchara mana ɗinkuna masu kyau , da safe bayan mun dawo daga tafseer sai ga driver gidan su jamilah ya kawo kaya kusan kala biyar a ɗinke, da wani abayah mai masifan kyau da tsadan gaske, ɗaya ledan kuma jaka ne da kalmi set 2, haka mummy ta haɗo aka kawo wai duk kayan sallah nane, ummi ta ƙirah mama akan suyi shawarah, haka mamah ta bata shawaran kawai ta sanar da Abba kada abu yayi nisa, nidai ko kaɗan kayan basu mun ba, don bana son mai kayan ballantana kayan, kawai kunyar jamilah ne yasa nake raga mishi, amma sai ya ƙirani sama da goma ban ɗauki wayan shi sau biyu ba, yawanci habiba ce ma ke ɗauka suyita hira akan course ɗinta, nidai nawa ido, a haka yace mun ran sallah zai turo a nema mishi ison zuwa muna gaisawa nidai ƙin amince mishi nayi sai habiba ne tace mishi babu damuwa hakan ma yayi.

Washe garin sallah iyayen Aliyu suka zo wurin Abbah na neman ison Aliyu ya gani yana so, kuma da neman iznin ya fara zuwa zance, cikin mutunci Abba ya karɓe su, kuma ya bada daman yazo, amma da sharaɗin baya son dogon nema, idan mun sasanta kanmu baya so abu ya ɗauki lokaci, kuma baya son yawan zuwa zance,

haka taron ya watse kowa fuskan shi cike da farin ciki, amma ni kuma takaici kaman zai kashe ni, baya ma da naga habiba ta saka hannu biyu tayi tagumi, duk sai naji abun bai mun ba, muna shigowa parlor nida habiba muka haɗu da mamie, fuskan ta cike da fushi ta kalle ni, babu kara tace, "sannu madam Aysha, wato an baki suratul yusuf an haɗa miki da surkulle sai murna kike kin samu mai so ko? Tou ayi dai mugani, amma insha Allahu bazaki riga habiba auruwa ba kam a gidan nan, kai hattah Raliya ma sai kin rakata, don ba rako mata duniya nayi ba ballantana na zura ido".....

"lallai ko zai tabbata kin rako mata duniya mushirikiya kawai, ke kam ban san ranan da zakiji tsoron Allah a zuciyar ki ba, gani kike duk surkullen da kikeyi wani ma haka yakeyi"? Cewar Aunty Rakiya da shigowan ta kenan gidan, tsaki mamie tayi ta wuce ta bar wurin batare da ta tanka wa Aunty Rakiya ba.

Ita ko Aunty Rakiya haka takama masifah har ta wuce ɗakin ummin mu, rai a ɓace takama masifa akan shirun ummi yayi yawa, sannan ta ƙara addu'a fah, don zuciyar mamie babu Allah a ciki, murmushi ummi tayi tace, "banda abunki Rakiya mamin su ta isa ta hana abun da Allah yayi nufi? Kuma ni kullum addu'a na akansu yake, babu dare babu rana, kuma insha Allahu khairan, ni damuwa na ma da ita Ayshan kaman yaron bai mata ba, gashi kuma mahaifiyar tana son abun, ni har kunya nakeji wlh".

Wuri Aunty Rakiya ta nema ta zauna, "tou idan Aysha bata so ae baza a mata dole ba, kawai addu'a zamu dage, idan babu alkhairi Allah ya kawo mata wanda yafi alkhairi, amma babu dole babu kuma kunya", amma dai abun bahaka naso ba, don ni banga aibin yaron ba, cewar ummi,

Ita ko yarinya taga aibu, kuma babu mai takura mata sai abun da taso" Aunty Rakiya ta faɗa, ita dai ummi murmushi tayi ta sake zancen ta koma wani chafter daban.

Ranan sallah na uku Yayah Aliyu yazo gidan mu, parlor Hjy ummah habiba ta kaishi, bayan sun gaisa ta kai mishi abun sha da cake ɗin da mukayi na sallah da cincin sai naje, hiran dai dani kam babu armashi, amma shi ds habiba kaman sun shekara da sanin juna, nidai ban da ehh da a'a babu abinda yake ji daga gareni, ganin haka sai ya maida hankalin shi kan habiba yana ta bata shawara akan karatun ta, tunda shima computer science yake koyarwa, nidai gaba ɗaya hiran ba wani ɗaɗani da ƙasa yayi ba, saboda nakasa jin wani abu akanshi, sai dai ban wani nuna mishi sosai a fuska ba, babu daɗewa sai ga Raliya ta shigo, ko gaishe shi batayi ba kanta tsaye ta kalli habiba tace, "kizo mamie na nemanki" daga nan ta juya ta fita a parlon, dukkan mu kallo muka bita da shi cike da jin kunyan abinda tayi, shikuma da yake

ba mai damuwa bane idon shi kawai ya mayar kan habiba yace, "tou Aunty habiba godiya nake, amma a ƙara riƙe mun wuta fah" ya faɗa cike da zolaya, itama dariyan tayi tace, "baka da matsalah sai dai ka nemi wani abun kuma daban" daga haka ta fita, shi kuma ya maido da hankalin shi na, "ina muka tsaya ne princess?"

Ɗago kai nayi na dube shi, muryah cike da rauni nace "babu komai",

Zura mun ido yayi har sai da naji nauyin idon shi akaina ya mun yawa, sai dube - dube nake tayi akan wayana, ba tare da nasan me nake ganiba, duk a takure nake, ganin haka yace, "tou princess nidai zan wuce sai munyi waya, fatan babu wani abu ko"?

Cikin gaggawa na amsa mishi da babu komai na gode," ina miƙewa kaman an ɗana mun abu, murmushi yayi yace, "tou a mun rakiya mana".

Zaro ido nayi ina kallun shi nace, "Rakiya kuma? ae za'a ganni, nidai kawai.... " sai kuma nayi shiru ina maida kaina ƙasa saboda irin kallon daya ƙureni da shi, bai wani ja ba ya juya ya fita yana cewa, "baki da saƙo wurin mummy"? Da sauri nace a gaisheta.

Bayan ya fita hjy ummah ta fito tana ya mutsa fuska tace, "ashe ke sokuwa ce ban sani ba? Wannan wani irin zance ne babu armashi? Sai dai yʻar'uwarki ce bakin ki? Tou a kul kada nasake ji ko ganin wannan ƙauyancin, don ko mutanen da iya kachi".

Tura baki nayi gaba ban bata amsa ba na fiche a parlon.

Wasa-wasa shaƙuwa tsakanin Aliyu da habiba sai yafi ƙarfi, wani lokacin ma idan ya ƙira waya na sai dai hiran ya koma da habiba, zuwa ɗari kuma hiran da ita yafi armashi, nidai nawa ido da binsu da kallo, a haka mukayi wata uku tare da shi, lokacin kuma mahajjata sun dawo makkah, da yake mummy taje, sai ga kaya na fitan tunani an kawo mun tsara ba, ranan ina wuta mamie ta jefah ni a ciki, haka tayi ta banbami tana cewa ummi ta rufe taurarin farin jinin yʻarta, don shigan habiba side ɗin mu tasan ba ƙaramin illah akeyi wa yʻarta ba, amma a zuba da ita insha Allahu sai ummin tayi kuka, kuma daga yau ta shiga tsakanin habiba da ni, idan ba

mugunta ba ummi ma taja kunne na da yarta, ko kula ta kanta ummi batayi ba, sai mamah ne ta fito ta watse ta iya son ranta ta kuma ce ta jira dawowan Abba da hukuncin da za'a ɗauka, don wannan mummunan fatan da takeyi idan ita ummi bata ɗauka ba ita mamah zata ɗauka, duk abunda akeyi Raliya tana tsaye sai bina da kallon banza ta keyi, ƙasa-ƙasa tana zuga mamie, haka dai akaita rikici.

Bayan dawowan Abba mamah ta tasu da maganan agaban kowa, kuma ta rantse idan Abba bai dakatar da matan shi ba ita zata dakatar, cike da banbami take magana, ita kuma mamie ta ɗaura ƙafa ɗaya akan ɗaya tana wani jijjigawa, a ƙarshe dai Abba yayi gyaran muryah yace,

"don Allah ku saurara mun, yanzu ko a tunanin ku akwai asiri? Kun ma yadda da akwai kenan? Tou ni ban yadda akwai ba, amma duk da haka zan tsawatar da irin wannnan muggan fatan da akeyi wa yaya na", ya juya yana duban mamie, "don Allah mamin su bana son tashin hankali, shin Aysha ke ba yarki bace? Tou me yasa zakina jifanta da munanan kalamai? Don Allah ku zama ɗaya kowa yabar maganan nan bana son ya fita ma, kuma da yau bana son a dinga shiga tsakanin yaya nah, a barsu suyi zumuncin su bana son a raba mun kan yaya a damuwan ku na banza da wofi", sannan ya maida kanshi kan ummi yace, "ummin su don Allah bana son abubuwa na chanfi a gida na, wannan maganan ya fito ne saboda mamin su bata da haƙuri ko kaɗan shiyasa idan ranta ya ɓaci sai tayita magana babu kan gado, amma bawai nufin ta ta cutar da wani bane, fatan kowa ya gane kuma maganan zata tsaya a haka"?

Murmushi ummi nah tayi ta kau da kanta gefe tace, " dama ni ka taɓa ganin na taɓa zargin wani a rayuwata? Nayi imani fah da ƙaddara mai kyau ko marar kyau, kuma ban saka zuciyata akan wani ya isa ya cutar dani ko yarah na ba, don na dogara da Allah, kuma nasan zai isar mun akan komai".

Baki a buɗe mamah take bin Abba da ummi da kallo, chan tace "tou haka zancen yake kenan ko? Kai a irin adalcin ka kenan iya abun da zaka ce kenan? Tou Allah ya mana jagora", sannan ta maida kanta kan ummi tace, "ke kuma baiwar Allah ya isar miki yadda kika ce, kuma Allah ya tsare ki da yaranki daga sharrin mai sharri, amma mukan mun sha tabara mun sha lahaula, duk sharrin mai sharri haka zai barmu," ta faɗa taa barin wurin tana faɗin ita ta gajji da ganin kayan ɓacin rai.

Bayan kwana biyu da mamie ta hana habiba shigowa side ɗin mu, sai zaman mu ya koma chan wurin hajiya ummah, amma kuma abinda na lura sai Raliya ma ta maida zamanta chan, amma duk da zamanta a wajen baya wani lasting sbd abu kaɗan zasu kanchale da Hafsy sai kuma hjy ummah ta fatattake su, nida habiba kuma ganin an koresu sai muyita dariyan su, a ranan kuma habiba ke gaya mun raliya ae yʻar aike ne, gulma take kaiwa mamie, nidai dariya nayi nace, "zata shiryu ae, yarinta ne yake damunta".

Gaba ɗaya sai zaman mu da kwanan mu ya koma chan, saboda mai aikin hjy umma da tayi tafiya, gashi zazzaɓi ya sako hjyr a gaba, sai Abba yace mu koma chan gaba ɗaya muna ɗebe mata kewa, mamie babu yadda ta iya sbd lokacin data so ta dakatar da habiba har cikin gida hajiya ummah ta shiga ta watse ta kuma ta kafa mata kyakkyawan worning.

A hankali na lura Aliyu ya janye ƙirana a waya, sai dai naji shi suna hira da habiba, duk da dai ba hiran soyayyah bane sukeyi, amma duk sai naji jikina yayi sanyi, sai dai bance komai ba, don ni idan ka cire ummi na duk duniya babu abinda nake so irin habiba.

Habiba ta matsa mana ranan friday muje gidan yayah mohd mu wuni wa Aunty Bintu, ban ƙi mata ba muka shiryah mukaje, gashi lokacin da mukaje fatima sister Aunty Bintu tazo mata hutu saboda Aunty Bintu cikinta yayi girma, haihuwa yau ko gobe, sbd ma ta daɗe bata samu haihuwan ba, murna wurin Fatima kaman yayah sbd ita dai son mu takeyi.

Zuwa la'asar sai naga habiba tana amsa wayan Aliyu, bayan sun gama sai ta juyo cike da farin cike tana duban mu tace, "sisto Yayah Aliyu yazo, mu shigo da shi parlor ko"? Ido na zuba mata kaman bazan ce komai ba, sai chan kuma nayi wani tunani, fuska na cike da murmushi nace "sisto tunda yazo ku gaisa ne kije kawai waje ki same shi mana".

Babu ɓata lokaci da magana na ta ja gyalen ta tayi hanyar waje tana faɗin "sisto ki fito tou ku gaisa, bari naje, yace zai kawo mun wani mini computer ne da yayi order shi ya iso, shine zai kawo mun nawa", daga nan tayi hanyar waje cike da sauri.

Zuciya nane ya yanke a lokacin *Aunty nice*, saboda sai na rasa dalilin da naji hankali na ya tashi, kuma kaman alaman kaman naji kishin yayah akayi tsakanin su yakai haka da yar'uwata? Amma banja ba sai na ture abun a raina, na maida hankali na kan Aunty Bintu da take mun tambayan bawai saurayina Aliyu bane yazo? Tou meyasa ni ban fita ba sai habiba? Ban iya nace mata komai ba, sai murmushi da na bita da shi, amma *Aunty nice* haka kawai naji zuciyana yana wani irin ɓaci, sai dai dana tuna habiba sister nane sai ture abun a raina.

Daga nan naga Aysha ta sunkuyar da kanta ƙasa tana wani murmushi marar armashi, har zuwa wani lokaci kaman bazata sake cewa komai ba, sai kuma ta ɗago ta dube ni fuskanta cike da murmushi tace, "*Aunty nice* ina son habiba komai na mallaka zan iya sadaukar mata, amma shaiɗan sai ya fara rinjayar zuciyata naji kaman Aliyu fah ya dace da ni, kuma ina jin wani iri a zuciyata kaman fargaban kada na rasa shi.

Yau ne habiba zata shigo amma shiru, sai ana fara ƙiran sallan magrib sai gashi ta shigo cike da farin ciki, hannun ta ɗauke da wani ƙaramin computer, ɗayan hannun ta kuma riƙe da wani leda mai ɗauke d turare masu shegen ƙamshi da kyau guda biyi, gefe nah tazo ta zauna jikin ta rawan murna ta ajiye ledan turaren ta buɗe computern ta mai shegen kyau ɗan ƙarami, "sisto kalli abunda Yayah Aliyu ya kawo mun, wallahi sisto yayi kyau nagode ki ƙara mun godiya a wurinshi, yace nagaishe ki ma sauri yakeyi," ta miƙa hannu ta ɗauko turaren ta buɗe tana cewa, "sisto ki ɗauki ɗaya a ciki, ranan ne muna hira nake bashi labarin turaren ashe ya saya mun, sai kawai naga ya haɗa mun da shi yau", "wani irin ta miki godiya kuma? Ina ce dayazo ke kaɗai ya nema? Tunda hakane ae kin mishi godiya ya wadatar" cewar Aunty Bintu, wanda na lura ta fini jin zafin abun, nidai duban computer nayi nace, "gaskiya sisto yayi kyau kin chaɓa sosai, amma turare kuma ae wake ya sayo nima kuma kinsan ina da turare, sai next time idan ya kawo miki kya bani yanzu kam ae kya kai gida ki nunawa mamie ae", na faɗa ina miƙewa don zuwa yin alwala, shiru fatima tayi tana bin kowa da kallo, amma duk hankalinta kaman ba'a kwance ba, chan ta kasa jurewa ta dubi yar'uwarta tace, "Aunty nikan Aliyun nan saurayin waye a cikin su? Na ɗauka fa shine saurayin Ayshaa?" da sauri habiba tace, "surayin ayshaa ne mana ni kawai shiri mukeyi sosai, kuma kinsan course ɗin mu iri ɗaya ne, shiyasa kullum hiran akan shawarwari yake bani inda zan dage da karatu, kuma laptop ɗina babba ne aka saya mun shiyasa yace zai saya mun wannan ƙaramin don zuwa school," "shima duk turaren na school ne ko"? Cewar fatima da ta bita da kallo ganin ta mayar da kowa shashsha, yare Aunty buntu ta koma yiwa fatima, daga nan kow a yayi shiru aka shige yin sallah, sai wurin ƙarfe takwas yayah mohd ya maida mu gida, nidai har zuwa lokacin bani jin sakewa a zuciyata, kuma abun mamaki har lokacin Aliyu bai ƙirani ba, kuma ina lura da su tun muna gidan yayah mohd ya ƙira habiba, babu daɗewa kuma mun dawo gida mun shirin kwanciya naga

ya ƙirata, duk da bawani dogon magana sukayi ba, na dai ji tace mishi zata kwanta ne, sannan ta ƙara mishi godiya, tana aje wayan kuma tace mun sisto Aliyu yana sonki sosai, dubi abinda ya mun, duk fa saboda kece, nidai ko kallonta banyi ba ballantana nace wani abu, Data na kawai na buɗe na shiga whatsapp, jammy ce muka haɗu muke ta hiran cikinta da yadda ta ke tafama da laulayi, dayake a group ɗin mu ne, saiga maryam ma ta shigo a ka cigba da ita, muna ta yiwa jammy tsiyan ta kusa zama mamah, amsa ta dawo mun da shi akan nima ae ina hanya don taji wai za'a zo gaisuwa ae nan da ƙarshen next month, tunda mummy tace bata so abun ya wuce December dis year, saboda haka nayi shiru nima next year zan zama mamah, sai naji abun da takeji,

Lokacin kuma habiba ta hau, amsan da ta bayar ne yasa na ɗaga kai na kalle ta, kuma lokaci ɗaya naji gabana ya yanke ya faɗi, me habiba takeyi ne haka? Ki kama kanki habiba cewar jammy, domin ba yardar ki muke nema ba na ita jarumar muke nema, kuma mun samu, saboda haka go gefe besty, tafaɗa tan turo emoji ne gwaliyo wa habiba, ita kuma habiba ta sake maida mata da, wlh da gaske besty sai na amince tukun ayi december, idan ban amince ba babu abinda yaya Aliyu zai yadda ayi, idan baki yadda ba kuma ki tambayeshi, ita ma sai ta turo emojin gwaliyo, nan ma abunda ta sake faɗa sai da yasa na ɗaga kai na dubeta, duk da hankalin ta yana kan wayanta bani take kallo ba,

" tou ko dai kina tunanin tafiyan Ayshaa ta bar ki ke kaɗai ne? Sai ki fito da miji besty a haɗaku rana ɗaya, kowa sai taji da kewan yar'uwarta lokaci ɗaya" , cewar maryam, amma sai habiba tace "ai na fito da miji besty bayyanan lokaci kawai muke jira, amma soon", dariya jammy tayi tace, idan mu bamu da labari ae siston ki tana da labari, kuma gaskiya ya kamata ki gaya mana ae mun zama ɗaya, yanzu kam ma mun zama family ɗaya, tunda besty zata sake dawowa gidan mu",

Dariya habiba tayi, tace abun sirri ne, goodnyt sis jammy, ta faɗa tana sauƙa a online, ni kuma dama maryam ta dameni ta private akan bata ganewa abinda habiba ta faɗa ba, don Allah na maida hankali na dinga kula Aliyu muna hira, amma ita hankalinta baya kwance, na dai kwantar mata da hankali akan insha Allahu babu wani abu, zolaya ne kawai irin na habiba, a ƙasan zuciyata kuma hankali na ba a kwance yake ba, haka dai hiran namu ta watse.

Abubuwa na rayuwa sai tafiya suke kwanakin mu kuma yana ƙarewa, a haka har mukayi sati biyu babu wani ƙira daga Aliyu zuwa gareni, kuma bai sake zuwa gidan mu ba, amma kullum zasuyi waya babu adadi shi da habiba, wanda yanzu ba ta amsa wayanshi a gaba na, sai dai ta tafi side ɗinsu ta amsa, kuma yanzu sau dayawa zaman ta a side ɗin su yafi yawa, tare muke tafiya sch, amma idan ka

ganmu tare irin na da tou sai dare, sau dayawa yanzu idan naji kaɗaici kawai sai na shiga wurin maryam.

Bayan wani yɨan kwanaki sai ummi ke tambaya na ko Aliyu yayi tafiya ne? Taga shiru ya daɗe bai zoba, amma sai nace mata yana nan kawai bai samun lokaci ne, a haka dai ummi ta mun ɗan nasiha akan rayuwa, wanda kullum duniya ita haka ne a tsakanin mu dukkan mu yaranta idan ta zauna sai ta mana nasiha, can sai hafsy tasa ka baki a maganan tana ce mun Adda Ayshaa wai da gaske Yaya Aliyu ne ya saya wa Adda habiba laptop ɗin nan? haka raliya tagaya mun har tana wani maganan banzan ta chan, wai yanzu baku kula juna keda Yayah Aliyu",

Murmushi nayi bance komai ba, sai Ummi ce ta tsura mun ido cike da mamaki, " Ayshaa meye gaskiyan maganan da yɨar'uwar ki takeyi"? Inji ummi.

"ummi nima ban san yayah akayi ba, kawai naga ya kawo mata tsaraban shi da wasu turare, kuma ni baya ƙirana a waya, ita ya ke ƙira kullum, tou ummie ban san me yake faruwa ba", na faɗa jiki na a sanyaye.

 "Amma shine ayshaa baki taɓa ce mun komai ba? Hakan da kikayi dai dai ne?" ummie ta faɗa, shiru mukayi na wani ɗan lokaci, kaman kowa bazai sake cewa komai ba, chan sai ummie nah tace, "abinda nake so da ke Ayshaa yadda kikayi shiru baki cewa habiba komai ba tou haka nake so kada kicewa Aliyu komai, zato zunubi ne ko ganin baki kula shi, shiyasa hala suke zancen komai shida habiban, don ganin yadda kuke da ita Allah masani, nidai ta wurina kullum addu'a nake muku, kema ki dage da addu'a insha Allahu khairan" tsaki hafsy taja tana harara na taace, "ummi tou meye ma ita Adda Ayshaan bazata buɗe baki tayi hira da shi ba wai sai wata ce zata mata hiran? Allah ummie ce mun raliya tayi wai yace Adda habiba tafi Adda ayshaa kirki da son mutane, har tana wani cewa ae kirki gadon shi sukayi, tou me suke nufi da hakan"?

Nidai hafsy bana son rikici da son faɗa, duk abinda tace kada taji bakin ki, bana so kice komai, nace Allah zai mana maganin komai, cewar ummie.

Ranan friday da dare dukkan mu mun hallara a babban parlon Abba, kasan cewar Abba yazo gari weeƙend, kowa yana nan banda yayah umar, da yake ƙarshen wata ne hattah yaya Ahmad ma yazo, kuma yayah mohd ma ya shigo, don a gidan shima yayi dinner da mu.

Gyaran murya Abba yayi, kowa ya maida hankalin shi kanshi, ni kuma lokaci ɗaya naji gaba na ya faɗi, don jiya a group jammy ke ce mana saturday za'a zo gaisuwa da tambaya, suna ta zolaya na, nidai banyi waya da Aliyu ba har yau, amma naji sunyi waya da mummyn shi, kuma Aunty Rakiya ma tazo gidan mu sunyi magana da ummin mu amma ni kuma bai ƙirani ba, amma a yanayin hiranmu a group sai naga kaman habiba tasan da hakan, duk sai naji ni a tsarge, ni ake nema amma ban san komai ba sai dai yɑr'uwata, a haka na tsinto muryan Abba yana cewa, "Alhamdulillahi ranan laraba ƙanin mahaifin wannan yaron Aliyu ya ƙirani, akan ranan Asabar wato gobe insha Allahu zasu neman auren Ayshaa, saboda haka nayi waya da yɑn'uwa na gobe mutum biyu zasu zo, sai ni da Mohd da Ahmad zamu haɗu mu karɓe su, ke Ummien su munyi magana da ke tun ranan, akan Rakiya zata zo ku haɗu duk wani abu da za'ayi na karɓansu sai ku tsara, abun da ake nema sai ku gaya mun", sannan ya dawo da kallon shi kan habiba, "yɑn biyu na yakamata ki turo mun naki don na haɗa ku rana ɗaya na aurar da ku, domin burina kenan naga kunyi aure rana ɗaya da yɑr uwarki", ya faɗa yana riƙo hannun habiba, ita dai sai smilling takeyi tana sunne kai ƙasa, "Insha Allhu zaka aurar da su lokaci ɗaya Abban su, ita ma zata samo nata in....." mama bata ƙarasa addu'anta ba mamie ta chafke da "insha Allahu ma habiba ta samu don zama ta riga ayshaa ta fiya gidan auren, sai dai ita ta biyota daga baya", ta faɗa tana bin mamah da wani kallon banza.

Murmushi mai sauti Abba yayi yana duban mamie yace, " Ranki ya daɗe kin taɓa ganin inda mace ta tsara aure ba tare da mazaa ba, ae nine ko yayunsu masu yanke aure ba ke ba madam" ya faɗa yana maida kanshi kan habiba, cike da farin ciki ya sake tambayanta, "twins wai da gaske na samu surukin? Yh baki sanar da ni ba tuntuni sai yanzu naji?" Abba shima gobe zai turo insha Allahu" habiba ta faɗa tana miƙewa da gudu tayi side ɗinsu.

Kallo mama ta bita da shi cike da mamaki, sannan ta dubi Abba tace, "Abban su wani irin maganane haka? Bamu taɓa ganin wani yazo ba sai dai muji wai za'ayi gaisuwan aure?, gaskiya ban taɓa jin irin haka ba"

"malama ae basai kin san neman ba, auren kawai yakamata ki sani, saboda ban san mugun nufin kowa ba kan yarah na, amma yanzu idan manya sun shiga kowa ma sai yaji", ta faɗa tana wani fari da ido kaman yarinya ƙarama, mudai lokacin Abba ya sallame mu muka bar shi da matan shi da kuma yayun mu.

Ganin hafsy zata takura mun da magana ni kuma gashi ji nake kaman kaina zai fashe da zuciyata, don ji nake Aliyu yama raina ni, raini mana yana tunanin zaman auren habiba ne zata mun da bazai dinga magana da ni ba sai ita? Tou Alhamdulillahi itama habiban ta samu nata mijin naga kuma yayah zaiyi, ko yanzu zai na ƙirana ko bazai ƙira ba? saboda haka sai na wuce side ɗin hajiya ummah kawai, itam ganinta zaune a parlon da mai aikinta suna kallon wani series na hausa ban wani zauna ba na wuce cikin ɗakin mu, domin nasan daga chan Abba nan zaizo da su yayah Ahmad, sai kawai na wuce ɗakin na kwanta, sannan na jawo wayana na shiga whatsapp, ganin maryam da jammy suna ta hira sai na musu sallama, ko amsawa jammy bata samu tayi ba ta ƙirani video call, harara na mata na wasa bayan na ɗaga, nasan gulmah ne kawai yake cinta, dariya ta kwashe da shi lokaci ɗaya, tana matar yayah meye ne yanzu duk kika zama wata silent da ke? Kin san fah ina masifar sonki shiyasa naji daɗi da yayah na ya zaƙuloki cikin ƙawaye na yace ga gwanar shi, abun ki sake mu tsara komai yadda ya kamata amma sai kike wani shareni kina basar dani, gashi kun koyi wani nuƙu-nuƙu keda yʼar'uwarki, wai har za'ayi tambayan auren ta gobe amma bata gaya mana mijin ba ballantana a ɗan gaisa a saba da juna, sai kawai yanzu take gaya mana, ni ban ma yadda da maganan besty ba, Allah dai ya kaimu goben, gashi abun yazo biyu idan d gasken ta keyi" ta faɗa tana wani dariyan rashin mutunci, nidai samun kaina nayi da sake jin faɗuwan gaba, ina kallon jammy cike da damuwa nace, " besty kodai Yaya Aliyu habiba yake son aure bani ba"? Ajiye bananan hannun ta da take ci tayi, da sauri tana duba na tace, "besty wani irin maganane wannan? Ta yayah ma haka zai faru? Yayah sokon inane?" murmushi nayi mai ciwo nace, "besty mu bar maganan wasa, nifa yafi 1month yaya Aliyu bai nemi waya na ba, zuwa wurina kuma ya daɗe, nifah ko wayan shi nagani shi da habiba ne, kuma yanzu ni ban taɓa ganinta da wani ba ko naji suna waya, idan ba shi ba, shi kaɗai yake ƙiranta kuma basu hira a gaba na, kinga ae hala ita ya koma yake so", na faɗa jiki a sanyaye, domin ni tun ranan da mukaje gidan Yayah mohd nake jin tsoro da fargaba, kuma tun ranan naji zuciyata ta aminta da shi da auren shi, amma kuma tun daga ranan shi kuma ya ɗauke kanshi akaina.

"kan bala'i" naji amon muryan besty jammy, wanda har na manta ma akan waya nake, maida dubana nayi da hankalina kanta, "amma besty wannan shirmen magana ne, kuma haka nasan bazai taɓa faruwa ba don wallahi duk asirin uwarta mummy bazata bar ɗan ta ya faɗa ciki ba, gaskiya haka ma bazai yiwuba, kuma laifin ki nema besty, tun kwanaki maryam ta mun magana akai, na miki magana sai kika nuna ke ba haka ba ae yʼar'uwar kice, kuma hira take tayaki kawai, in banda ke yanzu besty ae duniyan fa ta ɓaci ba nagida ba bare duk cin amana ya kama zuciyar mutane, amma babu komai bari na neme mummy", da sauri na tare ta nace, "a'a besty don Allah kada ki nemi mummy, ae za'ace ina zargin yʼar'uwata kuma ita ma ae tace ta same miji gobe zai zo, saboda haka Allah ya kaimu goben, komai ma ae Allah zai bayyana shi, idan shine ma zata aura ae babu komai *ANA BARIN HALAL*.... ae don kunya, sai na bar mata nima Allah sai ya dube ni ya bani

nawa rabon, tunda ita taga ya mata shima kuma yaga ta mishi, amma yanzu kam babu abinda zance don kada ya zama zargi.

"itace dai da shi za'a ce musu *ANA BARIN HALAL*.... dan kunya don ita ce ya kamata idan tana jin son shi ta haƙura don tsakanin ku da kunya, shima idan yaji ta mishi sai yayi haƙuri ya bari don kunya, kuma wallahi nasan ma insha Allahu haka bazai faru ba, don ae tare ya ganku kuma ya kware miki, ya ganta a lokacin mai yasa bai ce sai ita ba? Kayan dab da ƙasa kayan haushi" ta faɗa tana harara na, tana "nasan haushi na kike ji na aibanta yaɾ'uwarki, wallahi besty ni halin mamamta ne bana so, don ita habiba mutum ne har da ƙari amma batayi dace da uwa ta gari ba, wani lokaci fah a ɓoye mamanta ta dinga zuwa gidan mu wurin mummy, da yake mummy yaɾ no nonses ne ta watse ta bayan ta sallameta, inaa gaskiya bazai yiwu ba" ta faɗa tana mun sallama, nidai roƙonta nayi akan ta bar maganan Allah ya kaimu goben muga abun da Allah ya shiryah, harara na tayi ta kashe waya.

Tunda jammy ta sauƙa na ji komai ya fita mun a kai, sai kawai na kashe Datan na tsurawa wayan ido kaman ina hangen wani abu, kaman wanda aka tunatar dani wani abu ko aka umurce ni, sai kawai hannu na ya tafi kan number Yayah Aliyu nayi dialing number shi, duk jikina kuma yana rawa, kaman bazai ɗauka ba har ya kusa yankewa sai ya ɗaga.

"Hello" naji ya faɗa bayan ya ɗauki wayan, amma sai na samu kaina da kasa cewa komai nayi shiru, chan sai naji ya ƙira sunana, "Ayshaa! akwai wani damuwa ne"? Ji nayi ido na duk sun ciko da hawaye, ban bari sun zubo ba kuma ban amsa tambayan da yayi mun, shima shirun yayi na zuwa wani lokaci, chan kuma yace "idan babu wani damuwa zan kwanta, don kaina ciwo yake mun", nan ma shiru nayi, har zuwa wani lokaci kuma sai na kashe wayan gabaki ɗaya, naji wani irin ƙunci da ciwo a zuciyata, wato har baya son magana dani kenan ko? Na tambayi kaina da kaina, ban ce komai ba sai na maida kaina na kwanta nayi shiru, duk wani farin ciki na neme shi na rasa.

WASHE GARI

Da yamma wuraren ƙarfe biyar na yammah 5:00pm, yaɾan gidan su Aliyu suka zo, lokacin ni kuma ina ɗakin ummie nah ina kwance, don wani irin ciwon kai ne ke damu na, kuma ganin yanayi na sai ummi ta bani paracetamol na sha na kwanta, a wannnan lokacin kuma ummi suna tare da mamah a parlon ta bayan sun tabbatar duk wani abu da za'a buƙata ya kammmalah wuri ɗaya, haka chan side ɗin mamie ma tana tare da ƙanwarta da ƙawaerta da suka taso tare, kuma habiba tana chan side ɗin don tun jiya da ta tafi bata dawo wurin mu ba, a haka baƙin suka zo, Abba

da su yayah mojd da yan'uwan Abba ne suka tarye su, baƙi ne su huɗu a mota ɗaya, don haka naji hafsy ta shigo tana gayawa su ummi akan baƙin su huɗu ne, duk sai naji faɗuwar gaba ya mun yawa, har wani zazzaɓi ne naji yana son kamani a lokacin, sannan naji wani siririn hawaye wanda bansan da shi ba yabi ta gefen kunne na ya wuce.

Bayan shigan su mamah ta saka masu aiki da hafsy suka shige da abincin baƙin da akayi, snacks ne dasu kayan drinks, sai nono da fura da aka dama musu mai kyaun gaske yasha kwaƙwa aciki aka kai musu, bayan sun dawo bai wani fi 30mnt ba Yayah Ahmad ya shigo ya samu ummi yace su zo ita da mamah da ni, jikina na rawa na miƙe na ɗauki hijab ɗina nabi bayan su ummi, parlon cike yake da huhun goro kusan guda goma sai katun-katun nasu biscuit da su chewngum dasu alawa, suma ko wanne ya kai katun goma ɗin, a haka na raɓe a gefen ummi na na zauna, chan gefen Abba na kuma hajiya ummah ne zaune ta wani kima ɗauri kaman ranan ne za'a ɗaura auren, bamu daɗe da zama ba sai ga mamie sun shigo ita da habiba da ta sha wasu sabbin kaya kaman amaryah, nidai kallo ɗaya na musu na maida kaina ƙasa don wani kallon da mamie ta mun saida naji zuciyata ta yanke, don kallo ne mai ɗauke da alaman dariyan mugunta ko kuma tula maka haushi.

Shiru parlon yayi babu wanda yace komai sai Abba daya tsurawa ƙasa ido yayi shiru, duk fuskan shi a dagule da ɓacin rai, ɗago kai yayi ya zura mun ido, kaman baxai yi magana ba chan kuma sai ya numfasa da ƙarfi ya furta "Alhamdulillahi ala kulli halin, komai daga ubangiji yake mai kyau da marar kyau, Allah mungode maka", "Allah abun godiya mutum abun tsoro, ehhh mutum abun tsoro mana, ni ae tunda uwata ta kawo ni duniya ban taɓa chin karo da labcecen abun tsoro ba irin wannan, kai duniyar nan abun tsoro ne, mutum ma abun tsoro ne irin wannan mata da yayan ta labta-labta nan", hajiya ummah ta faɗa tana nuna mamie da habiba, mudai bakin mu shiru nida ummi, sai mamah ne ta kasa daurewa ta dubi ƙanin Abban mu da shima yayi tagumi tace, "Alhaji ƙarami me yake faruwa ne? Kaddai sun fasa ne? Naga duk kan ku babu daɗin gani",

" da fasawan sukayi ae dayafi sauƙi akan wannan irin lafcecen cin amanar da yar'uwarta ta mata da shi sokon saurayin Aliyu, ni yau naji abun da ya girmi shekaru na," umma h ta faɗa tana kama haɓa, chan kaman wanda tayi tunani ta sake cewa, "ni dama irin yadda nake sauraren hiran da yaran nan sukeyi da shi saurayin sai da na zargi haka, amma kuma bance komai ba gudun kada ace ni nake haddasa fitina, amma ko zuwan Rakiya wancan satin sai da na ɗan ƙyanƙasa mata amma firr tace mun haka baxai faru ba, sai naja baki na kawai na tsuke, don Aysha da habiba duk ɗayane a wurina, ban taɓa nuna banbanci ba Allah yana gani, amma yanzu kam sai ta Allah", ta faɗa tana hararan habiba da ta sunkuyar da kanta ƙasa

kaman wata munafuka, Bappan mu ne yace "hajiya ae duk babu abun da zai gagara, ae da yadda da amincewar ayshaan hakan duk ya faru, kuma a wurin mu duk ɗayane suke, kawai dai a saka musu albarka" Bappah ya faɗa yana gyara zaman shi.

"mukan saboda Allah a mana bayanin me yake faruwa mana, duk kunsa cikina ya ɗuri ruwa" cewar mamah.

"Khadijah" Abba ya ƙira sunan ummie na, a hankali ta amsa da "na'am Abban su",

"Ɗazu bayan yan gaisuwa da tambayan auren Ayshaa sun zo sai zance ya chanja, don bayan gaishe-gaishe da akayi sai aka sako zancen abun da ya tara mu, amma abun mamaki sai naji zance ya chanja kuma suna bani haƙuri da cewan ba maganan neman auren Ayshaa suka zo ba kaman yadda muka zata, wai sunzo ne akan habiba, saboda Aliyu da habiba sun fahimci juna kuma da yardar Ayshaa, da naƙi amincewa sai da nasaka muhammadu ya ƙira mun Aliyun, handsfree aka saka kowa yanaji, sai ji nayi yace sun kasa daidaitawa da ita Ayshaan ne, wanda daga baya tace saboda zumunci ya nemi yar'uwar ta habiba, jin haka yasa mukayi sallama, ban neme kuba saboda nasan tsakanin Ayshaa da habiba za'a ƙullah abun da yafi haka, kuma nasan saboda tana tsoron tunkarar mu zasu iya yin wannan dabaran, duba da haka yasa na amince mu ka koma tsayar musu da rana nan da wata 2, wato december first week idan Allah ya kaimu, amma duk da haka na taraku ne don naji ta bakin kowa a cikin su, meye dalili meye kuma hujkan su"?

Ajiyan zuciya kawai ummie ta ajiye idon ta a kaina, "babu wani hujjah da dalili sai dai son zuciya kawai da ake kitsawa yaran nan, amma gaskiya magana ni bn taɓa ganin irin wannan ba, anzo neman auren ƙanwa kawai sai a ɓuge dana yayarta"? Mamah ta faɗa tana wani hararan mamie.

"zainab don Allah bana son tashin hankali, ina ce Ayshaa da habiba kam duk abu ɗaya ne?" Abba ya faɗa ranshi a ɓace, tura baki gaba mamah tayi gaba, ƙasa-ƙasa tace "abu biyu dai".

Abba bai sake bi takan mamah ba ya maida hankalin shi kan ummie nah, murmushi ummi tayi tace, "Abban su ae abun da yayi Ayshaa shi yayi habiba, kuma abun daka hanga nima shi na hanga, zai yiwu Ayshaa ta ji nauyin ta gaya mana bata son Aliyu ne shiyasa suka yanke shawaran su ita da yar'uwarta, kuma hakan ae yayi dai-dai, don sun fitar da mu kunyan mahaifiyar yaron, nidai nawa addu'a ne, Allah yasa hakan shine mafi alkhairi a garesu baki ɗaya, ayshaa Allah ya kawo mata rabonta, habiba kuma Allah yasa ace gara da akayi", ummi tana faɗin haka taja bakinta tayi shiru.

"Kˈofar shiga aljannar ki da ban Khadija, wannan sanyi zuciya da halinkin wanda ko an cutar da ke baki nunawa saboda haƙurinki, Allah ya haskaka rayuwarki da ta yaranki, Allah yasa albarka a zuriyar ki, insha Allahu kuma khairan, miji kam na Ayshaa idan ya tashi zuwa duniya ne, Allah ya kawowa Ayshaa chanji na alkhairi", hajiya ummah ta faɗa, shima ƙasa-ƙasa mamie tace, "ba ameen ba," da sauri na juya na kalle ta, don daga ni har ummie na da yayah Ahmad da muke kusa da ita munji, harara ta wurga mun, da sauri na maida kaina ƙasa, bayan naga yadda habiba take ta haɗa zufah duk a furgice ta ke zaune.

"Alhamdulillahi, nagode Allah daya bani ke khadijah cikin iyale na", Abba ya faɗa yana duban habiba, "Habiba yayah nene gaskiyar maganan Aliyun"?.

"Abbah" habiba ta ƙira sunan shi, sai kuma tayi shiru kan ta a ƙasa, "ina jinki yˈan biyu nah" da sauri ɗaga kai na dubi habiba, wanda ita ma ni ta ɗago tana kallo, gaba ɗaya sai naji wani tausayinta saboda yadda duk na ganta a wani firgice, ga idon ta ya ciko da ƙwallah, da sauri ta mayar da kanta ƙasa, "Abba watarana muna zaune a side ɗin ummah nida ayshaa, sai tace ta nema na mata alfarma, ita dai bata son Aliyu kuma tayi-tayi taji tana son shi amma ta kasa, gashi tana jin nauyin ƙawar mu jamilah da kuma mummyn su, don Allah na taimaka mata na amshe shi ya zama nice zai aura, don sun gama magana da shi kuma ya fahimce ta, nidai naƙi amince mata har tayi fushi da ni ta daina kula ni, danaga abun zai kawo mana saɓani sai na sake neman ta mukayi zama, nan ta sake mun bayanin sun gama magana da Aliyun kawai amincewa na take jira, tou Abbah ganin bana so saɓani ya sake shiga tsakanin mu sai na amince, nan kuma tace mun bata son kowa ya sani ko mamie ce, har sai ranan da za'a zo gaisuwan wato yau, shiyasa mukayi shiru, itama mamien na ɓoye mata sai yau taji, don ce mata nayi wani ne ɗan katagum, kuma baya zama anan yana saudi, wannan shine gaskiyan maganan Abbah", ta ƙarasa faɗa idon ta yana zubar da hawaye, nidai tunda ta fara magana na shiga al'ajabi, don a duk zamana da habiba ban santa da ƙaryah ba, kuma daga ji wannan magana tsara mata akayi, kuma nayi imani da Allah ba asiri mamie ta mata ta burkita tunanin ta ba, don tun farko habiba ran ta yaso Aliyu, saboda haka ƙofa kaɗan za'a buɗe mata ta zurma, kawai *Aunty nice* naji tsoron ɗan adam a ranan ta bakin hajiya ummah, kuma nayi mamakin ashe duk ƙaunar mu da habiba namiji zai iya shiga tsakanin ƙaunar mu? Don ni ina jin ko yayah namiji yake bazai ɗauke hankali na ba, har na haɗa so da yˈar'uwata, ae *ANA BARIN HALAL*... don kunya, ko da naji son wani wanda ƙawata take jin so ko yˈar'uwata inaga zan iya yakice shi a raina, ya kicewa kuma na har abada, amma meyasa yˈar'uwata da nakeyi wa wani irin so ta mun haka, meyasa habiba ta yanke yadda da amincin da yake tsakanin mu na tundaga tashin mu?

Kallo na Abba yayi, sannan yace "haka akayi Ayshaa ta"?

Ɗago kai nayi na dubi habiba, wanda har zuwa lokacin jikinta rawa yakeyi, maida kaina ƙasa nayi na saka hannun cikin na ummie nah na riƙe, ina ji itama ta damƙe a hannu na tana sauƙe ajiyan zuciya, muryah ƙasa - ƙasa na amsawa Abba da, "hakane Abbah, duk abinda ta faɗa haka ne ya faru" da rawar muryah na ƙarasa maganan, dai dai nan kuma Bappan mu ya amsa da, "Allah ya muku albarka, kema ayshaa Allah ya baki miji nagari, don baza ace kinyi wauta ba, amma gaskiyar batu kam akwai wautan a al'amarin, don dai komai ya wuce ne ae, ina laifin kiyi shawara da mahaifiyar ki kafin ki zartar da komai? Don dai duk ɗaya ne kawai, Allah ya kyauta", ajiyan zuciya Abbah ya sauƙe ya maida hankalin shi kan mu gaba ɗaya,bayan yayi mana dogon addu'a ya sallame mu, amma muna miƙewa mamah ma ta miƙe da sauri tabi bayan mu, tana ita bazata iya wannan zaman kayan takaicin ba, don idan ta cigaba da zama rai zai ɓaci, ina kallon yayah mohd ya bini da kallo, yayah Ahmad kuma ya dawo kusa da ummi ya zauna.

Muna fitowa habiba ta riƙo hannu na muryah ƙasa- ƙasa tace, "sisto nagode da kika rufa mun asiri, wlh duk wannan abun ya faru ne bada son zuciyata ba, amma insha Allahu zan miki bayanin da zaki fahimta, yanzu dai nagode"' , tana gama faɗa ta sake hannu na ta wuce side ɗinsu da sauri saboda hango raliya da ta fito daga babban kitchen ɗin dayake wurin, nidai bin ta da kallo kawai nayi ban iya nace mata komai ba, Mtssss, tsakin raliya naji dabdani, da sauri na bar kallon inda habiba ta wuce nayi, na maida kallo na inda raliya take nayi, itan ma bance mata komai ba sai ido dana zuba mata, matsowa kusa dani tayi tana wani murguɗa baki, "mutum dai yaji kunya duk kyaun da yake gadara amma ya zama mai baƙin jini, baƙin jini kuma yanzu mutum ya fara, sai dai yaga ni wal ta gaban sh" tana rufe baki hafsy na kai mata mari a bakinta, "bakinki ya sari shegen guntun kashinki, insha Allah aniyar ku ta biku, ae kune masu abun kunyar da har babu kunya babu tsoron Allah kuka iya cin amana yar'uwarku, ae kuwa kune masu abin kunya, sannan da kike maganan baƙin jini, shin akwai wanda ya kaiku baƙin jini? Kun kasa raminku sai dai ku ƙwace na wasu? Abun kunya ae ya tabbata akanku zuriyar matsafah".. tana rufe baki kuwa suka kancame da dambe, kowa duka take kaiwa yar'uwarta, nidai jan hafsy nake ina roƙon su dasu bar wannan shirmen, da sauri yayah mohd ya fito shi da yayah Ahmad, tsawa ya daka musu daga bakin ƙofan da yake tsaye, da sauri suka saki junan su suna huci kaman wasu zakaru,

"ku wuce kubawa mutane wuri sokayen banza da wofi, ku gaba ɗaya rayuwar ku baku da hankali, kullum sai faɗa baku son zaman lafiya"?

Nidai ganin yayah mohd ya fara faɗa wanda ba kasafai zaka ganshi yana yi ba, nayi wuff na wuce ɗakin mu, ina shiga na wuce chan ɗakin ummie na, kwanciya nayi na faɗa tunanin yadda al'amura suka juye, yanzu abun da habiba ta mun akwai adalci

kuwa? Shin zan iya yafe mata har mu sake komawa kaman da? Shin idan tayi auren zan iya zuwa gidanta? Duk irin wayan nan habiba batayi tunanin faruwar su ba, kawai hankalinta kwance taji ta so abun da yake sona? Tashi nayi na zauna, wayata na jawo nayi blocking number Aliyu na kuma goge number, bayan na share duk wasu massege ɗin shi, sannan na tafi whatsapp na sake blocking ɗin shi na kuma goge massege ɗin shi, don dama a yawancin lokuta bani ke reply ba habiba ce, shiru nayi ina tunanin yadda rayuwa zata miƙe tsakanina da habiba kawai nakeyi, a haka naji shigowan ummie nah, hannunta riƙe da na hafsy da taketa huci, bayan ta kuma yayah mohd da yayah Ahmad ne.

Wuri suka samu dukkan su suka zauna, ummi zama tayi akan gadon tana riƙo hannu na, yayah mohd ma a gefenta ya zauna yana riƙo hannun hafsy, shi kuma yayah Ahmad kujeran dake ɗakin 3sitter ya zauna akai shima idon shi akaina, wani abu naji da ban taɓa ji ba na rauni a lokacin da yayah mohd yace mun, "Ayshaa akwai gaskiya a maganan da kuka faɗa ke da habiba a wurin Abbah? Don gaskiya ni nakasa gasgata maganan, don nasan babu yadda za'ayi ku iya tunanin shiryah haka a tsakanin ku ba tare da kinyi shawara da ummie ba, don kwanaki B<ntu ta fara mun wani zancen da bangane ba sai na da katar da ita, amma yanzu ina son sanin gaskiyan maganan"?

Faɗawa jikin ummie na kawai nayi ina jin duk dauriya na ya ƙare, ina jin babu abinda nake so irin nayi kuka, kukan ne nake tunanin zai saka na samu sauƙi, domin ni dai bawai shaƙuwa nayi da Aliyu ba ballantana nace ina son shi da hankali na zai tashi ba, amma abunda habiba ta mun shiyake bani tsoro da sakani cikin damuwa, yanzu da ace ina son shi haka zata rufe ido babu kunya babu tsoro ta so shi? Kenan habiba zata iya son mijin da nake aure ma idan yayi mata tayi, kuka nakeyi sosai ummie tana rarrashina.

"kiyi haƙuri ayshaan ummie, komai insha Allahu zai wuce, kuma mijinki special zai zo", cewar yaya Ahmad, wanda tashi yayi zai fita don shi wani iri ne da baya son ganin abun da zai tayar mana da hankali, bayi da dauriyan yayah mohd, kuma shi sanyin shi da haƙurin shi dama yafi na kowa, yana miƙewa yace, "ummie don Allah ku kwantar mata da hankali, ni zanje gidan Aunty Rakiya mu gaisa, zan koma leƙa wurin su M.G ɗa A.G, don munyi waya suna gari," zuciyata ce naji lokaci ɗaya ta yanke saboda jin sunan fararen abokan shi masu kama da larabawan nan daya ambata, bansan lokacin dana ɗago da ido na ina kallon shi ba, matsowa yayi kusa dani yace, "ko akwai abinda kike so ne na sayo miki"?

Hannu na miƙa mishi ya riƙe, muryah na yana rawa nace, "yayah ni waya nake so ka chanja mun", murmushi yayi yace "angama my sister, zaki ga waya mai kyau

insha Allahu", ya faɗa yana mun murmushi, a haka na sake mishi hannu ya juya ya fita, "wariyar launin fata, gaskiya kowa yafi son Addah Ayshaa akaina a gidan nan, yanzu fah kuka akasamu inayi amma babu wanda ya damu dani, amma ita kowa hankalinshi yana kanta, yaushe ma aka saya musu wayan amma don nuna so da sakalci har wani za'a sake mata wani, nidai bana son natan da za'a chanja mata nima sabo za'a saya mun ba kunce ba", hafsy ta faɗa tana turo baki gaba tana harara na, "tashi ki fita uwar rashin kunya, dama akwai wanda yace miki za'a saya miki waya ne yanzu? Fita kije ki ɗaura mun abinci" ummie ta faɗa tana nuna mata hanyar waje, haka ta miƙe tana Addah idan nagama don Allah ki bani akwalar wayar ki nayi game, nidai miƙa mata wayan nayi ban dube ta ba, ta juyo ummi ta wafce wayan tana, "rabu da ita sai ta gama aikin, idan kin bata wayan Game zata tsaya yi har abincin ya ƙone ko kuma tayi dare,

Bayan fitan tane yayah mohd ya dawo da duban shi kaina, ganin haka na bashi amsa da "wallahi yayah ni bansan duk abunda tace ba, kawai dai na bita a hakane don kar hankali Abbah ya tashi, kuma naga babu amfani tunda yaƙini ya koma mata na ƙaryata, don ni dai bazan sake kula shi ba tunda ya koma mata, akan ayi biyu babu gara itan suyi", na ƙarasa hawaye yana bin fuskana, riƙe hannu ummie tayi ta jawoni jikinta tana, "kiyi haƙuri insha Allahu zakiga alkhairin haƙurin da kikayi, ki barta da shi Allah zai kawo miki naki rabon, amma don Allah yanzu bana son wannan sakewa ki bar saurayi da ƙawa ko yar'uwa, duba da yadda rayuwar yanzun ya koma, amana yayi ƙaranci, ni dama tun lokacin da kika nuna mun bai kwanta miki ba sai na ƙara dagewa da addu'an neman alkhairi akai, kuma ko a yanzu ina ji a raina babu alkhairi a ciki shiyasa duk hakan ya faru", ummi tana rufe bakinta naji wani kuka yazo mun, Allah sarki uwa, gaskiya duk wanda ya rasa uwa dole ya koka *Aunty nice* domin ita wani abu ne na daban, nifa babu wani addu'a da nakeyi akan al'amarin amma kiji ita kuma tana mun, Allah sarki ummie nah, riƙo ta nayi sosai nace, "ummie amma duk da haka sai habiba ta so mutumin da yake sona? Kenan zata iya son mijin da nake aure ma kenan? Ummi ciwon ɗa nakeji a zuciyata bawai na rabuwa da shi bane, ina jin ciwon abun da yar'uwata da nafi so ta mun ne, yanzu dole danganta kar mu yaja baya" na faɗa ina share hawayen ido na, "babu komai sis insha Allahu tsakanin ku zai dai-dai ta, ke ae zuciyar ki mai kyau ce, kuma nasan zaki yafewa yar uwaki ki mata uzuri, insha Allah komai zai wuce" yayah mohd ya faɗa, sannan ya chanja topic ɗin, suka koma maganan haihuwar Aunty Bintu, inda yake gayawa ummie wai maiduguri take son zuwa haihuwa, amma shi gaskiya baya son hakan, itama ummie ta goyi bayan maganan shi akan gara ta haihu a ɗakin ta don babu abunda zai gagara.

Tunda ga ranan da abun ya faru mamie ta samu abun habaici, babu garin Allah da zai fito ya faɗi bakaji ta tana surutun masu rashin farin jini ba, a haka Aunty Rakiya watarana ta shigo ta samu hakan na faruwa, ae ko ta sille mamie tass, harta habiba

bata bari ba, don hajiya ummah ta gaya mata yanzu an hana habiba zuwa side ɗinta, ni kaɗai nake zuwa kwana a chan, aeko aka bar mamie da kame-kame tana bata haƙuri, tass ta zage habiba tana gaya mata indai cin amana da halin uwarta take so ta ɗauko wlh zata sha wahala, kuka habiba ta dinga yi, bayan mamah da Aunty Rakiya sun haɗu sun watse su, zuwa dare ina kwance a ɗakin mu na side ɗin ummah sai ga habiba ta shigo, yadda bata yi sallama ba ta shigo nima sai ban ɗaga kaina na dube ta ba, nidai ina riƙe da wayana muna chatting da jammy, haƙuri kullum take bani akan dukkan su basuji daɗin abinda ya faru ba, don mummy tayi rantsuwa ita dai babu yawun ta acikin maganan auren, don tun ranan tace babu jituwa tsakanin shi da mummy, shima Aliyun tace duk jikin shi yanzu a sanyaye yake, nidai ban tofah komai ba akai, don ummie nah taja mun kunne sosai akan al'amarin, saboda haka sai na chanja topic, na tambayeta yaushe zata fara karatunta? Tace sai bayan ta haihu,, so tanaga zai kai next year, haka mukayi sallama, ina kallon habiba ta gefen idon na tagama duk abinda zatayi na shirin kwanciya bata kulani ba, nima ganin hakan sai na rabu da ita, nayi shirin kwanciya na nima na kwanta.

Washe gari bayan mun idar da sallah na juya na kalleta nace, "sisto an tashi lpy"? A razane ta juyo ta kalle ni, amma abun mamaki sai bata iya ta amsa mun ba, kawai dai naga idon ta ya wani ciko da hawaye, ganin haka sai na koma kan gado na kwanta, na juya mata baya, ban farka ba sai wurin ƙarfe 8:00 shima hafsy ne ta shigo ta tashe ni, akan naje ummie tana nema na, dubawa gefen habiba nayi naga babu ita babu alaman ta, maida kallo na nayi kan hafsy nace, "da kika shigo kinga sisto ne?" tsaki tayi ta fita a ɗakin tana faɗin " ke kika san wata sisto, ni dai naga habiba ta wuce side ɗinsu tun wurin 6:30am, idan zaki yiwa kanki faɗan ta nutsu gara ma kiyi", ta wuce tayi hanyar waje.

Lokacin da na shiga ɗakin ummie na nasamu tana waya ne, a hankali na fahimci da mummyn su Aliyu take wayan, zuciya nane naji ya yanke, kasa kunnena nayi ina sauraran abun da suke faɗa, haƙuri kawai ummie ke ta bawa mummy akan ta kwantar da hankalinta komai nufine na Allah, Allah yayi babu aure tsakanin shi da Ayshaa, rabon da habiba ne, da yake ya wanci ummie idan zata amsa wayanta handsfree ta ke bari, sai idan na sirri ne sosai ba zata saka ba, tsaki mummy ta ja mai ɗan tsayi sannan tace, "wallahi ummin su rai na baya son haɗa iri da matar nan, don babu Allah a zuciyarta, amma bbu komai abunda ta keso bazata samu ba, don insha Allahu bazan bar ɗana a mallake ba, a farko kan sunyi nasaran chafko shi amma gaba kan tayi kuka da kanta", murmushi kawai ummie tayi sannan ta chanja zancen da wani chan daban, a haka kuma basu daɗe ba suka yi sallama.

Daga nan ummie ta juyo tana kallona fuskanta ɗauke da murmushi, ni kuma da sauri na ƙarasa wurin ta, gaisheta nayi, ita kuma ta tambayeni fatan babu wani

matsala ko? Murmushi nayi na kwanta a kafaɗan ta, bance mata komai ba nayi shiru kawai ina kwance ido na a rufe, nasiha da kwantar da hankali na ummi tayi ta mun, tunin naji zuciyata tayi sanyi, muna a haka wayan ta ya fara neman a gajin a ɗauke shi, hannu ta saka ta ɗauka sannan ta saka shi a handsfree, muryan yayah mohd naji yana gaisheta, ni kuma na ƙara gyara kwanciyata a jikinta, kawai sai naji yayah na gaya mata Aunty bintu ta haihu, da sauri na miƙe zaune ina fara'a idona akan ummie nah da duk fuskan ta ya gauraye da murmushi, "ta samu boy, daga ita har babyn duk suna lafiya, muna asibitin", ya faɗa ummie kuwa sai fara'a ta ketayi, "insha Allahu mamanku suna zuwa yanzu, Allah ya raya baby da imani, ita kuma Allah ya bata lafiya da lafiyan shayarwa, suna ajiye wayan na rungume ummie ina "ummie munyi ɗa, wayyo ummi nayi ɗa," da sauri na miƙe nace "ummie bari na shiga wanka na bi mamah muje muga baby", ko jiran me zatace banyi ba na wuce toilet da gudu na.

Kafin kace me duk gidan mu ya kachame da murnan haihuwan barin ma hafsy da ta ringa tsalle kamar yar 6yrs, haka muka shiryah sai *NI'IMA HOSPITAL* mukaje mukaga yaro fari kyakkyawa, kana ganinshi kaga jinin gidan mu, sak Yaya mohd kaman wanda yayi kaki, haka muka ringa murna muna ta ɗaukan babyn, bayan 1hr aka sallame su, lokacin Aunty Rakiya ta iso ita da hajiya umma, mu kuma dama da mamah mukazo da hafsy sai driver, abun mamaki har muka gama murnan haihuwan nan babu mamie babu yayanta ko ɗaya, kuma duk suna gida, ganin zuwan su ummah nayi tunanin ita mamin zata biyosu amma shiru, haka muka ɗunguma gidan zuwa gidan yayan mu.

Muna zuwa muka samu Fatima ta gama gyaran gidan ko ina sai ƙamshin turaren wuta yakeyi, dama ana haihuwan yayah mohd yace ta koma gida ta gyara, amma bata ɗaura abinci ba daga gida ummin mu ta sa akayi, ana zuwa mamah ta saka ruwa ta wanke baby tsaff, Aunty Bintu kuma Aunty Rakiya ta shiga ta gasa mata jiki ta fito ta barta ta ƙarasa wanka.

Bayan kwana 2 sai ga yar maman Aunty Bintu ta taho daga maiduguri, dama mamah tun ran haihuwar muke gidan tare, sai ranan ta tafi, amma ni ina nan tare da fatima, ummie tace na zauna na taimakawa fatima.

Ranan suna yaro yaci sunan Abban mu wato *USMAN* amma sun mishi laƙani da *AREEFH* sai wajen dab da magrin sai ga mamie da su habiba driver ya kawo su, muna zaune a parlor nida su maryam da fatima, da wata yar'uwar su da suka zo suna mai suna Ayshe itama, muna zaune suka shigo, muna haɗa ido da mamie ta

zabga mun hararah, ganin haka na ɗauke kaina a kan su, ganin akwai su maryam a wurin habiba ta tsaya, ita kuma raliya suka shige ciki ita da mamie, banyi niyyan kulata ba duba da ganin bata kula ni, duk da dai ni yau sati na guda da barin gida, ita kuma ba zuwa barka ma sukayi ba, kawai kaman daga sama naji muryan ta tana faɗin "sisto sabon waya kikayi ne"? Ɗago kai nayi ina duban ta fuska na ɗauke da murmushi na amsa mata da "ae yayi 2weeks ae, ranan da aka kawo ina gaya miki naga kin wuce kitchen da sauri, so nayi tunanin idan kin fito zaki zo ki gani ae", da sauri ta saka hannu ta karɓa tana juya shi, cike da mamaki tace, "kin san irin shi ne a hannun Baby", ta sake juya wayan a hannunta tace " Gaskiya wayan ta tafi da ni don tun ranan dana gani a hannun shi wayar ta mun, shi kuma yana cewa ta fi ƙarfi na, gashi kuwa a hannun sisto, aeko zan ce mishi batafi ƙarfi na ba, tunda sisto na ma shi ta ke riƙewa",

"chaɓ aiko tafi ƙarfinki, amma ta wani wuri kuma bata fi ƙarfin kiba, tunda naga alama ke duk abunda siston naki tayi sai kin nemi ƙwace shi zuwa gareki, kin ƙwace saurayi yanzu kuma kina shirin na waya, wai ke habiba baki ƙoƙarin yin abun kanki ne sai na wani? Inaga Babyn ma wanda kikayi ƙwacen ne kika mayar da shi Babyn ko?" cewar Fatima wanda ita dama kullum dare zamu kwanta ta dinga mitan wannan al"amarin, zuwan Ayshe ma jiya-jiya sai da ta bata labari, da yake dukkan su yan zafin kaine ita da ayshen sai abun su ya ɗauki zafi, ni dai da sauri na juya ina duban fatima da tayi maganan tana wani chin magani kaman zata kai duka, tana wani hararan habiba, miƙo mun wayan habiba tayi fuskan ta ɗauke da murmushi tana kallo na, bata tanka abun da fatima ta faɗa ba, sai ce mun tayi bari taje taga babyn sai ta dawo, hannu na miƙa na karɓi wayan da ta miƙo mun, tana barin wajen maryam taja wani dogon tsaki mtssssss, "yarinyar nan kullum na ganta kashe ni ta keyi da mamaki, kana ganinta kaman ta gari ashe zuciyar ta babu kyau ko kaɗan? Amma ba laifinta bane wlh, duk laifinki ne besty", maryam ta faɗa tana maida hararanta kaina, "good kin faɗi abun da yake zuciyata tun jiya, wlh tun jiya da fatima ta bani labari na kalli Ayshaa naga kaman bata wani damu ba sai kare yar'uwarta ta keyi, nace gaskiya Ayshaa itace mai laifin, don sai bango ya tsage kadangare yake samun ƙofa, idan ba sakacin Ayshaa yayi yawa ba ta yayah yar'uwata zata mun ƙwace a ƙaramin lokaci, haba jama'a wannan ma ae raini ne da chin fuska, sannan kuma babu daɗewa nazo ina buɗe miki baki ina miki dariya har ina miƙa miki waya na"? Aysha ta faɗa haushina cike da zuciyar ta, nidai bance komai ba banda mirmushin da nakeyi kaina a sunkuye ina kallon waya na kaman zan ga wani abu a ciki, amma zuciyata cike ta ke da damuwan maganan da habiba tayi, wato Aliyun ne ake ce mishi Baby? bayan haka ma yaushe yake zuwa gidan mu hiran da har taga wayan shi? Ikon Allah yanzu ya tabbata da gaske habiba tana son wanda ya so ni har yaso aure na?

Muryan Fatima ne ya dawo da ni kan tunani na danaji tana cewa, wai ko yanzu habiba ta kuskura ta dawo sai ta ƙara watseta, jin haka nayi saurin ɗago kaina nace mata "a'a fatima idan ummie taji raina zai ɓaci, don taja kunne na sosai akan maganan kuma tace bata son wani magana daga gare ni ya fito, don Allah ku bar

maganan don ni yanzu ma duk kunsa naji babu daɗi, don gani zatayi kaman na damu ne yasa na gaya muku, don Allah kubari".

"dole ae kowa ya bari, tunda me abun bata so, mu yan abi yarima a sha kiɗa kuma mai ya talo mana? Allah ya bada sa'a", cewar maryam.

Babu daɗewa aka fara ƙiran sallan magrib, daidai nan habiba tazo inda muke, still fuskanta ɗauke da murmushi, gefe na ta zauna tana sake karɓan wayan hannu na, ban ja ba na miƙa mata, ƙasa-ƙasa take tambaya na waya saya mum? Murmushi nayi ina kallon inda ta buɗe, gallery nane wanda babu pic kowa sai na hafsy, sai kuma wannan babyn da aka haifa, sai kuma dukkan mu har da yayah mohd da babyn da maman babyn da mukayi yau da safe, bance mata waya saya mun ba sai murmushin da nayi, dai-dai wani photon da nayi riƙe da babyn a hannu na, lokacin na karkato da fuskan shi ya fito sosai, ƙurawa yaron tayi ido tana murmushi, chan ta ce, "sisto yaron nan kaman ke kika haife shi, kunyi kama sosai, Allah ya baki miji fari ku haifi irin wannan" ta faɗa tana ƙara zooming pic ɗin, nidai ban bata amsa ba sai murmushin kawai da na faɗaɗa shi, idon hafsy kaman zai faɗo ƙasa tsabar hararan da ta ke jefo mun, bai isheta ba ta ƙaraso inda muke ta miƙa hannu ta karɓi wayan a hannun habiba tana cewa, " Adda zamuyi photo da ƙawata" ko jiran amsa na batayi ba ta juya da wayan tayi ɗakin Aunty Bintu, nidai duk sai naji kunyan habiba, gashi su maryam sun wani nuna kaman ma basu san da ita a wurin ba, bai ishe su ba Ayshee tace su tashi suje suyi sallah suyi addu'a Allah ya rabasu da zuciyar cin amana, fatima kuma tana ƙarawa da kuma zuciyar son zuciya da ƙyashi da hassada, ita dai habiba bata ko kalle su ba idon ta kawai yana kan waya na, har sai da hafsy ma tazo tayi nata iskancin tukun ta ɗago idon ta danaga alaman kaman da hawaye, amma fuskan ta cike da murmushi ta dube ni, lokacin kuma mamie da raliya suka fito daga ɗakin mai jego, idon mamie akan mu amma kasan cewar Aunty bintu na bayan ta bata iya cewa komai ba sai harara da ta watsa mun, ƙasa-ƙasa tana hararan habiba, "tashi mutafi Addah, ko kuma sai an ɗaga ki amaryar Ali"? Raliya ta faɗa babu ko kunya a idon ta, tashi mukayi dukkan mu nida habiba muka tsaya, wani kallo mamie ta bini da shi na ƙasƙanci, a gadaran ce tace "ke kuma kin yafe school ne kika tattaro nan kika zauna? Ko aure za'a cire ki a miki tunda karatun yana takuraki?" ta faɗa tana mun wani banzan kallo, "mamie ae sai da white blood ake auren ko? Ae kawai kiyi shiru mamie mu wuce" raliya ta faɗa tana wani dariyan iya shege, daga ni har habiban kallo muka bita da shi, ganin haka Aunty Bintu ta dubeni tace, "Ayshaa maza jeki ɗakin yayan ku ki feshe shi da shelktox, ki rufe duka windows ɗin plz" ganin na samu sauƙin cin zarafin su akaina nayi sauri na amsa da tou na wuce ciki, bayan na amsa da tou, sannan nayiwa su mamie sallama, wanda ina gani bata amsa ba sai bina da harara da tayi

Washe gari na shiryah tun da safe na musu sallama na wuce gida sbd monday zan koma sch, duk da an koma tun last week.

Ranan saturday da safe wurin 11:00am na fito da coolern da ummie ta sakawa yayah Ahmad masan da tayi tun safe na kai mishi side ɗin su, a cikin kwando na haɗa komai na wuce side ɗin su, ina fitowa naga wata arnen mota ja a ƙofan su, a zuciyata nace ɗan gayun gidan mu ya chanja mota ne? Yaushe naji ummie na mishi faɗan yawan chanja mota da yakeyi, ina ƙara matsowa varander sai naga takalma kusan kala uku, a zuciya na nace tou hala ba motan shi bane, sallama nayi a bakin ƙofan, sau biyu nayi tukun aka amsa mun, yayah Ahmad ne ya amsa mun sannan ya bani izinin shigowa, buɗe ƙofan nayi na shigo ina ƙara wani sallaman, ban ƙarasa ƙarshe ba na yanke sallaman ya koma ciki, ido na ɗan zaro kaɗan...sai kuma nayi saurin maida nutsuwan jikina dai-dai, ganin ina shirin sake abun hannu na, "*AUNTY NICE* kin san suwa nagani a zaune?" kallonta nayi fuskana ɗauke da murmushi nace "a'a sai kin gaya mun hajjaju",

Wani fari da ido tayi fuskan ta ɗauke da murmushi da wani yangan ta da take burgeni da shi, "Fararen nan nagani zaune a parlon".

Ina ajiye basket ɗin na sunkuya har ƙasa na gaishe su, bansan dalili ba sai na ji muryah na yana rawa, amsa mun gaisuwan sukayi amma ɗayan wanda naga kaman yafi tsayi kuma bai kai ɗaya jiki ba, lpy kawai yace ya maida kanshi kan wayan shi, ɗayan kuma wanda naga alaman yana ɗan jiki kuma yana da yawan fara'a, shi ya amsa mun fuskan shi kuma a sake, har ma ya tambaye ni suna, bayan na gaya mishi ya sake tambaya na s.s nawa nake? Nagaya mishi ina A.T.B.U zamu shiga level 2 next semester, zaro ido yayi cike da zolaya yace, "ashe mun kusa mu fara tara surukai, ni na ɗauka baki gama secondry school ba, wancan zuwan naga kaman ku biyu ne kan ku ɗaya ko"? Ɗaga kaina nayi alaman haka ne, "tou ina ɗayar? Don naji Ahmad na ƙiranku twins, hakane?" nan ma murmushi nayi na sake ɗaga kaina alaman haka ne, dariya yayi mai ɗan sauti yace, "inaga kema irin yayan kine, magana yana baku wahala", "kai kuma babu abu mai sauƙi a wurinka irin magana" naji ɗayan farin ya faɗa, da sauri na ɗago ido na kalle shi, abun mamaki ko kallon mu baiyi ba yayi maganan, daga gefe kuwa yayah Ahmad yana murmushi yace, " Ayshaa idan kin shiga kicewa ummi su A.G zasu shigo su gaisheta idan mun gama", miƙewa nayi da sauri ina amsawa yayah da tou, shi kuma ɗaya mai yawan fara'an naji yana faɗin "haba Barrister muna ɗan labari kuma ka sallameta? Bayan nasan dukkan ku yanzu kowa zai rungumi waya yayi ta faman danne-danne ku bar ni shiru", "tashi kije ciki ki isar da saƙon ki, ki rabu da yayanki mai yawan maganan nan," naji muryan ɗayan farin ya faɗa, da sauri na ɗago dara-daran ido na nadube shi, cikin sa'a kuma shima idon shi na kaina, rikicewa naso yi wanda bansan dalili ba, da sauri nayi hanyan waje.

Wajajen shaɗaya da rabi naji muryan su yayah da abokanshi a parlon ummie suna gaisheta, haka nakasa kunne nake sauraron gaisuwan su, inda naji yayah yana ambatan A.G da kuma M.G, ƙasa-ƙasa nake jin muryan ɗayan wanda bansan ko shine A.G ɗin ko M.G ɗin ba yana mata godiyan masan da aka kai musu, daga baya naji muryan ɗaya mai yawan fara'an shima yana godiya, zasu fita naji muryan shi yana tambayan hafsy ni, sokuwa naji tana cewa kaman bacci nakeyi, naji kaman na garzayo da gudu nace gani, amma sai na daure na gayara kwanciya na, a zuciya nace maganin mai baccin ƙarya, ɗazu ina ji hafsy na ƙirana nayi likimo, basu fi minti biyar da fita ba naji muryan Yayah Ahmed a parlon, da sauri na dirƙo a gadon nayi parlon, fuskana a murtaƙe na nemi wuri kusa da shi na zauna, idon shi akaina yace, "fatan kina lafiya dai ko"? Ɗaga kai nayi alaman eh, "yau kina azumin magana ne? Har kin sa M.G ɗazu yana cewa halin mu ɗaya, saboda shi Allah yayi shi mai son hira, baya so yaji an zauna shiru, da badan A.G ya sallameki ba haka zai ta cika mutane da surutu", ya ƙarasa faɗa yana dariya, nima murmushi nayi nace, "su ɗin yɗan gida ɗaya ne yayah"?

"maƙota ne kawai, amma sun dawo yɗan'uwan juna, kuma sai akayi dace sunan iyayen su yazo ɗaya",

Ummi tace "gashi ni har kama ma suke mun, yanzu dama maƙwafta ne ba yɗangida ɗaya ba? Kasan kullum da kake bani labarin su tun kafin na gansu na ɗauka yɗan gida ɗaya ne", murmushi yayi yana ɗaukan ruwan da hafsy ta ajiye musu yana buɗe bottle ɗin, "wallahi ummi nima farkon haɗuwa na dasu na ɗauka yɗangida ɗaya ne, irin kowa da maman shin nan, kinsan a school of low muka haɗu da shi A.G ɗin, ummi bamu mintuna kaɗan zakiji ƙiran M.G ɗin yana tambayan lafiyan A.G ɗin, kin san A.G ɗin yana da athsmah, kuma lokacin kaman ya ɗan matsa mishi, duk hankalin M.G ɗin a tashe, daga baya A.G ɗin ya gaya mishi ya haɗu da wani ɗan bauchi kuma yana taimaka mishi wato ni, haka M.G ya matsa ya karɓi wayana, ƙira akai akai yaji yyh A.G yake, na ɗauka nima yayan shi ne, ashe maƙwaftah ne suka taso tare, don kinga M.G a gidan su A.G ma yake zama ɗakin shi a gidan shima aka mishi saboda abotakan su ya dawo....." bai ƙarasa ba muakji sallaman yayah umar, haushi naji na ɗan harare shi saboda ya yanke labarin da yayah Ahmad yake bamu don so nakeyi naji ƙarshen labarin, kuma sanin halin yayah Ahmed dama maganan ba damun shi tayi ba, irin haka kawai kake ɗan jin maganan shi, hakan ma sai idan akwai ummie ko Abbah ko yayah mohd a wurin, da gudu hafsy tayi wurin shi ta rungume shi tana mishi oyoyooo, dama ta hannun daman shi ne, hararah na yayi dole na tashi naje mishi oyoyoooo amma ya matsa gefe yana gwale ni, "sai da kika dama tukun kika wani kwaso tsumman ƙafan ki ko"? Tou bana so koma chan da munanan idon ki a wurin da ƙaton kai" dariya mai ɗan sauti hafsy tayi saboda daɗin an kushe ni, tsayawa nayi kaman zan mishi kuka baki na a zunɓure, juyawa nayi na kalli yayah Ahmad nace "ka ganshi ko yayah" Rungume ni

naji yayi yana dariya yana faɗin "wane ni na gwale ki wanda tafi kowa kusa dani a duniya, kin san fah da tare ummie zata haife mu ke kuma Allah yayi ki mai sanyin jiki, shiyasa na fole ki da ƙafa kikayi baya na iso duniyan, tsabar sakarci da son jiki sai da kika ɗauki tsawon shekaru kina jinya kafin kika zo duniyan", ya faɗa yana dariya, gaba ɗaya su ummie ma dariyan sukeyi, sannan ya ƙarasa wurin yayah Ahmad ya ɗan sunkuya ya rungume shi yana yayah na rabin jiki na, yayah Ahmad yana murmushi yace, "kun iso lpy corpers?" yayah umar yana dariya yace, "yaya munyi passing out mun dawo kenan", ya faɗa yana wucewa wurin Ummie itama sunkuyawa yayi ya kwanta akan cinyanta yana, "Ummie na my first love na dawo na sameki lafiya cikin kwanciyar hankali, raina yayi daɗi" ya faɗa kaman yana wani ƙara rungumeta, domin gaskiya yayah umar shi yana da maƙon iyaye da yan'uwa, don zan iya ce miki duk cikin mu yafi irin nuna damuwa da nashi, shidai barshi da masifa da zafin zuciyan shi, amma yana nuna ma kowa so.

Hafsy ne ta shiga kitchen ta haɗo mishi masa da kunun gyaɗan da ummie tayi, dama ummie ita bata abinci kaɗan takanyi wanda ko baƙo akayi babu batun jin kunya, babu daɗewa mamah ta shigo daidai nan yayah mohd ma ya shigo, haba gaba ɗaya sai aka kachema da hira, kowa kaman zai cinye ɗan'uwan shi don so, irin wayan nan lokacin idan muka haɗu sai dai kaga ummie fuskanta kaman gonan auduga, ta juya kan wannan ta juya kan wannan, "Allah sarki ummin mu, gaskiya *Aunty nice* Allah yayi mana kyauta mai daraja da ya bamu ummie a matsayin uwa, macece mai tsoron Allah, Allah sarki ummin mu".

Sun kuyar da kai Hajiya Ayshaa tayi ƙasa tana share hawayen da ya biyo kan kyakkyawar fuskanta,nidai sai naji duk jikina yayi sanyi, na tsura mata ido a zuciyana nace, Allah yasa dai ummin nata na da rai, don ni nasan zafin mutuwar iyaye, uwa ko uba duk wanda ka rasa sai kaji kaman baka da sauran komai a cikin duniya.

Ɗagowa tayi ta dubeni tana share hawayen ta, amma fuskanta cike da murmushi, nima murmushi na mayar mata, bayan ta gama goge fuskan ta ta ɗago ta kalle ni sannan ta cigaba da bani labarin ta.

A irin wannan lokacin mamah takan zauna a side ɗin ummie, abun da na lura daɗi takeji idan ta ganmu dukkan mu a hallare, kuma sai kiga kowa a cikin mu yana nan-nan da ita, domin babu laifi mamah tana da zuciya mai kyau, kuma idan za'a wuni itama ranan ko abinci bata ɗaurawa anan take zama, saidai idan itace da girki zata tashi zuwa wani lokacin, sallan azahar da akayi ma zuwa sukayi sukayi sallan sannan suka dawo nan parlor, basu suka bar gidan ba sai bayan la'asar lokacin kowa yaci abinci sannan suka watse, ana sallan ishaa sai ga yayah umar da yayah ishaq aminin shi sun shigo, bayan sun gaida ummie basu wani zauna ba suka wuce chan side ɗin aminiyar su hajiya ummah, nan kuma hafsy ta bisu, domin na hannun damanta yayah ishaq yazo.

Washegari haka nayita kasa kunne naji yayah Ahmad yayi maganan su A.G amma shiru, nayita zura ido ko zanga sunzo, amma shiru babu ko gilmawar motan su, haka da yammah na wuce gidan su maryam, ina shiga ta taso da ihu ta rungume ni, maryam duk duniya idan kika cire habiba tou babu wanda yasan sirri na kuma nake iya gaya mata komai a rayuwata sai ita, ita jamilah abun da na lura wani irin so na Allah ya saka mata a zuciyarta, don gaskiya sun zaune sit ɗaya ne da habiba, amma don ta ita bataƙi dani take tare ba, don ni komai nayi dai-dai ne a wurinta, don har tsokanan ta sukeyi wataran wai mayyar Ayshaa, kuma bata gajjiya da kallo na, idan na kamata tana kallo na sai tayi murmushi tace, "Ayshaa duk duniya babu mai irin kyaunki, don ni da madkhuri kike mun kama, kyaunki yana da kyau sosai", nidai murmushi kawai nakeyi idan ta faɗa, lokacin zakiga habiba da maryam sun hayayyaƙo mata, ita maryam abunda na lura ita kuma son da take mun bata so taga wani yana mun irin wannan son, don kullum cewa takeyi Ayshaa nata ne, ita kawai kishina takeyi don ko habiba ne ta cika shige mun haushi maryam takeji, ita ko tafiya akeyi tafi so ta tsaya ta gefe ne, gaskiya *Aunty nice* bana gane wacece tafi sona a cikin maryam da jamila, amma nidai har ga Allah nafi son maryam, mun taso tare kuma muma maƙwaftaka, gashi ni ganinta nakeyi kaman yar gidan mu ita, ɗakin maryam muka wuce muka zauna, hannu nasaka nayi tagumi na zura mata ido, dariya ta kwashe da shi tace, "duk wannan tagumin na rashin jin ƙarshen su farare ne?" tsaki naja nace, "matsalata da ke idan ana magana mai muhimmanci ke ba'a nan kike ba", dariya ta sheƙe da shi tace, "tou ke yanzu wannene naki?"

Hararanta nayi nace "nawa kuma? Son su ma kenan nakeyi? Bakiji nace miki ni kawai kyau suka mun ba, amma yayah ma za'ayi ina mace na so su"?

Dariya maryam ta kwashe da shi da shi tace, "sokuwa tou ni nace miki son su kikeyii? Kawai dole akwai wanda yafi burge ki a cikin su shine nufi nah",

Ajiyan zuciya na sauƙe mai girman gaske nace "ni duk burgeni sukeyi, don dukkan su farare ne, kuma kyaunsu duka mai kyau ne, amma ɗaya baida magana ɗaya kuma yana da magana, kuma fara'ar fuskan shi tana burgeni", na faɗa idona akanta, shewa tayi tace tanaga mai fara'an ne zai zamu na hannun dama na, saboda ni shiru shi magana, abun zaifi, don idan na haɗu da mai shiru irina abun ba zaiyi armashi ba,

"me kike nufi ne maryam? Kina ɗauka ni ina son su ne?"

Kama baki tayi tace, "na isa nace ke kina son su? Ae babu so a wannan al'amarin kawai burgewa ne, nima har naji ina son ganin su, suna zuwa ki zabga mun ƙira", ta faɗa tana wani dariyar shaƙiyan ci, nidai tsaki nayi na miƙe don tafiya gida.

Kullum zuba ido nake naga farare sun zo gidan mu idan Yayah Ahmad yazo amma shiru kakeji, a haka aka kawo kayan auren habiba, domin Abba yace december tare da na yaya Ahmad za'ayi, saboda haka ita mamie tana ta shirye-shiryen ta da yan uwanta, don ta ɗaga hankali wa Abba dayace suje su sayi kayi kaya ita da mamah da ummin, amma fir taƙi yadda, shima ya dage bazataje ita ɗaya ba, sai da Aunty Rakiya ta saka baki tukun Abba ya bar mata, amma duk da haka komai na kayan ɗaki da parlor da su electronic Abba ya bawa Aunty Rakiya ta mishi, kayan kitchen da su kayan zaƙi kawai Abba ya bar wa mamie, koda yake Yayah mohd ne ya sayi set na gado duka biyun, da set na kujeru, yayah Ahmad Abba yace ya haƙura yayi hidiman haɗa kayan nashi auren, amma duk da haka sai da ya sayi deepfreazer, T.V da gascooker, Aunty Rakiya kuma ta sayi cottons na gidan gaba ɗaya, Abba dai kayan kitchen da tarkacen kayan zaƙi ya bayan don ko gara Aunty asma'u ne tace a bari zata aiko, bawai don ƙarfin Abba ya gaza bane, no kawai zumunci da ake da shi ne da kuma ƙoƙarin Abba wa kowa a zuriyan.

Aunty nice zakiyi mamaki idan nace miki jammy taƙi yadda suyi magana da habiba? Duk yadda habiba taso irin su haɗa kai da jammy abun ya gagara, nima maryam ke bani labarin abun da yake faruwa, ashe haɗa kayan ma mummy ne ta haɗo shiyasa mukayi mamakin ganin kayan, don a matsayin gidan su ba haka mukayi zaton gani ba, sai bakin mamie ya rufu ruff, baka jin wannan rawan kan, sai dai gori da zagin wata bata da farin jini wato ni, wlh ko ajikina, nidai damuwa na yadda habiba taƙi yadda mu tsaran yadda bikin zai tafi, don na rutsata a side ɗin hajiya ummah duk yadda naso ta bani haɗin kai mu maida komai ba komai ba, amma taƙi, sai wani nonnoƙewa ta keyi, ganin bazata bani haɗin kai ba sai na rabu da ita, don ko magana na mata bazata amsa mun yadda ya kamata ba, sai dai tayi murmushi tayi shiru, zuwa wani lokaci kuma sai ta fara share hawaye, ganin haka sai na fara rabuwa da ita, sai dai ina jinta suna waya da yan'uwanta na wurin mamin ta, kuma ina jin yadda suke magana akan hidiman bikin, a lokacin naji wai har sun fitar da ashobe.

Washe gari aka kai kayan auren yaya Ahmad, maryam ta shigo gidan mu bayan mun dawo akaiwan, gidan su yarinyar gidan tantsan yan boko ne, domin itama yar bokon ne, babu ƙaryah yan gidansu sun haɗu, hira muka ɓarke ni da maryam, anan ta keta bani labarin yadda mummy take nuna bata son auren Aliyu da habiba, kuma ko a gaban kowa tana kushe auren, jamilah ma ko maganan auren bata son a mata hiran, "chan ta matse musu", na faɗa ina tura baki gaba, a nan na bata labarin yadda mukayi da habiba, zagina maryam ta fara kaman ita ta haifeni, wai bani da zuciya tun da anguje ni da abu na haƙura mana, tagumi nayi na ƙura mata ido har taga ma ban baminta sannan nace, "besty bazaki gane bane, idan na ƙi shiga cikin hidimanta za'ace ko ina kishi ne ko ina mata baƙin cikin samun miji don ni ban samu ba",

Harara na maryam tayi sannan ta ɗaura da tambayan, "dama ita ta samo mijin ko ke kika sama mata, nike meyasa halinki na sokaye ne kam besty? Tou a hirr ɗinki na ganki cikin hidimanta, idan ita tayi niyyah ta nemeki fine, idan bata nemeki ba mu cigaba da hidiman na Yaya Ahmad", muna cikin hiran hafsy ta shigo tana wani ƙyalƙyala dariyan mugunta, har ƙasa ta tsugunawa tana tashi, kallo muka bita da shi, maryam na tambayanta meyake faruwa? Sai da tagama dariyan tukun ta bamu labarin dambatuwan da akeyi acikin gida yanxu, ashe mamie ne ta ɗagawa Abba hankali akan kayan yayah Ahmad, wai wannan kayan ba kuɗin yayah Ahmad bane ya haɗa kayan, dole Abbah ya dafa mishi, tunda hakane kuma dole ya bayar ta sake haɗawa habiba kaya, don na habiba basu da wani quality, shi kuma Abba yace mata bata isa ba, shidai yayi niyyan haɗa mata akwati ɗaya na kayan fitan biki yadda yayiwa Adda lokacin aurenta, daga nan ya ƙira Aunty Rakiya ya gaya mata yadda sukayi,shine fah Aunty Rakiya tazo ta sameta ta watseta, ke kam mamie sai kuka wai ana mata baƙin ciki don anga habiba ta samu miji ke baki samu ba, Aunty Rakiya ta zage ta tas tace wani mijin da sukayi ƙwace? Da ƙyar ummie taje ta kashe maganan, nidai banda dariya babu abinda nakeyi, Adda idan kukaga idon raliya dole kuyi dariya, hafsy ta sake tuntsurewa da dariya maryam na tayata, ni dai banji dariya ba sai wani abu daya tokare ni a zuciyata, wai ni nawa nake nema da mamie ke goranta mun rashin aure? Yaushe ma habiban tayi da za'a fara goranta mun?

Babu wuya wurin ubangiji, cikin satin nan aka fara hidiman auren su Yayah Ahmad da na habiba, gidan mu ya cika da dangin ummie da mamie, sannan kuma ga dangin Abban mu da suka zo, side ɗin su yayah Ahmad ma cike yake da friends ɗinsu, domin yayah umar ya kwashe nashi ya nashi sun koma gidan Aunty Rakiya shida yayah ishaq, sai suka mayar da gidan kaman majalisan angwaye, babu abun da kike gani sai shigan motoci da fitar su, gashi ummie tana wadata su da lafiyayyun abinci da kayan shaye-shaye kala da kala, hankali kwance suke hidiman su, yau ne gidan su amaryan suke liyafa thursday, habiba kuma kaman gobe friday naji hafsy tace za'ayi nata liyafan a farfajiyar gidan mu, wanda ita kuma zatayi ƙauyawa a gidan wan mamanta da yake gida dubu, kuma har lokacin bata ce mana komai ba, duk da ummie tace naje na shiga cikin ƙawayenta ko bazata kula ni ba, amma firr maman su maryam tace haka bazai faru ba, idan wani abu ya faru cewa za'ayi daga garemu ne, magani shi kawai kar a fara.

Wuraren 5:00pm mun gama shiryawan mu tsaf cikin wani arnen lace da yayah mohd ya ɗinka mana mu uku har da raliya, kowa da kalan nata amma zanen su ɗaya, nawa purple anyi mun gown mai lafiyan kyau, gaban an jera bakin lace ɗin tunda ga sama har ƙasa an kuma shiryashi da adon stones masu hasken gaske,

dama tun wurin azahar muka dawo daga gidan lalle, dayake Allah ya mana baiwar hasken fata zokiga yadda lallen yayi mana kyaun gaske, ranan laraba yayah umar suka kaimu saloon aka mana gyaran kai har da maryam da ummitah sister ta, yau kuma suka kaimu gidan lalle, nidai mamakin yayah ishaq nakeyi yadda yake ta wani kaffah-kaffah da hafsy, lace ɗin hafsy Red ne, don ita mayyar red abu ne, ita kuma raliya green, amma ban san ko yau zata saka nata ba, don ita ma ɗauke mana wuta tayi, garama mutumiyarta hafsy idan sun haɗu sukan ɗan taɓa hali, kuma dai su basu daina kula juna ba, saidai suyi faɗan kuma suyi hiransu, don komai sai ta bawa hafsy labari, amma yanzu sai naga wani ƙawance na musamman ya shiga tsakanin hafsy da ummitah ƙanwar maryam, don da tsabar kowa danata halin masifan basu zama inuwa ɗaya, daga baya ma tun suna primary ummitah ta koma lagos hannun sister mamansu data girma a gidan, tana aure ta tafi da ummitah sai ta bar anguwan mu, yanzu kuma Auntyn su sun koma spain da mijinta sai maman su tace ummitah ta dawo saboda bata son girman ta achan, tou sai suka ƙulle da hafsy kuma abun ya mun daɗi, saboda ummitah yʻar gayun gaske ne, wanda na lura yanzu hafsy ma tafara koyi da ita, muna shiryawa nida fatiman Aunty Bintu da maryam a side ɗin hjy ummah fatima sai kwashewa da dariyan mu takeyi, nima dai dariyan na fara ina cewa, "wallahi fatima ni a sokanci na ae da binsu zanyi goɗai-goɗai, da badan Aunty Bintu ta tunatar da mu ba ae sokayen yayu za'ayi masu bin ƙanne da masoyan su", dariya dukkan mu uku muka kwashe da shi.

"*Aunty nice* nifah ban lura akwai wata alaman ƙwollaliya ba tsakanin yayah ishaq da hafsy, yayah umar da ummitah ba, sai da Aunty Bintu tace idan mun shiryah sai mutafi wurin event ɗin tare, ta taho da motan ta, aiko nace mata dasu yayah umar zamu tafi, nan take zayyana mana abun da ta lura yake tsakanin su, tana dariya tace ko wasu irin yayun kawai ne zaku na bin yara goɗai- goɗai da masoyan su"? Dukkan mu dariya mukayi, wato sun raina mana hankali mune yʻan rakiya ko?

Mun fito haraban gidan mu uku muna jiran fitowan Aunty Bintu da ta tsaya suna magana da ummi, hannu na riƙe da Areefh wanda yayi wayo don ya kusa 4month koma ya cika yayi ɓul-ɓul, kaman nin shi da yayah mohd da yayah Ahmad dani ya fito sosai, wani ma idan bai san Baban shi ba zai ce nina haife shi, Allah sarki gashi har irin haƙurin mu ya ɗauko, muna tsaye jikin motan muna jiran Aunty Bintu sai ga su Yayah Ahmad da abokan shi sun fito a side ɗin shi suna wucewa wurin motocin su, muryan yayah Ahmad naji ya ƙirani, juyawan da zanyi kawai sai nayi ido biyu da fararen nan sun sha wani milk colour ɗin filtex, da sauri na ƙarasa wurin yaya Ahmad da yake tsaye yana ɗaura agogon shi, miƙo hannu yayi ya karɓi Areefh yana tambaya na dawa zamu je wurin event ɗin, yana tambayan idon shi yana kan Areefh, murya ƙasa-ƙasa kaman bana so wani yaji nace mishi, "da Aunty bintu zamu tafi" miƙo hannu yayi ya karɓi handbag ɗina, hannu yasaka a aljihun shi ya ciro kuɗi bunch guda yʻan 100 ya saka mun a ciki, idon shi akaina yace "wannan na liƙi ne, ina hafsy kuma"? Ya tamabaya yana duba cikin compound ɗin gida, a hankal nace "sun fita tare dasu yayah umar" sannan na mishi godiya sosai, kawai sai ganin M.G

ya matso kusa da mu fuskan shi da murmushi ya miƙa hannu ya karɓi Areefh, idon shi akaina yace, "ƙanwar mu mai kyau wannan babyn kaman ki da shi yayi yawa, ba lallai ki haifi ɗa mai kama da shi ba gaskiya, ɗan wurin Yayan mohd ne"? Ya tambaya gaba ɗaya hankalinshi yana kan Areefh, gaishe shi nayi fuskana cike da murmushi, lokacin Aunty Bintu ta fito, ganin ta fito na ƙara yiwa yayah Ahmad na miƙa hannu zan karɓi Areefh yaro kawai ya wani juya yaƙi zuwa, kuma ban taɓa ganin yayi ƙiwuya ba, dariya M.G yayi yace, "kai yaron nan ya burgeni, kinga shima baya so ki tafi M.G ya daina ganin lallen ki mai kyau ɗin nan," kunya maganan shi ta sakani nayi saurin ɗan yin baya kaɗan ina ɓoye hannu ni fuskana ɗauke da murmushi,

"don Allah kazo muje mana kana ɓata wa mutane lokaci fah", muryan A.G naji yana yiwa M.G magana, ɗago kai nayi da sauri na sauƙe akan shi, shima kuma alokacin gaba ɗaya idon shi yana kaina, saidai babu fara'a ko kaɗan akan fuskan shi, da sauri na juya fuskana na mayar kan M.G da yake miƙo mun Areefh murya ƙasa-ƙasa yace, "karɓi yaron kafin wannan masifaffen yayi yaga-yaga da ni", ina karɓan Areefh ya ɗaura mun wani bounch ɗin yan 100 ɗin akan Areefh ɗin, yana cewa "wannan ki ƙara na liƙin ko",

Da sauri nace, "a'a don Allah ka bari yaya Ahmad ya bani".

Cikin tsawa-tsawa kaɗan A.G ya sake cewa, "shi Ahmad ɗin ne yace miki mu ba yayunki bane? Ko kuma idan mun baki abu kada ki karɓa"? Murmushi M.G yayi ya juya suka tafi bai sake cewa komai ba, nima juyawa nayi wurin su Aunty Bintu don mu wuce.

Haɗuwa iya haɗuwa wurin programm ɗin Aunty Jeedah yayi kyau, don komai akace da yan boko babu bakin magana, hidima iya hidima anyi shi, gayu iya gayu mun ganshi, Aunty jeedah yar'gayu ce mai amsa sunan gayu na na'am, kuma ita ma babu laifi kyakkyawace ajin farko, amma dai bata kai Aunty Bintu ba, sai dai ta nunawa Aunty bintu gayu, duk da Aunty bintu babu wasa, sai dai ita Aunty jeeddah irin first class yan gayun nan ne, nidai farin ciki nakeji ganin matan yayu na duk babu na zubarwa, a zuciyana addu'a nake Allah yasa itama ta zama mai kirki irin Aunty bintu, domin Aunty bintu irin matan nan ne da samun su a cikin al'ummah sai an sha wahala, zuciyarta mai kyau ne, gashi suna zaune lpy da yayah mohd.

Muryan DJ ne ya karaɗe wurin da neman dangin ango, haka muka taso da yan'uwan ummie, Abbah da mu yan gidan mu muka shiga filli, Aunty bintu

Aunty Rakiya, Adda, Aunty asma'u, da wata yar ƙanwar maman mu Aunty halima suka taso a manya suka fara mana liƙin kuɗi na gasken gaske, kowa ka gani kwance bounch kawai takeyi tana liƙi, ganin hafsy nayi tana liƙi da yan 100 ɗinta, sai lokacin na tuna danawa, haka muka shiga liƙawa juna cike da farin ciki, daga nan kowa taje ta zauna.

Bayan ƙawayen amarya sun chashe sai DJ ya sake fito da amaryah tsakiyan fili, gayyatan yʻan'uwan ango yayi fili ds muzu mu fanshi amaryan mu, nan ma amaryah taga ruwan liƙi da muka fito muka mata, nidai ban ankara ba sai dana ƙarar da kuɗin jakana, kuma da na barshi hadda na wurin dinner na ajiye, saboda naji Ali jita zaizo, duk ɗaga idon da zanyi sai mun haɗa ido da amaryan mu, muna haɗa ido take aiko mun da murmushi, nima sai na mayar mata, Aunty Bintu na riƙe da hannunta suna rawa, Aunty Rakiya sai liƙa musu kuɗi sukeyi, gaskiya luyafan ya mun daɗi, sai bayan ishaa muka bar wurin, mun dawo gida bamu daɗe ba Aunty bintu ta kwashe mu duka har dasu ummitah da maryam mukayi gidan ta, dole sai driver ne ya ɗauko wasu, saboda akwai yʻan mata biyu da suka ƙaru ɗaya yʻar gidan Goggo ce ƙanwar ummi wato zainab, sai kuma hadiza yʻar ƙanin baban mu ne daga tafawa ɓalewa tazo, hadiza tana B.U.K tana karanta Accounting, itama yʻar gayu ne sosai, ga rawan kai, amma kuma tana da kirki da son zumunci, idan munje garinmu a ɗakin mamanta muke sauƙa, zainab kuma yʻar Goggo tana kashere, chan Gombe state, zainab bata cika son mutane ba kuma bata cika yawan magana ba, so ita zaiyi wuya ma ka ganta cikin mutane saidai irin haka ya faru kaman lokacin biki, gara ma yayarta Nanah mai sunan ummin mu, ita tana da son mutane sosai, yanzu ma bata da lafiya ne da nasan komai da ita za'ayi.

Gidan Yayah mohd flat uku ne dama a ciki yanzu an gyara na yayah Ahmad inda za'a saka amaryar shi, duk da Abujah zasu zauna amma nan za'a kawota, kai mutanen nan sun wuce reni, nan gidan ma sun jere mata shi, haka gidan dayake Abujan ma an jere shi, gidan dayake farkon shigowa shine aka barwa Yayah umar, na tsakiya kuma yayah mohd, wanda yake ƙarshe shine na yayah Ahmad, mun shigo bamu daɗe ba yayah Ahmad da yayah mohd suka shigo gidan, a parlor suka zauna suna hira, Aunty bintu macece mai himman gaske, gata da iya kula da miji, abun ya ban mamaki da naga ashe sai da tayi abinci tukun ta fita, haka ta haɗa abincin ta saka hafsy da ummita suka wuce da shi dinning wasu yayah, gidan kana shiga parlorn yayah ne da dinning section sai ɗakin shi toilet a ciki, sai kuma guest room a parlon shima haɗe da toilet, sai kabi wani ɗan corido da zai shigar da kai wani ɗan madaidaicin parlor mai ɗauke da ɗakuna biyu, shima ko wanne da toilet a ciki, shine side ɗin Aunty bintu, kuma ko wani side haka yake, gidan babu laifi yayi kyau sosai,ballantana da tasamu kayan kece raini.

Parlon muka shigo dukkan mu muka gaishe su, Yayah mohd na zolayan hadiza akan sunyi waya da bappanmu wai yayi mata cikiyan miji a birni ta bar ƙauye, da yake bakinta baya shiru haka ta dinga maida mishi amsan da ae shi tazaɓa, saboda haka ya bawa bappah amsan ta samu wuri, idan kuma bashi iyawa ga yayah Ahmad, shidai yayah Ahmad murmushi kawai yakeyi, haka tayi ta zolayan su shida yayah Ahmad, amma yayah mohd kaɗai ke maida mata amsa Aunty bintu na taya shi, yayah Ahmad dai sai murmushi yake yi baya iya cewa komai, ko ta tsokano shi sai dai yace ta jira Jeeddah shi tafi ƙarfin shi, zainab dai sai kallo ta ke binsu da shi kaman ba abokan wasanta ba, bayan sun gama chakalan junan su sai suka koma

ciki, Aunty bintu kawai aka bari a wurin sai ni da naje kusa da yayah mohd na zauna, hannun shi na riƙo ina dariya, shima dariyan ya fara yana, "akwai abunda bestyn yayah moh takeda buƙata kenan, dariya na sakeyi ina ƙara riƙo hannun shi, "yayah duk duniya kaida ummie kuna saurin ganoni, narasa sanin dalili", na faɗa ina dariya, Aunty bintu ne ta bani amsa itama tana dariyan mu, "saboda duk duniya sun fi kowa sonki, shiyasa kowani language naki suke ganewa", ɗago ido yayah Ahmaƈ yayi yana dubanta, kaman baxai buƌe baki ba, amma sai naga kaman bashi ba yace, "banda son kai matar yayah, nasu ne ya bayyana, amma ni son da nakeyiwa Ayshaa sai inaga kaman yafi son da uwa takeyiwa ɗanta, saboda ko jeeddah ta gane, idan nayi fushi tou hiran Ayshaa take mun na sauƙo, duk abunda yake saka ni farin ciki kawai na ganta tana annashuwa", ya faɗa yana maida kallon shi kaina, da sauri na sake hannun yayah mohd na koma jikin yayah Ahmad na kwantar da kaina a kafaɗan shi, a hankali nace yayah Ahmad baka taɓa gaya mun ba, sai dai abunda kullum nake tunani a raina shin acikin ku ni waya fi nuna mun so da kulawa ne? Sai na ga kowa yana sona, kaga yayah mohd na shaƙu da shi kuma bana iya ɓoye mishi komai na, kuma sai inaga shine yake bani solution na kowani abu da ya sha mun kai, kuma yana son farin cikina, kai kuma Yayah Ahmad kasan me nakeji akanka?" girgiza kai yayi alaman bai sani ba, riƙo hannun shi nayi nace, "duka rauni na yana kanka, haka kawai zuciyata take jin tausayinka ko shiru kayi sai na dinga jin babu daɗi, kuma duk ranan da kazo sai naji tou gidan ya cika, duk abun da yayi giɓi a gidan ya cika,"

"ni kuma duk wanda naga zai tayar miki hankali ko zai taɓaki sai na rushe duniyar shi gaba ɗaya, duk wanda ya taɓa mun ke zan tada ƙaramar yaƙin ƙare dangin shi duka", yayah umar ya faɗa yana shigowa cikin parlon shida hussainin shi yayah ishaq, dariya dukkan mu parlon muka kwashe da shi, da gudu naje na rungume shi ina dariya, "yayah umar nasan kana sona, ni ma ina sonka, amma kai kana mun tsawa wataran har sai nace kodai ba yayah umar ɗina bane" dariya yayi yana riƙe dani muka zauna, " bazaki gane bane Ayshaata, ina miki faɗa wataran don wancan autar ummi marar jin maganan, laifinta ne yawanci yake shafanta, amma daga Abba, Ummi, yayah mohd, yayah Ahmad, fitinanniyar ɗakin mu, duk babu wanda yakaini sonki", ya faɗa yana duban yayah ishaq da yake binshi da harara, shi kuma yayah umar yana mishi dariyar mugunta.

Shigowar hafsy da zunɓurarren baki a gaba ya sake bawa kowa dake parlon dariya, gefen Aunty bintu taje ta rakuɓe tana turo baki gaba tace, "Adda duk wannan son da suke faɗa miki suna miki duk abakine, ni nawa bazai faƌuba, ni nawa da nake miki baxai misaltu ba, har abada har gaban abadah baxan so abu kwatankwacin irin kiba a duniya, ni ko ummi da Abba bana jin ina da kusanci dasu sama da ke, ko yayan da zan haifa suyi haƙuri su biyo bayanki Adda, ballantana kuma miji, sorry ɗinshi" ta ƙarasa tana hararan yayah ishaq, murmushi yayi ya sunkuyar da kanshi ƙasa yana danne-danne a jikin wayan shi.

Gaba ɗaya hira muka kachame da shi, kaman ba jiran yayah Ahmad abokanshi sukeyi ba, sai da yaga wayan su yayi yawa tukun ya mana sallama ya tashi zaifita,

lokacinne yayah mohd yake tambaya na meye nake so? "kuɗin liƙi yayah zaka ƙara mun, nawa duk na ƙarar a wurin event ɗin yau, gashi akwai dinner".

Ɗan dawowa da baya yayah Ahmad yayi yace, "ki bar yayah moha, goben kituna mun na baki ko", godiya nafara mishi bai saurare ni ba yayi waje, harara na hafsy tayi," wallahi Adda duk kuɗin da aka baki sai mun raba, wannan ae wayo ne, sai ki lallaɓa kowa komai sai ke, tou ni ɗin da babu mai sona sai an bani", dariyar ta kowa yakeyi, Aunty bintu tace kada kiji komai ke baga ishaq ba ae kece favourite sister shi, kema kina da wanda ya damu dake over, kuma gani nan nima ke nafi so",

Turo baki hafsy ra sakeyi tace, "haba Aunty bintu nafasan gaskiya, Adda kema kika fi so, ina jinki fa ranan kikace Adda duk tafi mu kyau saboda tana kama da mijinki, wai har baki gajjiya da kallonta, wato nice mummunar wanda ake gajjiya da kallona? Daɗinta ma da Abba da Aunty Rakiya nake kama, kuma ina isar musu da saƙo za'a samu matsala da kowa, ni yanzu bandamu da ku soni ba bari na jira zuwan matar yayah Ahmad, naga ko ni zata kama? Idan kuma takama mai ƙwala-ƙwalan idon nan sai najira ta yayah umar da haƙuri, don ita kam nasan nice overoll" ta faɗa tana kallon yayah umar tana dariyan shaƙiyanci, dariya dukkan mu mukeyi, shidai yayah ishaq hararanta yake tayi, wanda narasa na menene, "

Haka mukai ta hira har saida yayah mohd ya bar parlon, yana tafiya Aunty bintu ta wuce kitchen, kallo na yayah ishaq yayi yace, "tou ae sai ki tashi ki koma ciki mai masoya da yawa, amma nidai ki sani favourite ɗina hafsy ce, duk da ma yanzu ta gama yaɓa mini baƙaƙen magana, wai nine na ƙarshe acikin wanda zata so, hala har da wannan ƙaton banzan yayantan", ya faɗa yana kai naushi wa yayah umar, nidai banbi takansu ba saboda nagane inda zance ya dosa, kawai miƙewa nayi nayi hanyan ɗakin Aunty bintu, ina kusa da shiga naji yayah umar yana yɗar'uwa ki turo mun ummitah plz, mirmushi kawai nayi na wuce ciki, babu daɗewa kowa ummitah ta fito parlon, kafin nan kuma yayah umar ya koma kan dinning yana jiranta, ina shiga ɗakin na kalli su maryam nace, "gara fah muma muyi takanmu mu samu abokanan rayuwa, don idan muka zauna ta boko tou zamu raka ummitah da hafsy ɗakin aure".

Wani fari da ido hadiza tayi tana wani juya jiki tace, "ke kenan da kika zauna zaman jira, ni dai akwai wani ɗan unguwan mu suraj, yana aiki yanzu da NNPC, shima yace mun yasan Yayah mohd suna tare a lagos amma yayah seniour shine, tou nidai zanyi wuff da shi, don insha Allah shekaran nan da zamu shiga zasu zo suyi gaisuwa", ta faɗa tana wani jujjuya jiki tana saka kayan baccin ta, kallonta kawai nayi ina dariya, na juya kan zainab nace yɗar'uwa kefa?

Harara ta mun tace, "sai kin samo na karɓa irin na habiba," dariya muka kwashe da shi, na juyawa wurin fatima nace,"kefa sis",

Itama dariyan tayi tace, "ni yanzu akwai wanda ya mun magana, amma baya ƙasan yana masters a London, yayan ƙawata ce, sunan shi kabir ɗan maiduguri ne shuwa ne shima, sai kumun addu'a Allah ya dawo da shi lpy," tafi dukkan mukayi muna

mata guɗa, kallon maryam nayi nace "besty yyh ke kuma ina muka dosa"? Murmushi tayi tace nidai besty gamu nan muna addu'a, ina ga wannan lokacin sai mundage kada yaran nan su bamu kunya, don naga har yʼan aika muka zama musu, ni ae bansan yayah umar me yake tafiya ba, jiya fah aikana yayi na ƙirata", dariya muka kwashe da shi nace nima baka shi yanzu ya aiko ni ba, kawai besty muma mu dage mu samu wanda zamuyi wuff da shi.

Muna gamawa muka fara tsara yadda zamu kwanta, nan ɗakin Aunty bintu akwai wani lazychair a ciki, kai na hau na kwanta, gadon kuma hadiza, maryam da zainab zasu kwanta, ɗayan ɗakin da yake gefe inda fatima suke sauƙa tace zasu kwanta ita da hafsy da ummitah, haka mukayi sallama kowa ta kama wurin kwanciyarta, ina rufe ido sai tunanin fararen nan ya faɗo mun a zuciyata, da sauri na buɗe ido na, ganin an kashe wuta sai na mayar da idon na rufe.

Washegari muna tashi muka raba kan mu, wasu sukahau gyaran gidan, wasu suka fara haɗa abun karyawa, muna gamawa kowa ta shiga wanka, wajajen ƙarfe 12:00pm muna shirin fita zuwa chan gida, a haraban gidan muna tsaye muna jiran fitowan Aunty bintu sai ga motan yayah Ahmad ta kunno kai, yana fitowa lokacin Aunty bintu ma tafito daga nata gidan, "yauwa Alhmdllh ga ango ma ya shigo sai ya rage wasu tunda har yanzu drivern bai zo ba", Aunty bintu ta faɗa tana gyara yafan gyalenta, yana fitowa ɗayan side ɗin ma aka buɗe sai ga M.G ya fito shima, yana rufe motan kowa ya ƙaraso inda muke, gaida Aunty bintu yayi tana tsokanan shi da ango kasha ƙamshi, shidai murmushi kawai yake bai bata amsa ba, sai hannu da ya miƙa ya amshi Areefh da yake hannun hafsy, wasa ya mishi yana ta ɓangala mishi dariya, sannan ya miƙawa hafsy yaron, mu kuma muka shiga gaishesu shida M.G, gaba ɗaya idon M.G yana kaina fuskan shi ɗauke da murmushi, Aunty bintu ta tambayi yayah Ahmad akan daga nan gida zai wuce? Ya amsa mata da ehh, yanzu ma yazo duba ac da aka chanja na ɗakin shine, yana so yaga ko sunyi yadda yake so, "tou shikenan bari mu baka mutum uku, dama driver muke jira, naga kuma ya ɓata mana lokaci tun ɗazu yake cewa zai fito ya kai aika ne," riƙo hannu na yayi muka fara tafiya chan side ɗinshin, yana amsawa Aunty Bintu da babu komai sai a bar mutum uku, bari ya duba ya fito,

Aunty b tace "tou maryam da hadiza kujira Aysha sai ku taho ku uku, fatima, zainab, hafsy, ummitah ku kuma ku shiga mutafi, uku a baya ɗaya a gaba,"

Ɗaga muryah hafsy tayi da ƙarfi tana "wlh yaya duk abunda ka bata nima sai an bani, don na lura da wayon da ake mun, kai da yayah mohd kowa ya samo sai ya yafito ta, yayah umar ne kawai mai tunawa da ni", tana gama faɗa ta wuce gaban motan da sauri don taga zainab tayi gaban zata shiga, anan ma sai da suka yi ɗan hali da zainab, tace dole hafsy ta koma baya ae itace babbah, amma firr hafsy taƙi fita, tana cewa ae ita tana riƙe da yaro a hannunta, ganin Aunty B bazatace komai

ba yasa zainab shiga gaban ta wani ɗaure fuska kaman....., ita dai fatima dariya takeyi ƙasa-ƙasa, gefe ɗaya maryam da hadiza suka koma suna jiran mu fito.

Muna shiga side ɗin yayah Ahmad na wangale baki, domin suna gama jeren babu wanda yazo a cikin mu, Aunty ma'u ne ma naji suna hiran haɗuwa da tsaruwan gidan, haka yayah Ahmad ya zaga dani ko ina na cikin gida, "kai gidan nan yayi kya yayah, gashi kuma ba'a nan zaku zauna ba, ae da Abujan aka kai kayan nan", na faɗa hannu na riƙe cikin nashi muna fitowa daga kitchen ɗin, dariya yayi mai ɗan sauti yace, "shatu na ae kayan da suka saka a abujan yafi wannan tsari da haɗuwa, nan kawai sunfi zuba kaya mai yawa ne, chan kuma 2bed room ne 1 parlor, amma chan ae yafi kyau, komai white aka saka achan, ɗayan ɗakin ne ma suka saka Brown bed, amma parlor da nawa room ɗin komai white ne," yayah nikan gidan nan ya mun kyau irin sosai ɗinnan, kuma ya dace da kai yayah nah", na faɗa ina kallon fuskan shi, murmushi yayi kawai,

M.G ne ya bani amsa da , "sister naga alaman irin wannan kayan zamu saka miki ko? Tou kiyi gaggawan kawo mana suruki idan kina soa miki irin wannan kayan", ya faɗa yana bina da kallo fuskan shi ɗauke da murmushi, saida naji faɗuwar gaba mai ƙarfin gaske lokacin da muka haɗa ido da shi, domin wani irin kyau yake da shi kaman wani india, gashi fara'a da murmushin fuskan shi yana ƙara mishi kyau na sosai sosai ɗinnan, don na lura kaman yasan fara'an na ƙara mishi kyau shiyasa yake yawan yi, gashi da wani dogon hanci da wasu manya - manyan idon shi masu masifar haske, abunda na lura yafi A.G manyan ido da dogon hanci, shi kuma A.G idon shi basu da girma sosai kuma basu da ƙanƙanci, sai dai sukuma round ne su masu yawan gashi ido da gashin gira, gashi na lura hancin bamai tsayi bane irin na M.G, sai dai suna da masifan kyau, kuma shi bai cika buɗe idon shi waral ba, yana ɗan lumshe su kaman yana tsoron wani abu ya faɗa mishi, sannan yafi tsayi kaɗan kuma bai kai M.G jiki ba, dukkan su dogaye ne, amma A.G yafi tsayi kuma yafi haske, M.G yafi kyau amma ba lokaci ɗaya zaka fahimci hakan ba, saboda farinsu da tsayin su yasa har ake ganin kaman suna kama, amma ni ranan ƙasa - ƙasa na ƙare musu kallo har na fahimci abunda mutane da yawa basu fahimta ba, yana faɗin haka na rufe ido na a jikin yayah Ahmad, dukkan su dariya sukayi, yayah Ahmad yace, "ayshaa tana kula samari ne ma, ae inaga bata ma kula su, amma duk ranan da ta kawo mun miji insha Allahu kayan da zamu saka mata sai yafi wannan burgewa da kyau", murmushi nayi ina kallon yayah Ahmad ina jin wani farin ciki a zuciyata da Allah ya bani yayun da suke sona, buɗe baki M.G yayi cike da neman zolaya yace, "waya gaya maka mai kyau bata da samari? ae Allah kaɗai yasan yawan su, ta ɓoye maka ne, amma ni zamuyi labule nasan duk zata lissafo min su, ni kuma sai na tantance na zaɓa mata guda ɗaya gwani", ya faɗa still idon shi yana kaina, nidai juyawa nayi nabar parlon ina jin dariyan su.

Shigan mu gidan muka tarar da A.G tsaye da wasu abokan su guda uku a ƙofan side ɗin su yayah Ahmad, shi dai yana gefe yana waya, amma tunda mukayi parking

muka fito ya maida kanshi kanmu, ƙura mana ido yayi kaman ranan yafara ganin mu, ganin yana wuya sai niyyan wucewa batare dana gaishe shi ba, amma na gaida sauran abokan yayan, don wasu ma sun ƙara fitowa, na juya naji muryan shi ƙasa - ƙasa yace, " Zonan" kaman zan nuna banji ba sai naji ya sake cewa, "ba ƙiranki nakeyi ba"? Da sauri na ƙaraso inda yake, bai cire wayan a kunnen shi ba naga ya wuce wurin motan shi bayan ya mun alaman na biyo shi, haka na juya na bi bayan shi jiki a sanyaye, boot ɗinshi naga ya buɗe yasaka hannu cikin wani jaka bayan ya zuge ziff ɗin jakan ya ɗauko wani envelope, miƙo mun yayi batare da ya cire wayan a kunnen shi ba, hannu biyu na saka na karɓa ina bin shi da kallon neman ƙarin bayani, "na dinner kiyi amfani da shi" yana faɗa bai sake bi ta kaina ba ya wuce inda su yayah suke, ko godiya ban samu daman yiba ya wuce, na juya sai naga idon M.G akan mu, ganin haka sai na fasa zuwa nayi godiyan kawai nayi cikin gida.

Ina shiga ɗakin ummie nah na wuce, tun a parlor na fara gaida mutane, a nan naga su Aunty b da su Aunty asma'u zaune, ummitah da maryam kuma sun fito zasuyi gidan su, nan maryam tace mun sai anjuma zasu shigo, ɗaga mata kai nayi don nasan ƙarya takeyi don tace bazata zo gayyan soɗiba, don habiba har yau bata ce mata komai ba, ko a group da jammy tayi magana bikin habiba bata ce komai ba, daga baya ma sai mukaga tayi left a group ɗin, nan kuwa jammy tafara masifa da kyar na danne ta, murmushi nayi kawai na matsa mata ta wuce, daga nan nayi ɗakin ummie na, dayake safiya ne su huɗu ne kawai a ɗakin daga ummi da goggo sai ƙawayen ummie guda biyu, gefen goggo kuma zainab ce ke zaune suna magana ƙasa-ƙasa, bayan na gaishe su na wuce wurin ummie, zama nayi a gefenta na gaishe ta, na miƙa mata envelope ɗin hannu na,ƙasa-ƙasa nake mata bayanin abokin yayah Ahmed ne ya bani wai na liƙi a wurin dinner, karɓa tayi ta buɗe, da sauri ta ɗago ta dubeni tace, "Ayshaa nasan bazaki roƙe shi ba amma meyasa zai baki kuɗi masu yawa haka, 100k ne fah yan 500, bounch 2, yayi yawa ae, kuma haka kawai ya baki"? Ta faɗa tana jawo wayanta, ni dai bance komai jin tana ƙiran yayah Ahmad yazo ya sameta a ɗakin mu, daga nan babu ɓata lokaci ta miƙe tace na biyota, muna shiga kowa sai ga yayah Ahmad ɗin ya shigo, dama muna shiga ta sallami su hafsy waje, ummie nuna mishi kuɗin tayi tana mishi bayanin wai abokin shine ya bani, murmushi yayi yace, "ummie A.G ne, zai bada abunda yafi haka ma, nima inayiwa ƙannen shi, wannan kuma ba wani abu bane a wurin shi, inaga jiya ne dana basu kuɗin liƙi sai M.G ya ƙara mata, shi a lokacin babu mint a jikin shi sai da muka bar wurin ya mun maganan na tuna mishi idan ya shigo ya bata nashi, nasan kuma shi nashi bugun girmane, ummie inaga babu komai rabonta ne",

"Tou kayi musu godiya dukkan su, kuma gaskiya kuɗin sunyi yawa tayi liƙi da su, ta ɗauki 20k kawai a ajiye sauran", murmushi yayah Ahmad yayi yace, "haba ummie shi da yabata 100k ae yana so yaga ƙanwar shi tayi fitan manya ne, idan bazaki bata duka ba tou a bata 50k, sai ki ajiye mata sauran, don naga hafsy umar da

ishaq ke mata komai ko suma kamun ƙafa ne Allah ya sani" ya ƙarasa yana miƙewa, yana fita ummie ta dube ni, "saura ki bawa ƙawayenki da yan'uwanki labari, gama ke kanki baya saiti, ko hafsy kada naji labarin kin gaya mata, don magana ne da ita yanzu zata isar da shi", ummi nagama faɗa ta miƙe riƙe da envelope ɗin ta fita a ɗakin, nidai ajiyan zuciya na sauƙe na nemi wuri na zauna, ban daɗe ba saiga su fatima da hadiza sun shigo, hawa gadon kusa dani sukayi, hadiza ta miƙe kwance fatima kuma ta zauna a gefe na, "wurin habiba fah muka fito, tana ta tambayanki, mukace kina ciki, duk tayi wani iri da ita," inji hadiza, daga gefe kuma fatima tace, "duk haushinta da nakeji sai kuma ta bani tausayi, duk ta damu sai tambayanki takeyi, chan kuma sai hawaye yazo mata gashi ana mata make-up, da ƙyar ta tsayar da hawayen, shima sai da wannan yar yayar mamien sun tace zata haɗata da mamie tukun tayi shiru, ganin banzan kallon da yan'uwan da ƙawayenta kemana ne yasa muka fito", duk sai naji babu daɗi a zuciyata, tunani na komai yake damunta? Duk sai naji babu daɗi, tagumi nayi ina kallon su, sai ga hafsy ta shigo tana tambayana ina waya na? Yayah Ahmad yana ƙirana, da sauri na buɗe handbag ɗina na ciro wayan da na saka shi a silent, ina fitowa da shi ƙiranshi yana sake shigowa,, da wuri na ɗauka "Ayshaa kizo M.G nason ganinki, kiyi sauri fita zamuyi",

Ina gama jin abunda ya faɗa nayi sauri na miƙe don naje ƙiran.

Ina fitowa nagan su dukkan su a waje, wasu sun shiga motocin su wasu suna tsatstsaye suna magana, hango M.G nayi tsaye a jikin motan su, wanda bansan wannene nashi ba wannene na A.G, wataran nakan gansu a Red, wataran a Black, so bansan nawaye a ciki ba, ƙarasawa nayi wurin shi bakina ɗauke da sallama, ɗago kansa yayi daga danna wayan da yakeyi ya sauƙe mun idon shi a kaina, abun mamaki yau babu wannan fara'an da yake fuskan shi, "meye schedules ɗinki na yau"? ya tambaye ni idon yana kaina, ɗan juya idona nayi sannan nabashi amsa da, "yanzu dai babu komai, sai zuwa anjima muna da liyafa da za'ayi acikin gidan nan," ina faɗa ido na yana kan masu decorating wurin, shima maida idon shi yayi wurin, muryan shi chan ƙasa yace, " barrister yace mun tare aka haife ku da amaryar, itace wannan twin sister ki da muka taɓa ganinku tare ko"? Murmishi nayi ina ɗaga mishi kai alaman hakan ne, ƙura mun ido yayi har sai da naji kunyan shi na sunkuyar da kaina ƙasa ina wasa da gyale na, kaman bazai sake magana ba sai kuma chan yace, "saura ke kenan, fatan dai bazai ɗauki wani lokaci ba zamuji kyakkkyawan labari"? Ɗan juyar da kaina nayi gefe ina murmushi, bance komai ba haka shima bai sake ce komai, amma idon shi yana kaina, chan na hango Yayah Ahmad da A.G suna tahowa wurin mu, a hankali na juyar da kaina ina kallon M.G nace, " yayah yace nazo kana ƙirana", wayan shi ya miƙo mun yace, "saka mun number ki zamuyi magana daga baya"

Hannu na saka na karɓi wayan nasaka mishi number na, ina miƙa mishi su Yayah Ahmad suna ƙarasowa wurin, wani kallo mai kama da harara naga A.G yayi mun sannan ya kawar da kanshi ya shige motan ta side ɗin mai zaman banza, sallama

na musu bayan yayah Ahmad yace zuwa dare idan an watse na dafa mishi ruwan tea.

Ana sallan la'asar gidan mu ya cika maƙil da mutane, haka muka fito muka nemi sit muka zauna da su Aunty Bintu da dukkan wanda suke side ɗin ummin mu, dama kuma Aunty Rakiya ta sauƙe mun kyakkyawan warning akan zuwa inda ƙawaye suke, bata hana mu fita wurin ba tace saboda hakki na yan'uwan taka, amma tayi hani da shige musu, ko ita hafsy an ɗakatar da ita da zuwa wurin raliya, muna zaune aka fito da amaryah cikin shigan ta maroon, ƙawayenta na familyn su da yayan ƙawayen maminta ne suka rako ta, bayan ta zauna babu daɗewa dangin maminta suka rako mamin ta ita ma har wurin zamanta, wayaga uwar amaryah ansha leshi ɗan gaske kana ganinta kaga anaryar Alhaji Usman umar (U.U Ɓalewa) dama kafin fitowan ta mamah da ummi sun daɗe a fili kowa tana table ɗaya da ƙawayenta, ɗago da ido na ɗaɗɗaya ne zanyi ban tarar da idon habiba akaina ba, kuma duk haɗa idon da mukayi sai ta sakar mun murmushi, nima kuma sai na mayar mata, a haka naji tsakin hadiza, da wuri na juya sai naga harara ta ke ɓalla mun, sanin me take nufi ya sa ban kula ta ba na juyar da kaina ina kallon masu rawa.

Har sai dab da magrib dangin ango suka iso, abun mamaki basufi mutum biyar ba, bayan table mai ɗaukan mutum goma aka bar musu guda biyu, saiga mutum biyar sun shigo, haka aka rakasu suka zauna aka kawo musu abinci, ana fara ƙiran magrib suka je fili bayan an ƙirasu da amaryah suka mata liƙi marar ma'ana, daga nan sukayi sallama suka kama hanya, ni acikin su ma bansan fuskan kowa ba, banda ƙanwar mummy guda ɗaya, haka dai aka cigaba da chashewa da DJ, mudai ana fara ƙiran sallan magarib duk mukayi side ɗinmu domin sauƙe farali, basu suka tashi a wurin ba sai wurin 9:00pm, shima sai da Abba ya dawo yace a sallame su tukun suka watse, ni lokacin ma ina kitchen ina dafe tea wa yayah Ahmad, da yake girkin ummie nane sai na haɗa hadda na Abba na, flask ɗin Abba na cika sai na yayah Ahmad, sai na cika wani wa don naji Aunty Rakiya ma tace zata sha, ganin akwai time sai na gasa bread wa yayah Ahmad don yana so sosai, hafsy na roƙa ta kai mishi lokacin da naji shigowan motan shi.

Wuraren 10:00pm muka fito tafiya gidan Aunty Bintu, da yake yau babu ummitah da maryam motan zata ɗauke mu ba sai an nemo driver ba, muna isa babu wani ɓata lokaci muka fara shirin kwanciya, da yake kowa ya gajji yau, a parlor muka

tarar da yayah mohd yana kallo, muna shiga ya miƙa hannu ya karɓi Areefh da yake bacci a hannun hafsy, dukkan mu gaishe shi mukayi sannan muka wuce, babu wani dogon hira a tsakanin mu dukkan mu mukayi bacci, cikin bacci naji vibration ɗin wayana, a razane na jawo wayan na duba mai ƙiran, sai naga number ne, da sauri na yanke wayan, sannan na kashe ta gaba ɗaya na koma na kwanta.

Ana sallan asuba babu wacce ta koma bacci, gyaran gidan mukayi tsaff aka turare shi da turaren wuta masu ƙamshin gaske, saboda idan mun fita baxa mu shigo ba sai lokacin kawo amaryah, abun breakfast muka haɗa, muna karyawa aka dinga shiga wanka, wuraren 9:00am muka shiga gidan mu, ana ta shirye - shiryen tafiya ɗaurin aure, da yake ƙarfe goma za'a ɗaura a masallacin gwallaga, daga na yayah Ahmad har na Habiba achan za'a ɗaura, parlon Abba dukkan mu muka shiga, achan muka haɗu da mamie da Aunty Rakiya tare da Abban mu suna magana, gaishe su mukayi muka fito.

Wuraren 11:30am gidan mu ya cika da yʻan'uwa da yayun mu, wanda sukaje ɗaurin aure daga dangin Ummie har na Abba duk sun hallaro gaisuwa da taya murna, gefe ɗaya kuma ga yʻan'uwan mamie da suke ta baza guɗa, nidai duk guɗan su yankar mun zuciyata takeyi, wato ya tabbata habiba ta auri Aliyu? Aliyun da ya soni, Aliyun daya gama cewa babu mace da yasani wanda ta kaini kyau, kuma yaji a duniya yana sonta sama dani, Aliyun da aka daɗe ana son aga macen da zaice yana so, wai yau yʻar'uwata da nakeyiwa so da ƙauna itace ta zama mallakin shi, itace zasuyi rayuwar aure ba ni ba? Tou Allah ya sanya alkhairi, Allah ya bani haƙuri da juriya.

Yau ma anko mukayi da hafsy, wata super da yayah Mohd yasaya mana, nawa ash nata yellow, gaba ɗaya munyu kyau babu ƙarya, ina lure da hafsy da ummitah jiki na rawa suke ta haɗa duk wani nau'in abinci da akayi a gidan wa yayah umar da yayah ishaq, yayah umar ne ke shigowa ya karɓa su tafi, nidai mamakin su yayah umar ɗin ma nakeyi, yabawa hafsy fah wurin 10yrs amma jibi yadda yake ta wani rawan jiki da kai wa ummitah, koda yake ni kaina bana gajjiya da kallon ummitah, domin duk gidan su tafi su kyau, ga wani diri da Allah yayi mata, ummitah ba fara bace, sai dai wani colour ta keshi mai hasken gaske, idan ka ganta sai kasake kallonta saboda wasu ido da takeda masu kyaun gaske, ga shagwaɓa kamar babu wata ɗiya a gidan sai ita, kullum kaga ganta cikin shagwaɓa take bansan yayah za'ayi da yayah umar ɗan zafi ba, hala fah sai ya biye mata a hakan, dariya nayi ni kaɗai na.

Ana sallan magrib babu daɗewa wannan number ta sake ƙirana, yanzu banƙi ba na ɗauka, murmushi nayi lokacin danayi karo da muryam M.G yana cemun, "mai kyau ina kika ɓuya ne yau? Gaba ɗaya ban ganki ba"?

Murmushi nayi na fara gaishe shi batare da na amsa mishi tambayan shi ba, amsawa yayi ina jin sautin murmushin shi, "jiya kinyi bacci ae na ƙiraki, naso da safe na ƙira mu gaisa Allah bai nufa ba, yanzu ma ina so na sanar dake idan an tashi tafiya dinner ki jira zanzo na kaiko idan babu damuwa".

Murmushi nayi na bashi amsan da "Allah ya kaimu yayah,"

Sallama mukayi yace sai yazo, yana zolaya na wai nayi ɗaurin da za'a san ƙanwar su 1 in town ne, dariya ne ya suɓuce mun na kashe wayan, ina murmushi a zuciyata nace, "nidai M.G yana burgeni, gaba ɗaya baida wani matsala kaman ɗan'uwan shi, shi baida wani sara sai hararan mutane da shegen son girma, ni mai yawan ɗaure fuska baya burgeni a duniya nan, ima son mutum mai faran-faran, gashi fari dogo ga fara'a", murmushi na sakeyi na miƙe nayi parlor wurin su hadiza.

Wuraren 9:00 M.G ya ƙira waya na yana tambayan mun shiryah,? Ido na yana kan zainab da take wani juyi a jiki mirrow tana kallon kyaun da tayi da aka mata make-up da aka mata, koni kallon kaina nake tayi ina ganin yadda na chanja kama, amma dai gaskiya yayiwa kowan mu kyau, domin ba'a wani tsauwala mana shi da yawa ba, muryan shi naji yana "tou ku fito na shigo gidan", amsa mishi nayi da "tou" sannan na kashe wayan, kallon su nayi nace su fito muje, dama Aunty Bintu tunda na gaya mata ɗazu tace yama fi mata sauƙi, don ita da yayah moha zasu tafi, hafsy da ummitah ma tare zasu tafi da su yayah umar, dama na gayawa ummie nah M.G yace zai kaimu, nasiha ta mun da mu tsare mutuncin mu kuma banda rawan kai, a haka muka fito, kowan mu tasha lace mai musulmin kyau, orange ne colour nawa, na hafsy black da golden, an mana wani fitted gown, ga gyalen mu shantily, munyi kyau dukkan mu kaman ka ɗauke mu ka ɓoye, *"MASHA ALLAH*"

Naji muryan M.G yana faɗi lokacin da muka iso jikin motan, shima lokacin ya fito ya buɗe mun gaban motan yana wani sara mun, hakan da yayi sai duk ya saka mun dariya, naji kunyan abunda yamun har sai dana ɓoye fuskana a tafin hannu na, Ya Rabbi M.G yana da kyau da burgewa, nidai halayen shi da ɗabi'un shi sun fara burgeni, ina son yabawa, ina son kulawa sosai, haka na shiga gaban na zauna, maryam, fatima, hadiza, zainab suka shige baya, ina jin shi yana tambayan su basu

matsu ba? Basu matsu ba suka bashi amsa dayake motan mai girma ce, amare tun yammah aka kaisu, habiba ma da yamma aka kaita gidan ta, amma dukkan mu babu wanda Aunty ma'u ta bari yaje rakiyanta, Aunty Bintu ma nan ta tsaya suka amshi amaryah, kuma ana magrib tana ciki. Wanda suka jagoranci amaryah zuwa gidanta, domin ummie tace a wuce da ita gidanta tayi shirin abun da yake gaban su, shiyasa gidan namu yayi shiru, domin duk an tafi kai amare.

Tunda muka isa M.G bai barmu mun shiga wurin programm ɗin ba, wanda aka shirya yi a *ZARANDA HOTEL* muna zazzaune a cikin motan yana ta jan mu da hira, inda hadiza da maryam suka fi mu zaƙewa wurin hiran, kuma daga dukkan alamu ko wacce a cikin mu taji daɗin yadda yake tafiyar da mu, ango da amaryah basu iso ba sai wuraren ƙarfe 10:00, wata irin jeep ce mai girma da kyaun gaske baƙa wuluk tana shaining ango da amaryah suka iso a ciki, gaba ɗaya kallo ya koma kan motan, inda wasu daga cikin angwaye da ƙawaye suka matso wurin motan suna jiran fitowan su, Ƙafan driver tana buɗewa naga A.G ya fito a ciki, fuskan nan kaman an mishi albishir da ranan mutuwan shi ko alaman ya taɓa dariya babu a fuskan, haka kawai naji yabani haushi, daga nan ango da amaryah aka buɗe musu suka fito.

Kaiii yau wace rana Yayah Ahmad fuskan shi cike da fara'a? Sai wani dariya yakeyi kaman bashi ba, yana fitowa ya matso gefen amaryan shi ya riƙo hannun ta, bamu san me aka gaya mishi ba gaba ɗaya wurin suka ɗauki dariya, angwaye da amaren duka, shi kuma ya ɗan rungumo amaryan shi kusa da shi, dai-dai lokacin M.G yace muje wurin mu gaisa dasu sai mu shiga.

Muna isa wurin yayah Ahmad ya miƙo mun hannu na ƙarasa wurin shi ya rungumoni jikin shi yana sunkuyawa kunnen amaryan yana mata magana, inaji ta saka hannun ta tajawoni kusa da ita, dayake fuskanta rufe yake da mayafinta, gaisheta nayi zuciyana cike da ƙaunar ta, bayan mun gaisa abokan shi suka fara maganan a jera yadda za'a shiga DJ yana announcing shigowan su, jin haka mukayi niyyan shigewa cikin hall ɗin.

Juyawan da zanyi naji an riƙo hannu na an jawoni, tunani na Yayah Ahmad ne, amma juyawan da zanyi sai naga hannun A.G ne riƙe da nawa, ina ji ya jawo ne baya kusa da ƙofan da ya fito na motan, gaba ɗaya idon M.G yana kanmu, Yayah kuma kallo ɗaya yayi mana ya sake maida kanshi kan abokin shi da yake maganan su gyara yadda za'a shige.

"ki maida hankalin ki nutsu a wurin nan, idan kikayi wani abu da bai mun ba zaki koma gida a ƙafa", A.G ya faɗa mun murya ƙasa-ƙasa wanda nima da ƙyar nake jin

shi, ga wani yankewar zuciya da na samu kaina inayi akai - akai, bai ishe shi ba ya sake cemun, "wani irin kwalliya ne aka miki gaba ɗaya ya maida ki kaman dodo? Ga wani gyale kaman wani gidan sauro?"

Zuciyata naji ya ɓaci na yanda ya wani kushe ni, turo baki nayi gaba kaman zanyi kuka, "zan buge mummunan bakin nan idan baki gyara shi ba", "kana bugewa zan buge naka, kabarta yan'uwan ta suna jiranta zasu shige ciki" M.G ya faɗa yana ƙarasowa inda muke, harara A.G ya mishi sannan ya sake hannuna, yana sake ni da sauri na ware nabi bayan su maryam jiki na yana rawa.

Tunda muka samu wurin zama muka zauna maryam da hadiza suke ɓaɓɓaka dariya, gaba ɗaya haushin su ya kamani, don na rasa me yake saka su dariyan, ɗaure fuska nayi naja tsaki nace, " amma dai za kusa a raina mu irin wannan dariyan ƙauyancin da kuke yi, tou meye ne ma kuke wa dariyan"? Na faɗa ina hararan su, kaman wani jira suke nayi magana sai suka sake kwashewa da wani dariyan, wanda har suka saka fatima ma ta ɗan dara, tana kallon su tace, "haba ku kuwa ku daina dariyan nan mana ae zaku saka ido ya dawo kanmu, gashi ma yanzu na hango Aunty b ta wani tsura mana ido,"

Sokaye ne ae na faɗa ina ƙara hararan su, dai-dai lokacin DJ ya isar da saƙon shigowan ango da amaryah, dole suka tsagaita da iskancin dariyan nasu muka maida hankalin mu kansu, ango da amaryah ne a gaba, bayan amaryah jerin friends ɗinta ne, bayan ango ma jerin friends ɗinshi ne, wato ko wani aboki yana jere da ango.

Sulaiman da yusuf sune asalin abokan yayah Ahmad wanda suka taso tare tun primary, kuma an taso dasu anguwa ɗaya, da babu abunda yake rabasu dare da rana, yanzu ne kowa aiki ya banbanta musu garin zama, sai haɗuwan su ba irin da ba, sulaiman da yusuf duk sunyi aure kusan shekaru biyu baya, saboda auren su babu nisa a tsakani, kuma ko yanzu sune jagaba a hidiman, don bayan ango sulaiman ne, sai A.G, bayan A.G kuma yusuf ne, sai wani abokin shi nura babah, sai M.G sai wasu da bawani zuwa sosai sukeyi ba, ido na yana kansu har suka ƙarasa wurin zaman su, gaskiya matar yayah Ahmad mai kyau ce masha Allah na faɗa a zuciyana, high table ɗin ango ne kawai da amaryah a zaune, suna rakasu suka koma wurin zamansu suka zauna, gefe ɗaya amare ɗaya gefen angwaye.

Babu ɓata lokaci aka fara programm ɗin, inda aka ƙira babban yayah mohd ya buɗe taro da Addu'a, sannan aka ƙira babban abokin ango wato sulaiman ya bada tarihin ango, abun gwanin burgewa ya bada tarihin shi cike da burgewa da ilimi, yana gamawa wuri ya kaure da tafi, da yake saida ya gama yi mishi iya shege a ƙarshe wanda yasaka kowa a hall ɗin darawa, ina ganin yayah Ahmad bini-bini yana sunkuyawa kunnen amaryah yana mata magana, gaba ɗaya mamakin shi ya cika

ni, dama yana sakewa haka? Sai wani murmushi yakeyi wanda yaƙi barin fuskan shi, bayan ƙawar amaryah ta bada tarihin ƙawarta sai aka fara abun da ya tara kowa, fili aka baje wa ango da amaryah domin rawa, fitowar su aka saka musu waƙan *ALI JITA* na amaryah da ango, haba zokiga abokan ango yadda suke baza naira kaman basu so, ina hango Nura Baba sai naji ɗan tausayin shi, domin yanuna yana son habiba har yayiwa yayah Ahmad magana lokacin zamu fara rubuta exams na SSCE, sai yayah yace yayi wuri yayi maganan ya bari sai ta shiga university, shima lokacin yana shirin tafi UK masters ɗin shi, har Yaya Ahmad ya ƙirani agaban Nura Baba ya tambayeni akwai wanda habiba take kulawa ne ko sukayi maganan aure da shi, a lokacin nace mishi bamu kula kowa dukkan mu, ya juya ya kalli Nura yace kaji abunda nagaya maka ko? Yaran nan basu fara zance ba, amma insha Allahu na maka alƙawari suna farawa zan maka magana, Nura ustaz ne shi ɗan sarauta ne me kuma sanin ya kamata, yana da kirki da zumunci sosai, kallo na yayi yace, "sister amana yana hannun ki, ki kula da ita kada kibarta ta kula kowa, ke kuma nasan gudumawanki na tsaro da zan baki," ya faɗa yana dariya ni da yayah Ahmad ma dariyan mukayi, sannan ya kwaɓe ni da kada nagaya mata, amsa mishi nayi akan bazan faɗa ba amma nasan bazan iya riƙewa ba, a wurin na tafi na barsu suna ta zanta maganan tafiyan Nuran, sai da mukazo kwanciya bana mantawa ina ta kallon habiba da take gyara mana wurin kwanciya ni kuma ina shiryah mana books ɗin da mukayi karatu ina ta murmushi, gajjiya tayi da kallon da nake mata tace, "sisto akwai wani jarida ne kam"? Dariya na kwashe da shi nace, " amanatul amana, azabatul axaba, dariya muka kwashe da shi don tare muka ƙarasa faɗa, yawanci idan ɗaya zatayi wa ɗaya gulman da aka kwaɓeta haka mukeyi, kamo hannu na tayi muka koma bakin gadon muka zauna, Bayani dallah -dallah na mata, ina gama gaya mata ta wani zaburo ta dafah ƙirji tace, "ustaz nura baba"? Ɗaga kai nayi alaman ehh, fuskana ɗauke da murmushi, rungume ni tayi tace , "Alhmdllh sisto, gaskiya naji daɗin wannan jaridan, kuma nutsuwar shi yana burgeni, matsalar ɗaya ne, ni guntuwa shi guntu, amma duk da haka babu matsala yaran zasuyi kyau masha Allah, kinsan ni bana son farin mutum, gashi nuru ba fari bane irin kalan mijin da nake so", hararan ta nayi cikin wasa nace , "yarinya baki da wayo, ae farin mutum duniya ne, yarinya miji ya tashi a bacci kiga farin jiki ae duniya ne, amma baƙin fata nayi juyi cikin dare nayi arba da baƙar cinya ae razana zanyi", na faɗa muna kwashewa da dariya, habiba ta kaimun duka a cinya.

Lokaci guda naji kewan habiba yazo mun, abun yana mun ciwo yanzu duk irin wannan ƙauna da shaƙuwan da yake tsakanin mu habiba ta yarda akan namiji muka rabu? Muryan maryan naji akaina tana cewa, "ke matar farare ana ƙiran familyn ango a fili, ke kuma kin tafi duniyan tunanin waye dai a ciki oho", ta ƙarasa faɗa tana dariya, hararan ta nayi na miƙe domin muje filin, don gaba ɗaya idon yayah umar yana kaina, ina cewa bazan fito ba zaizo inda nake, dama yayi mun warning agida, ko bazanyi rawa ba ya ganni a fili.

Muna fitowa aka sako mana waƙan Ali jita, haba zokiga su fatima da su hafsy, maryam ummitah, hadiza yadda suke chashewa, Aunty b sai chashewa takeyi yayah mohd yana dubanta fuska ɗauke da murmushi, liƙi yafara kaman ba gobe, dangin mu na gefen ummi da Abba duk sun fito, fili ya kachame da ruwan kuɗi, ballan tana da yayah umar da yayah ishaq suka kamo hannun ango suna liƙa mishi kuɗi suka shigo da shi fili, ae gaba ɗaya abun sai ya baɗa cittah da unga, Aunty Asma'u, Adda, Aunty b da mu duka muka fara mishi liƙi, yayah umar ya riƙe hannun shi yana rawa, abun mamaki dayawa kawai sai ga yayah Ahmad yana wani chashe rawa, ae dukkan mu muka hau ihu ana liƙa mishi kuɗi, Yayah mohd yana dariya ya jawu su dukkan su ya rungumesu, muma mukaje muka rungumesu nida hafsy, *AUNTY NICE* sai da naji hawaye yazo mun alokacin, domin yadda naga wani farin ciki da ƙaunan juna a fuskan mu duka, Aunty B sai video take mana ita dasu maryam da su ummitah, domin hattah hadiza da zainab yayah mohd ya rungumu su, Adda har wahaye ta fara lokacin da yayah Ahmad ya riƙo ta ita da Aunty ma'u yana rawa da su, kai zumunci akwai daɗi, Allah ka ƙara haɗa kanmu baki ɗaya, haka muka cinye lokacin mu kowa ta koma wurin zama, anan DJ ya sake gayyati familyn amarya, suma suka fita suka chashe nasu.

Bayan ƙawaye da amaryah sun fito sun chashe, mun musu liƙi sosai, sai aka ce amaryah ta tsaya a fili ita kaɗai, sannan ango yazo ya nuna mata irin ƙaunar da yake mata, wurin yayi tsitt, fitowan ango yazo ya tsaya gaban amaryah ya ƙura mata ido yana wani binta da kallo fuskan shi ɗauke da murmushi ita kuma ta sunkuyar da kanta ƙasa, sautin waƙan *ALI JITA* kawai yake tashi a hankali, inda yake raira waƙan □□□Gimbiyata sai ke, soyayyar mu har abada, ko rana da wata sun daina haske, Gimbiyata sai ke, soyayyar mu har abada, i luv u baby, sarauniya baby soyayyarmu har abada□□□ waƙan mai ratsa zuciya, yana zuwa wurin ya rungumeta a jikin shi, gaba ɗaya hall ɗin aka ɗauki tafi da shewa, ya saka hannun shi ya ciro zube ya saka mata, ya riƙe hannun suna rawa a hankali kaman wasu turawa, sai ganin yayah mohd nayi a fili yana musu ruwan kuɗi sai liƙa musu kuɗi yakeyi, haka muka sake tasowa muka liƙa musu, a haka abokan ango suka fito suna ta liƙa musu kuɗi, ɗago idon da zanyi charaff sai a cikin na A.G, muna haɗa ido ya mun alaman na fita, ban wani ja ba kowa na juya na fara barin wurin, a lokacin kuma sulaiman ya fara mana liƙi nida hafsy da su yayah umar, yanayi yana tsokan hafsy da "jerry ina tom ne kan ban ganta ba"? Dukkan mu muna dariyan hafsy da ta turo baki gaba, hakan ne ya saka na dakata da fita a filin, inda M.G ma ya shigo ya fara mun liƙi, don kaɗan yayiwa ango da amaryah ya dawo kaina, lokacin fatima ta riƙe hannuna a dole sai nayi rawa, M.G yana murmushi yace, " yauwa fatima gara ki saka ta tayi rawa, auren yayah barrister guda baza tayi rawa ba? Ae bai yi dai-dai ba", ya cigaba da liƙa mun shida sulaiman da nura baba da wasu a cikin friends ɗin su da suma hankalin su ya dawo kaina, mantawa nayi da kashedin A.G na tsaya hannu na riƙe da ɗan ƙaramin purse ɗina, na rungumeshi ina ɗan juyawa, ni ba rawa ba ni ba tsayuwa ba, a haka DJ ya sallame muka koma.

Zuwa 11:00pm aka tashi a dinner ɗin, fitowa mukayi inda motan su Aunty b yake, yayah umar da yayah ishaq suka ɗauki ummitah, hafsy, zainab a motan su, yayah mohd kuma shida Aunty b a gaba, baya kuma ni, fatima, hadiza, maryam, a haka muka wuce gidan yayah mohd, muna shiga motocin angwaye na suna ta shigowa, sun dawo da ƙawayen amaryah, dare yayi bai dace a mayar da kowacce ƙawa gida ba, cewar yayah mohd daya gayawa angwaye, saboda haka dole a gidan amaryah zasu kwana, idan yaso gobe sai ango ya dawo gidan shi, haka kuma akayi, muna jin shiga da fitan motocin angwaye gidan, har kusan 12 sai ga ƙiran M.G, ina ɗauka ya tambaye ni don Allah idan babu damuwa na kawu ruwa mai ɗan zafi a cup A.G zai sha magani, idan na fito suna wurin motan shi, tashi nayi na ɗauki ƙaramin flask mai ruwan zafi a ciki da cup, kallon hadiza nayi nace ta raka ni don Allah, muna fitowa na tsaya ina duba inda motan M.G yake, sai naga an kunna wutan mota an kashe, alaman naga inda suke, ƙarasawa mukayi, dai-dai nan M.G ya buɗe gaban motan ya miƙo hannu ya karɓi flask ɗin, duk hankalin shi a tashe, gefen mai zaman banza kuma yayah Ahmad ne zaune ya juya baya yana kallon A.G yana ta mishi sannu, a hankali na maida kaina ina kallon A.G dake zaune a bayan motan, sai hakki yakeyi yana ta maida numfashi daƙyar- daƙyar, hannun shi riƙe da inhela yana fesawa, gaba ɗaya fuskan shi tayi zufah, Allah sarki sai naji gaba ɗaya ya bani tausayi, kaman bashi bane ɗazu yake ta wani faɗi a wurin dinner, amma dube shi yanzu yana ta kanshi cike da azaban fusgan numfashi da yakeyi.

Fifita ruwan M.G yakeyi da cup ɗin da marfin flask ɗin, ganin haka yasaka na karɓa ina yi mishi, shi kuma ya ɗauko magani a gaban motan ya ɓalli guda ɗaya ya miƙawa A.G, ina ganin shi ya karɓa gaba ɗaya jikinshi yana rawa, sai wani hawa da sauƙa ƙirjin shi yakeyi a laman numfashin yana mishi wahalar jawowa, duk jiki na sai naji yayi sanyi, barin ma yadda naga hankalin M.G ya tashi sai naji duk nima na rasa nutsuwa lokaci ɗaya, miƙa hannu A.G yakeyi alaman a bashi ruwan, ganin haka yasa na buɗe ɗayan gefen inda yake zaunen na miƙa mishi a hankali nace, "sannu ga ruwan", ɗago kai yayi ya kalle ni kaman bazai karɓa ba, sai kuma ya sake jan wani numfashin da ƙyar ya saka hannu ya karɓa, a hankali ya shanye maganin da ruwan ɗumin, duk ido muka ƙura mishi kaman zamu karɓa mishi, yayah Ahmad sai sannu kawai yake mishi, M.G ko kaman shine ciwon yake jikin shi, a hankali naji muryan shi yace, muje ka kaini gida M.G, ango nagode sannu", ya faɗa wani tari na zuwa mishi, haka ya tsaya da maganan yayita tarin suna mishi sannu, nidai bansan lokacin da na buɗe bayan motan na shiga na zauna a gefen shi ba, don gani nayi kaman numfashi zai ɗauke, ga wani hakki da yakeyi har kana jin sautin numfashin yana sarƙewa, zama nayi ina duban shi ina ta jera mishi sannu, sannan na dubi yayah Ahmad muryan na yana rawa kaman zanyi kuka nace ,Yayah ko asibiti zaku kaishi? Da ƙyar fa yake numfashi", na faɗa ina maida kallona kanshi,

Ajiyan zuciya M.G ya sauƙe yace, "taurin kaine da A.G, nace mu wuce asibiti yana wani cewa idan yasha ruwan ɗumi da maganin zai sauƙa, gashi kuma numfashin har yanzu bai dai-dai ta ba, ni ban san meyasa baya son asibiti ba wlh, gashi ciwon shi na asibiti ne",

"yayah tou ku kaishi basai kun jira shi ya yarda ba", na faɗa ina ƙara matsawa kusa da shi, ɗago kai yayi ya harare ni murya a shaƙe yace "ke ina wasa da ke ne? Bana son manyance fah, ce miki akayi bazai faɗa bane kina wani shirin yin kuka"? Ya faɗa yana ƙara maida inhelan bakin shi ya zuƙa sannan ya maida kanshi kan sit ɗin motan ta baya ya kwantar, dukkan mu shiru mukayi muka zuba mishi ido, baka jin ƙaran komai sai na heater da yake kunne, ita dai hadiza tana tsaye ta side ɗin yayah Ahmad ta ƙura mana ido, niko shigewa ne jikin A.G kawai banyi ba, saboda ni bansan ma lokacin da na sake matsawa kusa dashi daf ba, ina jin ya sake fara tarin na matsa kusa da shi nace, "plz yayah kuje asibitin mana dare nayi kuma kana shan wahala", na faɗa idona yana wani cikowa da hawaye,

Ɗago kanshi yayi ya ƙura mun ido, abun tausayi duk idon ya maida su ciki ciki ya lumshe su kaman baya iya kallon mutum, yana kallo na yana jan numfashin shi da ƙyar, a hankali yace, "M.G muje asibitin" har ya faɗa idon shi yana kaina, ni ma kuma ban ɗauke ido na ba akanshi, ina ji kaman na fashe da kuka, ajiyan zuciya M.G yayi ya gyara zaman shi, ya dubi yayah Ahmad yace, "kai ka koma masauƙi kai da sauran abokan mun, ni zan wuce da shi duk abun da ake ciki zakaji ni insha Allahu", hararan shi yayah Ahmad yayi yace, "idan na tafi ma baccin ba iya yin shi zanyi ba, zan gayawa Nura baba ya tsaya akan komai tunda yusufsun wuce gidajen su, ni sai muje kawai", ya ƙarasa faɗa ya na ciro wayan shi a aljihun shi domin ya ƙira nura baba da suke chan cikin parlor da ƙawayen amaryah.

"Nima yayah M.G zan biku asibintin", na faɗa ba tare da na san maganan ya fito bakina ba, harara na A.G yayi, shi kuma M.G ya juyo ya kalle ni fuskan shi ɗauke da murmushin dole, "ki koma gida dare yayi, insha Allahu komai zai zo da sauƙi, akwai alluran da suna mishi zaiji sauƙi, har ma yafi ki yin bacci," ya faɗa yana maida kanshi kan Yayah Ahmad.

Hannun A.G naji ya riƙo hannuna ya riƙe da ɗan ƙarfi kaɗan, da sauri na ɗaga kaina ina kallon shi, shima kallona yakeyi, sai dai wannan kallon yau ɗin babu harara a ciki, idan ban yi ƙarya ba sai naga kaman kallo ne na rarrashi, ganin haka sai naji jikina yayi sanyi har wani hawaye naji yana so ya zubo mun, girgiza kanshi yayi alaman no, kada na fara kukan ya mun, ajiyan zuciyan M.G na sake ji shi yasa na maida kaina kanshi sai naha idon shi gaba ɗaya a kanmu, kunya naji kuma naji na ɗan ruɗe kaɗan, ganin haka sai yayi murmushi yace, "kije hadiza na jiranki ku wucce gida zan ƙiraki kiji yayah ake ciki, yana gama faɗa na zare hannu na a hankali a na A.G, bai wani ja ba ya sake mun hannun na juya na fita a motan, a hankali nace "Allah ya sauwaƙa yayah A.G" ina faɗa na yi sauri nayi hanyan cikin gida, hadiza na bina a baya har muka shiga ciki na rufo ƙofan muka wuce ɗaki, muna shiga hadiza ta nemi wuri ta zauna ta zabga wani uban tagumi, ni kuma bakin gado na wuce na zauna ina jina kaman akwai abun da na rasa na farin ciki a zuciyata, kallon mu fatima tayi tace "lafiya dai malamai kuka shigo kaman masu mummunan labari"?

"Hmmm, akwai ja a gaban mu, ehh nace akwai charkwakiya a gaba, nidai dije sai zuru, naga abunda ba'a gani ba, ehh naga abun al'ajab," hadiza ta faɗa tana ƙara wani tagumin kaman tsohuwa mai shekara 100, hararanta maryam tayi tace, "ke wallahi dije jan rai ne da ke, meye ne kam? Ango ne ya haiƙewa amaryah a gaban idon ku"? Gaba ɗayan mu dariya muka kwashe da shi, don hattah zainab da baƙin halinta na share mutane sai da ta kwashe da dariya, nima duk damuwan da nake ciki sai da na dara, ita ma kanta mai maganan dariya abunda ta faɗan yɷa dawo yana bata, tana dariya tace, "wallahi al'amarin yayah Ahmad tsoro ya koma yana bani, kunga wani rawan kai da yakeyi kuwa? Kaiii maxa sai a hankali duk yadda kake ganin su barsu kawai a yadda suke, tou na sani ko kunje kunƙi barin wurin, shi kuma haƙurin shiya ƙare ya zaburar mata? Don ina razane da shi a wurin dinner nan kada ya bamu kunya,Allah ya rufa asiri dai aka gama taro lafiya", dariya muka sake kwashewa da shi, don wallahi abunda ta faɗa gaskiya ne, koni nayi ta mamakin shi.

Duk yadda suka so jin gulmar hadiza taki tofawa, wanda ni ban ma gane akan me take maganan ba a lokacin, haka muka ɗan taɓa abubuwan dariyan mu, a hankali fatima tace "ko yayah habiba yanzu? Tunda ance surkuwarta ta hana dinner da komai, nasan yanzu ɗaki daga ita sai Ali sai abunda suka ƙullah" dariya dukkan suka sheƙe da shi, amma ni kuma sai naji wani mummunan gaɗuwan gaba,wanda har ya kaini da duba agogon hannu na, ganin ƙarfe 2 saura sai naji wani abu ya chaki zuciyata, runtse ido naji lokacin da naji muryan maryam tana cewa zuwa yanzu kam ko an kashe big boss ko ana kashe busawa masu tsaron gidan, habiba kuma hankali ya kwanta, yadda taci burin dogon miji ya kuma an haɗe da su zulaihatu", ta ƙarasa faɗa suna ƙyalƙyalewa da dariya, don duk wanda yasan habiba yasan ta da wannan language ɗin na zulaihatu, kowa yasan ma'anar da ta ɗaura kalman zulaihatu akai, ga habiba da masifan son aure da ma, ni ko a sch idan naji ana hiran aure da abunda ya ƙunsa kunya nakeji, kuma bazak ji baki na ba, amma habiba duk shirun ta tanajin an fara hiran aure zakaji ta akan gaba, yanzu kaji ta tana, "kai auren baƙi dogon mutum duniya ne, don yanzu zakayi kiciɓus da hajiya zulaihatu mai lafiyar zuciya", ya faɗin haka kowa zai kwashe da dariya, don an san me take nufi, tana farawa nake janta mu bar wurin, na ringa ranƙwashin kanta kenan tana dariya, ana cikin dariyan naji sauti wayana, da sauri na ɗauka, su kuma duk sukayi shiru suka ƙura mun ido, muryan M.G naji yana ce mun "bakiyi bacci ba har yanzu?" murmushi nayi nace, "yanzu muke shirin kwanciya" "Tou ki kwanta ki huta shima yayi bacci, an mishi allauran Alhamdulillahi ya sauƙa har ya kwanta", ya faɗa yana mun sallama.

Ajiyan zuciya nayi, sannan na maida kaina na kwanta.

Washe gari tunda asuba Aunty B ta tashe mu, haɗuwa mukayi dukkan mu a kitchen muna haɗa breakfast na amaryah da friends ɗinta, ga kuma na yayah Ahmad da friends ɗinshi, don duk yau zasu koma, so kafin 8:00 mun gama komai, na amare aka kai side ɗinsu, na angwaye kuma yayah ne da yusuf suka zo suka ɗauka, nidai lokacin da suka zo ma na shiga wanka, 10:30 mun gama komai mun shiryah, nan mukayi wa Aunty B sallama zamu wuce gida, domin driver yana waje ummie ta turo

yazo ɗaukan mu, haka muka fito gudu - gudu mukaje side ɗin amaryah muka gaisheta, tayi kyau tana sanye cikin wani lace black mai ratsin golden, fitted gown ne ya yi matuƙar amsan jikin ta, Gsky Aunty jeeddah tayi babu ƙarya yar gayu ce na nuwa, da fara'a sosai a fuskanta ta amshe mu, bayan mun gaisheta muka mata sallama zamu tafi, da sauri ta miƙe tana tmbyn meyasa bazamu zauna ba sai anjima? Da murmushi a fuskan mu nace mata ummie tace mudawo zamuyi aiki a gida, amma insha Allahu zamu zo, har bakin ƙofah ta rakamu hannunta na riƙe da hannuna, ina kallon hafsy sai harara na takeyi, ai kuwa muna shiga mota ta juyo tana harara na, " Adda wannan karon kan inaga sai Abba ys shiga lamarin mu, don babu yadda za'ayi ki ƙwace Aunty B, yanzu ma ki ƙwace Aunty jeeddah ba, duk iyayin ki sai kin bar mun ɗaya", ta faɗa tana wani tsuke baki da fuska, dariya muka kwashe da shi, ina riƙo ta jikina dama a gefe na take zaune, "haba hafsy masoyiya tah, ni dukkan su ma na bar miki, har mai zuwa a gaba ma, nidai fatana Allah ya bar mun ke, shine babban buri na," kwanciya tayi a kafaɗa na tana ƙyalƙyala dariya kaman ba ita bace take harara na yanzu, "Adda ae mai zuwa na gaban kai ae dama tawa ce, sai yadda nace", ta faɗa tana zungurin ummitah, mudai dariya muka musu.

Muna sauƙa a motan muka wuce side ɗin hjy ummah mu gaisheta, a parlor muka sameta dasu Aunty ma'u, Aunty Rakiya dasu yayah umar, gaishe su mukayi sannan na shige ɗaki na ajiye kayana.

Angama biki da 1week Yayah Mohd da yayah Ahmad suka fara shirin komawa Abuja, domin wannan karon yayah mohd zai tafi da Aunty B, sun kama gida wuri ɗaya da yayah Ahmad, gidan offstair ne ɗaya yana sama ɗaya yana ƙasa, ko wanne yana ɗauke 1 parlor 2 bedrooms, ana saura 2dys su tafi Abujan, Aunty b da Aunty jeeddah suka zo gida dukkan su suka wuni, ranan wani farin ciki na musamman nake gani a fuskan ummie, don lokacin ɗaura lunch tare muka shiga kitchen da su Aunty b, ummie dai tana zaune parlor da su yayah, don dukkan su ranan a parlon ta suka wani, akai - akai zakiga mamah ta shigo, abinci kala 2 akayi, domin ko wacce abinda mijinta yake so ta girka, suna ta raha a tsakanin su, nidai sai kallon su nakeyi ina jin daɗi a raina, nida hafsy da fatima aka barmu da haɗa drinks, mukayi zoɓo mukayi kunun aya, sannan hafsy ta sake haɗa tarmarrin juice, wai tasan shi yayah umar yake so, nidai kallon ta kawai nakeyi don nasan ƙarya ne, yayah umar kunun aya yake so shida yayah Ahmad, yayah mohd ne mai son zuɓo, yayah isgaq ne mai so, duk da ban ganshi a parlon ba amma nasan babu daɗewa zai zo, don inaga wataran a gidan nan ma yake wanka idan banyi ƙarya ba, haka muka je muka jera komai a ƙasan parlorn bayan mun shimfiɗa babban ledan cin abinci, domin ummi tace kada a ɗaura akan dinning

Suna dawowa a sallan azahar dukkansu suka shigo parlorn, murmushi nayi ganin harda yayah Ishaq, babu wani kunya ko takura na wani surkunta, ita ummie ta gaya musu su ɗauke ta uwa, itama yayya ta ɗauke su, ita dai bata son raini, amma duk abunda suke buƙata wanda uwace keyi tou bata ɗauke musu ba su tunkareta, kuma ko wani matsalah ne idan baifi ƙarfinta ba su sameta, bata son su nemi iyayen su sai sunga gazawanta, zuwan su sama sai da ta zaunar dasu da mazajen su ta musu nasiha sosai, sannan ta nemi haɗin kansu dasu zauna da junan su lafiya, kallon Aunty jeeddah tayi tace, "Hauwa maijeeddah, yanzu ne kika shigo cikin mu ke, domin ita Bintu ta riga da ta daɗe da shigowa, mun santa ta sanmu, domin ta zauna dani ɗaki ɗaya na tsawon shekara guda, yanzu kece kika shigo kuma bana so ki ɗauki kanki kaman baƙuwa, kema ki saka a ranki tuntuni kina tare a cikin mu, yanzu kece ƙarama kafin auta na ya kawo ta shi, abunda nake so dake kiyiwa Bintu biyayyah kamar kina tare da babbar yarki, ku haɗa kanku kada ku bada ƙofan da za'a shiga tsakanin ku, domin haɗin kanku shine ƙarin haɗin kan yayya na, ni kuma shine burina da nutsuwata, mu haɗa kai dukkan mu mu zama abu ɗaya, shine fata na da buri na, kuma dukkan ku irin so ɗaya nake muku, babu wacce tafi wata a wurina sai wacce tafi kyautata mun, kuma tafi zaman amana da mu, ni wacce umar na zai aura tun bata zo ba iri ɗaya nake jinku a zuciyata, yadda dukkansu yayyan iri ɗaya nake jin su a raina, saidai wanda yafi kyautata mun" nasiha sosai ummie ta musu, kuma tayi wasu yayah ma, bayan fitan matan su ma ta ƙara yi musu, domin yadda muka taso da son junan mu tana so abun ya miƙe har kan yayya da jikoki, inda ta nuna musu haɗin kan matan su shine nasu haɗin kan, domin idan matan su babu haɗin kai zai shafi zumuncin su, don kowa nashi ya sani, haka dai aka zauna cin abincin kowa cike da farin ciki, filet ɗaya Aunty B ta zuba musu da Aunty jeeddah, nima da hafsy da fatima filet ɗaya muka zuba yadda muka saba ci da hafsy tare, yaya umar da yayah ishaq na nasu tare, yayah mohd da yayah Ahmad da ummie filet ɗaya suka zuba, domin yawan cin lokuta tare suke cin abinci, da ƙyar kiga ummie nacin abinci dani ko hafsy, amma yayah Ahmad da yayah mohd yawanci tana cin abinci tare da su, tun bama yayah mohd ba, shi yawan ci duk irin abunda ummie keso na abinci shima yana so, don ko zuwa yayi duk inɗa ta zauna yana gefenta, idan ta koma ɗaki zakiga baya wani daɗewa zai bita, idan tayi kitchen ma zaki ganshi ya bita, toilet ne kawai da bayida iko baya binta, kuma har yanzu idan ya zauna zakiga ya jingina da ita, narasa wani irin ƙulafucin uwa yake da shi a zuciyan shi, Areefh dai yana gefen yayah umar, don tunda suka zo yake wurin shi domin son shaƙu sosai.

Gaba ɗaya parlon ya ɗauki shiru, banda ƙaran spoons sai Areefh da yake ta gulaniyan shi, a haka mukaga an ɗago labulen parlon da sallama, Abba ne ya shigo, hannu ya saka ya riƙe haɓan shi yana duban mu ɗaya bayan ɗaya, idon shi ya tsayar akan ummie yace, "baiwar Allah irin wannan wariyar launin fata haka? Haba baiwar Allah ae sai aɗan taimakawa marayan Allah ɗan ɓoto a gayyace shi yazo shima ayi wannan ciye-ciyen da shi, kayan daɗi iya kayan daɗi amma sai a ware ni gefe guda"? Ya faɗa yana neman wurin zama a gefen yayah umar da yayah ishaq, mudai parlon gaba ɗaya dariya muke mishi, sannan kowa yana mishi sannu da

shigowa, hararan su yayah mohd yayi yana cewa, "ni ae tunda naga muhammadu an fito a sallah bai wani tsaya munyi hiraba ya wani kamo hannun ɗan'uwan shi Ahmadu sukayi gaba har suna tuntuɓe na xargi wani abu, ubana ne kawai da ishaq suka ɗan tsaya da mummunan ɗansu muka ɗan zanta, a lokacin nace tou anya babu wani abu da ake ɓoye mun?".

Dariya ummie tayi tace, "wallahi kana raina, duk loma ɗaya idan nayi naji daɗin girkin da yayana suka shirya mun sai na tuno ka, kawai dai babu yadda zanyi ne na share, don nasan amaryah ta shiyah maka table da danasha", ta faɗa tana kallon shi da dariya, dukkan mu dariya mukayi ganin yadda Abba ya wani kama haɓa yana hararan ummie, kallon sa ya maida kan su Aunty b yace, "yanzu yarana hadda ku anuna mun wariya ko"? Sun kuyar da kai Aunty B tayi tana dariya, a hankali tace, "Abba nima fah kana raina shiyasa na zuba maka naka a flask, yana kitchen dama jira nakeyi muna gama na bawa hafsy ta kai maka", ta ƙarasa tana dariya.

Spoon yayah umar ya miƙawa Abba yana cewa, "rabu da kowa Abba muci abinci tare, kaga nima ware ni sukayi, dama kullum haka ake mun, shiyasa kaga sau ɗari wurinka ko wurin hajjaju makkatu nake zuwa ci, don yayah mohd yana shigowa yake cinye abincin gidan nan shida ummin shi," ya faɗa yana kai loman abinci bakin shi, dariya mukayi ummie tana cewa, "wallahi yaron nan kaji tsoron Allah, nafi yawan cin abinci da kai fah, yanzu ka fito da tsirfah kala -kala kace baka cin wannan baka cin wannan" haka dai akayi ta raha ana cin abincin, wanda Abba sai da yaci duka girki kala biyun yana ta santi, ana gama ci muka tattare komai, sannan Abba yaja yan mazan suka tafi side ɗin shi, mu kuma dukkan mu muka wuce wurin hajiya ummah, ummie kawai muka bari.

Wuraren ƙarfe 9:00 na dare suka yi shirin tafiya, lokacin yayah Mohd yake gayawa ummie Abba yace umar, ishaq, hafsy, raliya da ni zamu musu rakiya, da yake flight zamu bi sai yace zamuyi 1week mu taya su shiga sabon gida sai mudawo, gaba ɗaya muka ɗauki murna nida hafsy, ita ma fatima sai taji daɗi, domin dama har ta fara mitan ita kaɗai zataje ta dawo, don itama ta fara ATBU damu, tou anyi idan lokacin school ne zata zauna damu, idan anyi hutu sai ta wuce Abujan, haka muka rakasu wurin motocin su muna ta murna.

Washegari hafsy mukaji muryan mamie tana ta zabga masifa, da ta kwana biyu batayi ba, don tunda aka gama bikin nan batayi wani abun azo a gani ba, sai da hafsy ta fita ta jiyo don tsegumi, tazo tana gaya mana wai akan maganan komawan su yayah Abujah ne, wai Abba ya sake ƙarar da kuɗin shi wurin saya musu gida, ita bata yadda ba su yaya matan ba yaya bane? Nan Abba ya watse ta yace mata gida ba saya akayi ba, rent suka kama kuma kowa da kuɗin shi ya kama, amma

haka ta dinga rantsuwa akan Abba ne yasaya, idan ma kamawan ne shi ya kama, kuma bazata yadda ba, shi kuma yace kada ta yadda ta kaishi ƙara koton ƙulin duniya, sannan tace kuma babu inda raliya zataje, kala taje a cutar mata da yɗa, yadda aka so cutar da habiba a mallake mata yɗa, a nan ne Abba yace mata ita taso shi ya gajji da fitinan ta, shi dai yayi ƙoƙarin haɗa kan yɗayɗan shi, amma tunda ita ta raba ita taso, itace da baƙin ciki gaba ba shi ba, nan mamie ta sake maimaita "raliya fah bazata je ba, kalan idan sun dawo kace suje gidan habiba? Wanda bansan wani sharrin za'a shiga mata da shi ba? Kowa yanzu ya tsaya kan nashi, don baza je a wargaza mun zaman lafiyan yɗa ba, ita kuma wannan da tauraron ta ke haskawa baza'a je a wargaza mata nata, domin an haɗa kai da mutanen borno ae babu abun da bazasu tsayawa mutum ba, anan ne mamah ta fito ta mata jan ido tukun ta koma ɗakin ta.

Murmushi ummie tayi tace ita dama bata saka aranta raliya za'a bar ta taje ba, saboda haka ita ta sani fitina kawai maganan zai jawo, Allah ya kyauta kawai ummi tace, mudai babu abinda ya dame mu shirin kayan mu kawai muka cigaba dayi, muna ciki shirin naga ƙiran M.G na shigowa wayana, kallon waya na tsaya yi ban ɗauka ba, don tun ranan da suka isa Abuja bai sake ƙirana ba, ban san kuma dalili ba.

Har wayan ta yanke ban ɗauka ba, ƙira na biyu ya sake shigowa shima har ya yanke ban ɗauka ba, daga nan bai sake ƙira ba, kallo na hafsy ta tsaya yi, chan dai ta kasa haƙuri tace, "Adda kaman ƙiranki naga Yayah M.G nayi?" kallon wayan nayi ba tare da nuna mata wani alama da zata fahimci komai ba nace, "kinsan shi da son labari yanzu sai ya hanani abun da nakeyi, ni kuma abunda mamie tayi yau na duk ya ɗaga mun hankali bana jin son magana, shi kuma yanzu zai fara tambayan yyh nake me yake faruwa?" na faɗa ina ɗaukan wayar don na maida ita silent.

"Allah sarki Adda ae mai sonka ne yake damuwa da damuwanka, ni kuma wallahi bakiji yadda nake son ki da yayah M.G ɗin nan ba, don ranan ma sai da mukayi ta gulman ki nida yayah ishaq", ta ƙarasa tana dariya, na ɗago kai ina kallon ta cike da mamakinta, "gulma na kuma name kukayi ke da yayah ishaq ɗin"? Dariya ta cugaba dayi sannan ta dawo kusa dani ta zauna, hannun ta tasaka ta dafa kafaɗa na tana magana cike da dariya a fuskanta, "kina rawa yayah M.G yana miki liƙi kukayi bala'in yin kyau, shine yayah ishaq yake tambaya nah saurayinki ne? Nace mishi a'a kawai kuna shiri ne, sai yace Allah yasa shirin ya koma soyayyah don kun dace da shi sosai, kuma wallahi Adda kun dace sosai ga shi kyakkyawa da shi, don ni yafi mun wancan ɗan'uwan shi mai ɗaurarren fuskan", ta faɗa tana wani ya mutsa fuska.

Nidai murmushi kawai nayi bance mata komai ba, don ko ni M.G yana burgeni kuma kyaun shi yana mun kyau, fara'ar shi tana sakani nishaɗi, da fatan nasu zai zama gaskiya da nayi farin ciki sosai, amma dai iya zuciyata na bar abun.

Washe gari muka lula birnin tarayyah mu da yan'uwan mu da matayen su, koda mukaje gidan mai gadi ne ya buɗe mana gate, babu laifi compound ɗin zai iya ɗaukan motoci guda uku, ga flowers masu kyau da ƙamshi a shuke, gidan sama da ƙasa ne, ƙasa shine na Yaya mohd sama kuma yayah Ahmad, da shike kafin biki Aunty B da yayah sun zo sun saka komai a gidan su, amaryah ma anzo an mata mata jeren, kawai ɗan sharewa da gogewa kawai mukayi, sannan aka shimfiɗa bedsheets, a side ɗin yayah mohd muka sauƙa nida fatima da hafsy, su yayah umar kuma hotel aka kama musu, amma munyi hira tare dasu, kuma babu abinda muka girka, order kawai aka mana, washe gari da yammah muna zaune a parlorn Aunty B mukaji buɗe gate da shigowan mota, ba'a wani ɗau lokaci ba yayah Ahmad ya ƙirani a waya yace nazo sama na same shi, ɗaukan ɗan ƙaramin gyalen abayan jiki na nayi na fita.

Ina shiga parlorn shi bakina ɗauke da sallama nashiga, Yayah Ahmad da su M.G nagani zaune a parlorn gaban su cike da kayan snacks da drinks da Aunty J takawo musu, hannun kujeran da yayah Ahmad ke zaune naje na zauna, na ɗaura hannu na a kafaɗan shi na sunkuyo kaɗan setin kunnen shi ina gaishe shi, dariya yayi yana amsa mun, ganin M.G yana kallon mu fuskan shi ɗauke da murmushi, shi kuma A.G ko ɗago kanshi ya kalle ni ma baiyi ba, niko don yau ɗaya na bashi haushi sai na kalli M.G fuskana cike da fara'a nace yayah M.G mun same ku lpy? Shima cike da fara'a ya amsa mun da munzo lafiya? Bayan mun gaisa na juya kan yayah Ahmad ina ce mishi gani.

"Dama M.G ne yace a ƙiraki ku gaisa, shine daman ƙiran, yyh hafsy fa babu wani damuwa ko?" ya faɗa yana riƙe da hannu na da yake kafaɗan shi, murmushi M.G yayi yana kallon mu cike da sha'awa yace, "barrister kuna burgeni kai da yan gidanku, kuna ƙaunar junan ku sosai, har sai naji dama ina da ƙani ko ƙanwa mana, da na nuna mata ƙauna kwatankwacin irin naku, amma insha Allahu zan so mata na irin haka da yaya na", da sauri na ɗago kai na kalle shi, shi kuma ya wani ɗaga mu giran shi duka biyu yana murmushi, sai kawai na samu kaina da maida mishi murmushin.

Baby sis baki gaida A.G ba shine fah ya taso ni akan muzu mu muku sannu da hanya, tun jiya ya matsa muzu naƙi" ya ƙarasa faɗa yana ƙunshe dariyan fuskan shi, "amma wallahi kayi girman banza tunda baka daina ƙarya da ƙazafi ba, munzo dai duba amaryah da ango ba yaran nan marasa kunya ba, bana son jan raini M.G", A.G ya faɗa muryan shi a ɗan cike da ɓacin rai yana hararan M.G, shikuma babu abinda yakeyi sai dariya, yayah Ahmad na tayashi, ni kuma jin abunda A.G ya faɗa sai na maida kallona kanshi fuskana ɗauke da jin haushin yarfen daya mun, harara ya zabga mun, nima ban wani ɓata lokaci ba na zabga mishi harara na murguɗa baki ina guna-guni ƙasa -ƙasa don yaji haushi, ae kuwa nan take ya ƙule, miƙewa

yayi da sauri ya tsaya yana duban M.G yace, "tou ƙaton banza maƙaryaci sai ka tashi mu tafi tunda ba'a abun arziki da kai, yanzu sai kaja yarah su raina mutum", ya ƙarasa faɗa yana zungurin ƙafan M.G.

"wani raini kuma? Daga faɗan gaskiya? Tou shikenan muje kada na sake suɓutan baki", ya faɗa yana miƙewa, hannu ya miƙawa Yayah Ahmad yana dariya shima yayah Ahmad ɗin dariyan yakeyi, hararan su A.G yayi ya juya kaina yana kallo na fuska a murtaƙe, kaman baxai ce komai ba sai kuma yace, "ke baki iya suturce jikinki ba ko?" Ban samu daman bashi amsa ba ya wuce ya fita da sauri, nidai kallon kaina kawai nayi naga shigana baiyi muni ba sannan na maida kaina kan su M.G da yayah, suma kallona suke fuskan su cike da dariya, M.G ne yace "kada ki damu baby sis, yau ɗan'uwa na acike da zafin kanshi yake, tunda aka taso da maganan tafiyan mu karatu hankalin shi baya jikin shi, sai faɗa kawai yakeyi," dariya suka sake kwashewa shida yayah, "ae kasan A.G baya wani son tafiyan nan, shi damuwan shi yayi aure, kuma wai ae nigeria ma ana karatu, shi wajen ne baya son zuwa", yayah yafaɗa yana ƙara dariyan fuskan shi, M.G ma dariyan mugunta kawai yakeyi yace, "ae barrister duk inda ya biyo ya rushe maganan tafiyan nan yayi amma Daddyn shi yaƙi sauraron shi, ƙarshe ma ya ɓuge da wai asthman shi yana yawan tashi idan ya fita waje, nan ma Daddyn yace sai yaje dai, haka babu yadda ya iya ya dawo yace shi tou sai yayi aure tukun ya tafi, Daddy ya tmby shi waye yake nema aje ayi magana nan kuma yayi shiru yana muzurai," dariya suka kwashe da shi suna tafawa, M.G ya kalle ni yace, "baby sis ku shiryah gobe in the evening zamu ɗan zagaya da ku kusha iska" godiya na mishi na juya na fita, ina sauƙowa na samu su fatima na gaya musu gobe idan Allah ya kaimu su M.G zasu fita damu shan iska.

******

Wuraren ƙarfe 5:00pm yayah Ahmad ya ƙiramu a waya mu fito, saboda mun saka fita a zuciyan mu tun muna idar da sallan la'asaar muka shiryah, dukkan mu shigan abayah mukayi, Hafsy onion colour, fatima ash, ni kuma blue black nasaka, ko wanmu tayi kyau masha Allah, motan yayah Ahmad shi da Aunty jeeddah ne da Aunty B sai Areefh da yake riƙe a hannunta, sao motan yayah mohd kuma dama yau ya tafi lagos zaiyi 2dys ya dawo, yayah umar da yayah ishaq sai hafsy ne a ciki, motan M.G kuma A.G nagaba sai ni da Fatima abaya, a tsaye a gaban motan muka samu M.G, tou anan muka gaishe shi fuskan shi cike da fara'an shi, yana ta zolayan mu wai munyi kyau kaman zamuje fadan shugaban ƙasa, mudai murmushi dukkan mu mukayi, muna shiga motan wani fitinannen ƙamshi ne yake tashi mai daɗin

gaske, fatima ce tafara gaishe da A.G, juyowa yayi kaɗan gefen da take, wato bayan sit ɗin driver ya amsa mata mata, nima a hankali na gaishe shi, amma sai yayi kaman bai jini ba, murguɗa baki nayi na masa gwalo ta bayan shi, don nasan yaji tsaf gaisuwan danayi, narasa dalilin daya sa mutumin nan yake jin haushi na, kome na mishi ohoo, mintsini na fatima tayi a cinya tana harara na, kallon tanayi ina tura baki gaba alaman naji zafin mintsinin, alama ta mun da na gaishe shi, hararanta nayi na sake murguɗa baki a ƙeyan shi na ɗaga kafaɗa alaman naƙi, a haka M.G ya shigo, "*JABI SHOPRITE* zamuje kun taɓa zuwa wurin Aysha"? Ya faɗa yana tayar da motan bayan ya ɗan juyo ya kalle ni, murmushi nayi nace mishi, "ehh muna zuwa, yayah mohd yana kai mu ko yayah Ahmad idan munzo hutu", juyowa kaɗan yayi ya sake kallo na yace, "ok kuna zuwa wa Abbah hutu ne? Na ɗauka su ummie ne kawai suke zuwa", "muna zuwa yawanci a ramadan ko idan mun samu dogon hutu", na bashi amsa, kafin yace wani abu A.G yace, "don Allah malam ka maida hankali a toƙin da kakeyi kada ka chika mun kunne da yawan magana",

Murmushi A.G yayi ya maida hankalin shi kan driving da yakeyi bai tanka mishi ba, a zuciyana nace ganshi kaman wani Boss, na ɗan murguɗa baki na cike da jin haushin shi.

Muna gama yin parking kowa ya fito aka jera ciki, bamu shiga wurin shopping ɗin ba muka wuce wurin shan iska, muna isa muka zauna nida fatima da M.G, ina kallon A.G suka zauna suna magana da Yayah Ahmad, gefe ɗaya kuma yayah ishaq ne da hafsy, Aunties kuma suna tare, bamu daɗe da zama ba M.G ya yafito yaya umar, yana zuwa yace "ga amanan fatima ka tayata hira, bari muyi gefe zan yi magana da Ayshaa please", ya faɗa yana miƙewa tsaye, kallon fatima yayi yace "please teemah a bani aron baby sis zamuyi wani shawara ne da ita," murmushi tayi ta ɗan kalli yayah umar da yake zama tace, "babu komai Allah yasa muji shawara mai kyau", murmushi yayi ya wuce ina biye da shi a baya,

Ɗan gefe dasu kaɗan muka zauna, muna zama na ɗago kaina na dubi inda su A.G suke zaune, abun mamaki sai naga ya bimu da kallo, ɗago kan danayi na kallesu yasa shi harara na, nima ban ɓata lokaci ba na murguɗa mishi baki, dariya yaso bani ganin zaro ido da yayi yana ɗaga mun duka giran shi biyu, alaman na raina shi ko, juyar da kaina nayi kan M.G shiru yayi yana kallo na, kaman baxai ce komai ba, chan sai naji ya sauƙe ajiyan zuciya mai ƙarfen gaske wanda har sai da na ɗago kaina na dube shi.

"shawara zamuyi ni dake baby sis, amma kafin nan ina son ki san waye M.G" kallon shi nakeyi bance komai ba, amma dai na maida hankali na gaba ɗaya kanshi, don na daɗe da wannan burin a zuciyata.

MUKTAR GARBA (M.G)

Shine cikakken suna na, gidan mahaifina yana unguwar kobi da ke cikin garin bauchi, mahaifiyata Fatima wacce muke ƙiranta da suna Goggo mu bakwai ta haife mu, yaranta guda shida manyan uwa ɗaya uba ɗaya suke,nine autan su wanda kuma mahaifina daban da su, gaba ɗaya yaranta maza ne, bata taɓa haifan yʼa mace ba, Malam Garba shine sunan mahaifin yayuna wanda nima da sunan nake amfani da shi, malam Garba malamin makaranta ne a *KOBI PRIMARY SCHOOL* unguwa ɗaya suke da mahaifiyata, auren soyayyah sukayi da Goggo, Goggo nah faran macece bafulatana yʼar *KAFIN MADAKI* amma girman garin bauchi, sunyi zaman lpy da mijinta malam Garba da yʼan uwan mijinta sosai, kuma babu laifi suna rayuwar su cike da rufin asiri, Babban wanmu sunan shi

Auwal, sai Sani, Salisu, Rabi'u, sai twins da tayi na ƙarshe wato Hassan da Hussain, gaba ɗaya tsakanin su shekara bibbiyu ne, yʼan biyun suna da shekara biyu mahaifinsu Allah ya mishi rasuwa, lokacin yayah auwalu yana da shekara goma, yayah sani takwas, salisu shida, yayah rabi'u huɗu, yayah hassan da hussain kuma suna shekara biyu, domin an yaye su suna tafiya ko ina da ƙafan su, dukkan su kuma farare ne sol kaman mahaifiyar mu, gashi kowa a cikin su yana hanci tamkar na goggo, sai dai kamanin su ɗaya da mahaifin su, Yayah Hassan da hussain ne kawai suka ɗauko fuskan Goggo sak, mijin goggo ya rasu ne sakama kon ciwon wuni ɗaya tak, a yanda ake bani labarin mutuwan ya bugi jama'an da suke cikin gidan, domin gidane mai girman gaske a kobi, shashi- shashi ne a gidan, gidane daya ƙunshi family dayawa, gashi malam Garba mutum ne na kowa, gashi baida tashin hankali yana zaune lafiya da kowa, bayan rasuwan shi da kwana goma mahajjata suka dawo lafiya cikin ƙasashen su, wanda yayi daidai da dawowan ɗan'uwan shi da suke yʼayʼan bappanu, kuma sun tashi saʼoʼi juna, akwai shaƙuwa mai yawan gaske a tsakanin su, wato *ALHAJI ALKALI ABDULLAHI* haka ya samu jagorancin yʼan'uwa da abokan zumunci har zuwa sa shin mahaifiyar malam Garba, hannun shi riƙe da na yayah salisu da yayah rabi'u, bayan shi kuma su yaya auwal da yayah sani ne ke biye da shi da sauran yʼan rakiya, kuka sosai yayi a ɗakin Inna, domin itama ganin shi sai duk hankalin ta ya tashi tayi ta kuka ana bata haƙuri, alkhairi sosai ya ajiye mata ya koma jaddada mata insha Allahu babu komai zai kula da su, daga nan ya taho ɗakin goggon mu, nan ma ansha kuka ba kaɗan ba, domin tsakanin Alkali Abdullahi da Malam Garba akwai shaƙuwa sosai, duk da yayi kuɗi baida makusanci irin malam Abdullahi, duk da matan shi basu so, domin gani suke ajin mijin su ya wuce na tarayyah da malam Garba, amma furr ya nuna musu basu isa ba, sudai suna zumumcin su, amma matayen su basa zumumci, gara ma uwargidan wani lokaci ta kan leƙo goggo, irin ko anyi rasuwa ko ta haihu ta shigo tayi barka, itama ko suna bata shigowa, amma takan dai ɗan leƙo, ita yʼa ɗaya ta haifah wanda a lokacin ta kai shekara shabiyar, domin Alƙali ya riga malam garba aure, kuma tun da ta haifi yʼarta mai suna safiya ta samu matsala a mahaifanta bata sake haihuwa ba, safiya na da shekara uku Alƙali ya ƙara aure na biyu, ita

amaryar tana isa da izzah domin ita yar cikin fada ce, tana ji da sarauta ita ko ɗaga kai ta kalli mutane da mutunci batayi,

Tana da shekara ɗaya ta haihu ɗa namiji, bayan shekara ta ƙara ɗa namiji, wanda tare aka haife su da yayah auwal, na uku sa'an yayah sani ne shima namiji, lokacin alƙali ya ƙaro wata yar wani Ambasoda tana karatu a Bacas, itama tunda tazo ta haifi nata yara mata guda biyu alokacin, a wannan lokacin ne malam garba Allah yayi mishi rasuwa.

Alƙali yayi kuka sosai ana bashi haƙuri, daga nan ya tafi, bayan tafiyan shi aka shigo da kayan abinci sosai gidan, inna tazo har gefen Goggo ta raba abincin biyu ta ɗauki ɗaya ta barwa goggo ɗaya, daga wannan lokacin Alƙali ya an bawa yaya auwal kuɗi idan an kwana biyu a shigowa goggo da shi, tana arba'in ma ya sake haɗo kayan abinci aka kawo,.

Haka dai rayuwa tayi ta ja har goggo ta ƙarashe takaba, Alƙali bai gajji da hidima da su ba, makarantan da Malam Garba wanda ake ƙiran shi da Baba suka cigaba da ɗaukan ɗawainiyar karatun su yayah na, bayan shekara aka saka su yayah hussain a makaranta, sannan a wannan lokacin Alƙali ya bijiro da maganan auren Goggo, innah kuwa tayi ruwa tayi tsaki ta dage akan sai anyi, domin maganan gaskiya ta hanga ta hango babu wani tsayayye da zai iya cigaba da kula da su irin shi, kuma idan goggo tayi aure duk watsar mata da yara zatayi, don babu mai iya riƙeta da yaran nan, matan Alƙali kaman zasuyi ƙaramin hauka da sukaji maganan auren nan, domin maganan gaskiya Goggo irin kyawawan matan nan ne, wanda kyaun su yake firgita mutum, amma babu yadda suka iya Allah ya nufa akwai rabon haihuwata a gidan dole sai Goggo taje, ya ɗago kai ya kalle ni bayan ya faɗi hakan, nima ɗagowa nayi na kalle shi, amma lokaci ɗaya sai naji jikina yayi sanyi saboda ban taɓa ganin rashin murmushi a fuskar shi ba sai yau, fuskan shi na kallah sai naga kaman shi da A.G yau, kamane bawai kaman hanci ko ido ko wani abu ba, kama ne dai kaman na yanayi, juyar ds kai na nayi na kalli gefen da su yayah suke zaune, abun mamaki karaf idon mu ya haɗe da na A.G, ya ɗan kwantar da kanshi saman kujeran da yake yana kallon mu, yayah Ahmad kuwa suna ta hira da Aunty J, kawar da kaina nayi da ɗan sauri ganin ƙura min ido da yayi, kallon na yar kan M.G, ajiyan zuciya ya sauƙe bayan ya ajiye ruwan da ya ɗauka ya sha.

Ranan jumma'a aka ɗaura auren su a babban masallacin jumma'a da yake ƙofar fadan bauchi, kuma a ranan Goggo ta tare gidan ta, Baba nah yaso goggo ta tare da dukkan yaran nata, amma inna ta hana kan, cewa tayi daga baya za'a kawo yan biyu da Rabi'u, sauran kuma zasu zauna anan, tunda gida biyu ne tsakanin gidan Baba na da gidan mu.

Tunda ga ranan da Goggo ta shiga gidan auren ta bata samu nutsuwa da kwanciyar hankali ba, dukkansu matan gidan da yaran gida haɗe mata kai sukayi suka hanata sakat a cikin gidan, hattah da masu aikin gidan basu ganinta da mutumci ko girma, don ko aikin gidan Uwargida (hajiya hauwa) bata amince a ringa yi mata ba, sannan

yaranta rabiu da yʻan biyu sun sha wahala da dukan gaske a hannun yʻan gidan, har ta kai zaman su yafi ƙarfi a chan wurin Inna, yawanci sai kwanciya ke dawo da su gidan, ranan girkin Goggo kam ma achan gidan mu suke kwana a ɗakin Inna cikin kulawan Yayah Auwalu, Baba na duk yadda yaso ya bada kulawa wa goggo na da yʻan'uwa na abu ya gagara, Goggo tasha wahala a hannun kishiyoyinta har tsawon shekara uku Allah ya nufa ta samu cikina, laulayin da Goggo tayi ya wuce tunanin mai tunani, don ko ruwa bata isa tasha ba sai ta dawo da shi, abun da yake iya zama a cikinta shine ruwan sirki wanda Inna ke aiko yaya Auwalu ya kawo, domin shi kaɗai ne yake shigowa gidan basu hantare shi ba, don shi babu fuskan rainia tare da shi, cikina yana wata uku bai cika huɗu ba Baba na ya saki Goggo, babu wanda ya isa yace ga dalilin shikan, shi dai kawai shigowa yayi ya miƙa mata takaddar saki ya kuma ce yabata wunin yau kaɗai ta tattare kayan ta tabar gidan, a lokacin yayah auwalu yana tare da ita, shiru yayi yana sauraron kukan goggo wanda gaba ɗaya ta rame ta fita a hayyacinta, sai ɗan dogon hanci a fuskanta, fita yayi yaje ya gayawa inna, babu ɓata lokaci Inna ta turo ƙanwar ta inna yʻanbiyu, haka aka tattare kayan goggo aka dawo da shi ɗakinta na gidan Malam Garba, dama akwai sauran kayan ta a ciki har da katifan ta na da, dayake ɗakin ciki biyu ne da parlor a tsakiya, su yaya suna ɗayan ɗakin goggo ta dawo nata ɗakin,abun tausayi tunda goggo ta dawo lafiya ya gagara, laulayi na yau daban na gobe da ban, haka inna yʻanbiyu ta dawo ta zauna da ita, saboda inna tana fama da ciwon ƙafa sosai, cikin goggo na wata bakwai amma bata taɓa zuwa awon ciki ba, domin tun da ta fito Alƙali bai taɓa waiwayan ta ba, lokacin da yayan Baban mu ya tare shi da maganan zuwanta asibiti cewa yayi ba zai iya ba, cikin ma taje ya bar mata shi duniya da lahira, shi sauran yaran da yake da shi ma sun ishe shi rayuwar duniya.

Gidan Alhaji inuwa mai Gwal shine gidan da yake maƙwabtaka da mu ta gefen dama, gida ne da zance duk kobi babu gidan da aka tara yʻan gayu masu tafiya da zamani a gidan, Babban ɗan shi Garba inuwa ma'aikaci ne a banki, lokacin yana ji da tashen samartaka da kuɗi, domin ɗan gata ne a wajen mahaifin shi, don kuwa shi kaɗai ya haifa ɗa namiji kuma babba, sai ƙannen shi mata guda biyu, bai daɗe dayin aure ba yana xaune a fadaman mada, amma duk weeƙand yana gida da amaryar shi wacce ake ƙiranta Aunty Rashidah, ma'aikaciyar asibiti ce mai bala'in tsabta, gata da sauƙin kai da son mutane, gata yʻar masu kuɗi don lokacin idan akace miki gidan mutane a GRA ne tou shi na musamman ne, Goggo na ta iya kitso sosai, lokacin sai surkuwar ta matar Alhaji Inuwa mai suna Dadda tasaka ƙannen Garba suka rakota kitso wurin Goggo, shigowanta wurin goggo taji a zuciyarta Goggo ta mata domin yanayi tsabtar Goggo da haƙurin ta ya taɓa zuciyar Aunty Rashidah, shigowan ta na biyu ta samu Goggo tana jiƙa shinkafan masan ta na gobe, domin Goggo da taji sauƙi sai ta riƙe sana'ar Inna na suyan masa domin su rufawa kansu asiri, ita kuma goggo yʻanbiyu da yake bata taɓa haihuwa ba tana nan tare da su domin kula da inna.

Sun zauna yin kitso Aunty Rashida ta tambayi Goggo a wani asibiti take awo? Murmushi kawai Goggo tayi ta gyara ta fara tsaga kanta domin kitse mata shi, har suka gama yaryara kitson goggo bata ce mata komai game da maganan awon cikin ba, har sai da zata fita tacewa Goggo gobe idan anyi masan zata turo driver ya karɓa musu da yake sunday ne, sannan ta miƙawa goggo kuɗi mai ɗan kauri tace ta shiryah taje asibiti domin fara awo, cike murna goggo tayitq godiya, wanda har inna da inna yanbiyu suka fito suna tayata, idon inna cike da hawaye take duban goggo da take ta share hawayen da yaƙi tsaya mata a idon ta.

****

Ai kuwa ranan monday goggo batayi aikin masa ba tabarwa su inna ta wucce asibiti, haka ma'aikatan sukayi ta mata masifan rashin zuwa da wuri, ita dai bakin ta shiru sai ido da take bin su da shi, bayan angama komai ta fito zata dawo gida suka haɗu da Aunty Rashida da ta fito gaisuwa cikin asibitin specialist ɗin, ganin goggo na ta sauri zata tari abun hawa domin tafiya ta tsayar da ita,

Goggo fuskanta ɗauke da murmushi ta tsaya suna gaisawa, murmushi daya kasance nida yan biyu mu muka ɗauke shi, domin ni ba sosai ake gane abun da yaɓata mun rai ba kamar Goggo na, don fudkan mu kullum ɗauke yake da mirmushi, wannan kuma ba wani abu bane na daban halittah ne da Allah ya kanyi mutum da shi, bawai rashin aji bane ko kamun kai, kawai halittah ne na ubangiji, ya faɗa yana duba na alokacin fuskan shi ɗauke da murmushin, nima murmushin nayi ina sunkuyar da kaina ƙasa, don samun kaina nayi da jin kunyan shi mai girman gaske *Aunty nice* ga shi murmushin shi wani irin kyau yake ƙara mishi, gaskiya *Aunty nice* M.G mai kyau ne, kyaun da idan kina kallon shi zakiji zuciyar ki tana samun nutsuwa na musamman, gashi M.G mutum ne mai zuciya mai kyau.

Murmushi nayi ina kallon fuskan hajiya ayshaa da take wani lumshe ido tana buɗewa cike da yanga, daga alama kuma zuciyar ta ba ƙaramin so takeyi wa M.G ba, domin sunan shi kawai idan ta ambata sai naga fara'a a kan fuskarta.

Kallon shi nayi ina ƙara jinjina labarin a zuciyana,

Ayshaa muna unguwa ɗaya da mahaifina amma ban taɓa sanin shi ɗin mahaifina bane, ni har nakai 11yrs ban san shi mahaifina bane, kuma baa taɓa barina na shiga gidan ba, domin yayuna sun razana ni da shiga gidan, yaran gidan ma basu shiga gidan mu, abun da nasani dai akwai wata mata mai aikin su masifaffiya da take shigowa gidan mu, domin bayan tafiyan yayah auwal sai abubuwa sukayi yawa

wa goggo da innah, gashi kitson ya ɗan ja baya a hannun goggo saboda ta fara girma, an fi zuwa wurin yarah, ita sai ɗaiɗaiku ne suke shigowa irin su Aunty Rashida, dole goggo ta fara karɓan surfen gero na kunu, idan tayi tana dakan hannu na garin kunun, wannan yana kawo customers dayawa, amma goggo tana shan wahala sosai, dole ta haƙura da masa yayah sani da yayah Rabi'u suke hidiman innah yɗan biyu na taimaka musu, alokacin kuma su hassan sukan fitar dashi da safe su sayar, ni kuma ina riƙe da ƙaramin ruban kananzir ɗin inna, Allah yayi mu da hanzari, muna sayarwa zamuyi gudu- gudu muyi shirin makaranta, tanayi, abun haushin kuma Baba na yana son kunun tsamiya na dakan hannu, tou wannan mai aikin ita ke shigowa da shi takawo goggo ta daka su bata kuɗin, kuma goggo bata taɓa nuna baxata yi ba saboda tana samun kuɗinta chass idan tayi, (wannan labarin true life story ne, kada kuji haushina akan abunda goggo takeyi na ƙasƙantar da kanta na aikin gidan tsohon mijinta, hakan ya faru ne, wasu abun ma zafin su yasaka na cire su a labarin,).

Ana shirin kama azumi gidan Baba na aka aiko wake buhu guda da geron da goggo zata gyara musu, haka ta haɗa kan yayah sani, yayah rabiu da ita kanta sukai ta aikin surfe wake suna gyarawa, tsaf ta gyare shi ta zuba a wasu boketai da aka bayar ta zuba, sannan tayi aikin geron shima tsaf ta haɗa garin kunun kafin afara azumin, wannan masifaffiyar mai girkin gidan Baba na ita tazo da wasu samari biyu suka ɗauki kayan, sannan wannan azumin babu gidan da Baba na bai aika kayan azumi ba sai gidan mu, haka sallah yazo yayi hidima wa maƙwafta da yɗan'uwa da abokan arziki amma banda mu, bana mantawa wannan kuɗin da goggo ta haɗa da shi ta mana kayan sallah, wani yadi wai shi Bambalasta shi tasaya mana, ruwan ƙwai, ranan sallah mukayi wanka mukayi tsaf da mu, nidai sai murna nakeyi bakina a buɗe ranan ina dariyan daɗi, domin idan naga yadda yadin yake wani walai-walai sai na ƙara jin farin ciki, haka mukaje ɗakin inna wanda tun tsakiyar azumi bata ji daɗin jikinta ba, muka gaisheta mukayi mata sallaman zamu wuce masallaci, hannu ta miƙo mun, gaban ta naje na tsuguna, a hankali ta dafa kaina tace "ubana Allah yayiwa rayuwar ku albarka, ayi haƙuri da rayuwa da yadda tazo, duk cikin yaran nan kai nake tausayi babana, idan anje masallaci ayi addu'a",

Murmushi nayi ina duban ta nace, "zan miki addu'a ki samu sauƙi innah" itan ma murmushin tayi ta ɗan juyar da kanta inda yayah sanie yake tsaye tace, "Auwalu idan yayi waya a gaishe shi ku mishi biyayyah banda raini, auwalu ubane", haka muka fita zuwa masallaci,

Bayan an sauƙo an dawo gida duk unguwan mu labarin kayan da yaran Alƙali Abdullahi suka saka kawai akeyi, don har wani kallon su aka tsaya anayi, saboda wancan lokacin ba kowa bane yake sayawa yaran shi kaya masu tsada, amma su baban mu komai yi musu mai kyau yakeyi.

Hannu na riƙe dana yayah rabiu muka tsaya muma abakin titi muna kallon yaran alƙali, akwai wani ɗan shi masifaffe, babu abunda na mishi kawai naji ya zabga mun ranƙwashi ƙwaff akaina, "shege da ido kaman na tsohon maye, ka wani zurawa mutum su", ya faɗa yana ƙara shambe ni da ƙafan shi, ihu nasaka da ƙarfi ina rungume yayah rabi'u, hannu na yayah rabiu yaja muka fara tafiya yana tacewa saurayin "Allah ya isa da ka doka mun ƙani, kuma wuta balbal a kabarin ka", juyowa ɗan gidan Alƙalin yayi zai daki yayah Rabi'u sai abokanshi suka riƙe shi, ɗayan yana cewa "haba mana Tijjani yaron nan kam ba ƙanin ku bane? Kuma naga bai maka komai ba ka dake shi, ba girman ka bane, wuce mu tafi", ƙwafa Tijjanin yayi sannan ya juya suka tafi mu kuma muka dawo gida ina ta kuka, yayah hassan da yayah hussain suna ta lallashi na.

Muna shiga gida muka samu yayah sanie zaune a gefen goggo yana cin abinci, cikin sanyin shi da sanyin maganan shi ya tambaye su meya sameni? Nan kuwa hussain ya zayyano mishi duk abinda ya faru kaman zaiyi kuka, hannu yayah sanie ya miƙo mun, gefen shi na zauna yana ta lallashina, sai da yace mun zai saya mun chinchin ɗin shagon tela tukun nayi shiru, abinci goggo ta zuba mana nida su yayah hussain tace na zo muci, bana wasa da abinci a rayuwa na Ayshaa, shiyasa naji na huce daga ranƙwashi mai zafin da yayah T.J yayi, ballantana na hango nama akan shinkafar da goggo ta dafa mana, dariya nayi ina kallon M.G cike da tausayin shi, shima dariyan yakeyi domin naga alaman ya tuna wannan lokacin ne sosai.

"Ayshaa wato na taso ina son abinci especially idan naga namomi akai, amma alokacin Allah bai bamu ba, idan naje gidan su A.G abinci ne cike fal da nama, gashi kakan shi Alhaji Inuwa mutumin kirkine shida kakar A.G, haka zasuyi ta fama dani naci amma ina nasha kwaɓa da training ɗin yayah auwalu, bana iya ci, sai dai nayita haɗiyan yawo, idan kinga naci tou A.G ya biyoni gidan mu da abincin shi wai muci tare, mu kuma abincin mu yawanci kwaɗon garin kwaki ne, ko ƙanzon da goggo ke tarawa na matan dake cikin gidan mu yan'uwa, idan kinga sakekken abinci tou tuwo ne ko kuma gwaten tsaki, sai ɗanwaken dawada alabo da ake mana, amma Ayshaa komai mukayi A.G yana ci, idan ya kawo abinci hankalin goggo ya tashi ta rasa yadda zatayi da shi yaci shi kaɗai, amma fir sai yaƙi yace shi da aboki zai ci, saboda A.G shi yasaka mun sunan aboki tun bamu fi 3yrs ba, idan zasu tafi yayi ta ihun da aboki zai zauna, har nima nafara ƙiran shi da aboki, yanzu kuma yakance M.G aboki, ko M.G friend, ni kuma nace mishi A.G friend ko A.G aboki.

Sai da innah wata rana tayi goggo maganan tayi haƙuri ta barmu muci abincin mu tare, rabo nane ya tsaga ana su shiyasa Allah ya haɗa kanmu, nan inna take cewa goggo, ae shi Mukhtar abun tausayi ne, bai taso ya samu kulawan da yara suke samu daga iyaye na daɗi ba, yayun shi malam Garba yayi iya ƙoƙarin shi, saboda haa ta barmu kada a tauye ni dayawa, sannan goggo ta haƙura, idan yazo sai a fara cin nawa, nan kuwa A.G zaici sosai yana jin daɗi, ballan tama idan goggo taɗan yaryaɗa mana mangyaɗa ta ƙara yaji akai, idan munzo cin nashi wataran nama kusan shida, takwas ake zubawa akai, haka zakiga yayah hassan da yayah hussain

suna fakaitan idon goggo suna ɗan miƙa mana hannu, na dinga musu dariya ina ɓincina musu nama kaɗan, amma sai kiga A.G ya basu ɗaɗɗaya wataran har yayah rabi'u, ni kuma na cinye nawa,

A.G ya soni, iyayen shi sun soni da kakanun shi, babu abunda bazan iya yiwa A.G ba arayuwa idan bai saɓawa addini ba, a wannan shekaran Daddyn A.G ya dawo ƙasan, kuma a wannan lokacin Allah ya karɓi ran innah, munyi baƙin ciki da kewan innah, goggo tayi kuka har sai da ta kwanta jinya, sannan rayuwa ya sake yiwa goggo ƙunci, bayan anyi sadakan bakwai kuma wani mummunan labari yazo mana na tashin su A.G zuwa London inda daddy yayi karatu ya samu aiki, duk da ƙanƙancin shekaruna naji zafi da ciwon tafiyan su A.G, ranan da zasu tafi sai da nayi kuka, shima A.G ihu ya dinga yi yana abarshi a wurin aboki, rarrashi akayi ta mishi sannan suka tafi, wannan ranan dole a gidan Alhaji inuwa na kwana, domin nayi kuka har saida nayi zazzaɓi, haka kakar A.G tayita lallashi na, da taji jikina akwai zazzaɓi sai tace wasu yayah Rabi'u sucewa goggo zamuje asibiti, da muka dawo ma ta barni na kwana a wurinta, da safe da kanta ta mun wanka ta saka mun kayan A.G da mummy ta bar mun su dayawa, har da su school bag ɗinshi.

Rayuwa tayi mun babu daɗi, babu innah babu A.G, duk wani abun dsɗi da innah ta samu sai ta ɓoye mun, ko jikokinta bata bayarwa saboda tausayina take ji, sannan akwai balbalin ɗan wan mijinta da yake da ɗan dama-dama a cikin gidan, shima ba wani sosai badai, amma yafi mutane dayawa a cikin gidan, tunda shi akwai T.V a gidan shi kuma suna ɗan kunna generator, yakan sakawa inna abinci rana da dare, kuma shi sukanyi shinkafa sukanyi taliya da su doya, saboda matar shi ma malamar makaranta ce, babu laifi sukan ci abinci har da salak, tou Inna bata cinyewa, sukanci da inna yanbiyu, sannan takan ɗiba mun nida su hassan da hussain, sai dai ni takan ƙara mun, idan kuma an saka nama ko kifi tou wannan nawa ne, ko ita bataci.

Ayshaa innah ta mun so da gata da bazan taɓa mantawa ba, burina da fatana na saka sunanta cikin yayana, sannan na saka yayah auwal nasaka A.G, ya faɗa yana kallo na, murmushi nayi nace Goggo fah?

Shima murmushin yayi ya kama haɓa yace, "Inna, Goggo, mummy, sune sunan yara na mata, A.G, yayah auwal, yayah sanie, rabiu, hassan da hussain, Abdullahi (baba nah) Abubakar (baban mu) duk insha Allahu sai nayi" ya faɗa yana dariya, nima dariyan nayi nace, "kace mata huɗu zakayi kenan"?

Girgiza kai yayi yace "mata ɗaya shine burina, sai dai idan banyi dace ba na ƙara wata, ballantana ma insha Allahu zan dace, yaran babu yawa fah Ayshaa, mata uku, maza 7, yara goma ne fah" zaro ido nayi nace sunyi yawa ae yayah M.G wa mace ɗaya, sai dai biyu kowa tayi biyar - biyar".

Murmushi yayi ya ƙura mun ido, "tou a shawaranki da zaki bani mata 2 kenan zanyi? Hakan ya miki?"

Hararan shi nayi cikin wasa nace " nidai babu ruwa na bance ba, kalan matar kan taji haushina idan kace ni na baka shawaran kayi mata biyu",

Kallo na yayi yana murmushin shi mai kyaun nan, "a misali idan kece zaki iya haifah mun yara goman babu ƙorafi da ragwanta"?

Ɗago kai nayi da nufin magana amma kallon da yake mun ya saka na maida kaina ƙasa da wuri ina riƙe wayana da ɗan ƙarfi, baki na turo gaba nace, "ni kuma yayah? Ni ae bazan iya haifan yara da zasu wuce uku ba, kuma ni ae kaiyayah nane", murmushi yayi mai sauti yace, "tou ae yayah yana iya auren ƙanwa, kenan misali idan ke zan aura dole mata uku kenan zanyi?" kallon shi nayi da sauri nace "uku kuma?"

Girgiza kai yayi yana murmushi yace, "uku mana sisto, ke kiyi uku, ta biyu tayi huɗu, ta uku tayi uku, ko kuma suyi biyar biyar saboda suma su saka sunan nasu iyayen",

"Nidai bana son kishiya, kuma wallahi yaran sun maka yawa", na faɗa ina juyar da kaina gefe saboda haushi ya bani da yace mata uku zaiyi, dariya yayi sosai yana kallo na, " wato Aysha baki son kishiya ko? Lallai ko idan nine mijinki sai kin daure kin haifi dozin, nawa goma naki biyu, sai dai idan cin girma zanyi na barwa ƙanina A.G, don shima irin ki ne mai raki, yarah uku zuwa huɗu yace mun yake so, don baya son hayaniya, kinga tsarinku zaizo iri ɗaya kenan".

 "Haba yayah M.G idan zaka mun fatan aure ae baxaka mun fatan wannan abokin kan ba, wannan ae kullum sai ya daki mace ae daga alaman shi, kuma mutum baya fara'a bai magana, wacece zata iya zama da shi"?

Dariya ya kwashe da shi yace, "tou ae kema baki yawan magana, kinga ae kunyi daidai kenan, gidan zaiyi daɗin zama kuma", ya faɗa yana dariya.

 Tura baki gaba nayi nace, "ni yayah duk da bana yawan magana ae ina son hira, kuma ni ina murmushi, amma shi fa? Ni dai ka daina kwatan tani ma dashi, don tsoro ma yake bani, wannan ae sai...." sai kuma nayi shiru ganin shi yana tahowa inda muke, dukkan mu shiru mukayi, M.G ya ƙura mishi ido ni kuma na sunkuyar da kaina ƙasa,

"Friend ya kamata mutafi numfashi na yana mun wani iri, "

Ɗago kai nayi da sauri na dube shi cike da tausayi, amma sai ya hani manna mun hararah, gashi kuma numfashin shi yana jan shi da kyar, da sauri M.G ya miƙe tsaye yana riƙo hannun A.G ɗin, "aboki ina inhelar ka"? Ko akwai ƙura ne a wurin"?

Murtuƙe fuskan shi kawai yayi baice komai ba, duk sun maida kallon su inda yayah Ahmad yake tahowa, bayan ya iso yake sannu wa A.G, sannan yace ya gama clearing bilƙ ɗin su taho mutafi, ae magrib ya gabato shi yasa ma numfashin yake haka, ga sanyi yana sauƙa, nima miƙewa nayi jiki na a sanyaye, ga labarin da M.G ke bani ga kuma yanayin A.G dana gani, gaba M.G yayi yana danna wayan shi alaman doctor yake nema, shima yayah Ahmad juyawa yayi ya nufi inda su Aunty jeedah suka miƙe ana shirin tafiya,

Tafiya nafarayi sai naji muryanshi yace, "idan kin koma ki dafa mun lipton mai kayan yaji", juyowa nayi na dube shi, sai naga ko kallo na baiyiba wayan shi yake dannawa, sai bance komai ba kawai na wuce gaba zuwa wurin su Aunty.

Koda muka isa gida kowa haraman sallah ya fara, muna idar wa fatima ta juyo tana kallo na, batace komai ba sai ido da ta zuba mun, gajjiya nayi da kallon nace, "wannan irin kallon fah teemah"?

Murmushi tayi ta ce, "naga alaman M.G yagama tsaraki kin tsaru yau, don naga sai wani annuri ne ke fita a fuskar ki,"

Nima murmushin nayi na girgiza kai na, "wallahi babu wani tsari teemah, kawai labarin rayuwa mukeyi, amma ba abun da kike tunani bane ya faru", ina gama faɗan haka na miƙe tsaye ina naɗe hijab ɗina, bana son mucigaba da zancen don banyi niyyan sanar da kowa yadda mukayi da M.G ba, don wannan sirrin shi ne kuma bai gama gaya mun ba, sannan bansan maƙasudin zaman namu ba ballantana har na fara isarwa wani, sai na chanja topic ɗin maganan da, "teemah kunyi waya da maryam ne yau da muka fita?" "eh ta ƙirani wai wayanki akashe, sannan hadiza ma ta ƙira" muna cikin maganan hafsy ta shigo, wani kallo ta ke mun na alaman gulma na muntsininta, bana so ta sake jawo wani magana sai na yi hanyan fita na bar ɗakin, parlor naje gefen Aunty na zauna kusa da ita, kallo na tayi tana murmushi tace, "yʼan matan ummie yyh akayi?" murmushi nayi na kalleta nace wai wannan abokin yayah Ahmad ɗinnan ne wai na dafa mishi tea, ni kuma wallahi maganan su teemah da hafsy ne bana so, don Allah Aunty kice wa ke zan dafa".

Dariya ta ɗanyi kaɗan tace, "babu komai bestyn husby na, bari su fito sai nace ki dafa mun tea ki kuma zubawa jeeddah a flask, kinga sai ki ɗauka kaman zaki kai mata sai ki kai mishi, amma yyh ake ciki akwai wani update ne"?

Murmushi nayi na girgiza kaina nace, "Aunty babu komai fah wallahi, ni bamu cika wani shiri bama da shi, kinsan baida lafiya yana da asthma, inaga shiyasa yake son shan tea ɗin", ina rufe baki su teemah suna fitowa, basu wuce minti biyar ba Aunty ta umurceni da na dafa mata tea, idan nagama kuma na zubawa Aunty J, yadda dai muka tsara, haka na tashi naje na haɗa na dafa shi tsaf sai ƙamshin kayan haɗin su na yʼan maiduguri yakeyi, sannan na haɗa sandwich, M.G kaman yasan nagama

abunda nakeyi sai ga call ɗinshi, ina ɗauka yace gasu nan a parlon yayah Ahmaɗ shi da A.G.

Ajiye musu basket ɗin tea ɗin nayi akan center table ɗin da yake gaban M.G, Kallo na yayah Ahmad yayi yace ki zubuwa A.G shine zai sha, fatan dai kin saka kayan yaji ko? Ɗaga kai kawai nayi batare da na buɗe baki na amsa ba, har gaban A.G ɗin naje na durƙusa na ɗauki cup na zuba mishi sannan nasaka sandwich ɗin a kan wani plet, na miƙa mishi, kallo na yayi fuskan shi ta nuna alaman yana shan wahala, don har wani ja tayi ta kan hancin shi, murya ƙasa-ƙasa naji yace, "ki ƙara mun sugar" kallo na sake binshi da shi "na saka sugar fah sosai, taɓa kaji", eyyh kallon yau babu masifa da harara a ciki, sai mai da kanshi yayi ya kwantar ya lumshe ido, nidai ina kallon shi da cup a riƙe a hannu na, sai naga kaman numfashin yana jan shi a hankali a ƙasan ƙirjin shi, duk sai naji ya bani tausayi, murya ƙasa - ƙasa wanda babu wanda zaiji sai shi nace, Yayah A.G sannu, ka tashi kasha tea ɗin kada yayi sanyi",

Buɗe ido yayi a hankali ya ƙura mun sannan yace, "nace ki ƙara mun sugar kinƙi, bazan iya sha babu sugar sosai ba", da sauri na ajiye cup ɗin na ƙara zuba spoon ɗaya, bayan na gauraya shi na miƙa mishi, hannu ya saka ya karɓa, ina kallon shi daya kurɓa ya ɗan runtse idon shi, a hankali yake shan tea ɗin, cike da tausayi na miƙa mishi bread ɗin, babu musu ya saka hannu ya karɓa, shima a hankali ya ke gutsura, abun mamaki naga yaci har biyu, sannan ya shanye tea ɗin, rufe ido shi ya sakeyi yayi shiru, naga shirun yayi yawa gasu yayah Ahmad suna zaune akan dinning shi da M.G suna cin abinci suna ɗan taɓa hiran su, sai na miƙe zan tafi chan side ɗin yayah muhammad kawai sai naji muryan shi yace, "ki ɓalla mun maganin nan nasha plz", juyowa nayi na kalle shi, amma har lokacin idon shi a lumshe yake, tsayawa nayi shiru kaman bazan ce komai ba, sai kuma na ƙarasa inda yake na sake durƙusawa daidai inda gwaiwan shi suke na miƙa hannu na karɓi satchet ɗin maganin da yake miƙo mun, dubawa nayi naga guda ɗaya zan ɓalla na bashi, cike da mamakin shi wato ɓalla maganin ma bayajin iyawa, ko kuma samun wuri ne oho, haka dai na ɓalle mishi na buɗe baki nace "gashi", ɗagowa yayi idon shi duk sunyi kalan tausayi, hannu ya saka ya karɓi maganin, idon shi na kaina yace "ruwan ma sai nayi tambaya"? Juyawa nayi na ɗauko goran ruwan da nasan Aunty j ne ta kawo musu da drinks ɗin, zuba mishi nayi a cup na miƙa mishi, idon shi yana kaina ya saka hannu ya karɓa, bayan ya shanye ya sake yin shiru, ni kuma ganin yayi shiru ya saka na sake niyyan miƙewa don na tafi, "ban sallameki ba tukun madam" ya faɗa yana ƙura mun idon shi.

Turo baki nayi gaba alaman na gajji,

"gobe insha Allah by 9:00pm tafiya na school, akwai wani abu da kike so?"

Da sauri na ɗago kaina na dube shi, bansan yayah akayi ba naji bakina yana furta, " gobe kuma? Wani irin school kuma? Tafiya zakayi kabar Yayah M.G shi kaɗai?".

Ido ya ɗan ƙura mun kaman mai nazarin wani abu, chan kuma sai ya ɗaga kai ya dubi M.G na wani lokaci sai ya dawo da kallon shi kaina, duk yanayin shi sai naga ya canja, wannan ɗaurewa da masifan sai naga kaman babu su a yau, "M.G ne kawai damuwan ki? Baki tunanin ni yayah zan kasance? M.G kawai kike tsoron ya shiga wani yanayi bani ba ko?" ƙasa yayi da fuskan shi har dab da fuskana, a hankali naji ya furta, "ke baki da damuwa da tafiyan da zanyi ko? Zan daɗe fah, amma duk bai dameki ba sai M.G ne damuwanki ko"?.

Yana gama faɗin hakan ya miƙe tsaye bai sake duba na ba ya wuce direct hanyan waje, da sauri naga su yaya Ahmad sun miƙe suna tambayan shi jikin ne? Girgiza kai yayi alaman a'a ya fice a parlon, sallama M.G ya mun ya bi bayan shi, shima yayah Ahmad yabi bayan su, ajiyan zuciya nayi jikina duk yayi sanyi, tou ni mai nace mishi wanda baiyi dai-dai ba? Duk sai naji hankali na yayi mummunan tashi, ga wani yankewa da naji zuciyana yayi, haka na daure naja ƙafana na koma wurin su Aunty B.

Lokacin da na shimfiɗa kafaɗa na a gado sai na neme bacci na rasa, ina jin fatima da hafsy suka gama wayoyinsu suka kwanta, amma ni nakasa bacci, kuma ba komai bane ya hanani bacci sai yanayin da A.G ya fita a ɗazu, narasa tausayin shi nakeji ko me? Ko ganin baida lafiya amma kuma zaiyi tafiyan a haka makeji oho, ko kuma barin M.G da damuwan da M.G zai samu kanshi ne nake ji oho, nidai ranan ban samu nayi bacci ba har wurin sallan Asubah, saboda haka muna idar da sallah nace musu kaina yana ciwo, haka suka rabu dani na koma nayi bacci, ban tashi ba sai wuraren ƙarfe shabiyu na rana, ina tashi wanka na shiga sannan na fito parlor na gaida Aunty B, nan na samu suna ta kiciniyan haɗa girki domin 2:00 yayah muhammad zai iso, sai wani shirye-shirye Aunty B takeyi kaman wani tafiyan shekara guda yayi, duk an share gidan an baɗa mana ƙamshin su na borno, hattah Areefh yasha gayu, a lokacin hafsy ta matsu kusa dani tace , "Adda yau fa zuwan su yaya M.G biyu gidan nan neman ki, ya ƙira wayan ki akashe," kallon ta nayi nace, "shine baki tashe ni ba hafsy? Shi kaɗai ko su biyu"?

"su biyu suka zo Adda, ae yace na tashe ki a zuwan su na biyu, sai kuma ɗayan ɗan'uwan shin yace a barki tunda nace kanki ne yake ciwo, amma yace ki ƙira shi idan kin tashi", tana gama gaya mun yadda sukayi na juya na koma ɗaki domin kunna wayana, haka kawai naji ina so nasan yayah suke, kuma lafiya suka zo har sau biyu nema na?.

Ina kunnawa wayan maryam na shigowa, raina a ɗan jagule na ɗauki wayan, "besty meye haka ne, tun jiya nake ƙiranki wayan ki akashe, sannan nace ki ƙirani shima shiru, monday fah zamu koma school kunje kun rashe, baza ku dawo bane kam?" ta faɗa ba tare da jiran mun gaisa ba, ajiyan zuciya na sauƙe domin ganin wayan

M.G da yake shigo mun, "besty yi haƙuri bari na ɗauki waya don Allah", katse wayanta nayi na ɗauki wayan M.G.

"Ayshaa wa kika samu haka?" gaishe shi nafara ba tare da na bashi amsan tambayan shi ba, shima bai bi takan tambayan da yayi mun ba, kawai ya shiga tambaya na yayah jikina? "da sauƙi" na bashi amsa, "Ayshaa munzo sau biyu kina bacci, dama A.G zai miki sallama ne, kin san da tafiyan shi a nan abuja ne, sai ga shi kuma ya koma ta lagos, kuma flith ɗin shi 1:00 ne, so yanzu ma muna hanyan airpot," "ina yayah A.Gn"? Kawai nasamu kaina da tambayan shi, bai jira me zance ba kawai ya miƙawa A.G wayan, baice mun uffan ba da ya karɓi wayan, amma dai nasan ya karɓi phone ɗin, saboda yadda nake jin fitan numfashin shi wanda bai daidai tu ba har yanzu, nima shirun nayi bance uffan ba, har zuwa wani lokaci sai naji yace, "yayah akayi"? Ajiyan zuciya na sauƙe da ƙarfi sannan nace, "yayah numfashinka", shiru na sakeyi, shima yayi shirun na ɗan wani lokaci, kafin chan yace, "shine damuwan ki?"

"a'a ni bashi bane",

"meye tou"?

Sai da naja lokaci mai ɗan yawa kafin nace, "Allah ya kiyaye hanya, ka kula don Allah",

"Hmmm" kawai yace sannan ya miƙawa M.G wayan, sallama M.G yamun akan sun iso zasu shiga ciki, idan ya dawo zai neme ni, mukayi sallama na kashe wayan, tagumi nayi da dukkan hannu na biyu, ban ankara ba sai naji dariyan hafsy, juyowa nayi da sauri na kalle ta, ashe tana zaune akan gado ta ƙura mun ido, tambayanta nayi yaushe ta shigo, tana dariya tace mun tun lokacin da nake soyayyah ta shigo, lokacin idona a rufe ban sani ba, hararanta nayi na fice a ɗakin.

Washe gari muka koma bauchi cike da tsaraban mu da su Aunty j da Aunty B suka bamu, gefe ɗaya ga wani shooping na ban mamaki da M.G ya kawo mun, su fatima ma nasu daban,.

Muna komawa da 1week muka koma sch, kuma a wannan lokacin maryam tayi sabon saurayi likita ne mai suna Dr Abdoul, yana aiki a T.H, sunje da mamanta ne bata da lafiya Allah ya haɗa su, haɗuwan su da Dr ya fara kwancewa maryam lissafi da soyayyah, gashi lokacin ma zainab ma ta haɗu da wani ma'aikacin banki mai suna Abdoulmaleek, ɗan gayu ne shima sosai, hadiza tana nan da suraj ɗin ta, haka fatima ma tana nan tare da kabir ɗan maiduguri, da yake duk munyi addn ɗinsu a cikin group ɗin mu, sai ya kasance 9:00 na dare sai mun haɗe a group ɗin ana zuba chafter, yanzu dai ya kasance nice ƙwalli ɗaya banida ma shinshini, don yau mun haɗe an saka zainab a gaba da tsokana, duk da rashin maganan ta da baƙin halinta yau sai da tanka har da dariyan ta, domin sunan da mukaje tana gayawa Abdoul

ɗinta wai handsome, duk tsiya muka fara mata anata voice note ana shan dariya, da taga abun ya mata yawa sai ta mayar da chaftern ta kaina, "tou ke ayshaa har yanzu baki samo mana naki gwanin bane? Ko rawan ido irin na yaran GRA kikeyi ne"?

Jammy ce ta bata amsa dacewa, "wan irin rawan ido kuma? ae kinsan da badan wani dalili ba da yanzu besty na gidan auren ta, gwaninta special ne zai zo, duk da teemah ta ɗan tsegunta mun wani lafiyayyen soyayyah da akeyi a ɓoye", ta faɗa tana ƙyalƙyala dariya, sticker na zaro ido teemah ta turo, irin yyh akayi jammy ta tona mata asiri, nan kuwa zainab tafara tambayan waye?, haka mukai ta sharhin mu har 10:00 tayi, daga nan maryam tace zatayi waya da luv, hadiza kam dama bata daɗe ba ta mana sallaman cwit yayi ƙira, haka dai ta ɗaɗɗaya aka watse, sai ni da jammy ne ƙarshen sauƙa, bayan munyi sallama na koma na kwanta nayi shiru ina tunanin habiba, yanzu wasa gaske duk wani alaƙa da muka taso a ciki da ita ya rushe? Duk irin wannan yanayin idan ya faru ita nake tunani, gashi duk wata alaƙa dake tsakanin mu mamie ta bunne shi, ganin tunanin zai mun yawa sai na tashi na fito parlor nayiwa ummie nah sallama na wuce side ɗin hajiya ummah, ina shiga parlor na samu yayah ishaq da ummitah zaune a parlon suna hira, hjy ummah kuma tana fitowa da ga ɗakinta kenan, gani kuwa ta wani kalloni tana ya mutsa fuska, "jirgin danƙaro an ƙaraso ne"? Ko kulata banyi ba na wuce kan dinning ɗinta ina haɗa tea, "tou baiwar Allah idan kinji haushi yau naji ance ga wani yazo wurinki hira mana, kuma da baki so na faɗa kin wani haɗa fuska kinje kina ɗiba mun kayan shayin da ɗana ya saya mun don gadara ko? Tou daɗinta na nan gidan ɗana ne halak malak ba na wani ba, ballantana anuna mun iko", ta na gama faɗa kuwa hafsy ta juya kanta tana cewa, "kaji mun mata wai gidan ɗanta? Tou ae munfi iko da gadara akan gidan da komai na gidan, mufa nan gidan mahaifin mune",

Hararanta hajiya ummah tayi, baki agaba tace, "kaji marar hankali, tou ke idan an barki sai ki ɗauka ke wata abarce a wurin shi? Tou ae shi usman daba don farin cikina ba don ƙaniyar ku da duk ya maida ku zaman tafawa ɓalewa, duk kuje ku saje da su hadiza", dariya dukkan mu mukayi, yayah ishaq ya miƙe yana dariya yace, "ni wallahi surutunki ma ya ishe ni, duk kin takura ni kin hanani ƙarasa I Luv u na, bari na tafi ma na bar miki gidan, gidan da ba malam umaru bane yayi amma ake damun mutane da gadara", kafin ya ƙarasa hanyan fita hajiya ummah ta jefe shi da kofin hannunta, "ɗan banza mai wargajejen baki kaman na ubanshi, ae abunda malam yayi har ka mutu bazaka iya ba, har wani gida ne Usman yayi na nunawa a duniya wanda malam bai yi shi ba? Ja'iri ni irin gatan da malam ya nuna mun ni da ƴaƴana ae ƙaryan Usman yayi shi, har kuna wani ɗagawa gaku ƴaƴan wani ko"?

Dariya muke mata gaba ɗayan mu, don dama ƙarshen faɗan kullum haka yake komawa, ana taɓo mijinta zata koma kare shi, dariya yayah ishaq yayi ya fice yana ƙara mata ɓacin rai da, "wargajejen bakina fah na mamana na ɗauko, don baba na yafi kyau", da gudu ya ƙara sa fita saboda ya ƙara ƙular da ita, tsayuwa tayi ta rasa abun da yake mata daɗi, nida hafsy kuma sai dariya muke, bata kula mu ba ta

wuce ta kashe T.V ta, sannan ta kalli hafsy ido a ɗaure tace, " maza tashi ki tafi inda kike kwana sokuwa mai nacewa soyayyan ɗa namiji, bakida zuciyar karatu irin na yar'uwar ki sai zuciyar son ƙaton banza mai babban baki, tashi ki fita marasa kunya", ta faɗa tana nunawa hafsy hanyar waje, dariya hafsy tayi ta gyara zama tace, "anan min zan kwana, babu mai fitar dani a duk inda yayi mun a gidan nan, idan mutum ya matsa kuma na ƙira Abba yanzu yaji irin sakayyar soyayyan da yayiwa mahaifiyar shi take mishi nata, bata son yayan shi, bata son su raɓeta",

"amma dai Allah wadaran munafuki mai haddasa fitina tsakanin ɗa da uwa, ni yaushe naƙi yayan usmanu? Yoo ko gadona yayan usman sukace na sauƙa su kwanta ae sai na sauƙa, ballantana ɗan banza cikin wani ɗaki na daban? Tou a hirr ɗinki kika ƙirashi kika tayar mishi da hankali", tana faɗa ta juya zuwa ɗakin kwanciyar ta tana ta mita, mudai dariya mukeyi nida hafsy, don babu abunda yake rufe bakinta irin ace za'a gayawa Abba bata son mu, Allah sarki hajiya Ummah.

****

Kwanci tashi babu wuya a wurin ubangiji, yau wata shida da aure su habiba da yayah Ahmad, sannan yau ranan laraba 06/06/ 0000 muka tashi da labarin habiba ba lafiya wai tayi misscarrige, haka mamien ta da raliya sukayi ta sintirin zuwa asibiti, da yake Abba yana gari babu yadda muka iya, ana sallan magrib yace duk mu shiryah muje asibiti mu dubata, da yake a Ni'imah clinic take, ana sallah muka fito, da ummie, mamah da hafsy driver yaja mu sai asibitin, muna isa kowa saiga Aliyu zai shiga, bayan sun gaisa da su ummie muma muka gaishe shi, duk idon shi yana kaina ya amsa mana gaisuwan, bin bayan shi mukayi har ɗakin da habiba take kwance, muna shiga muka sameta a zaune maminta na bata tea tana sha, ganin ma tare sai mamie ta wani haɗa rai kaman taga mai ɗaukan ranta, ko kunyan idon Aliyu bataji ba ta wani kawar da kanta ta cigaba da bawa habiba tea ɗin, har gaban gadon mukaje dukkan mu muka gaisheta, ko ganin idon su ummie ne sai ta ɗago ta amsa mana fuskanta ɗauke da murmushi, amma kana ganinta kasan ta sha jinya, tayi baƙi ta rame, ni har raman ta ma da baƙin ya ban tsoro, kaman ba habiba yar gayu ba duk tazama kaman wata yar ƙauye, gefe ɗaya kuma kan carpet hajiya umma ne zaune tare da raliya, wanda kallo ɗaya ta mana ta cigaba da danna wayan ta, gefe ɗaya muka koma muka tsaya nida hafsy, domin mun gaida mamie ko kallon mu batayi ba, gara ma su ummie ta amsa gaisuwan su fuska a ɗaure, chan kuwa najiyo hajiya ummah tana tambayan Aliyu ina mummyn shi, "nikan Aliyu ita mahaifiyar taka kam bata gari ne? Naga har yanzu banga idon ta ba ko wani daga gidan ku? Ko dai baka gaya musu bane kana jin kunya irin na yan fari? Tou ae

yanzu anci gaba ko haihuwa ne ae za'a faɗa ballantana ɓari, ɓari ma irin wannan da Allah ya kiyaye ba'a rasa rai ba", murmushi Aliyu yayi baice komai ba, sai mamie ce tayi magana ranta a ɓace, "hajiya ae ta ƙira taji yayah jikin, kuma tace tana tafe wani abune yasha kanta, amma kuma ae bai kamata ayita magana ba, naga wanda ya zama mishi dolen ae yana tsaye akan komai", ta faɗa tana ƙara ɗaure fuskan shi, mitsi-mitsi da ido hajiya ummah tayi tana kallon mamie, "ni kikan Hauwa neyasa bakijin kunyan shera ƙarya ne? Ina nan ɗazu da la'asaar muke jajanta rashin zuwan ta da rashin ƙiran wayan da batayi ba? Shima Aliyun wani sintiri ya tsaya yakeyi akai? Ina tunda yazo ya ajiye ta yace zaije office bai dawo ba sai wurin ƙarfe biyar, hidiman komai inace Abbanta ne a tsaye akai shida ɗanshi Umaru? Ga Aliyun nan ae a tsaye shi kam bazai zabga uban ƙaryan nan ba, tun da yazo a tsatsatsayen sai yanzu ya dawo, ko coolern abinci ɗaya banga ya shigo da shi ba, kuma hakkin sune bana Usmanu ba, dubi habiba inda ta lalace tafita hayyacin ta, haka aka basu ita? Kawai ƙatuwar mata baki son a faɗi gaskiya".

Hajiya ummah ta faɗa tana miƙewa tsaye, shidai Aliyu shiru yayi yana wani murmushi chan ƙasa-ƙasa, idon shi akan habiba da taketa sharan hawaye, babu daɗewa yayi waje abinshi, "sai a haƙuri dai za'a dinga yi, yanzu ta lafiyan ta kawai za'ayi ummah ba wai ta abinda sukayi ba, idan basu zo bama ae mu munzo, kuma Alhmdllh tunda mahaifinta na tsaye akai ae yafi akan ace babu kowa", ummi ta faɗa tana matsa jikin gadon domin rarrashin habiba da ta fara ƙara sautin kukanta, tsaki hajiya ummah tayi tana kallon mamah tace, "baiwar Allah ku tashi mu tafi, ae gaisuwan ya isa haka, na Allah da annabi kam ae munyi shi, kinga ae da yasan basu da gaskiya daga shi har iyayen shi da yʻan'uwan shi ae kinga fita yayi, yoo ba dole ya fita ba, yaga na banza ya samu, an tula mishi uban dukiya ankai gidan shi ya dawo yana cin uban ta la'ada waje, gashi ya lafta mata uban cikin da bai shiga mahaifah ba yabar mahaifinta da ɗawainiya, shi ko a kwalar rigan shi, ina zai damu daman yadda ake so, tunda junin mutane chushen mata ce ae kaɗan kuka fara gani, dama matan chushe ina take daraja".

Kuka mamie ta fashe da shi, cikin ɓacen rai take magana, " hajiya naga dai da habiba da ayshaa duk ɗaya suke a wurinki, amma kullum sai ki nuna ayshaa sune yʻayʻa nawa kuma ba yʻayʻa bane, idan mijinta da yʻan'uwanta basu zo ba ae bai kamata ki tallata ta a duniya ba, ae sai ki rufa mata asiri, tunda kowa yasan kowani aure da irin jarabawan shi, ae gara dai wanda tayi akan wadda batayi ba, ayshaan ko mashin shini tana da shine? Ae itace abun magana ba habiba da mijinta yake tsaye akanta ba, ina ruwana da uwar shi idan bata so? Shina ae kowa yasan ba banza bane an shiga an fita an raba tsakanine kawai, amma ni ae nagode Allah da naga nawa yʻar a ɗakin aure, ga ƙaramar ma tana shirin tafiya, wasu fah? Saidai suga a nayi".

"A hir ɗinki hauwa, wallahi a hir ɗinki da jinin usmanu, insha Allahu Aysha da hafsy sai kin ɗauki yʻayʻan su da jikokin su, kuma insha Allahu auren sai ya rufa miki asiri,

ki rubuta ki ajiye koda bayan rai na ne, kuma na ƙara jin bakin ki ima magana kina yi wallahi zakiga matakin da zan ɗauka, don ko shi wanda ya ajiyeki sai na juya mishi baya kiga idan auren naki zai yiwau, shashasha marar tarbiya, duk kinbi kin ɓata tarbiyan yaranki, nan rumi-rumi yara sun taso tare amma mugun halinki da banzan nonoki sai da kika ɓata tsakanin su, kikasa yʻarki tayi ƙwacen mijin auren yʻar'uwarta, da yaki Allah ba azzalumin bawan shi bane sai Allah ya baku nasara domin ya kare Ayshaa don tasha nono mai kyau da tsafta, zuciyarta bata gurɓace ba irin na yʻarki da tasha mummunan zuciya nata ya gurɓace, insha Allah miji ɗangaske ayshaa zata samu ba mai dukan mace ba, inba tozarci da wulaƙanta kai ba ina duka ya mata har aka samu cikin ya bar mahaifan, ko dama bai shiga ba, tsabar babu Allah a zuciyar ki kuma kina mummunan fata a wasu? Kijira kiga yayah naki zasu ƙare tukun", hajiya tana ƙarasa faɗi tayi hanyan fita waje, hafsy da ke bin raliya da harara ban san me ya haɗu suba tom & jerry naga tabi bayan ummah, ita ma raliyan na binsu da harara, ita dai mamie kuka ta cigaba da yi tana guna-guni ƙasa -ƙasa, tsaki mamah tayi ta dubi habiba tace, "Allah ya baki lafiya, idan kinga dama ki gyara halayenki tun baki makaro ba, idan kuma baki gajji da wahala ba ki cigaba da biyewa uwarki, ita kuma ta cigaba da ɗoraki a hanyar da bata dace ba, inace yau wata shida da yin auren ki? Amma duk lokacin da kika shigo gidan kin fi ƙarfin ki shiga ɗakin kowa ki gaishe shi saidai idan kin haɗu damu a waje ki gaisa damu, kuma nayi imani da Allah su yayunki da sukayi hidima dake a auren ki baki taɓa zuwa gidan kowa ko ƙirasu ki gaishe su ba, tou wallahi kikabi ta haikar uwarki abun bazai miki daɗi ba gaba, domin mu duk nan mutuwa zamuyi mu barku tare, yayunki sune iyayenki, shi kuma aure haƙuri akeyi, kiyi biyayyah wa mijinki da iyayen shi, idan kika bi ta uwarki zaki sha wahala", tana gama faɗi ta juyo ta kalli mamie da ke kallonta da harara, itama hararan mamin tayi tace, "idan ke mai shirya ce Allah ya shirye ki, kuma magana da kika maidawa ummah ki tabbatar Alhaji yaji, idan kin dawo sai kiyi mishi bayanin wani dama kika samu da tana magana kinayi, mahaukaciya futsararriya".

"Tou uwar gami karki bari ƙuda ya riga ki, ni dai insha Allahu nafi ƙarfin mace, tsakanina da Alhaji kuma sai Allah, duk munafurcin mutum kuma ae ko dan haihuwa Alhaji zai zauna dani", juyowa mamah tayi ta dubeta tana murmushi, "ae da haihuwa irin taki gara da Allah ya bar ni ba haihuwan, don idan bazan iya tarbiyantar da yʻayʻan ba gara na xauna haka, kuma wani kalma na rashin ɗa'a ya sake fitowa a bakinki zuwa gare ni, tou wallahi zan manta a asibiti muke na nuna miki ni ɗin *ZAINABU* ce kinsan bana ɗaukan wargi, kuka habiba ta fashe da shi tana, "wayyo Allah nikan na shiga uku, don Allah mama kuyi haƙuri, mamie don Allah ki daina jawowa ana rashin zaman lafiya, da wanne zanji ne kam"? Ta faɗa tana ƙara ɓarkewa da kuka, lokaci guda naji hawaye ya zomun, don wallahi ni shaida ce habiba bata so taga ana wannan tashin hankalin, kuma gashi ni tunda naji dukanta Aliyu yayi sai naji hankali na yayi mugun tashi, gaba ɗaya tausayinta ya rufe ni, juyawa nayi na fita a ɗakin duk jikina a sanyaye, gashi nasan maganan da habiba tayi dole ne sai mamie taci ubanta idan mun tafi, duk da dai nasan yanzu bazata doketa ba, muna fita mukaga Aliyu tsaye a jikin motan shi yana waya, ganin

fitowan mu ya kashe wayan ya taho har inda motan yake, ƙofan gaba inda hajiya ummah ta shiga ya riƙe murfin motan, fuskan shi ɗauke da murmushi yake mana sallama, tsaki hajiya ummah taja lokacin da motan ta fara tafiya, cike da ɓacin rai tace, "ni wallahi na raina wayon Aliyu nan, idan akace maka zai iya saka hannu ya daki mace, macen ma irin habiba sokuwa ae sai abun ya baka mamaki, ta wani gefen ne kawai bazan yi mamaki ba, idan na tuna nonon uwarta da yake yawo a jikinta, amma abun takaicin ɗaya ne ace jinina kuma jinin usman ta zama boran miji da uwar miji?"

"hajiya ae ba jininki abun ya bi ba, jinin uwarta ne yake yawo a jikinta, itama uwar da badon ta Allah ya taimaketa ba darajan yʻayʻa ae da boran ce a gidan namu"..... ae bata gama rufe baki ba ummah tace "ae boran ce kuwa a gidan usman, tou wa tafi daraja a cikin ku? Idan ba duban yarah ba da tsoron Allah irin nawa ae da tunin usman ya sallameta, tou tsoron riƙon yʻayʻan fitina kawai nake jiye muku, don jifa kam har dana dodon ningawa za'a na muku, idan ba masifa ba irin na hauwa saurayin yʻar uwarta kisaka ta janye shi? Don wannan al'amari kam a yawon asirinta ta samu sa'a, amma taga ranan asiri ae, don Alhaji yace mun tana ta masifah ɗazu, wai ashe tunda akayi auren babu wani ɗan'uwan shi da yaje gidan ta, ita ma ko taje gidan iyayen na shi surkuwar ta mata tsakani da ɗakinta, idan taga dama ta fito su gaisa idan bata so ba kuma har su bar gidan bata fitowa, shima Aliyun kullum gorin ta cuce shi ba ita yake so ba amma mashiryiciyan uwarta ta asirce suka juya mishi hankali zuwa kanta yakeyi, rayuwar fah Alhaji yace mun babu daɗi, don ko kuɗin makaranta uban ne ya cigaba da biya, don uwar yaron tace yaronta bazai wahala a banza ba, yanzu ma wai auren yʻar ƙanwarta ake nema mishi, shine maka sudin dokan, sunje jiya gidan maman nashi, itama yarinyar ashe tazo, suna zaune suna hira da Aliyun a parlon maman shi sai marar kunyar ƙanwar tata ta gansu, kin san ba tarbiya take da shi ba, ashe da zasu tafi taje har ɗakin da yarinyar take ta zazzageta, ita kuma yarinya mai tarbiya ce bata tanka ta ba, sai da suka tafi ta gayawa maman Aliyun, ita kuwa uwa ta ƙira tace yaja kunnen ƙanwar matar shi, kuma kada ya sake shigo mata dasu gidanta, ae kuwa inda ya shiga bata nan yake fita ba, yace dole raliyan ta bar gidan a daren, ina ga ita kuma yʻar uwar ku taƙi ne, shi ko zuciya ya ɗebe shi yayi ta bugunta har abun yazo da tsautsayi,"

Dariya mamah tayi babu wani shakkah a ranta tace, "hakki ne kawai hajiya, ae kaɗan ta gani, ae idaɓ junin mutum hassada ne ya ringa ganin abun da baya so, duk wanda yace ruwan wani bazai tafasa ba tou insha Allahu nashi ko ɗumi bazai yi ba, ta cigaba dai kada ta daina".

Ita dai ummie bata ce komai ba sai jinjina magana da take tayi, nima duk sai naji hankali na ya tashi, a haka muka iso gida gaba ɗaya kowa ranshi babu daɗi, muna isa kuwa ummi da mamah da hajiya ummah suka wuce parlon Abba, ni da hafsy dai side ɗin ummin mu muka wuce, muna shiga hafsy ta wani zabga mun harara, "ke wai Adda tausayin su kike jine? Wallahi gara ma ki daina don bakiji me banzan

raliyan nan ta faɗa bane akanki", "bance ki gaya mun ba tunda banji ba, kuma ke hafsy ko babu zuciyar imani ajikin ki ae zaki tausayawa habiba, ae ba raliya da mamie zaki duba ba, ita zaki duba", na faɗa ina neman wurin zama a parlon, tsaki tayi itama ta nemi wurin zama ta zauna, "nikan Adda bana tausayinta, don banga abun tausayi ba, lokacin da taci amanar ki ita ta tuna da tausayin kene? Ina wani falli ma takeyi ta ƙwace miki miji? Ni wallahi ya mun daidai, dama mai siffana sheɗanun nan ya laftawa dukan da sai bakinta ya kumbura yayi, amma itama ana tafe, nata laftan yana zuwa", ta karasa faɗa tana kwashewa da dariya, nidai ido kawai na zuba mata, tana dariya tace ,   " bari manyan mu ya shigo musha dariya" yayah umar take nufi, nidai ko maida mata amsa banyi ba, don haushi ta bani kawai na ɗauki remote ina kunna T.V.

Kaman jira yake ta ambaci sunan kuma sai ga shi sun shigo tare da ummin mu, fuskan ummie a ɗaure ta nemi wuri ta zauna, gefe ɗaya kuma yayah umar ma ya zauna a gefen ummin mu, "ummie tou ke ina ruwanki da wani shiga abun da bai shafe ki ba? Ki barsu kawai Abba ya ɗauki duk matakin da yaga zaiyi dai-dai".

Ajiyan zuciya ummie tayi cikin rashin jin daɗi tace, "ita hauwa hankali ne bata da shi, amma yaran ae abun tausayi ne, yanzu yaushe akayi auren da har duka zai fara shiga? Ni wallahi habiba tausayi ta ke bani, kuma zan nemi ita mummyn Aliyun muyi magana, meye laifin ita habiban da zata bari haka yana faruwa"? Da sauri yayah umar ya riƙo hannun ta da ta ke shirin ɗaukan wayanta yace, "haba ummie na don Allah kada ki fara yadda Abba yace, wallahi duk abinda ya biyo baya kanki mamie zata mayar, ki fita sha'aninta da yaɣanta, ae dai kinji mai Abba yace, tou babu ruwanki naki ido ne kawai".

Shiru ummie tayi tana kallon mu ɗaya bayan ɗaya, chan kuma tace , "Allah ya kyauta", sannan ta miƙe tayi hanyar ɗakinta, tana shigewa hafsy ta ƙyalƙyale da dariya, ƙasa-ƙasa ta shiga korowa yayah umar labarin abubuwan da ya faru, dariya sukayi tayi har suka ban haushi, ganin zasu ƙara ɓata mun rai kawai sai na fita na wuce side ɗin ummah, ina fita suka sake kwashewa da dariya da ƙarfi don naji.

Ranan da aka sallami habiba mamie tayi niyyan wuto wa da ita gida, amma fir Abba yaƙi amincewa, bada son ranta ba aka wuce da habiba gidan ta, Abba kuma ya hana raliya zuwa, ita mamin yace bazata zauna ba, idan har ta damu da aje a kula da yaɣar tou ta nemo wata yaɣar'uwarta ta aika, haka kuma dole tayi,

Umman ta ƙanwar mamanta ta ɗauko ta, tunda ta dawo gida ta fara sauƙe mana habaici iya son ranta, ganin abun zaiyi yawa mamah ta fito ta taka mata uban warning, babu yadda ta iya tayi shiru, ganin tana cikin damuwa ta shirya ta tafi

Abuja wurin Abba, raliya kuma ta haɗa kaya ta wuce gidan ƙanwar mamin, dama duk wacce taga zataje Abuja wurin Abba baya hanawa, yawanci ma ita da mamah ne suke yawan zuwa, ita ummien mu sai ta ɗauro ko zataga likita tukun take zuwa, haka dai muka samu gidan yayi shiru na tsawon sati biyu kafin suka dawo tare da Abba.

****

Muna ta shirin fara rubuta exams yayah Ahmad ya ƙira ummi yace idan anyi hutu zaizo ya ɗauke ni, ummi ƙin amince mishi tayi, amma da taji Aunty jeeddah ce babu lafiya sai ta amince, M.G kuma rana ɗaɗɗaya ne bamu waya da shi, gashi munyi wani kyakkyawan sabo da shi, dana tambaye shi ya cigaba da bani labarin daya fara bani sai ya ƙi, yace sai ranan da yazo bauchi tukun, sannan tun ranan bamu sake hiran A.G ba da shi, gashi ina son tambayan shi yayah jikin A.G amma na kasa.

Ranan laraba muka gama rubuta Exams ɗin mu, Alhamis kuma su hafsy suka gama rubuta neco, sai wani falli suke ji da shi, mu kuma mun gama level 2 sai shirin shiga 3, sannan a wannan lokacin ne aka saka ranan auren fatima, itama hadiza ana shirin zuwa neman auren ta, murna kaman zamuyi yayah muke ji.

Friday yayah Ahmad yazo bauchi tare da Abba, zuwan sune mukaji labarin wai za'a zo gaisuwan auren raliya da wani ɗan ƙawar mamin ta, abun ni mamaki ma ya bani, haka kuwa akayi ranan saturday suka zo, kuma a son ransu sunso a saka musu rana , amma Abba yaƙi amincewa da buƙatan su, yace gaskiya sai ta shiga university za ayi, babu yadda suka iya haka suka yadda.

Washe gari sunday muka kama hanyan Abuja, da yake da mota yayah Ahmad suka zo da Abba, don ba kasafai Abba yake bin jirgi ba, yafi tafiyan mota ko dan yayi saye-sayen tsaraba, parlon Abba muka shiga yi mishi sallam nida yayah Ahmad, a can muka tarar da mamah da mamie a zaune, daga gani kuma wani abunne ya haɗasu Abba ya nemi su, don muna shiga na tsinci muryan mamah na cewa Abba yaja kunnen matar shi, banji me yace ba muka shigo, kuma sai duk suka dakata da maganan suka dawo da kallon su kanmu, gefen Abba naje na ɗan tsuguna ina ƙara gaishe shi, hannu ya saka ya dafa kaina, "sisto na har an fito za'a yi himmah ko"? ɗaga kai nayi alaman eh, fuskana ɗauke da murmushi, domin Abba ne ya fara saka mun sisto, kafin habiba ma takama, da yake sunan sister shi naci, "Allah ya tsare hanya Ayshaa kuma don Allah idan anje ko ina kada a chanja hali da tarbiyan da muka baku, a ko'ina kuke ku nuna ko jinin Usman ne, kuma don Allah a zauna lafiya da matan yayun ki, kinga dai yadda mahaifiyar ta ke zaune da mutane? So plz kuma duk inda kuke haka nake so, Allah yayi albarka ya kawo mazaje na gari", ya idasa

faɗa yana ciro kuɗi a aljihun shi masu yawa yana miƙo mun, itama mahma nasihar ta mun, sannan ta dubi yayah Ahmad tace, "duk zaman lpyn da zai biyo baya daga gidan ka kaine, idan ka mutunta matar ka yan'uwanka su mutunta ta, idan ka wulaƙanta ta su wulaƙantata, idan ka nunawa matarka yan'uwanka suna da daraja ta mutunta su, saboda haka kai zan jawa kunne don munga iya gudun ludayin muhammadu naka ne bamu gani ba, kaga dai yadda yarinyar nan Bintu take naknak da ku, tou daga muhammadu ne, shima kuma bai bari anci mutuncin matar shi ba, kaima sai ka kiyaye," godiya yayah Ahmad ya mata sannan muka musu sallama gaba ɗaya muka miƙe, tsaki mamie taja tana faɗin "halan miji zakije nema mata a Abujan ko? Tou nema mata miji mana tunda kaf bauchi an rasa me tayawa".

"Wuce ku tafi malam Ahmadu Allah ya tsare hanya, Ayshaa idan rabon yana Abuja Allah ya kawo mana babban rabo wanda zai kai yan baƙin ciki masu ciwon hassada makka", mamah ta faɗa tana bin mu da murmushi kaman bata faɗi wani abu zuwaga mamie ba, nima murmushin nayi na juya muka fita, ina kallon yadda Abba ya zubawa mamie uban harara kuma daga gani jira yake mu fita ya dirarmata,

Sai wuraren ƙarfe biyar muka isa, yayah ne ya tayani ɗaukan kayan muka shiga side ɗin shi, bamu samu Aunty j a parlor ba, ɗakinta na wuce yadda yayah ya umurceni, ina shiga kuwa na ganta dunƙule akan sallayan da tayi sallah tana bacci, ganin haka na ajiye troley nah a gefe, sannan na fito a hankali na tattara ledodin da ummie ta haɗa musu tsaraban bauchi na shige da su kitchen, ina fitowa kuma na haɗu da yayah Ahmad shima ya fito daga room ɗinshi zai shiga na Aunty j, cikin sanyin muryar shi yace, "ɗauki na gida yayah muhammad ki shigar musu da shi," da sauri kuwa na ɗauka nayi gaba, tsaban ɗokin naje naga Aunty da Areefh, don nasan fatima bata iso ba don munyi chatt tace mun sun gama Exans, amma sai ta ɗan huta zata zo, har na zolayeta kodai kabir zai shigo ƙasan ne ya sa bata taho ba, dariya tayi tace ae idan kinga kabir ƙasan nan tou ki fara shirin miƙa ni, dariya mukayi tayi ina zolayanta.

Ina shiga kuwa na haɗu da Areefh yana buga ball a parlon su, gefe ɗaya kuma yayah muhammad ne ke ta aiki a laptop ɗinshi, six month banga Areefh ba, amma da yake muna yawan video call bai manta ni ba, sake ball ɗin yayi da gudu yayo kaina, shima yayah muhammad ajiye aikim da yakeyi yayi ya ƙura mana ido yana murmushi, bayan na ajiye kayan hannu na da sauri na tare Areefh na rungume shi muna ƙyalƙyala dariya, yana rungume a jikina na wuce wurin yayah muhammad, rungumeshi nayi ina dariya, shima dariyan yake ya rungumo ni tare da areefh yana oyyoyoooo bestyn yayah, muna haka Aunty B ta fito daga kitchen tana, "maraba da maman areefh, bestyn Baby na, dukkan mu dariya mukayi saboda Aunty B idan taso ta iya barkwanci, ajiye areefh nayi na ƙarasa wurin ta nayi hugging ɗinta, dukkan mu cike da farin ciki muka taho parlon muka zauna, gaishe su nayi suma suna tambaya na su ummie da su mamah, yayah muhammad yana tambayan ina

hajiya ummah daro? Dariya mukayi saboda tuna last month da yayah yaje dagewa tayi sai ta biyo shi taga su Aunty B, wai ae mugunta ne tunda ya mayar da su Abuja yaƙi kawo su, ita zata saka a maida shi lagos ɗinshi su kuma su dawo nan kusa ya fi mata, da ƙyar aka lallaɓa ta akan zasu zo hutu ae kwanan nan, dariya mukayi sosai, Aunty ta miƙe zata koma kitchen nima sai na miƙe, juyowa tayi ta harare ni, "koma ki zauna ki huta ke da yayanki ku ƙara gaisawa, nima na kusa gamawa, jeeddah ce wai ke son cin miyar ɗanyar kuɓewa shi yasa kika ganni iwar haka a kitchen," murmushi nayi na koma na zauna muka cigaba da hira da yayah na, a haka kuma yaya Ahmad ya shigo suka gaisa, shima wuri ya samu ya zauna yana rungume da Areefh, hira suka fara na yadda maganan neman auren raliya ya taso suke yi, inda yayah muhammad ya juyo yana tambaya na ko akwai wanda muke tare ne? Girgiza kai nayi alaman a'a, "babu komai kar kisaka wani damuwa a ranki kinji besty, shi aure lokaci ne, kuma duk surutun mamie kada ki bari ya dame ki, insha Allahu mijinki special yana nan tafe, ki dage kiyi karatun ki kawai, daga ke har hafsy insha Allahu zakuyi aure na mutunci," yayah muhammad ya faɗa, yayah Ahmad yana jijjiga kai alaman haka ne, nan ma yayah Ahmad ke cewa, "nawa ma suke ne, yanzu ne fa zata je level 3, hafsy ko yanzu ne ma suka gama ss 3 ɗin, just 17yrs ne fa, Aysha suna 20yrs, gaggawa ne kawai irin na mamie har take wayannan surutan, ni dai nacewa ummie kada ta ɗaga hankalinta, komai zaizo a lokacin da Allah ya hukunta, "

"Hakane Ahmad, ae tun jiya da Abba ya gaya mun abun da ke faruwa na ƙira ummin har nace mata idan taga hankalinta zai tashi ta biyo Abba ta taho Abuja ta kwana biyu, amma taƙi wai kula da hajiya umma, ga umar ya gama service yana gida", cewar yayah muhammad, hira suke tayi nidai ina sauraran su rabin hankali na kuma yana tare da Areefh, a haka har aka ƙira magrib suka fita sallah, idan kin gansu kaman wasu yan biyu, don su ina ga ko abokai da baka ganin su tare sai junan su, ban taɓa ganin wa da ƙani da suke so close irin su ba, ko abun da ya shafi office gidajen su tou da junan su suke hiran, don da ku zuwa hira yayah muhammad zai tafi maiduguri tare suke zuwa kaman wasu aboka ne, kodan halin su yazo kusan iri ɗaya ne oho, amma banda nida hafsy, ayi shiri ayi tsiya, don ma mi bana kula tane, amma yanzu naga abun yafara mata sauƙi, tana yawan bibiyata muyi hira, ko tsakaninta da yayah ishaq ni take zuwa tayi shawara da, tom ɗinta an samu ɗan matsala ko sai daga baya?

Side ɗin yayah Ahmad na tafi ɗauke da Areefh a hannu na, ina shiga na haɗu da Aunty jeeddah tana fitowa daga ɗakin yayah Ahmad, da murmushi ta tarye ni, ni kuma naje da sauri na rungumeta, bayan mun gaisa ta tambaye ni su ummie sai na wuce ɗakin ta nayi sallah, na idarr ina askhar sai gata ta shigo hannun ta ɗauke da kilishin da ummie ta saya mun, stool ɗin dressing mirrow taja ta zauna, ina ganinta har wani lumshe ido takeyi tsaban daɗin kilishin da takeji, sallaman Aunty B ne ya sakani fasa tsokanan da nake da niyyan mata, ita ma Aunty B ɗin bakin ta ɗauke da murmushi tace, " kai jeeddah anya tuwo na zai samu wurin shiga kuwa? Naga alaman kwantai zaiyi yau tunda an samu kilishin bauchi," murmushi Aunty j tayi,

"Aunty wallahi yanzu na na shigo na tura ayshaa karɓo mana tuwon ne, sai naga tana askhar".

Dariya Aunty B tayi tace, "tou ku fito parlon na shigo da abincin, chan su Abu areefh suna cin nasu kada mu damesu, naga hira yau sukeji da shi, ko sunyi sabon kamu ne suke irin wannan ƙus-ƙus ɗin yau? Don naga suna ganina suke chanja topic".

Zaro ido waje Aunty j tayi, "haba Aunty ae ko ke bakici a miki kishiya ba ballantana ni da cin amarcin ban fara ba, kawai dai wani hiran su ne na daban da basu gamawa suke yi", dariya Aunty B ta kwashe da shi ina tayata, don ganin yadda Aunty j ta wani lanƙwashe kai kamar zatayi kuka, "waya gaya miki muma mum fara cin amarcin mu? Me ma akayi? Hala ma har ku gama na ku akawo amaryah ni bamu gama ba", Aunty b ta faɗa tana juyawa zuwa parlor, bakin ta ɗauke da dariya, da sauri Aunty J ta rufa mata baya tana, "haba Aunty ki dena irin wannan wasan, nifa ko hiran za a ƙara aure bana so ballantana aje ga batun za'a mun kishiya, Allah dai ya tsare mu da ita,", ta faɗa tana jan kujeran dinning ɗinta tana zama, muma zaman mukayi muna dariyan Aunty J, a haka muka gama cin abincin na tattare nayi side ɗin Aunty B na barsu zaune a parlor suna wani hiran daban, tattare wanda su yayah suka gama ci nayi na wuce kitchen duk na wanke su, mopping na sakeyi na fito parlon, ɗago kai yayah muhammad yayi yana kallona fuskan shi cike da murmushi, "hajjaju makkatun, yar Abba da ummie jikar ummah, ƙanwar Muhammadu da Ahmadu Adda da ummaru da habiba, yayar raliya da hafsy ikon Allah" dariya muka kwashe ni da yayah Ahmad, gefen shi nazo na jingina ina dariya, shima dariyan yayi yace, "baxaki mun liƙi bane sisto"? Dariya yayah Ahmad yayi yace ae kuwa kachi liƙi, da dollers ma kuwa zan maka", yana rufe baki wayana ya fara ƙara, da sauri na duba screen ɗin sai naga yayah M.G ne.

Murmushi nayi na maida wayan a silent, ɗago kai nayi sai muka haɗa ido da yayah muhammad, ganin irin kallon

 tuhuman dayake mun, bansan lokacin dana fara dariya ba ina rantse mishi ba fa wani bane daban

Yayah M.G ne fah na faɗa ina yi hanyar barin parlon, dariya suka kwashe da shi su biyu, ina jin muryan shi yana cewa yayah Ahmad kaji mun yarinya da tsarguwa, tou idan tayi wari zamuji ae, nidai ban ƙarasa jin sauran abun da suke cewa ba nayi gaba, sai dai ima jin dariyan yayah Ahmad, ina shiga parlon ban saurari su Aunty J ba na wuce ɗaki, rufo ƙofan nayi na nemi wuri na zauna, kaman jira yake call ɗinshi ya sake shigo mun, cikin nutsuwa na ɗauka ina mishi sallama, "sisto nayi fushi, nayi fushi da ke, munyi waya da ke fa jiya, amma ko kice mun zaki shigo Abujah, adalci kenan?"

Rufe fuskana nayi kaman yana kallo na ina dariya nace, "nifa na ɗauka yayah Ahmad ya gaya maka"? "sauƙe tou don dai kam bai gaya mun ba, kuma bashi ne

ya kamata ya gaya mun ba, kece ya kamata naji daga wurinki, yanzu sai da A.G yagaya ya tukun na san kinzo, hala har muyita waya baza kice mun kinzo ba, don kada ɗan marayan Allah yazo ya ganki".

Cike da mamaki nace, "shi kuma yayah A.G ɗin yayah akayi yasan nazo"? Dariya ya kwashe da shi yace "wurin yayanki yaji kin san shi da bin dindigi yasan komai da yake faruwa a ƙasan, yakan riga sanin wani abun ma misali kaman wannan", ya ƙarasa faɗi yana murmushi, ajiyan zuciya na sauƙe, ni dai mamakin abun kawai nakeyi, "tou shi ina ruwan shi da sanin me nake ciki? Na ɗauka ma ya manta dani ae zuwa yanzu"? "kina ƙanwar aminin shi ne zakice ina ruwan shi da sanin me kike ciki? Tou ae yanzu ko shi barrister ba lallai bane yabi ƙwaƙwafin rayuwar ki irin A.G, kinsan shi fa yana da mugun kiyayewa akan abunda yasa a gaba, yanzu hala ma result ɗinki ma ya riga ki sani" ya faɗa yana dariya na.

Nidai share maganan nayi na cigaba da gaishe shi, "sai kin koma sch tukun zaki bar Abuja ko"? Najiyo muryan shi yana mun tamabaya, "ehh insha Allahu" na bashi amsa.

Kafin ki tafi insha Allahu zan shigo, domin yanzu akwai wani aiki dana tafi yi a Benin, kafin komawanki insha Allahu zan dawo", daga nan muka ci gaba da hiran mu yadda kullum muka saba, har muka gama hiran bamu sake sako sunan A.G a ciki ba, bayan mun gama wayan ne na fito zuwa parlor, anan na samu yayah Ahmad ya shigo, ashe ita kuma Aunty B har ma ta tafi gidan ta, ban wani ja lokaci ba nayi musu sallama na koma ɗaki, domin ummie tana yawan tunatar damu, idan munje gidan yayun mu muna rage zama a wuri idan suna tare da matan su, idan an taɓa hira kaɗan mu basu waje.

Kullum idan na tashi da asuba, ima idar da sallah nayi azkhar zan gyara gidan gaba ɗaya, kuma har side ɗin Aunty B nake zuwa na gyara, domin ummie ta horar da mu aiki, duk da sanyi na zakiyi mamakin yadda nake aiki, amma idan an haɗa ni da hafsy ne tou babu mai ganin saurin nawa, sai dai banbancin ƙyalƙyale wuri, gidajen nasu babu wani datti, sharewa nakeyi nayi mopping sai na kunna turaren wuta a kowanni sashi, domim tun dare nake wanke-wanke, kuma tunda naje bamu ɗaura abinci a side ɗin yayah Ahmad, wannan Aunty B ta ɗauke, sai dai idan tayi ta saka na kowanne side, ina gama gyara ko ina nake zuwa na kwanta tare da Areefh a side ɗinsu, sai Aunty b ta gama haɗa breakfast nake fitowa na mishi wanka nima nayi, don gaskiya bana tayata aikin breakfast, saboda ko dankali zata soya tun dare nake fere mata, ranan da zatayi masa ma ni na kwaɓa mata shi da wuraren ƙarfe huɗu na asuba, so bayan na musu ayyukan su sai na ɗan kwanta na huta, amma abincin rana tare mukeyi, don gaskiya ba kasafai nake barinta da aiki ba, na dare ma tare mukeyi, don ma bamu cika yin abinci da rana ba, saboda su yayah basu nan, magrib suke dawowa sai kawai ayi abinci ɗaya, zaman mu gwanin ban sha'awa,

kullum muna tare da juna, gashi akwai ƙauna mai girman gaske tsakanin mu da matan yayun mu, don gaskiya ummie a tsaye ta ke da Addu'an haɗin kan iyalanta, kuma Alhmdllh Allah ya amsa mata.

****

Rayuwa kullum ciki take burirrika, amma kwanakin mu kuma kullum ƙarewa suke, a haka hutun mu ya ƙare, dama 3weeks aka bamu, a haka har na shiga sati na huɗu, wanda lokacin nafara shirin komawa gida, zo kiga yadda hankalin Aunty j gaba ɗaya ya tashi, nidai har wani tausayi take bani, haka yayah Ahmad yayi ta rarrashinta akan idan ya maida ni zai taho da hafsy, insha Allahu ita ma zataji dadin zama da ita, babu yadda ta iya saboda ni karatu nake.

Ana saura kwana 2 na koma sai ga M.G ya dawo daga tafiyan da yayi, tun ana gobe zai dawo ya gaya mun na mishi special girki, saboda haka ranan Aunty B ta tayani muka mishi abinci kala biyu, sannan mukayi snacks kala wurin uku, muna gamawa na kwashe su zuwa side ɗin yayah Ahmad na jera akan dinning, sannan na wuce naje nayi wanka na shiryah cikin wata baƙar abayata mai kyau, Aunty Asma'u ce ta kawo mun ita bana da taje aikin hajji.

Wuraren ƙarfe uku suka shigo gidan shida yayah Ahmad, leƙowa nayi muka gaisa hannu na riƙe da na Areefh, ɗaga dukkan giran shi yayi yana kallona cike da mamaki, " barrister yayah naga kaman Ayshaa ta ƙara girma da tsawo? Anyɗa zamu barta tagama school bamu aurar da ita ba"? Ya ƙarasa faɗi yana dariya, juyawa nayi da sauri na koma cikin ɗaki nima ina dariyan, gaskiya na daɗe banga yayah M.G ba, sai naga ya wani ƙara haske da kyau, gashi komai yayi kyau yake mishi, yanzu ɗaga giran da yayi sai yayi mun bala'in kyau a fuska, ina jin su suna ta hira da yayah Ahmad suna cin abinci, suna kan dinning ɗin har aka ƙira sallan la'asaar, daga nan suka wuce zuwa masallaci, bayan sun dawo ma suka cigaba da hiran su har zuwa wani lokacin, sai chan daga baya yayah ya ƙirani maje parlon, ima shigowa kuwa ya sake ƙura mun ido, fuskan shi ɗauke da murmishin shi mai kyaun nan, "ki zo ku gaisa da M.G, bari mu ɗan fita da yayah muhammad, bazamu daɗe ba zamu dawo", hannu na riƙe da gefen gyalen abayata ina kallon yayah har ya

fita, bayan sunyi sallama M.G sai ya ƙura mun ido, har ajikina nake jin kallon da yake jifah da shi yayi mun yawa, saboda haka sai naja kujera na zauna, ƙasa-ƙasa na sake gaishe shi, kuma ban yadda dana sake yadda mun haɗa ido ba, shiru wurin ya ɗanyi na wani lokaci, kaman bazai ce komai ba, har na sake ɗago kaina amma sai charaf idon mu suka sake haɗu, da sauri na mayar da kaina ƙasa ina wani zazzare ido irin na rashin gaskiya.

Murmushi yayi sannan yace "yʏan mata ina labari"? Ɗagowa nayi na kalle shi, domin kalmar da ya jefe ni da shi wai *YʏAN MATA* ya taɓoni, kasancewar bai taɓa ƙirana da hakan ba, giran shi ya sake ɗaga mun fuskan shi ɗauke da murmushi, kafin ya samu zarran sake jefo mun wani maganan, sai ga wayar shi tana kawu wuta, alamar tana neman agaji, ina kallon shi fuska cike da murmushi ya ɗauka, "mummy barka da yau yyh bauchi"? Sannan jimawa kaɗan na sake ji yace, "insha Allahu zan shigo very soon mummy nah,"

Bayan yayi shiru na wani lokaci yana sauraran me wayan sai kuma naji yace "ganin nan ma wurin ayshaan mummy" babu daɗewa ya miƙo mun wayan ƙasa -ƙasa yana cemun. "mummyn muce na wurin A.G.

Cike da jin kunya na amshi wayan na shiga gaisheta, "Doughter nah yayah kike? Hope dai babu wata damuwa ko? Kuna gaisawa da A.G dai ko?" cike da jin kunyar ta na amsa mata gaisuwan, sauran kuma naji nakasa sakewa nace komai, sai murmushi kawai nake tayi kaman ina gaban ta, fatan alkhairi ta mun sosai da addu'a, sannan na miƙawa yayah M.G wayan cike da jin kunyar matar, sallama sukayi ya kashe wayan, ƙura mun ido yayi fuskan shi ɗauke da murmushi, "itace mummyn mu ƙwalli ɗaya da muke ji da ita nida A.G, itace mahaifiyar A.G dana fara baki labari wato Aunty Rashida, macece mai ilimin gaske da kirki, akwai shaƙuwa sosai tsakanina da ita, tana sona sosai kaman ita ta haifeni, abun mamaki kuma hiran da zamuyi da ita bazaki taɓa ganin A.G sunayi ba, wani lokacin idan tayi magana taga bai ce komai ba sai ta hau shi da faɗa, "ni dai idan baxaka ringa amsa mun magana ba a daina zama kusa dani, haba mutum yana naniƙe da kai amma kuma bazai yi magana da kai ba yadda ranka zaiyi daɗi", sai dai ni kiga muna hira da ita sosai, amma kuma idan kinga irin son da take mishi zakiyi mamaki, don idan ciwon shi ya tashi ta dinga kuka kenan, tana masifar son shi sosai".

Murmushi nayi ina sauraron shi, "kin san duk abun da ya shafi A G tana so, ballantana da taga ya damu da ke bakiga yadda take mugun sonki ba,", ɗago kaina nayi cike da mamaki nace "ya damu dani ko kuma dai ya damu da jin haushi na, har labari na yake bawa mummyn? Dama ya riƙe sunana ne?"

Dariya yayi yace, "ae duk abunda ko ni ko barrister ya damu da shi tou A.G ma ya damu da shi hala ma har yafi damuwa da shi, kin san tsakanin shi da barrister akwai wata ƙauna mai ƙarfin gaske, don tunda ga kaina bai sake sakewa da ƙaunar wani ba sai barr."

Murmushi nayi ina jijjiga kai alamar ina tare da shi, wayan shi a karo na biyu ta fara kukan neman agajin a ɗauke ta, murmushin fuskan shi ne ya wadata lokaci ɗaya, sannan kuma ya ɗauki wayan yana ƙara wadata murmushin, "A.G friend, kaman kasan yanzu hiran ka nakeyi", shiru yayi yana sauraran wayan, nidai ido na yana kanshi, can sai naga ya kwashe da dariya yana, "wallahi nida Ayshaa, yanzu ma na haɗa su suka gaisa da mummy",

Kallo ni yayi sai naga ya miƙo mun wayan, kasa karɓa nayi kaman yadda ɗazu na karɓi na mummy, "karɓa mana A.G ne a layin", babu yadda na iya haka na saka hannu na karɓa, da ƙyar na kai wayan kunne na, shiru dukkan mu mukayi, ina ganin M.G kuwa ya wani ƙura mun ido yana smilling.

Nima smilling ɗin nayi nace bari na haƙura da typing ɗin nan, sai kuma gobe idan mai kowa mai komai ya kaimu.

Numfashin shi naji alaman ba daidai ba, daga dukkan alamu abun yana kusa ne, sai naji hankalina kuma ya tashi, har bansan lokacin da bakina ya furta, "yayah baka da lafiya ne"? "kin damu ne da kisan lafiya na"? A.G ya mayar mata da amsa, runtse ido na nayi saboda yadda zuciyana naji ya yanke, daga jin yadda muryan shi yake fita babu lafiya, "sorry yayah A.Gn mu ka daina faɗa da fushi kaga baka da lafiya, kuma ni.....kuma shikenan dai yaya jikin"? Na tambaye shi, "kin taɓa ganin nayi fushi da ke? Na tafi banida lafiya anma bakiyi tunanin ƙiran kiji yaya nake ba, hakan kuma bai saka nayi fushi ba, ki tsoraci ganin fushina kawai, sannan meye kuma....kuman da kike son faɗi"? Ya ƙarasa yana ɗan tari da jan numfashin shi a hankali, " babu kawai zance tou kadawo mana tunda baka da lafiya, kuma ae kaima baka ƙirani ba",

"idan na dawo me zan miki? Akwai wani dalili ne da zai saka na ƙiraki? Ko ance miki kowa nake ƙirane"? Tura baki nayi gaba kaman yana kallo na, murya chan ƙasa - ƙasa nace, "tou nima kowa ne nake magana da shi"? "me kikace? Wato kin raina ni ko? Nine kowan ko"? Buɗe ido nayi ina zaro su don banyi tsammanin zaiji abinda nace ba, amma sai nayi diris nakasa bada amsa saboda yadda naga idon M.G ya koma, kaman wani marar lafiya, amma ganin na buɗe ido sai ya jefe ni da wani murmushi wanda bai wuce lips ɗin shi ba, da sauri na miƙa mishi wayan, yana ƙara murmushin fuskan shi ya karɓi wayan yakai kunnen shi yace, "Friend yaya ƙarfin jikin? Amma yau kam ina ganin zasu sallameka ae ko? Don naji daddy yace zuwa friday zai dawo".

Hankali na ne naji ya sake tashi, wato a kwance a asibiti ma kenan yake? Wayyo Allah dama ban miƙa wayan ba, hannu bibbiyu na saka nayi tagumi ina kallon M.G

da suke ta magana, zuwa chan naji yayi masa sallama ya ajiye wayan, kaman a sama na jiyo muryan shi yace.

"Tafiyan A.G wani abu ne da ya daƈe yana muƙurƙusa na, idan kinga na shiga gidan kakanun shi wato gidan Alhaji Inuwa tou sai ranan jumma'a, shima ba ko yaushe ba, domin yadda rayuwa ya ƙara juyawa goggon mu, Aysha goggo tasha wahalan rayuwa na kula da mu, kuma bazaki taɓa ganin gazawanta akan komai ba, goggo kitso ya janye a wurinta, yanzu ƙarfin sana'anta surfe ne da dakan hannu sai kuma masan da takeyi da safe, kuma babu lalaci ko kunya zamu fitar da tallen masan nida Hassan da hussain, da kuma kananzir ɗin inna yɗan'biyu, wanda yanzu itace zaune a ɗakin innan mu.

****

Shekara na takwas yayah auwal ya gama school ɗin, wanda baya zuwa hutu sai ƙarshen shekara, domin yayah auwal ana hutu yake tsayawa da wani mutum ɗan bauchi mazaunin chan lagos, yana taimaka miki shi da zaman shagon shi, a haka yayah yake ɗan tara abun buƙatun shi na karatu, wanda kuma bayan wasu yɗan watanni ya kan turowa goggo da wani abu, lokacin da ya dawo gida yayi wani fari tass da shi, idan ka ganshi sai ka ɗauka balarabe ne ko wani bature tsabar farin shi, yayah sanie kuma yana level 2 a A.T.B.U, yayah Rabi'u this year ya rubuta weac da neco, amma shi hankalin shi gaba ɗaya akan ball ne, don ma yayah auwal ya gaya mishi dole fah sai yayi karatu, twins kuma suna S.S 1, ni kuma ina aji huɗu na primary, haka mukai ta murnan dawowan yayah auwal, babban abun farin cikin kuma yau shinkafa da miya goggo ta dafa mana, gashi har nama aka saka, nidai murna nan shinkafan yafi mun murnan dawowan yayan mu ma," A.G yana zuwa nan sai da muka kalli juna mukayi dariya, domin wani nishaɗi yake ji idan yana maganan shinkafan nan, nima kuma abun daɗi da dariya yake sakani, domin idan ka dube shi a yanzu yadda Allah ya dafa mishi baxaka taɓa tunanin ya shiga wani mawuyacin rayuwa ba.

****

"Rayuwa ta cigaba da tafiya har nagama primary, baki tambayeni wa yake biyan kuɗin makarantar su yayah ba? Don ni dai har zuwa lokacin Aunty Rashida (mummy) ke biyan nawa, kuma idan an ɗauki lokaci tana mana aika, daga baya ma Daddy ya haɗa har da twins yana biya mana, karatun yayah auwal goggo ce ta sayar da wani gonan ta na gado, kuma yayah bai tsaya a neman kuɗi ba, son sai daga baya yake gayawa goggo har wanki da guga yayi a lagos kuma ya samu, so shi ya cigaba da biyan kuɗin shi, sai abun da yafi ƙarfin shi wannan ɗan'unguwan mu da yazama mishi uban ɗaki ya taimaka, yana gama service ɗinshi kuma ya tattara ya koma chan lagos ɗin, domin ya tsaya mishi ya samu koyarwa a wata private school, yayah sanie kuma da yayah rabi'u wannan bappan namu ne ya taimaka musu, sai kuma abunda goggo ta kalata, yayah rabi'u result ɗin shi baiyi wani kyau ba, saboda bai maida hankali ba, ba kuma babu kan bane, tsantsan ƙwallo kawai da yasaka a ranshi, saboda haka *BACAS* ya je yayi diploma ɗin shi a *PUBLIC ADMIN* yana gamawa kuma ya samu ɗaurin gindin fara buga wasan ƙwallo a team na wikki, kuma Alhamdulillah ya shiga a sa'a, don babu daɗewa sunan shi Rabi'u ya ɓace, sai dai kiji ana cewa *JOHN ZAKI* kuma babu laifi duk gidan mu babu sama da shi a son walwala, duk wani abun da yasa mo goggo ne, sai kuma ni ɗan lelen shi, don a lokacin asiri na yafara rufuwa da kayan gwanjon da yake tsinto mun, ga takalma har kala uku nake da su alokacin masu kyau, ina son ƙwallon a raina amma fir Goggo ta fige mun, kullum john zaki ya shigo na ringa tsalle ina mishi waƙan yɑn ball kenan, tou anan zakiga fushin goggo, rarumo abu takeyi ta jefeni, "ae wallahi yadda Rabiu ya ƙeƙashe yaje ƙwallo kai kam ƙaryar ka, don da wuri zan taroka", shidai dariya kawai zaiyi kiji yana, "sai goggon mu" hararan shi takeyi ta shareshi, idan su twins suna nan su kama dariya suna cewa, "ana yafito mata na goro kuma zakaji tace, "tou Allah yayi albarka Rabiu", dariya kowa yakeyi har goggon, don yadda suka iya kwaikwayon muryan mutane.

Bana mantawa lokacin da zamu gama primary, wani abokina da muke zaune sit ɗaya da shi Sulaiman, zasu koma kaduna da zama, dama baban shi banker ne, ya rubuta mun number wayan su, da yake landline ne lokacin, akan idan sun tafi zamuyi waya, shirme irin na yarinta, nasan fah unguwar mu gaba ɗaya gida biyu ne kawai masu wayan, daga gidan *Alƙali Abdullahi* sai gidan *Alhaji inuwa* gidan Alh inuwa kuma sun tafi umarah lokacin, kuma naji ance daga chan zasu wuce England su duba A.G da baiji daɗi ba, don ni naraka Goggo yiwa kakar A.G sallama, anan take gayawa goggo A.G asthman shi yana yawan damun shi, don lokacin wai har oxcygen aka saka mishi, duk da yarinta na damuna amma sai na shiga halin damuwa, gashi mun daɗe bamu gaisa ba, don an hana mu gaisawa, A.G duk ranan da ya gaisa dani iyayen shi sunce ya kan ɗauki tsawon lokaci yana fushi da kowa, makarantar ma ƙin zuwa yakeyi, idan an matsa kuma yayi ta kuka kenan, gaba ɗaya sukan kasa gane kanshi, gashi dai Allah ya ƙara basu haihuwan yara biyu amma duka mata ne, sun koma da 1year aka haifi *HUDA* wato A.G ya bata shekara shida kenan, sai bayan three years kuma aka haifi *HEEDAYAH* amma duk

da haka son A.G daban ne a zuciyar iyayen shi, gashi kuma shi kaɗai ne mai ciwon asthmah ɗin, sai *HUDA* da ita tana da yawan mura amma ita bata da shi, sai dai ana kiyayewa sosai, bayan mun dawo ne nima nasamu kaina a damuwa da tunanin rashin lafiyan A.G, saboda haka na ɗauki paper da biro naje ɗakin yayah sanie, zama nayi a gefen shi nace "zan rubuta letter wa friend, idan nayi mistake ka gyara mun kaji yayah", murmushi yayi ya dafa kaina yace, "babu mistake ɗin ma da xakayi ae kai nasan gwani me mai brain", daɗi naji sosai na hau rubutu, gaisuwa na mishi da tambayan yayah jikin shi? Sannan na bashi labarin abokina sulaiman, na kuma tambaye shi yaushe zasu dawo ƙasan"?

Gyara kaɗan yayah ya mun, da farin ciki na wuce gidan su A.G na kai letter na akan akai mishi, itama kakarshi da farin ciki ta karɓa, ta kuma mun alƙawarin zata kai mishi insha Allahu, daɗi naji na dawo gida.

Lokacin da muka rabo da abokina sulaiman, sai nayita tunanin ina zan samu waya na ƙirashi? Babu ɓata lokaci na tuna da gidan Alƙali, banyi shawara da kowa ba na wuce direct gidan, don na taɓa jin yayah hassan da yayah hussain suna labarin wayan a tsakar gida yake, kuma ana barin mutane suna ƙira da shi, don sun taɓa raka wani abokin su yayi waya da yayanshi da yake Abuja, tuna haka ya sakani tafiya gidan kai tsaye, cikin sa'a kuma ina isa saiga yʏar'gidan mai suna Ummatiti, domin lokacin ita ɗin budurwa ce, ganin ita tana da sauƙin kai don bata da hayani da faɗa irin na yaran gidan, ba kamar ƙanwarta waleedah ba, da sauri naje inda take shirin shiga gidan na rusuna nace, "ina wuni Aunty ummatiti" da hanzari ta juyo ta kalle ni fuskanta ɗauke da murmushi tace, "ƙanina yau kaine da kanka kake gaishe ni? Yau ka kawo mana ziyara ne? Lallai girma ya fara zuwa", tana faɗa hannunta riƙe da ni, nidai ban kawo kalmar ƙanina da ta faɗa da wani muhimmanci ba, kawai dai na ɗauka don ta girme ni ne.

Ina murmushi na nace, "nazo ki taimaka ki ƙira mun abokina mana Aunty", na faɗa ina miƙa mata takardar da yake ɗauƙe da number shi, murmushi tayi ta miƙa hannu ta karɓi takardar, tana riƙe dani muka fara shiga cikin gidan, "haba ƙanina kai da gidan ku sai ka nemi izini na? Kaima fah mai yiwa wani alfarma ne", nidai sai daɗi nakeji muka shige gidan, lokacin babu kowa a tsakar gidan mai cike da interlocks, tsakar gidan mai girman gaske, yana ɗauke da wani varender mai kyau, wanda zai sadaka da babban parlon iyalen gidan, ana a gefe akwai wani friedge dogo da aka ɗaura telephone ɗin akai, babu kowa sai masifaffiyar mai tuwon gidan sun nan, muna shiga ta fito daga kitchen fuskan ta ɗauke da fara'a tace, "lale maraba da uwar masu gida, uwar ɗakina kin dawo kenan"? Murmushi Aunty ummatiti tayi tana saƙo da wayan ƙasa, "eh Babah na dawo, gashi yau na haɗu da autan mu wai yazo zaiyi waya, shine fah ya tsaya a waje yana neman alfarma, bayan shima mai yiwa wasu aƙfarman ne", ta faɗa tana saka numbobin akan wayan, nidai daɗi kaman zan yi tsalle, ɗagowa tayi ta kalle ni tace, "ƙanina ina ga ana kan layi ne, amma zo kaga yadda ake yi, ni zan shiga na chanja kayane, idan baka gama da wuri ba zan

fito mu sake gaisawa, sai na kaika ka gaida mamana," murmushi nayi domin wani daɗi nakeji idan tace mun ƙaninta nan, duk da bawai wani kyau take da shi ba, don baƙace sai dai doguwa ce kamar mahaifin mu, amma banga ta yi kyau kaman shi ba, sai dai akwai jininshi a tare da ita, so baza ace bata da kyau ba, don akwai ido da dogon hanci, sai dai baƙar fatan kawai.

Tana juyawa ban wani ɗau lokaci mai tsawo ba na gwada saka numbobin yadda ta gwada mun, ae kuwa sai naji wani ƙuwwwwt, ƙuwwwwttt, alamar yafara ringin, banji ɗaukan wayan ba sai naji wani abu mai azaban zafi na ɗaukan hankali a gadon baya na, da ƙara abun da fita a hankali na duk alaokaci guda naji shi, kuma ban ƙara jin komai ba ko fahimtan komai ba sai zuwa wani lokaci da naganni kwance a ɗakin goggo na, goggo da innah yʻan'biyu da dukkan yayuna, banda yayah auwal da baya nan duk suna tsaye akaina, gefe ɗaya kuma ga Umar mai chemist a tsugune akaina yan gyara mun drip, kaman ma yana chanja wani ne, don maga kaman sabo ake ɗaurawa, tashi naso yi amma sai naji wani azaban zafi a bayana, bansan lokacin da nace, "wash Allah"

Da sauri goggo ta riƙe ni idon ta na zuban hawaye tace, "mukhtari na sannu ko, ka tashi?.... Mekake so?" ta faɗa hawaye yana ƙara bin fuskanta, gefe ɗaya kuma Rabiu ne ya riƙoni jikin shi yana mun sannu.

Mai da ido na nayi na rufe ina jin wani mummunan azaba a jiki na, ga wani nauyi da naji kaina yayi mun, ga hannu na ɗaya da naji kaman ba ajikina yake ba dom azaban azaba, a hankali na sake buɗe idona nace, "goggo na ciwo nakeji, me ya same ni ne"? Kuka Goggo ta fashe da shi gaba ɗaya ta rungume ni a jikinta, muryanta da jikinta gaba ɗaya suna rawa, "haba mukhtari na, meyasa ga cikin malam Garba, kaƙi ka fito a cikin wanda bai san daraja da girman ka ba? Wanda me aikin boyi - boyi ma agidan shi tafi daraja da girma? Wannan abu yana mun ciwo ni Fatima, wannan abun yana firgita ni, Allah ka raya mun mukhtari na, Allah ka ɗauka ka shi ɗaukakan da kake yiwa bayin ka nagari makusan tanka, Allah kayiwa mukhtari ni tanadi na alkahiri duniya da lahira, Allah ka ciyar da su a jikinka yadda basu ƙaunar ka Allah ka ƙaunace shi", ta ƙarasa tana fashewa da kuka, chan kuma naji muryan Bappan mu yana cewa, "ashha Alƙali basu kyauta ba, yau har an ƙure wannan baiwar Allah mai haƙuri, gaskiya basu kyauta ba Allah ya saka maka mukhtari, Allah ya fitar maka da hakkinka akan duk wanda yake da hannu aciki, don wannan kam ba halin Alƙali bane, yaran wasu ma ya riƙe, yaran nashi ma nawa ne? Amma duk gidan cike yake da yaran yʻan'uwa, ashsha abu bai yi daɗi ba", ya faɗa yana matsawa jikin ƙofa, inna dai sai kuka take tayi Allah kaɗai yasan me yake sakata kuka, nima sai lokacin na fara kuka don ganin yʻan'uwa na da goggo na suna ta kukan, wanda ni har lokacin ban san me ya faru da ni ba, don sai daga baya goggo ke hiran da yayah auwal da yazo tukun na sani, kin san waye ya mun haka"?

 Girgiza kai nayi alaman a'a, fuskana cike da tausayin shi har da goggon shi da yʻan'uwan shi,

Murmushi yayi ya sunkuyar da kanshi ƙasa yayi shiru na wani lokaci.

Shifaɗo mai tuwon gidan mu, wata muguwar bafulatana ce garin su yana kusa da yankari, ni ban taɓa ganin muguwar mace ba irinta, ashe ganin yadda Aunty ummatiti tayi mun sai ranta ya ɓaci, windon ɗakin maman su ummatiti ta zaga ta kai mata gulman, ita kuma maman su Aunty da yake itama muguwar ce sai tace maza ta koreni, babu ɓata lokaci kuwa shifaɗo ta shigi ɗakin da ake zuba itace, ƙato ta ɗauko, shine ta zanga mun a baya na, gashi jikin shi akwai ƙwarzane na faskare, shine yayi mun wani yanka a bayana, Allah ne kawai ya kiyaye bata naƙasa ni ba, domin ba ƙaramin ciwo taji mun ba, amma abinda zai baki mamaki da haushi abu ɗaya ne, haka aka ɗauke ni ranga-ranga aka kaiwa goggo nah, yan gidan mu ne suka nemo wani ma'aikacin chemist yazo ya dubani, bayan yayi mun dressing ya ɗaura mun drip, shima a duk ƙoƙari na goggo ne, don da bappan su yayah auwal yaje ya samu Baba nah da maganan abunda ya faru, sai yace shi tou me zai iya cewa akai? Yaron ne ae mai laifi,, me ya kai shi gidan, shi ae yace kada a taɓa dosan shi da al'amurah na, jikin kowa sai da yayi sanyi a gidan mu, shine kukan da goggo na tayi kaman babu gobe, nidai an dake ni an daki banza, don ko gidan mu babu wanda ya biyo bayana banda Aunty umatiti, don ita har kuɗi tabawa goggo akaini asibiti, amma goggo taƙi amsa, ta mata godiyan shigowan da takeyi dai, anyi abun da yan watanni ne yayah auwalu yazo, a lokacin ne kuma naji goggo tana mishi bayanin abunda ya faro, anan kuma masan Alƙali shine mahaifina, lokacin dana fahimci haka nayi kuka baka ɗan ba, don wallahi ayshaa banyi farin ciki ba,", ya faɗa lokaci ɗaya dana taɓa ganin ranshi babu daɗi fuskan shi a wani irin yanayi.

Ajiyan zuciya nayi na share hawayen da bansan lokacin da suka zubo a idanuna ba.

Muna haɗa ido yayi saurin kawar da nashi gefe, sannan ya cigaba da bani labarin, "Ayshaa nayi jinya sosai, don da ƙyar ciwon ya warke, amma lokacin dana warke sai naji ko ƙofan gidan Alƙali bana son gani, duk wani abu daya ƙunshi yan gidan kuma sai na kiyaye, Babbar jikar shi yar gidan safiya lokacin ake bikinta, Babanta wani babban mutum ne a cikin garin bauchi, don shahararren ɗan siyasa ne, ita kuma sa'o'i suke da umatiti, watarana na fito ta lungun da zai kawo ni gidan mu ɗauke da tallen masa na sai mukayi kicibus da ita tare da umatiti, tsayawa umatiti tayi hannunta riƙe da haɓan ta tace, "ɗan'uwa idonka kenan? Wato guduna ma kakeyi ko? Tou ko kaƙi Allah kai ƙanina ne, kuma favourite ƙanina", ta faɗa fuskanta cike da fara'a tana miƙa hannun ta ta sauƙo da tallen masa na, nidai murmushi kawai nakeyi don gaskiya ita bazan iya rabuwa da ita ba, kuma baxan iya ƙin kulata ba yadda aka ce kada na ƙara kula yan gidan alƙali, buɗe daron masan tayi taga saura guda ɗaya ne a ciki, tana kallona fuskanta da murmushi tace, "wayyo ƙanina yayi kwantai ɗin guda ɗaya, tou nawa ne a bani naci"? Murmushi nayi na ɗauko leda na

saka masan a ciki, cike da kunya na miƙa mata nace, "Aunty gashi ba sai kin bada kuɗin ba, dama zan kaiwa mai baran gefen gidan mu ne", na faɗa ina cike da kunyanta, "wasa nake maka ƙanina", ta faɗa tana juyawa wurin ta gefentan tace, "wannan fah shine ƙanin mu wanda baba ya auri matan malam garba",

Murmushi ɗayar tayi tace, "ae naga kaman shi sosai da kaka wallahi, ae ko yau zan gayawa mama naga autan su", itama umatiti dariyan tayi tace, "ɗan farin gidan mu ba," kallo na tayi tana nuna ta gefenta tace,   "ƙanina wannna ƙatuwar da kake gani yʻar kace, domin mamanta ce babbar yar mu, auren ta za'a fara wannan satin, fatan dai zaka zo mana ko"?.

Murmushi nayi idona akan amaryar mai suna ummulkhair, itama murmushin tayi tace, "zakazo ko kawu"?   Faɗin kawun daa tayi yasaka na ƙyalƙyale da dariya, suma duk dariyan sukayi, ummul ɗin tace, "kana dariya ko? Sai kaga na turo mai auren nawa yazo gaishe da kawu mukhtar tukun zaka yadda kai kawu ne inaga", dariya na sake ƙyalƙyalewa da shi, kyautan kuɗi ta bani amma naƙi karɓa, da suka matsa mun nace , "za'a mun faɗa ne a gida idan anganni da kuɗin," basu ja ba suka mun sallama nima na musu na wuce ina ta waiwayan su, a ƙarahe zasu fita lungun suka ɗaga mun hannu, cike da farin cike na shigo gidan mu.

****

Rayuwa ta juya damu yadda ta so, mun sha wahala kaman abubuwa baza su wuce ba, sauƙin mu idan iyayen A.G sun mana aika mukan ɗan farfaɗo, ko kuma idan Alhaji inuwa ya waiwaye mu, sannan har zuwa wannan lokacin su suke biya mun kuɗin makaranta, amma duk da haka idan akace mace ita zata riƙe marayu, gaskiya akwai wahala, Allah sarki goggo, ta wahala da mu tayi hidima da ɗawainiya damu sosai, babu abinda zamuce sai dai Allah ya biyata, haka rayuwa tayi ta ja damu har yayah sanie ma ya gama karatu, a lokacin kuma yayah auwal ya samu scorlaship zuwa masters ɗin shi a spain, murna kaman zamuyi yaya da ranmu.

Kafin tafiyan shi ya tattaro ya dawo bauchi, lokacin kuma yayau sanie ya tafi service a *KADUNA* bayan tafiyan shi da 1month yaya auwal ma ya tafi, ga yaya rabiu lokacin bai cika zama ba, suna yawan fita ball da club ɗinsu na wikki, munsha wahalan kewan su, a lokacin kuma na ƙara dagewa da ƙwazon tallen masa, don zuwa lokacin innah yʻanbiyu ta haƙura da sayar da komai, mune dai kawai muke iya ɗawainiya da ita, babu abunda ya dameni da mutane, har nazo aji biyar na secondry ina tallen masa na, lokacin su twins suna karatu a maiduguri.

****

Yayah sani ya kwana biyu bai samu aiki ba, don sai da ina ss 2 tukun ya samu aiki a CBN, daga lokacin abubuwa suka fara mana sauƙi na rayuwa, abun farin ciki kuma muna gama secondry school su A.G suka dawo ƙasan, lokacin dsddy yayi ƙerarren gidan shi a fadaman mada, lokacin da A.G suka dawo ƙasan idan kin ganshi kaman wani bature, gashi lokacin shirun shi ya ƙaru sosai, ranan tsabar murna kuka A.G ya fara da ya ganni, a gidan Alhaji Inuwa muka kwana babu wanda ya hanani, har gida mukaje da goggo tayi wa mummy barka da dawowa, idan kaga mummy baxaka ce ita ta haifi A.G ba, domin mummy irin mutane masu faran -faran da mutane ne, gashi tana da son hira, amma A.G ko yadda kika san kurma, sai dai kuma yana da bala'in fahintan mutane a rayuwar shi, zaman lokaci kaɗan zaiyi da kai ya fahimci kai waye, kuma zakaga kaman baya hankalce da kai,

Ayshaa naji daɗin dawowar su A.G ba kaɗan ba, result yana fitowa babu ɓata lokaci muka samu admission a *ABU ZARIA* Law suka bawa A.G, ni kuma Mechanical engenearing, haka muka sake ƙullewa kaman bamu taɓa rabuwa ba, a wannan lokacin kuma farina ya samu dama da sararin sake dawowa, don komai daddyn su yake mana babu banbanci, hatta sutura babu banbanci a tsakanin mu, ballantana kuma mummy da tafi sakewa ma da ni akan A.G.

Muna gama university Daddy ya sayawa kowan mu mota, nawa fari na A.G baƙi, amma duk iri ɗaya ne, a lokacin kuma yayau auwal yazo nigeria, yayi wani irin zama babban mutum gashi ya samu aiki acan bayan ya gama karatun shi, yazo da maganan auren shi da yar ubangidan shi da suka zauna a lagos, dama mutumin ɗan nan unguwar mune kobi, zama ne kawai ya kai shi lagos ɗin da iyaleshi.

Babu ɓata lokaci aka saka rana, kafin ya koma kuma akayi auren su, yanzu maganan da nake miki suna chan spain da familyn shi, yaran shi uku duka maza, yayah sanie kuma yana zaune a lagos da matar shi itama yar bauchi, yaran su huɗu, mata biyu maza biyu, sai yayah rabi'u da yake zaine a nan bauchi, amma yana da team a waje da yake zuwa bugawa, kuma yayi nisa a harkan ball sosai, yaran shi biyu duka maza, sai twins, yayah hassan yana auren yar ƙanin su innah, Ɗan su ɗaya, sai yayah hussain da yake auren sister A.G *HUDA* su kuma twins suka haifa duka mata, yanzu saura ni autan goggo" dariya duka muka ƙyalƙyale da shi.

Bayan mun gama service sai A.G ya tafi law school, anan suka haɗu da Barrister Ahmad, anan kuma Allah ya haɗa jininsu sosai, nima dalilin A.G Allah ya haɗa

jininmu, nasamu kuɗi a cikin shekara biyu na ban mamaki Ayshaa, Daddy shi yayi mun hanya ta hannun wani mutumin shi bayarabe a lagos, na samu contract bana wasa ba, sannan yaxo ya haɗani business da wani abokin shi balarabe, inda shima yayi mun hanyar haɗuwa da wasu a china, tou shine sanadin arzikina, wanda sanadi addu'an iyaye ne yake tafe dani, yanzu haka nayiwa goggo gida a bauchi, ɗuk wani abun jin daɗin rayuwa goggo ta samu, sai dai inna yanbiyu shekara biyu Allah yayi mata rasuwa, baki tambaye ni ina Baba nah ba"?

Murmushi nayi ina kallon shi cike da tausayin rayuwar shi nace, "ae nasan bazaka manta ba, idan an zo wurin zaka gaya mun".

Murmushi shima yayi yace, "gaskiya ne kam."

Baba nah ya aurar da yaranshi dukkan su, ummatiti tana auren wani ɗan bauchi, a lokacin banker ne, mamanta tana ta ɗaga kai wa mutane, don ya mata kaya na fitan hankali, auren su nada 5years yaran su biyu, alokacin banki suka mishi halinsu, bayan an sallame shi aiki sai abubuwa suka dagole musu, amma dai Baban mu bai barshi haka ba sai daya sama mishi aiki a ATAP, samun dai ba irin na da ba, ita dai ummatiti bata damu ba, saboda tana son mijinta, yanzu haka yaransu shida da shi, sai mai bi mata *WALEEDAH* ita wani ma'aikacin nefa ta aura, yanzu haka suna zaune a federal low-cost bauchi, ita ma yanzu haka tana da yara kusan shidah, duk da rayuwa ba yadda suka so ba, sai dai godiyar Allah, ita babbar yarmu yanzu mijinta girma ta cin mishi, gida de idan kin gani ginin gidajen manya ne, amma babu komai na kwabo a hannun shi, hakan yaran ta biyun su TJ duk babu wanda yayi dogon karatu a cikin su, kaman ƙaramin sune ma yayi diploma, duk dai nauyi ya hau kansu na iyalai, kuma Baban ne dai a tsaye akan kowa.

Lokacin da muke service Baba na ya kwanta jinya Kidney, duk wani kuɗi na Alƙali ya ƙare akan jinyan nan, India aka fita da shi aka cire kidney ɗin shi aka mishi dashe, dawowan su nigeria bai ɗau lokaci ba ya sake kwanciya jinya a Gombe, gashi su Tijjani basu bar shi ba da sata, komai nashi sai godiyan Allah, haka akai ta sayar da kadaran shi ana jinya, wata ranan Monday da bazan taɓa mantawa ba Aunty ummatiti ta ƙirani da safe a waya, da yake muna zumunci da ita, kuma ina zuwa gidan ta, sai dai gidan mahaifinane kawai ban taɓa shiga ba tunda abun nan ya faru, Yayah safiya ma ina zuwa gidan ta, domin ni da ummul yar ta muna

zumunci, don duk shigowanta bauchi sai ta nemi ni, idan naje ne wurinta muka saba da yayah safiya, ita yayah safiya kana ganin mu kasan yayan mutum ɗaya ne, saboda yanayin zubin halittan mu iri ɗaya ne, hatta da bakin mu akance irin na Alƙali ne, banbancin ni fari ita baƙa, lokacin da ta ƙirane ta ke gaya mun Baban mu ne yasaka ta ƙirani a waya yana nema na, tsoro maganan ta ya bani, don ban taɓa tunani ko zaton Alƙali zai nemi ni ba, nidai ban bata cikakken amsan zan zo ko bazan zoba, zuwa yamma ta sake ƙirana, shiru nayi ban ce komai ba, sai da ta matsa mun tukun nace Goggo bazata bari ba shiyasa, shiru tayi zuwa wani lokaci, bata sake cewa komai ba sai sallama da ta mun,

Na ɗauka ta bar maganan kenan, amma kawai ranan laraba sai ga yayah Rabiu ya shigo ana idar da sallan Magrib, bayan sun gaisa da Goggo ne sai ya ƙira number yayah auwalu, dogon bayani yayiwa goggo akan Alƙali ya neme shi a waya akan don Allah su taimaka mishi naje yana son ganina, da ƙyar yaya auwal ya lallaɓa goggo, don sun fi awa biyu ana abu ɗaya, ranan goggo taci kuka kaman yau komai suka faru, bayan sun gama ne yayah rabiu ya ƙirani na shigo, bayanin duk yadda baba nah da yayah auwal sukayi Yaya Rabi'u ya bani, sannan ya umurceni na shiryah gobe insha Allahu da sanyin safe zaizo mutafi Gombe asibiti na gaida babah nah,.

Faɗin baba nah ɗin da sukayi sai duk najini wani iri daban, ina kallon goggo yadda take ta kallo na cike da tausayawa, hakan duk sai yasa naji hankali na ya ƙara tashi, nidai tsakanina da Baba nah babu sabo, don zance a girmana na gaisa da shi kusan sau biyu, ɗaya lokacin auren yayah auwal ne, na fito daga ƙwallo shi kuma suna tsaye tare da limamin unguwar mu a ƙofar wani gida, daga gani kuma gidan abokin shine, don shima alƙali ne, kallon da liman ya bini da shi yasaka na tsaya na gaishe su, har na kure layin idon Alƙali yana kaina, sai wani haihuwan ummatiti na uku, ina zaune a parlon ta sai gashi ya shigo shida abokinshi da mijin Aunty umatiti, babu yadda na iya dole na gaishe su, lokacin farkon shiga na university, wannan ranan ma har na fita idon shi yana kaina,

Saboda haka duk sai naji hankali na a tashe, zuwa dare kuma sai naji na samu kaina da tunanin tou yyh jikin nashi yake da har yake nema na? Tou idan naje me zaice mun? Haka dai na haƙura na kwanta.

****

Washe gari wuraren ƙarfe goma na safe muka shiga asibitin Gombe, muna shiga Aunty umatiti ta fito ta tarye mu har zuwa ɗakin da Alƙali yake, koda muka shiga mun samu yana bacci, a haraban asibitin illahirin matan shi ne da yaƴan shi zaune a kan darduma, gaishe su mukayi amma suka mana wani irin amsawa, mudai bamu tsaya bin takansu ba muka wuce ciki, a ciki muka tarar da Yayah safiya da mamanta, wato uwargidan Alƙali, sai kuma Tijjani, da fara'a matar ta amsa gaisuwan mu, wanda naji suna ce mata *HAJIYAH* sannan na risina na gaisa yayah safiya, itama da fara'a ta amsa mun, har tana tambaya na "yayah karatu", banzan kallo Tijjanin ya mana lokacin da muke gaishe shi, amma daga ni har yayah sanie bamu bi takan shi ba, saboda babu abunda ya fimu kuma muna cikin kyakkyawan kama da shiga.

Shiru ɗakin yayi bakajin komai sai ƙara na'ura sai kuma nishin Alƙali kaɗan-kaɗan, alaman jinya taci jikin shi, gaba ɗaya ya rame yayi baƙi, sai naji tausayin shi da tausayin kaina ya kamani, yanzu wannan ɗin mahaifina ne a kwance? Wanda yayi silan zuwa na duniya? Sai naji wani rauni da ban taɓa samun kaina a ciki ba, tsakin da Tijjani yaja ne lokaci ɗaya ya maida hankalin mu kanshi, "tou wai tunda kun samu yana bacci kujira mana a waje sai ya tashi tukuna", yafaɗa kaman zai kai mana duka, murmushi hajiya tayi tana kallon shi, "wani irin magana ne haka Tijjani? Ae yadda Alhaji yake ta jiran isowar mukhtari kyaunta ae yana farkawa ya fara cin karo da shi, kai kafita ne da kake cewa wasu su fita? Ko ka manta duk matsayi ɗaya kuke taƙama da shi a wurin shi? Yadda kake ɗa na halak, haka fa kowa da ka gani agidan nan yake a wurin shi", hajiya ta faɗa still fuskan ta da murmushi, kyaɓe baki Yayah safiya tayi ta harari Tijjani ta mayar da kanta wurin Aunty umatiti suna magana ƙasa-ƙasa.

Tsaki ya sake ja yace, "hajiya me ya kawo wannan maganan ka nan? Idan dukkan mu ɗaya ne a wurinshi ae dai ni bai jefar da ni ya barwa duniya ni ba, kuma idan shi wannan da bani da tabbacin ɗan Alhaji nema na gaske ya shigo ya zauna, tou shi ɗayan fah? Gayyan meye nashi shi kuma?"

Murmushi yayah Rabi'u yayi ya gyara tsayuwar shi yana facing ɗin Tijjanin, "gayyan autan shi na biyo, nazo da ɗan halal wanda mahaifinka ya nunawa duniya wannan ɗin ɗane kuma na halak, tunda kusan kwana nawa yake roƙan akawo shi su gana idan akwai rabon ganawan, kuma ina mai maka albishir cewa ɗan da aka barwa duniya, tou duniyar tayi mishi riƙo na gata da mutuntawa sama da wanda aka adana a gida ya ɓuge da tanɓelen rayuwa, rayuwar ma na hakkin wanda basuji ba basu gani ba, kuma wa kake da suna, tijjani ne kake ko wa? Tou kachi darajan jinin mahaifina da yake yawo cikin jinin naka mahaifin, kuma chi darajan jinin ƙanina da yake yawo cikin naka jinin, kuma kachi darajan marar lafiyan da yake kwance cikin bautar ubangiji, da wallahi idan na haɗa maka yawo da majina da haɗin jini a bakinka, da har abada ko shege ka gani bazaka sheganta shi ba ballantana ɗan halal, idan kuma kana jayayyah da hakan tou kaje wurin tsohuwar ka ta baka

amsan *MUKHTAR ALƘALI ABDALLAH* ɗan waye? Waye sanadin rashin girman shi a gidan mahaifin shi? Tou amma....." Yayi shiru yana girgiza kai bai ƙarasa ba, sai ya juya kaina yace, "M.G zan ɗan shiga gari, duk yadda ake ciki ko Alhajin ya tashi ka ƙirani, sannan duk abinda ya faru kayi haƙuri darajan wannnan" ya nuna mun Baba nah da yake kwance, ɗaga kai nayi alaman naji, sanann yayi sallama wa hajiya ya juya ya fita.

Tsaki Tijjani ya sakeyi ya juya ya fita a ɗakin, tsaki Aunty umatiti tayi ta nuna mun wurin zama sannan ta fita a ɗakin, bayanta yayah safiya tabi, aka barni daga ni sai hajiya a ɗakin, haƙuri hajiya tayi ta bani, ni dai bance komai ba sai murmushi, anan take bani labarin yadda Alhaji ya burkice tun suna India akan a nemo mishi ni nayafe shi, shi kam a nemo mishi Fatima da abunda ta haifa ɗan shi, haka dai akaita rarrashin shi ya haƙura, suna dawowa nigeria kuma sai abun ya mance mishi a kai, amma tun wancan satin ya ɗaga hankalin shi akai, tana kallo na tace, "kasan duk abunda ba na Allah da Annabi ba akwai ƙarshen shi, sai dai ba'ayi haƙuri ba, tou kaima ina ga tsakanimka da mahaifinka da aka shiga ne Allah ya kawo ƙarshen abun, duk da dai nasan ba haƙura za'ayi ba, sai dai Allah ya mana jagora kawai, amma akwai hakki kan, kaima sai ka dage da azkhar sosai,"

Ta faɗa idon ta akan Alhaji da yake ɗan mutsawa, nima da sauri na maida idona kanshi, wanda da hankalina yake kan hajiya cike da rashin fahimtar maganan ta, da rashin fahimtar inda maganan ya dosa, miƙewa nayi tsaye lokacin da naji muryan mahaifina yana, "ina mukhtar ɗin yake? Ku ƙira mun shi muyi bankwana, ku nemo fatima ta kawo shi na ganshi, ku bada kayan sallan shi akai mishi Yayah", abun da yake ta maimaitawa kenan hajiya tana riƙe da hannun shi, ido na zuba musu ina jin wani irin tausayin shi a raina, zabgegen mutum ƙarfaffah shine yau ya dawo ɗan ƙarami da shi, gaskiya jinya batayi ba, babu babban maƙiyi irin ciwo, kallo ni hajiya tayi tana mun alaman na matso.

Ina tsaye inda nake idona akan su, duk jikina yayi sanyi, ƙura mun ido Alƙali yayi, bayan ya gama buɗe idonshi akai na, muryah ƙasa-ƙasa na mai jinya yace, "mukhtar" kallon shi nakeyi kawai bance komai ba, hannun shi ya ɗago mun yace, "taho gareni auta, zo kagaya mun ka yafe mun, ina Fatima?"

A hankali naja ƙafafuna na ƙarasa har bakin gadon, banyi yunƙurin miƙa mishi hannu na ba yadda ya so, sai kawai naji hajiya ta jawo hannu na ta haɗa da na Alƙali, a hankali na ɗago idanuna na sauƙe akanshi, wanda naga fuskan shi cike da murmushi, numfashi yake ja cike da wahalan jinya yace, "mukhtar ina sonka ina son mahaifiyar ka, mukhtar ina son ka ina son yayunka su auwalu, amma haka kawai na wayi gari duk kun ƙaurace mun, Hajiya tagaya mun wai ni da kaina nace bana son Fatima da kai, wai na sallameku bayan na sake ta, ina yayana su Auwalu su Sanie? Banƙi ku ba, zuciyana tana sonku sosai, nakasa neman ka ne mukhtar, amma duk inda kake zuwa talle ko wasan ƙwallo ina bibiyanka, har makarantar ku

nake zuwa na ganka, amma ina jin tsoron na maka magana," ajiyan zuciya ya sauƙe hawaye yana bin kuncin shi, "kayafe mu duk abunda ya faru a tsakanin mu, kayafe mun mukhtar, idan Allah ya bani lafiya zanje nabawa fatima baiwar Allah haƙuri, damo sarkin haƙuri, Allah ya mata albarka, Allah yayiwa zuriyarta Albarka, na yafe mata, ita ma kace ta yafe mun inda hali," hawaye ne naji suna bin kunci na ganin yadda fuskar shi take zubar da hawaye, zai sake buɗe bakin shi yayi magana nayi sauri na ɗaura hannu na na rufe bakin shi, kai na ke girgiza mishi, "Babah kayi haƙuri, ni baka mun komai ba, idan ma kamun na yafe maka duniya da lahira, nine ma nake son kayafe mun hakkin ka da yake kaina wanda bantaɓa sauƙewa ba, duk abunda ya faru mun yafe maka daga ni har Goggo, kullum tana ce mun na yafe maka kada na ƙullace ka a zuciyata har ranan da zaka neme ni, saboda akwai hakkin haihuwa na da kayi Baba, ni kamun komai a rayuwa da nazam ɗaya daga cikin yayanka, kai dattijo ne mai nagarta, kai adali ne kuma mafi girman alkhairin uba acikin duniya," hannu na hajiya ta riƙo kawai sai naji ta fashe da kuka, daga bayan mu ma kukan mukaji, wanda ba kowa bane sai Aunty umatiti da yayah safiya, sai mijinta da suka rako ya duba jikin Alƙali.

"Alhamdulillahi da tsatso nagari! Alhamdulillahi da uwa ta gari!! Wannan ya nuna mun kai halataccen ɗa ne daka fito ta tsatso mai kyau, ya nuna mun Fatima tayi namijin ƙoƙari wurin baka tarbiya, Allah ya saka mata da mafificin alkhairi, Allah ya saka ta cikin aljannatul firdausi" "Ameen" dukkan mu muka amsa da shi, duk wanda ya shigo a ranan gaishe da Alhaji sai yayi mamakin yadda gaba ɗaya ya rungume hannuna a nashi, don ko bacci yayi sai nayi dabara nake zare hannu na, lokacin da yayah Rabi'u ma ya dawo, Alƙali yayita neman gafar shi, ya kuma nemi da ya nema mishi gafaran yan'uwa na da mahaifiyata, Yayah Rabi'u ko agaban kowa ya ƙira goggo da dukkan yayu na ya saka wayan a handsfree duk suka gaishe shi, suka kuma jaddada mishi sun yafe mishi, da ma kuma shi ubane a garesu, mahaifi kuma ba ya laifi wa yayan shi idan yaran yan albarka ne kuwa, kuka yayi tayi lokacin da suka gaisa da Goggo, wanda har yasaka dayawan mu zubar da hawaye.

Yayah Rabiu bai yadda mun juya ba a ranan, ganin yadda hankalin Alƙali gaba ɗaya yake kaina, haka muka kwana a Gombe, nikan ma a asibitin na kwana, yayah ne ya nemi masuƙi.

****

Washe gari alhamis Alhajin mu ya tashi jikin kuwa da sauƙi sosai, don har aka zaunar da shi, wuraren ƙarfe 11:00 na safe muna shirin tafiya ya riƙo hannu na, murya chan ƙasa yace, "ayaba nake so ka saya mun naci", jin abunda yace na fita jikina yana rawa na ciro wallet ɗina naje na sayo ayaba masu kyau da girma, haka kurum naji na saya mishi ruwa, bayan naga ruwa masu yawa a ɗakin, lokacin da na dawo na samu an maida shi ya kwanta, bai samu yaci ayaban ba shi dai yana riƙe da hannu na har ya koma bacci, ganin haka sai Yayah Rabi'u yace na jira har sai ya tashi tukun mu kama hanya,

Tijjani kuma shi da yan'uwan shi da mahaifiyar su tunda muka zo sai suka ƙi shiga ɗakin, asibitin ma ranan basu wani zauna sosai ba, ita kuma maman su umatiti darajan yayanta da take tsananin son so takan amsa gaisuwa na, kuma takan zauna a inda nake, sai dai fuska babu sakewa.

Baba bai farka ba sai wurin magrib, haka na bashi ayaban nan yaci, sannan na bashi ruwan da na sayo yasha sosai, yana gama sha ya dubi ƙanin shi yace, "malam bello kaga ikon Allah ko? Ni bam taɓa ciyar da mukhtar ba amma ni kuma yau ya ciyar da ni, kuma nayi imani da Allah da halal ɗin shi ya ciyar da ni,".

Shiru ɗakin yayi babu wanda ya sake magana, sai chan ya ɗago kanshi ya sauƙe a kaina yace, "mukhtar na yafe maka nima ka yafe mun, Allah ya inganta rayuwarka duniya da lahira, jikina yana bani kaine tauraron da zai haska gidana bayan raina, ina neman alfarma ka kula da kowa da zuciya ɗaya, kayi saboda Allah kayi saboda jini na mahaifi da ya haɗa ku, insha Allahu duk mai cutanka bazai sake samun dama ba akanka har abada, Allah ya tsare gabanka ya tsare bayanka, nagode mukhtar, naso na saka maka suna Abubakar Garba, amma Allah baiyi ba, duk ranan da ka haifi ɗa ina so kasa sunan Malam Garba," yana faɗin haka ya maida kanshi kan kafaɗa na ya kwantar, bai sake cewa komai ba sai yayi shiru.

Mudai ranan bamu tafi ba, saboda Babah yaƙi barin mu tafi, don yayah yana zuwa muna mishi sallama ya girgiza kanshi yace dare yayi, mu bari gobe sassafe idan Allah ya kaimu sai mu tafi, haka ko muka haƙura, jiki dai Alhmdllh yayi dama-dama, har bayan ishaa na sake bashi ayaban rabi yaci, sannan ya miƙo mun rabin naci, haka ya zauna ido biyu bai koma bacci ba, wuraren shaɗaya na dare su yayah suka tafi inda suka sauƙa, aka bar ni daga ni sai Tijjani sai hajiya da maman su umatiti, shabiyu da rabi kowa yayi bacci sai ni da Tijjani ne idon mu biyu, shima Alhajin lokacin yayi bacci, a haka dai nafara ɗan gyanggyaɗi Ƙafan Alhaji yana kan cinyana, wuraren ƙarfe ɗaya naji shi yana ta kakari kaman yana son amar da abu, da sauri na buɗe ido na, anan naga hajiya ta buɗe ƙofan ɗakin ta shigo, bayanta maman su umatiti na biye da ita, "lafiya" naji tana tambayan Tijjani da shi ma ya

miƙe a lokacin, nurses muka ƙira muna musu bayanin amai yake son yi amma ya kasa, haka suka fara ƙoƙarin su don taimaka mishi, hajiya kuma ta koma jikin gadon tana ta mishi addu'a, nima ganin haka ya saka na fita a ɗakin naje nayi alwala na dawo, bayan sun gama abun da zasuyi sun fita na ƙarasa kan gadon na zauna inda kanshi yake, a hankali na maida kan shi kan cinya na ina mishi addu'a, a hankali ya buɗe ido kaman mai son kallo na, amma sai naga idon wani wuri yake kallo, ina mishi addu'a ina shafa mishi, hajiya ma da mama suna tayi, shidai Tijjani yana tsaye a bakin ƙofa ya ƙura mana ido, amma hankalim shi duk a tashe yake, muna haka har wuraren ƙarfe biyu da rabi, chan sai naji bacci yana ɗan ɗauka na, a haka dai har baccin yaci ƙarfina, kaman a mafarki naji muryan hajiya tana salati, mamah na taya ta, shi kuma Tijjani yana cewa, "hajiya wayace muku rasuwa yayi? Ku jira na ƙira ma'aikatan asibitin tukuna," jiki na rawa na tashi na gyara kan Babanah, na bi bayan Tijjani, sauri muka ƙira ma'aikatan suka shigo, duk wani wuri a jikina rawa yakeyi, waje suka saka muka fita, har tsawon wani lokaci su ka leƙo suka ƙiramu nida Tijjani, da sauri muka shige ɗakin, ido na mayar kan gadon da na bar Babanah akai, sai naga an lulluɓe shi har fuskan shi da bargon shi, zuciyata naji ya yi wani irin masifan yankewa, ido na ƙura mishi ban san me zanyi ba a haka naji muryan nurse ɗin yana cewa, " sai haƙuri bawan Allah yaya za'ayi kwana ya ƙare, Allah ya jiƙan Baba", da yayah Tijjani yake, shi kuma Tijjani yana kuka kaman zai yi yaya, a haka su hajiya suka faɗo ɗakin suna kuka suma tambayan Alhaji babu ko? Haƙuri ake ta basu nidai na rasa yanayin da nake ciki, ihuu zanyi? Kuka zanyi, addu'a zanyi? Komai ya tsaya mun chakkkk.

Gaskiya rashin iyaye wani abu ne mai ciwo da babu kwatankwacin shi, duk da babu sabo ko shaƙuwa a tsakanina da Alƙali, amma tabbas rashin shi ya buge ni, bugu ma bana wasa ba, domin ɗan zaman da nayi da shi a halin rashin lafiya na kwana biyu, sai naji kaman tunda na fara rayuwata muke tare, naji ciwo naji ciwon rashin mahaifina, ina tsaye duk iyalen Baba Alƙali suka shigo asibitin, kowa ka gani kuka yake, Aunty umatiti ne ta rungumeni tana kuka, amma haka dai ina tsaye ban iya komai ba, gari ya fara haske sai ga yayah rabiu ya iso duk a firgice, wurina ya taho ya riƙoni jikin shi, sai lokacin naji nayi wani ajiyar zuciya, wanda ya ɗan lafar da turirin da zuciyana yakeyi, yayah rabiu ne ya taya yʻan'uwa na da maxajen su aka gama komai aka ɗauki gawan Alƙali sai bauchi.

Yayye na babu wanda bai ƙira wayana ba, amma nakasa iya ɗauka, nidai har zuwa wannan lokacin babu wani kalma da ya fito daga bakina, babu wani hawaye da ya zubo daga idona, ganin bana ɗaukan wayan ya saka yaya rabiu ya amshe wayata ya kashe, don ko ƙiran A.G ma kaɗai ya isa a kashe wayan, muna isa ƙofar gidan naga mutane maƙil a ƙofar gidan, haka dai muka sauƙo iyaye mata da yayye na suka shige cikin gidan, mu kuma muka fara ƙoƙarin fito da gawan, ana fito da shi yʻayʻan shi da ƙannen shi suka shige da shi cikin gida, amma ni sai na tsaya a waje tare da yayah rabiu da su yayah hassan da hussain, muna tsaya anan waje muna ta gaisawa da jama'a, duk da dai ni kan kaina a sunkuye yake a ƙasa sai su yayah ne

ke amsa gaisuwan, muna haka chan wani ƙanin mahaifinmu ya fito daga cikin gida wurin da ake yiwa Baba Alƙali wanka, har inda muke tsaye yazo ya tsaya, "mukhtar ka shigo kayiwa mahaifinka addu'a", kallon shi nayi zuciyata tana wani irin tafasa, wai na shigo nayiwa mahaifina addu'a? Yana raye basu yi sanadin na shigo ba sai da ya bar duniya? Aiko bazan shiga ba, girgiza kai nayi alaman a'a, duk kallo na suka tsaya sunayi, daga nan naga yayah hassan ya wuce zuwa gidan mu, haka mutane suka taro a kaina suna magiyan na shiga, amma tunda na sauƙe kaina ƙasa ban sake ɗagowa ba, ballantana wani yayi tunanin zan ji kunyar shi nayi abunda suke so, bawai ban yafewa Alƙali bane ko banji nasihar shi ba, a'a gidan ne kawai da sukayi sanadin rashin shiga na tun yana da rai nake jin bazan shiga ba, ae baya raye, abunda suke ƙulafucin an bar musu, kafaɗa na naji an dafa, ko ban juyo ba nasan hannun goggo ne, lokaci ɗaya na sauƙe ajiyan zuciya, batace mun uffan ba ta saka hannunta ta riƙoni har zuwa cikin gidan inda aka keɓe ta varender baya na side ɗin Alƙali, binta nayi babu musu har inda gawan yake, bayan mu kuma yayu na suke biye da mu, ko wanne a cikin su ka kalli fuskan shi kuka yakeyi amma banda ni.

Har gaban gawan mahaifina goggo ta mun rakiya, dukkan ahalin shi suna wurin, matayen shi, yayyayen shi maza da matan su, yayunshi da ƙannen shi, jikokin shi da aminan shi duk suna wurin, da yake wurine mai gurman gaske, hatta surakunen shi suna tsattsaye a wurin, tsugunar dani goggo tayi a gefen yayuna maza wanda suke durƙushe a daidai kanshi suna mishi addu'a.

Addu'a sosai goggo ta mishi, ta ƙira sunan shi ta tabbatar mishi da duk wani abu daya faru ta yafe mishi, hajiya da wasu daga jama'an wurin sai da sukayi kuka lokacin da ta ɗago hannuna ta ɗaura a kanshi, tace, "Abdullahi rahmar Allah ta isar maka har kabarinka, halayen ka nagari, da jinƙan ka da kyautatwa talakawa dana ƙasa da kai Allah ya kai rahmar kabarinka , Allah ya haɗaka da mala'ikun rahma, Allah ya baka ikon amsa tambayoyin kabari, ga ɗanka Mukhtar ya yafe maka, Allah ya yafe mana gaba ɗaya, sai lokacin naji kukan gaske mai ƙarfin gaske yazo mun, abunda ya tokare ni a ƙirjina naji ya wuce kaman na haɗiye abu, ina kuka ina mishi addu'a, gaba ɗaya iyalen shi sai suka fashe da kuka, lokacin da nace na yafe mishi Allah ya jiƙanshi, sai naji yayah safiya ta runguma ni tana Alhamdulillahi, Allah ya maka albarka mukhtari, wannan lokacin dai nima dawowa nayi layin yan'uwa na mata, don da ƙyar su yayah hassan suka ɓanɓareni daga jikin gawan Baba nah lokacin da za'a fitar da shi, nayi kuka kaman numfashi na zai ɗauke.

Muna futowa aka saka shi a motan ɗaukan gawa, haka dukkan mu yayyan shi da ƙannen shi muka shige wannan motan, ina zaune dai-dai ƙafafunshi, sai hawaye nake sharewa, mu muka sakashi a kabarin shi, muka kuma zuba mishi ƙasa, lokacin da aka kammala komai aka fara shirin juyowa sai naji hankalina yayi masifaffen

tashi, tunani na yanzu fa za'a zo fara mishi tambaya, kuma tsakanin bawa da ubangiji shi kaɗai yabarwa kanshi sani, tsakanin bawa da bawa shine abun tsoro, Baba nah ya samu yabo a wurin jama'a, tou tsakanina da shi fah sai Allah ya iya kama shi fah? Duk da naji a zuciyata ni na yafe mishi, kuma dama ban tashi da wannan ciwon azuciyata ba saboda uwa ta gari danayi dace da ita, amma sai naji tsoro ya kamani, bansan lokacin da nasake furta, "Baba nah nayafe maka, na yafeka Babana har abadan", da sauri naji wani ƙanin shi ya rungumo ni yana kuka, sai yayah rabiu ma ya kamoni yana kuka muka fara tafiya, muna zuwa wurin shiga mota Alhaji Inuwa ya riƙo ni muka shi motan shi, nayi kuka a motan kaman zan shiɗe, bai bani haƙuri ba bai kuma hanani ba, sai baya na dayake ɗan bubbugawa kaɗan kaɗan har muka isa gida.

Nidai ban sake jin sha'awan na shiga gidan ba, don ko gaisuwa da ake shiga ayi acikin gidan wa iyalenshi ni ban shiga ba, inda Alhaji Inuwa ya zauna nan muka zauna nida yan'uwa na da suke taya ni jimamin rashin da aka mun, nidai ko kallon mutane bana yi, na sunkuyar da kaina ƙasa ina yiwa mahaifina addu'a.

Wuraren bayan sallan la'asaar sai ga A.G nawa ya iso tare da barr Ahmad, wanda ranan shine rana ta farko da muka fara haɗuwa da shi, kawai dai munyi sabo ta waya ne, tun isowar A.G naji wani sabon kuka ya taho mun, shima zuwa yayi ya riƙe hannu na, da ƙyar bakin shi ya furta, "sorry" daga nan bai sake iya yace komai ba, sai hawaye da yake ta sharewa.

Bayan anyi sallan ishaa muka shige cikin gidan mu wurin Goggo na, lokacin da mukaje na kalleta sai naji wani sabon tausayinta ya kamani, Allah sarki Goggo dukkan yayanta yau sun zama marayu babu iyaye maza, goggo na taga rayuwa a cikin rayuwarta, gaba ɗaya sai naga ta zabge wanda har girmanta ya bayyana kanshi sosai, kanta a ƙasa ta amsa gaisuwan mu, ina hankalce da ita yadda duk bayan wasu mintuna sai ta goge hawaye a idon ta, gefen ta na koma na zauna, a hankali na saka hannu na riƙo nata da ta ɗaga zata share hawayenta, kasa ɗagowa tayi ta kalle ni tayi, sai kawai ta kwantar da kanta a kafaɗa na tana kuka, "sannu mukhtar, sannu da rashin da aka yi mana yau, na tausaya maka na tausayawa kaina auta nah, zuciyata tana mun ciwo auta na, baka san daɗin mahaifi ba, baka raɓe shi ba har ya bar duniya, wannan wacce irin rayuwa ne muke ciki? Allah ya jiƙan Alƙali, Allah ya gafartawa malam Garba, Allah ya kai hasken kabarin su gabaki ɗaya", rungumeta nayi ina kuka a hankali, shiru parlon yayi banda sheshsheƙan kukan mu dukkan mu baka jin komai, a hankali A.G yazo ya rarrashi goggo tayi shiru, sannan ya riƙo hannuna muka fice a parlon muka wuce gidan su, nidai ranan sai bacci ɓarawo ne ya ɗauke ni.

****

Bayan anyi bakwai kowa ya watse, a washe garin rasuwar kuma yayah sanie ya iso, da yake raunin shi mai yawa ne, kuka ya dinga yi kaman mace, kada ki manta Ayshaa kinsan ko ba matsayin mahaifina Alƙali yake ba dama ɗan'uwan Baban su ne, saboda haka sun haɗa abu dayawa da Alƙali wanda dole suji mutuwar shi, don ko irin yadda aka tarwatsa rayuwar mu aka raba tsakanin mu yaci ka tausaya mun wannan rashin, ballantana kuma suma Bappan su ne kuma mijin mahaifiyar su, kuma mahaifina, Ayshaa ranan da Alƙali ya rasu sai Allah ya haɗa idanuna da wannan mai tuwon gidan alƙali wanda ta kwaɗa mun itace a baya, ganina a cikin gidan duk sai ta ruɗe, ranan uku tazo zata shiga gidan har ƙasa ta kai tana gaishe mu, nidai amsa mata kawai nayi na juyar da kaina, gashi ta manyanta lokacin, don ta kai goggo a shekaru, dama lokacin mijinta ya rasu ne tafara aiki a gidan mu, tun bayan anyi auren Alƙali da maman su umatiti kaɗan tazo gidan, shiyasa nasu ya zamo ɗaya, domin kowa gwana ce a munafurci, wajen zuwa tsubbu kuma nasu yazo ɗaya da mahaifiyar su Tijjani, don a wurin tane muka samu ƙabarin yadda akayi aka shiga tsakanin Alƙali da goggo, da ni kaina,, zanin Goggo da tayi shanya suka yanka, akwai wani malami ko bokan su zance a garin Dass, shi ya musu aikin da aka shiga tsakanin Baba Alƙali da Goggo na har abada, alokacin har abun cikin sai da akayi aikin rabasu, wato ni, kuma ta zaga ta gayawa maman su umatiti, ita dai tace neran ta bazaiyi kuka a wurin neman asiri ba, amma tunda sun fara ita zata taimaka musu da bakinta, kuma haka akayi ga asiri ga munafurci da akai ta haɗawa Goggo har sukayi nasara ba don Allah ya fi son su ba, sai don jarabawa na dana Goggo a haka yazo, su kuma Allah yana musu talala.

Bayan anyi arba'in ɗin Baba na suka ɗago maganan rabon gadon shi, haka suka tsaya tsawon sati guda suna harhaɗa abun da ya bari, nidai babu irin neman da basuyi mun ba amma naƙi zuwa, lokacin da Yayah safiya ta matsa mun da ƙira sai nace na wakilta mijinta a nawa, don ko dasuka nemi goggo itama baya na ta bi, yayah auwal nema da ya ƙirani bayan arba'in nake gaya mishi yadda mukayi da su, shiru yayi kaman baxai ce komai ba, sai chan daga baya yace, "auta kodai baka yafewa Baba bane"?

"Subhanallahi, yayah ae ni ban taɓa riƙe shi da zafi a zuciyata ba, kullum goggo kyawawan halayen shi take sanar mun har na girma, bata taɓa aibanta shi ba yayah, ko ita tace mun ta yafe mishi ballantana ni da yayi sanadin zuwa na duniya?

Wallahi ba haka bane, kawai dai naga saboda gado dama suka raba ni da shi, tou ni narayu da wuya da daɗi, gado kuma suje ni sadaka ma zanyi wanda zai isarwa Alƙali har kabarin shi".

Ajiyan zuciya yayah ya sauƙe, sannan yamun fatan alkhairi sosai, ya kuma mun nasiha, wanda kullum tsakanin mu sai ya mana.

Lokacin da aka gama rabon gadon shi kowa ya tashi da abunda Allah ya hukunta iya rabin shi ne, Alƙali jinya ta cinye kuɗin shi, sannan kadarorin shi su Tijjani sun sayar, abun da yayi saura gidan shi ne, sai wasu filayen shi da suke chan bayan gari, sai motocin shi guda biyu, sai wani gidan hayan shi ɗaya da yake dutsin tanshi, haka aka raba gado kowa ya karɓi rabon shi, lokacin da mijin yayah safiya ya ƙirani, tare mukaje da yayah Rabi'u, bayanin komai ya mun, ya kuma gaya mun abunda yake nawa rabon, acikin gidan mu side ɗin Baba na shine ya tashi a rabo na, sai kuɗin da aka sayar da wannan gidan da motocin Baba da filayen shi aka raba mana, kuɗin na barsu hannun mijin yayah safiya nace ina son a nemi inda babu ruwa a yi, ko da a masallaci ne ko kuma ƙauyen da suke buƙatan ruwa, ina so yazama sadakatul jariwa wa Baba nah, shi kuma gidan na barwa yayah umatiti, saboda nasan basu da ƙarfi ita da mijinta, yanzu haka ma baya komai, side ɗin Baba kuma parlor ne babba da bedroom da toilet, sannan kuma parlon ma akwai wani toilet a ciki da kuma ƙaton store, sai sama kuma ɗakuna biyu ne da ƙaton kitchen da store shima a wurin, kuma akwai fili a wurin, duk nace na bar mata, ɗago kai yayah safiya tayi tace, "mukhtari fushi kake da Baba ne wanda har baka son gadon shi"?

Jujjuya kaina nayi alaman a'a, "fushi kuma yayah? Na isa nayi fushi da mahaifina nayi kuma tunanin gamawa da duniya lafiya? Waneni yayah, nidai kawai a zuciyata naji ina so na sadaukar mishi da dukiyan, gidan kuma ummatiti ta fini buƙata, ina tausayinta da yadda rayuwa ta juya mata, gashi bata aiki sai ɗan sana'an da take taɓawa, kuma gidan haya suke har yanzu, wannan wurin kuma zasu iya fitar da ƙofar su daban basai sun shiga ta gidan ba, nima kuma Allah zai buɗa mun wani lokacin", ina gama faɗin haka ta fashe da kuka tace, "tabbas Alƙali yayi gaskiya, gashi ba'aje ko ina ba komai ya fara nuna kanshi, Mukhtar Allah ya saka maka da alkahiri, tabbas ka taimaki umatiti, domin duk gidan mu ita da Tijjani suka fi kowa shan wahala, shi yaƙi tsayawa yayi karatu ko yayi wani sana'a, duk kuɗin Baba ya tsole mishi ido, gashi kuma yadda rayuwa ta mai da shi".

Haka muka gama rubuta duk yar jejeniyan da zamuyi, aka tsayar da magana kuma za'a samu lawyer da alƙalin da ya mana rabon gadon.

********* lokacin da saƙo ya isarwa umatiti, kawai sai gata a gidan mu ita da mijinta da yʻar'uwar ta, sun yi kuka sunyi godiya wa goggo, don son samu bana nan, naje wurin A.G baida lafiya, tou na tafi duba jikin shi, a wurin suka ƙira mahaifiyar su, wanda lokacin suna takaba, duk da sun fita arba'in, amma ba kowa bane yake sakewa ya fito, kuka maman su tai tayi tana neman gafarar goggo, daga nan kuma tayi ta godiya tana saka mun albarka.

Daga gefe na koma umatiti ce ta ƙirani tana kuka tana mun godiya, mijinta ma karɓa yayi yai godiya, sannan mamanta ma ta karɓi number wayana tayi ta neman gafara na tana kuma bani haƙuri, kafin kice me magana ya zagaye gidan Alƙali, ƙannen mahaifina duk sai da sukaje sukayi wa goggo godiya, sannan suka karɓi number na sukayi ta mun godiya, har hajiya sai da ta kirani tayi ta saka mun albarka, nidai har nafara jin kunyar ɗaukan baƙon number, a haka dai naga wata baƙuwar number ta shigo mun, ina ɗauka kuwa ashe Tijjani ne, kin san meya ce mun"?

Girgiza kawai nayi alaman a'a ina share hawayena, murmushi yayi yacigaba

Yana ɗauka kawai naji yace "mukhtar kai kuma yayah akayi ka kyautar da wurinka wa mace? Ina laifin cikin mu ko ni ko shehu ae sai ka bayar wa ɗaya daga ciki, yanzu fah kaman wa mijinta ma kabayar domin gaba yʻayʻanta ne zasu gaje wurin kaga ya koma na mijinta, kawai kace mata ka fasa, idan yaso sai ka bani ko kabawa shehu".

"a'a yayah baza ayi haka ba, kaga fah ita umatiti yʻar'uwar muce, kuma itama tana cikin rashin wurin zama, kawai ayi haƙuri da hakan idan muna tare kowa ma zai mallaki nashi, fatan dai Allah ya jiƙan Babah da rahma", ina jin da ƙyar ya amsa Ameen ɗin, don ba haka yaso ba, kuma babu yadda ya iya dani, tunda gida dai nawa ne, koda goggo taji yadda mukayi da yʻan'uwa na daɗi taji, don ko ita abunda tace kenan, sun raba tsakanina da mahaifina akan gado ne, tou suje gado baya gaban mu, fatan mu kowa Allah ya bashi nashi.

****

Haka rayuwa tayi taja damu har suka fita Takaba, bayan nan kaɗan umatiti suka fitar da ƙofan da zai shigar da su gidan, kuma wurin yayi kyau, suka tare a ciki, iyaye mata kowa side ɗinta ya fito a gadonta, sannan duka cikin gidan da wani babban fili inda ɗakunan masu aiki da kitchen na waje yake, da wurin packing mota duk gadon su tijjani ne, suma anware wa kowa nashi, babu wuya wurin ubangiji komai namu yayi ta tafiya yadda Allah ya so har muka zo kowa ya samu abunyi, shi A.G barrister ne, yana aikin shi anan Abuja office ɗinsu ɗaya da Ahmad, sannan akwai wani chamber da suke zuwa chan tare, ni dai Contractor ne, kuma ina ɗan taɓa ƙananun business na fita da abu waje, kaman china, sai kuma na shigo da nasu, Abuja kuma mun sayi gida a wuri ɗaya nida A.G, domin plan ɗinmu kenan, yanzu haka kowa jiran abokiyar zama yakeyi, duk da dai shi A.G ya samu, nine dai nake laluɓe", ya ƙarasa maganan murmushi ɗauke da fuskan shi, sannan idon shi kuma zube a kaina, ganin haka sai na maida kallona ƙasa, "kinji taƙaitaccen labarin *MUKHTAR GARBA* Da ɗan'uwan shi *ALIYU GARBA INUWA* Kinji irin abotan da yake tsakanin mu, da amintan da yake tsakanin mu ko, kinji irin rayuwar dana sha a rayuwata mai daɗi da marar daɗi, kinji irin hidima da kyautatawan da A.G da iyayen shi har da kakanun shi sukayi a rayuwata dana yʻan'uwa na har dana yayye na,? Dalilin baki tarihina da labarin rayuwar mu abu ɗaya ne, a tunaninki akwai wani abu wanda bai kaucewa addini na da shari'a ba da A.G zai so naƙi mishi? A tunani na da ana kyautan rayuwa A.G ya chanchanci na mishi, A.G sun inganta rayuwa ta batare da sun goranta mun ko a wasa ba, A.G ya mayar da iyayen shi nawa, yʻan'uwan shi nawa, mahaifiyar shi ta haɗa yʻar ta aure da yayah na ba tare da shi ya nema ba saboda ta ƙullah dangantaka mai ƙarfi a tsakanin mu, akwai abunda bazan iya yiwa A.G ba don ya samu farin ciki a rayuwan nan ba"?

Girgiza kai kawai nakeyi ina kallon shi cike da tausayawa, a haka na sake tsinkayo muryan shi ya cigaba da cewa, "shawaran da nake so muyi da ke, kina ga yakamata na nemi auren yʻar'uwar shi *HEEDAYAH*"?

Wani irin mummunan faɗuwan gaba naji yazo mun, har wani rawa naji zuciyata ta nayi, buɗe bakina nayi kaman zanyi magana, amma sai naji yaƙi buɗewa, tsoro da firgici naji sun sauƙa mun a lokaci ɗaya, "dama M.G ba sona yakeyi ba? dama duk shirme zuciyata take ƙulla mun? Kasa ɗago kaina nayi na dube shi, shiru wurin ya ɗauka na wani lokaci, chan ya buɗe baki zaiyi magana, kawai naji kaman an zaburar dani, naji bakina yana furta "Har zuciyar ka kaji kana sonta ko kuma kawai don ka faranta mishi ne"?

Ido ya zuba mun kaman yana nazari, chan kuma sai naji ya sauƙe ajiyar zuciya a hankali ya fara magana, "Ayshaa tun ranan da na fara ganinki naji nasamu matar da nake so, matar da rayuwarta, tsarinta, tarbiyanta, komai nata ma ya mun, Allah - Allah nakeyi mu koma gida nayi shawara da A.G, amma kin san meya faru"?

Ɗago idanuna nayi na zuba mishi su, murmushi yayi mai alaman ciwo a zuciya yace, "muna shiga parlon mu A.G ya kallo ni fuskan shi cike da fara'an da idan bani ba da dama basu san yana da ita ba yace, "aboki ina ga nakusa aure", zaro ido nayi cike da firgici nace, "ka samu wacce ta maka kenan",?

Duk jikina yana ɗan rawa ta ciki, murmushi yayi ya wuce ya buɗe fridge ya ɗauko bottle ɗin ruwa ya kafa bakin shi yasha mai yawa, sannan ya juyo har inda nake ya saka hannu ya bugi ƙirjina yace, "matsalan tayi yarinya, kuma bansan yaya zanyi na tunkareta ba, ban san me zance mata ba", ya ƙarasa faɗi yana wuce kan kujerun parlon ya zauna fuskan shi da murmushi, " komai nata yayi mun, ina yawan mafarkinta, ina yawan ganinta a irin yanayin dana ganta yau, sister barrister ta mun, aboki ta mun, amma bansan yayah zanyi ba, sai ta ƙara girma"

Kinji abun da yace mun.

Da sauri na kalle shi raina duk a dagule nace, "kasan ko habiba yake nufi, kuma gashi tayi aure, sai dai idan yana son cousin ɗin mu, hadiza ko zainab?" na faɗa kaman babu nutsuwa a tare da ni, murmushi yayi ya ƙura mun ido, "kece yake nufi Ayshaa, duk yadda A.G yake gwada miki zakice baki fahimta ba? A.G fah har ciwo yayi saboda zaiyi nesa da ke, da tare zamu tafi karatun amma yayi cancel nawa, yana tsoron kada muyi nesa da ke wani yayi wuff da ke, idan ya dawo ina tunanin zan je nayi nawa, ko kuma ma tachan-tachan kawai na haƙura" ya faɗa yana murmushi, "nidai ban fahimci nashi ba, naka kawai na fahimta", na faɗa ba tare da na so hakan ya fita daga bakina ba, a razane dukkan mu muka ɗago kai muka kalli juna, ni nayi saurin kai hannu na bakina na rufe, shi kuma ya zaro ido yace, "Ayshaa son da nake miki yana bayyana kan shi ne? Bayan ke akwai wanda suka fahimci hakan?" ya faɗa gaba ɗaya a firgice.

Hawaye naji yazo mun nasaka hannu na da sauri na shareshi, "kasan kana so na tou meye hujjan ka naƙi bayyana mun? Meye hujjan ka na takurawa kanka da son auren heedayah? Meye hujjanka M.G?" na faɗa ina jin wani firgici a zuciyata.

"Duk abubuwan da nagaya miki A.G dafamilyn shi sun mana bai kai na bar abunda nake so don farin cikin A.G ba?" harara na aika mishi nace, "har a zuciyarka ban kai kayi fito na fito da kowa ba kenan?"

Murmushi yayi yana duba na yace, "ban taɓa ganin wata a rayuwa naji ina sonta ba sai akan ki, kuma ɗari bisa ɗari kin mun a matsayin matar aure na, haka A.G ko a wasa ban taɓa jin yayi maganar zaiyi aure ba sai ranan da ya ganki, kuma nayi imani da Allah son da nake miki bai kai wanda A.G yake miki ba, zan iya haƙura da komai a rayuwa idan A.G yana so, ae ba karya ba malam bahaushe yace, *ANA BARIN HALAL..... (DON KUNYA)* Ayshaa ae da kunya A.G ya nuna mun ga abunda yake so ni kuma nace nima shi nake so, A.G baya son magana amma akanki yana jure yayi, duk dare idan zamu kwanta zai takurani na bashi labarinki, wanda har na fara ƙure labarin, farin ciki yake shiga idan yaji sunan ki ko wani abu da ya shafeki, nikan ki taimaka ki bani haɗin kai A.G ya samu farin ciki".

Ajiyan zuciya na sauƙe mai ɗan ƙarfi na miƙe tsaye, shima miƙewan yayi yana "yayah naga kaman tafiya zakiyi"? "ehh hakan yafi, don naga baka son farin cikina dana ka, kawai A.G shine damuwanka, baka tunanin kai ma ka auri abun da kake so"?

Matsowa yayi kusa dani sannan yace, "zan iya son sister A.G, saboda son da nake mishi?" "ni kuma saboda me zan iya son A.G"?

Ɗago manyan idanun shi yayi ya zuba mun so, "saboda ni da farin cikina zaki so A.G".

Ido muka ƙurawa juna har na tsawon lokaci, a raunane naji muryan M.G yace, "ki taimaka mun na ɓoye sonki da nakeyi ayshaa, ki taimaka mun na sakawa A.G da alkhairin shi gareni, bana so kowa ya taɓa sanin na soki, banso zuciyana ya fallasa kanshi a gareki ba, har na fara tsoron kada A.G ya fahimta, ko barrister, kinsan yayanki ma yasan irin son da A.G yake miki, hattah mummyn shi ta sani, don muna hiran da ita sosai, ballantana lokacin da yafara ciwo akan tunanin barinki, don Allah kimun wannan alfarman Ayshaa", yana faɗa ya ɗaga hannayen shi duka biyu yana roƙo na, jikina naji gaba ɗaya yayi sanyi, ido na zuba mishi a hankali nace, "ni dai bam maka alƙawarin zan so shi ba, kuma na maka alƙawarin babu wanda zai san ni ko kai wani yataɓa son wani, amma ni bazan so shi ba, ɗaya kenan, kaima kuma ban amince ka nemi yɑr'uwar shi ba, kajira lokacin da Allah zai haɗaka da wacce kake jin sonta sai ka aura, nima zan jira wanda zai mun na aura", ina faɗa na juya nayi ciki, zuciyata kaman zatayi bindiga ta fashe, zama nayi na zabga wani uban tagumi na faɗa duniyar tunani, ina haka har naji an fara ƙiran sallan magrib, da ƙarfi na furta, "nidai A.G bana sonka, tunda M.G yaji baya sona ya haƙura ? Tou nima na haƙura da kowa zan jira wani daban?" na faɗa idona yana cikowa da hawayw, jin tahowar Aunty J yasaka ni tashi na shige toilet nayi alwalah, har akayi Esha'i ina zaune akan sallayata, bayan na idar na miƙe na ninke abum sallan na chanja kayana, don wankan ma bana jin zanyi, dama tun shigowara na kashe wayata, sai a lokacin na kunnata, ummie na ce ta ƙiran, bayan mun gaisa ta tambayeni yau shiru, murmushi nayi bance komai ba, sai hafsy ta karɓi wayan, bayan mun gaisa take bani labarin, yau ma habiba a gida ta kwana, wai sun sake wani faɗan da Aliyu, wai ta raina mishi yɑn'uwa da iyaye, bata son zuwa ta gaishe

su, haka dai abubbuwa babu daɗi wallahi, jikina a sanyaye mukayi sallama, ko whtsapp ban hauba na kwanta nayi shiru ina tnanin rayuwa.

Duk yadda M.G yaso muyi wani magana naƙi bashi dama, domim haushin shi naji ya kamani, shirin komawa na bauchi kawai nakeyi, ranan da zan tafi tun wurin ƙarfe biyu M.G ya kawo mun wani jaka cike ɗa abayu kala-kala masu shegen kyau kusan kala biyar, sai takalma da jaka guda biyu, da wani agogo mai kyaun gaske, sai wasu turare kusan kala uku da body misk, text na mishi ni bazan zoba, kuma kada ya bari yayah ya gane, babu yadda ya iya ya bawa yayah Ahmad ya shigo da shi, sai da yakawo ne yake ce mun wai mummyn suce ta aiko mun, wai duk tsara bane, duk kyaun da suka mun sai naji raina ya ɓaci, domin nasan saboda A.G ta kawo, amma haka na shirya kayana wurin biyar na yammah jirgin mu ya sauƙa a garin bauchi, yayah umar ne da yayah ishaq suka ɗauko ni, murna ummie da hafsy sukayi na dawowa na, ranan kusan raba dare mukayi muna ta hira.

Duk yadda nayi sai da M.G ya shawo kaina muka cigaba da gaiswa ta waya, amma naƙi muyi hiran A.G da shi, haka shima babu wani hira na soyayyah da yake haɗa mu da shi, sai dai muyi labari kawai na ratuwa, ko na school ɗin mu, a haka Yayah Ahmad ya sayi ticket hafsy ta tafi Abuja.

Sorry nayi mistake a baya akan Fatima ta fara ATBU, taso farawa har yaya yasama mata admission Through yayan M.G Hassan da yake lecturing a ATBU, amma sai Yayanta yace ta dawo unimaid kawai, haka bata so ba ta tafi, muma mun cigaba da zuwa school nida Maryam.

A wannan karon kuma aka saka ranan auren fatima da kabir, domin yazo nigeria, sannan aka saka na maryam ma da Dr, duk dai tsakanin bazai wuce 2month ba.

Da ƙyar M.G ya shawo kaina muka fara gaisawa da shi ta waya, don sai da yace mun, "Aysha kada kiji haushi na don Allah, son da nake yiwa A.G zan iya mishi komai, kuma abunda na fahimta son da yake miki yafi ƙarfin wanda ni nake miki, don Allah kiyi haƙuri ki bashi dama".

Nidai ban ce mishi komai ba, shiru kawai nayi, shima jin baxan ce komai ba ya cigaba da maganan shi.

Rayuwa da lokaci abun tsoro ne, duba da yadda suke guduwa, a haka har bikin Fatima yazo, lokacin muke ta shirye - shiryen tafiya maiduguri, Aunty B takai 1week da wucewa,mu kuma sai week ɗin muke shirin tafiya, Mamah da ni da su maryam, zainab, hadiza, sai Aunty J, mota biyu muka tafi da shi, ranan da zamu tafi da asubah na buɗe data na, whatsapp na hau zan tura message wa jammy, sai naga baƙon number an mun magana, gaisuwa ne da tambayana yayah shirin tafiya maiduguri, sannan ake jaddada mun na kula da kaina, nidai ban damu da na bi takan message ɗin ba nayi abun da yake gabana na sauƙa,

Mun shiga maiduguri wuraren la'asaar, sauƙi aka kaimu chan gidan yayan su Fatima, mu dai bamu wani daɗe ba muka wuce wurin Fatima da ƙawayen ta,

Bamu dawo bauchi ba sai ranan sunday, gaskiya bikin su yayi kyau sosai, mun sha ƙamshi kam, kuma munyi tsaraban ƙamshi, muna dawowa da 1month aka fara shirin auren maryam, nidai gaba ɗaya na zama busy a lokacin, satin bikin maryam A.G yazo ƙasan, da safe ranan thursday muna shirin shiga gidan su maryam wurin lalle sai ga habiba ta shigo wujiga - wujiga da ita, duk fuskanta a kumbure, a compound ɗin gidan mu muka haɗu da ita, gaba nane naji ya faɗi, dole naja na tsaya ina kallon ta yadda take tafiya take wani irin kuka, duk jikina yayi sanyi da yanayin da ta ke ciki, hafsy ce ta jawo hannu na tace, "don Allah Adda mu tafi, yanzu tsayuwar nan sai mamie ta ƙala mana wani sharrin, ko tace gulma ne ya tsayar da mu, jiki a sanyaye na bi bayan hafsy muka wuce, tunda muka shige naji ni babu walwala, haka akai ta sha'anin lalle har yamma muka dawo gida, washe gari friday za'ayi liyafan da mamanta ta haɗa mata, a haraban gidan su za'ayi, saboda suma filin gidan su yana da girma duk da bai kai namu ba, a ranan kuma da safe haɗiza ta shigo bauchi, wurin azahar kuma zainab ta shigo unguwar mu, tunda suka zainab ta iso muke ta shirin shiga gidan su maryam, anan hafsy suka shigo ita da ummitah, kallon su muka tsaya yi ganin irin ɗan banzan dariyan da sukeyi, don har ƙasa hafsy ke sunkuyawa, ganin haka hadiza ta tsaya da jan zip da take niyyan yi mun, baki buɗe tace, "da alama dai kun hangi wawan zama ne ko?" dariya suka sake ɓallewa da yi, " Adda wallahi abun dariya da tausayi ne ya faru a gidan nan, ashe jiya da muka ga shigowan Adda habiba, ashe Aliyu ya ƙara lafta mata na jaki ne, natan tausayi abun ya bani, don ance tana da ciki ƙarami, kunga ae bai kyauta ba, duk da dai ya kai 4month, ita kuma marar kunyar ƙanwar nata yau sai ta bishi har gida, ita da ƙanwar wanda zata aura, yanzu haka dai maganan da nake miki an kaita wurin mai ɗauri, don ko ya ɓalla hannun marar kunya, wai ta zare key ɗin motan shi, tana mishi magana yaƙi sauraran su ya fice wurin motan shi zai bar

gidan, ita kuma sakaryar sai ta nuna mishi ita jinin mamie ce, ta saka hannu ta chafko key ɗin motan wai sai ya tsaya ya mata bayanin me yake gadara da shi da zai daki yʼar'uwarta don zaiyi aure? Bai jira komai ba yayah nah Ali gadanga kam, ya murɗe hannu sai da ya targaɗa ya karɓi key, kuma ya ingizita ta zube a wurin ya fice, bayan ya umurci mai gadi yayi waje da su, yanzu mun shiga parlon hajiya ummah muka samu Abba yana mata bayani, shi bazai ɗauki matakin komai akan abunda yayiwa raliya ba, don ita ta jawo ita taje har gidan shi, kuma tayi mishi rashin kunya, amma akan adda habiba kam zai ɗauki mataki, don auren kawai yace zai raba, kuma itama hajiya ummah ta goyi bayan hakan, har take cewa ae rabawan shi yafi dai-dai, don babu laifim Aliyu ba son habiba yake yiba dole aka mishi da asiri, wallahi ran Abba a ɓace ya fita, ita dai raliya yau ta gamu da gamonta", ta ƙarisa suna ƙyalƙyala dariya, suma su hadiza da zainab dariyan suke har suka ban mamaki, ina jin jadiza tana cewa, ae kuwa Allah ne ya kama raliya da shegen ƙaton hancin ta irin na mamin ta, lokacin da na shiga gaida mamin na samu zasu fita ita da figaggiyar ƙawar nata, har tana wani mun banzan kallo ita marar kunya, nidai ban kula ta nata ba na shige parlon su, ina hango habiban tayi sauri ta shige ɗakin mamie, nidai ban bi ta kansu ba na gayar da mamin tana amsa mun rai duk a ɓace, ashe zata haɗu da gamunta ne marar kunya", zainab ce ta ɗan ya mutsa fuska tace, "Abba ya mun dai-dai gara ya raba wannan gantalallen auren kowa ma ya huta, ita kuma habiba idan tayi hankali da rayuwar cin amana tou tayi karatun ta nutsu, idan kuma batayi ba sai ta zo ta gama iddah idan sakarcinki ya kai ki kin sake samu mijin aure ki tallata mata ta sake amshewa, don naga ke ba kan gado bane da ke, ita kuma raliya kaɗan ta gani, ajuri zuwa rafi", baki na buɗe ina kallon zainab da magana ma baƙin halinta baya barinta tayi, "zainab nice mai laifi kike gani"? Na tambayeta, dariya ta ɗanyi kaɗan tace, "wallahi Ayshaa ke nake jin haushi ba habiba, kawai dai ban nuna miki bane saboda naga baki son gaskiya, tun farko ma mai ya kai ki bayyana mata manemin ki? Kinsan halin mahaifiyarta da mugun fatan da take muku, amma idan anyi magana sai kuce mutum ya cika mugun hali, yanzu rayuwa ba komai ake bayyana shi ba ko ciki ɗaya kuka fito da mutum, amma ke har hira kike barin su sunayi,"? Ta ya mutsa baki alaman haushi na takeji, kallon ta nayi baki a buɗe, "yanzu dai komai ya wuce ku fito mu wuce wurin maryam sai ƙiran wayata ta ke tayi.

Muna zaune wurin liyafa naji wayata tana vibration, ɗaukowa nayi na buɗe sai naga M.G ne, katse ƙiraɓ nayi na tura mishi message muna wurin liyafah, babu daɗewa yayi replying ɗina da A.G ya shigo, insha Allahu bayan sallan ishaa zasu shigo, duk sai naji na ɗan burkice, da ƙyar na mishi reply da "is ok".

Ana idar da sallan isha kuwa babu daɗewa sai ga wayan M.G wai sun iso, da ƙyar na bashi amsa da muna gidan su maryam, dariya yayi kaɗan jin yadda na ɗan burkice, "mu ƙaraso gidan ne ko kece zaki ƙaraso gida" ya tambaye ni, "ehh ku shiga wurin hajiya ummah yanzu zan taho", na bashi amsa, "ok bari mu shiga mugaida ummie tukun", yana faɗa ya kashe wayan, nidai duk sai naji nutsuwata tayi ƙaranci, ina ɗaga ido muka haɗa ido da zainab, alama ta mun da idon ta akan na fita basai nagayawa wani ba, haka ko akayi ban bari an hankalta ba na tashi na ficce.

Side ɗin ummah na shige, gaishe ta nayi sannan na wuce ɗaki, ina kallinta tana ta bina da harara, ni ko kula ta banyi ba, don nasan draman da suka sha ɗazu ne da hafsy da ummitah take jin haushi na, wai yara ƙannen bayana sun fini wayo kowa ta riƙe gwanin ta, su kuma suka gwasale ta, kacha- kacha sukayi har tace duk sai ta hana jikokin ta auren su, bari Allah ya dawo da su lafiya, da yake duk sun tafi Training na soja a NDA kaduna, da taga sun haɗe mata kai sai ta dawo kaina da yabo, ni kuma na ƙi kulata na fita, shine ban shigo ba sai yanzu, ban gama abunda nakeyi ba kuwa naji muryan sallaman M.G, ina ji suna gaisawa da hajiya Ummah, ita kuma kaman zata cinye su don murnah, sai maimaitawa take da "Allah sarki jama'an Ahmadu na, wato duk da Allah baisa Ahmadu yazo ba kunyi kara kunzo gaishe mu ko? Barka wallahi naji daɗin zuwan ku, Allah dai ya muku Albarka," sannan ta juyo tana ƙwala mun ƙira wai na fito na kawo musu ruws, amsawa nayi na fito, gaishe su nayi a jam'i, sannan hajiya ummah tace, "kuran baya sai ki buɗe fridge ki ɗauko ruwa da ɗan abun zaƙi wanda ɗana Usmanu yake sayowa donni da baƙina ki kawo, don dai badon kowa yake kashe kuɗin sa ba sai donni", ina jin tafara musu bayanin faɗan mu na ɗazu suna ta dariya, na ƙarasa kitchen na haɗo abunda duk ta lissafa, bayan nakai musu ne na wuce ɗaki na basu wuri suyita shan labarin nata, bayan mintuna goma naji ta sake ƙwala mun ƙira haka nafito na dawo parlon na zauna, ina jin tana ta mitan tafiya na, har tana cewa M.G ae ban waye ba a rashin wayewa na yar'uwata ta ƙwace mun mijin aure, yanzu dai kana ganin ta kaman mai hankali ko? Tou fosss take babu kan gado, idan ba rashin wayo ba ni kuma wani hira zan muku y kuji daɗin shi zamanin mu ba ɗaya ba? Ya wuce gaisuwa da ɗan wasan jika da kaka ae sai su, kodan farin fuskarta ae sai ku kai goma na dare baku ankara ba, nikan ae tun ɗazu nake ga mao shirun nan kaman ya daka tsalle ya fice don gajiya da hirana", dariya M.G yayi yana kallona har na zauna a gefe ɗaya, bayan ta wuce ɗakinta M.G ya juyo yana kallona fuskan shi cike da fara'a yace, "wato ke ƙwacen samari ake miki ko? Koda yake hakan na ya mana dai-dai don ke ba rabon su bace, rabonki gashi nan tafe akan lokacin da ya dace", yana faɗa yana kallon A.G da dariya a fuskan shi, ɗago kaina nayi kawai sai idon mu ya haɗu da A.G daya ƙura mun ido, haushin shi naji ya kamani, gashi yayi wani irin fari yayi kyau, sai dai kuma kaman ya ɗan faɗa kaɗan, murguɗa mishi baki nayi na ɗan harare shi, kaɗan kai yayi alaman dai nida shi.

Wato M.G da A.G dukkan su kyawawa ne kuma farare, banbancin M.G yafi fari kuma yafi kyau, sannan idon M.G a bayyane suke, shi kuma A.G idon shi a lumshe suke, sai wani dalile ne yake saka shi buɗe su, idan ya buɗe kuma zakiga girman su da

kyaunsu, don shi Allah yayi mishi kyakkyawan ƙwayan ido, sai kuma tsayin su kusan ɗaya ne, M.G shi yana da ɗan jiki fiye da A.G, shiyasa an fi ganin tsayin A.G, sannan A.G gashin kanshi mai laushi ne irin na fulani, hancin M.G yana da tsayi sosai, while A.G nashi dai-dai suke, amma suna da kyau sosai na tsarin zaman su akan fuskan shi, duk a wannan haɗa idon da mukayi da shi na ƙare mishi kallo, wanda ban taɓa tsayawa na ƙare mishi kallo ba, amma duk da haka banji yayi mun ba, idona na mayar kan M.G da naji yace bari ya ɗauko abu a mota, bayan ya fita parlon ya ɗauki shiru na wani lokaci, chan kaman an mishi dole na tsinkayo muryan shi yana cewa, "ke baki iya gaisuwa ba ko? bakijin magana ko?",

Hararan shi nayi ƙasa-ƙasa nace, "kunnen ka dai bayaji, ae na gaisheku", na faɗa ina ƙara tura bakina gaba, ido ya ƙura mun wanda har naji kaifin idon na shi a jikina, hakan ya saka na sake ɗago idona na kalle shi, shiɗin ma kallo na yake babu ƙiftawa, da sauri na sauƙe idona ƙasa, "kedai ɗago kanki ki kalli kyakkyawar fuskana ki ɗan samu peace of mine", naji muryan shi ƙasa -ƙasa yana faɗa, murguɗa baki nayi nace "ni har akwai wani kyaun fuskan ɗa namiji da zan gani har ya burgeni? Ni ban ma ga kyaun ba".

Wani sautin dariya naji kaɗan ya fito daga gareshi, wanda ya ban mamaki har na ɗago na dube shi, don ko murmushi ban taɓa tsammanin yana yi ba, "zakiyi bayani wataran, duk ran da Allah ya baki ɗa ko yɑa, mai kyaun fuskan nan zakiyi bayani idan kina shayar da shi", yana faɗa ya miƙe tsaye, dukka hannayen shi a zube cikin alhajihun wandon shi yace, "gobe what time kike free"? Kaman bazan amsa mishi ba kuma dai sai nima na miƙe na ce, "gobe fah shine ranan bikin gaba ɗaya, ni bana free".

" saboda baki da wayo yadda kaka tace ko? Inaga a gidan amaryan zaki kwana, tunda ance gobe za'a ɗaura aure, wuni, kai amaryah, akwai wani abu bayan wannan"?

Harara na sake jifan shi da shi, "a gidan amaryan zamu kwana ae", na bashi amsa kai tsaye, juyowa yayi kaɗan ya kalle ni, bakin shi a ɗan mele ya wani ya mutsa fuska yace, "kada ma ki fara, don ki sani naki ranan auren bana tunanin ma wata ƙawa zata miki rakiya, so gara ki daina wahalar da kanki a na wasu, angon ki da yammah zai zo ya ɗauki kayan shi,babu maganan rakiya ballantana maganan kwana",

 "chabɗi jam ae dai ba lalle kadan mijina ba ballantana ka bashi shawaran hakan", na faɗa ina zaro idona, ɗan murmushi kawai yayi yace, "zoki rakani yarina, babu amsan da zan baki zakiyi bayani lokacin,"

Ba don naso ba na raka shi, a mota muka samu yayah M.G yana kwance yana waya, tasowa yayi hannun shi riƙe da wayan yana kallon mu cike da murmushi a fuskar shi ya miƙo mun wayan yana cewa, "ku gaisa da GIWATA".

Zuciyata tace nai ta yanke Rasssss, har rawa jikina ya fara, da ƙyar na saka hannu na kari wayan, ɗan ƙaramin muryantq marar gurman amo ne ya daki kunne nah, "Aunty Beauty barka da dare, ae basu ce mun zasu zo wurinki ba da na bada saƙon gaisuwa na, don nasan wannan lion ɗin naki ban isa nace zan biyo suba, don sai ya ɓal mun yan yatsuna", ta faɗa tana dariya, nima ɗan murmushi kaɗan nayi marar sauti nace mata, "barka da dare", da dariyan ta tace, "sorry Aunty nine yakamata na gaisheki sai na tsaya suruti, Aunty beauty yayah kike? Hope dai mun samu karɓuwa, don Giwa na yace yau zai je rakiya, tou Allah ya sanya alkhairi, Allah yasa ke rabon yayah nane, Ameen ya rabbi", zuciya nane naji ya hautsine, wato dai daga dukkan alamu M.G ya fara neman Heedayah kenan? miƙa mishi wayan nayi ba tare da na bata amsa ba, karɓa yayi batare da ya nuna alamun damuwa ba yace, "Giwata bari nadawo zamuyi magana", yana faɗi ya katse wayan, hararan shi A.G yayi yaja tsaki yace, "ka cika shiririta wallahi, yarinya ƙarama kake wani cewa Giwata? Wallahi zata rainaka", ya faɗa yana buɗe wurin zaman mai zaman banza ya zauna, shidai M.G dariya yakeyi ya ɗan rusuna kaɗan yace, "da girman kujeran babban yayahmai bani aure da aurar da ni, ni na'isa nace wani abu? da ba don kada ka hanani Giwata ba ae danace, Allah kaɗai yasan me kace yanzu a ciki kafin ka fito, hala ma suƙawa kayi kayi sallama", yana faɗa ya buɗe gaban motan ya shige yana dariya, hararan shi A.G yayi baice komai ba sai dawo da idon shi kaina yayi, "goodnyt sai munyi magana" hararan su dukkansu nayi na juya na koma ciki, a zuciyata nake cewa dama ban rako su ba, na fito ne don muyi sallama da M.G ashe rabon naji takaici ne kawai ya fito dani wajen, raina ranan a ɓace na kwanta, wanda dukkan su sun kasa gane kaima, haka suka haƙura da tambayana suka kwanta.

Washe gari aka ɗaura auren maryam lafiya, akayi wuni cike da farin ciki da nishaɗi, ana idar da sallan la'assar aka fara tafiya kai amaryah, saboda za'ayi buɗan kai a gidan su angon, kunsan yan bauchi da hawa da buɗan kai, ina tsammanin ganin ƙiran M.G tun safe amma shiru, haka ɗai na sake a ka cigaba da hidiman bikin, muna gama shiri sai ga Hafsy ta shigo, ƙirana tayi tace mun na fito gasu Yayah M.G da Yayah A.G a waje suna mun magana, raina naji ya ɓaci, amma ban neme wulaƙantasu ba na fita inda suke, lokacin da na iso jikin motan still M.G waya yakeyi, ɗaga mun hannu kawai yayi ya cigaba da wayan shi,A.G ne ya ƙura mun ido, hararan shi nayi na juyar da kaina gefe ban gaishe shi ba, shima shirun yayi kawai yana kallona, ganin haka yasaM.G ya juyo yace, " Aysha kiyiwa zainab da hadiza magana mu wuce gidan amaryan ko".

Idona na mayar kanshi nace, "akwai motocin da angwaye suka turo ae,su zamu bi", ina faɗa naga M.G ya mayar da kallon shi kan A.G yana dariya ƙasa -ƙasa.

"Bana son musu zaki yiwa Ahmad musu ne? Ko dan kinga M.G yana wasa da ke? Wuce kije ku fito, ban amince ki shiga motan kowa ba", ya faɗa fuskan shin nan babu alaman annuri, ba don naso ba na juya na shiga neman su Hadiza, don wannan masifaffen bazan iya da shi ba.

Bayan motan muka shiga mu uku, hadiza, zainab da kuma ni, tunda muka shiga na kama bakina nayi shiru, daga hadiza sai M.G suke hira a tsakanin su, daga ni har A.G babu wanda aka ji bakin shi har muka isa gidan amaryah, sun daɗe a waje kafin suka tafi, da niyyan after magrib zasu zo su ɗauke mu.

Buɗan kan yayi kyau sosai, amaryah tafito cikin Alƙyabbah fara mai rastin golden, tayi kyau sosai da ita, ango sai wani washe baki yake cike da farin ciki, ana idar da sallan ishaa su Yayah M.G suka zo, wayana naga call ya shigo da baƙon number, har sai da naga zai tsinke tukun na ɗauka, ko a bacci aka tashe ni bazan kasa gane muryam shi ba, "idan kun shiryah muna waje", iya abun da ya faɗa kenan ya katse wayan, murguɗa baki nayi na share shi, don lokacin angwaye sun shigo kenan, haka ƙawaye da angwaye sukai ta hira da tsokanan juna, ni da zainab dai bakin mu shiru, amma hajjah khadijah kam sai zuba ake tayi da sauran friends ɗin amaryah, mudai bamu fito ba sai wurin 8:30, kuma M.G basu sake ƙirana ba kuma basu tafi ba, angwaye ne suka fara ɗaukan ƙawaye, sai lokacin naji wani irin tausayi da kaɗaici ya zo mun, Allah sarki maryam yanzu munyi nesa da junan mu, duk sai naji babu daɗi, muna haɗa ido da ita naga idonta ya cika da wahaye, da dabara nace zanje kitchen na ɗauko ruwa, sai da na fita na ƙira su hadiza a waya, suma cikin dabara suka fito, ummitah da hafsy ma fitowa sukayi, kaman sun san mun ƙaro ko kuma da ma suna da shirin hakan sai naga kowan su a motan shi yazo, babu yadda na iya dole na shige gaban motan A.G, domin muna fitowa naga ya ƙira ummitah da hafsy ya buɗe musu bayan motan shi, sannan ya bar gaban a buɗe ya wani ƙura mun ido, M.G dai yana ta wani sake murmushi a fuskan shi ya buɗewa hadiza gaba, ya buɗewa zainab baya, suna shiga naga ya rufe, dole na wuce gaban motan A.G ɗin na zauna, ko kallon inda nake baiyi ba ya tayar da motan shi, ina jin su hafsy suka gaishe shi amma ni nakasa buɗe baki na gaishe shi, sai ma juya kaina danayi ina kallon waje ta glass ɗin motan, chan na tsinko muryan shi yana tambayan su hafsy, "hafsat me kuke son ci"? Da yake ba mutunci bane ya ishe ta sosai kawai sai naji tace, "tou nidai nida aminaiyata muna ƙauna da kaza, kazar bauchi club, ita kuma Adda suna mutunci da tsiren wurin, don tana son harkan tsire," tana faɗa ummitah na taya ta da, "ae har soya milk Adda tana korawa time to time", ka marasa mutuncin ko dariya basuyi ba sai wani ɗagawa juna kai suke irin alaman kowa ta faɗi dai-dai, murmushi mai ɗan sauti naji A.G yayi, wanda har sai dana juya na kalle shi, "ku kuma kuna ƙauna da wani abun shan"? Ɗan dariya hafsy tayi tace, "ae muna madaran son coca-cola, wataran har pepsi mukan kora, idan ka ganmu da yogouth tou mutanen mu suna na, dole suke haɗamu da shi, har mun saba sha yanzu".

Ni wallahi hafsy da ummitah tsoro suke bani, yarah gaba ɗaya babu kunya a idon su, don wani dariya suka kwashe da shi suna wani godiyan iskan ci lokacin da yace, "yanzu dai a haɗa muku coke,pepsi,yogouth"? Dariya suka kwashe da shi suna godiya muke Babban yayah, kace har gobe zamuyita sha, don idan Allah ya kaimu sai munyi order hajiya shawarmah, sai mu haɗa da yogouth ɗin, yanzu mu karya ƙashin kaza da coke da pepsi na ummitah", murmushi yayi ya miƙa hanyan bauchi club, nidai kaman na fashe da kuka saboda haushin su hafsy, sai wani leƙo kai gaban motan suke kaman wasu sukaye suna ƙara godiya, har muka shiga bauchi club fuskan shi da murmushi, wanda hakan yake ta bani mamaki, amma nasan tsantsan shaƙiyan cin su hafsy ne yake bashi dariya, muna parking naga motan M.G ma yayi parking a gefen mu.

Tare suka buɗe motan suka fito, suna fita na juya ina hararan su, da sauri hafsy tace, "wallahi Adda kika ce wani abu recording ɗinki zanyi, yana shigowa na kunna mishi", ta faɗa tana ɗaga wayanta sama tana nuna mun, ita kuma ummitah cike da shaƙiyanci tace, "ae best friend nikan ma har na ɗana, tana kwabsa mana zamu antaya mishi", juyar da kaina kawai nayi na rabu dasu, sai wani dariyan rashin mutunci suke tayi, zuwa chan kaina yana ƙasa naji muryan hafsy tace, "wooww gaskiya gayen nan ƙarshe ne, friend kiga wani taku da yakeyi kaman wani Basaraken zaki, gaskiya matar shi ta more da haɗaɗɗen miji ɗan wanka da aji," ummitah ta amsa mata, "da kuma dace da miji ɗan ƙamshi, saboda Allah hafsisin london bakiji ƙamshin motan shi kaman daɗin zai saka kiyi bacci ba? Nifa na tsorita da gayen nan, don har na fara manta sunan saurayina, meye ma sunan shi friend"? Hafsy na dariya tace, "shege ƙamshi, ƙamshi ya gagara ae, sunan samrayinki, isiyaku zakaran bauchi club", dariya suka ƙyalƙyale da shi wanda har saida suka saka na ɗan dara, don tsiyar su tana da yawa, kuma saida suka saka na ɗan ɗaga kaina ma dubi A.G da yake shirin ƙarasuwa, ashe ya chanja shigan shi ba irin ta ɗazu bane, yanzu wata faran yadi ya saka mai ɗan shara -shara, sai wani lumshe ido yakeyi shi kaɗai yana tahuwa, da sauri na sauƙe kaina ƙasa zuciyata na bugawa da sauri -sauri,gefen shi kuma M.G nashi ne.

Buɗe motan yayi ya shigo, juyawa yayi kaɗan baya yana duban su hafsy da suka wani nutsu kaman gaske, murmushi yayi yace musu, "yanzu insha Allahu zasu kawo, sai kuma shawarman account ɗin waye za'a tura so dat goben sai kuyi ordern,", da sauri ummitah tace "zubasu kawai a acct ɗin Adda, don duk ƙawancen mun nan da kake gani akan almanu sai mu munafurci junan mu, bawa Adda kawai don ita mai amana ce, zata mana order gobe, inda chanji ma bazata ha'ince mu ba zata raba mana", tana faɗa hafsy na gyaɗa mishi kai, "eh yayah A.G hankaɗa su wurin Adda, don mu akwai ɗan sauran nutsuwa a tare da mu, ƙarshe idan ma ɗayar mu kasa sai ta ha'inci yar'uwarta duk ta saka rechage card ko data, don ba kan gado bane wataran damu".

Abun mamaki wallahi dariya A.G ya ƙyalƙyale da shi, sakarun suma suka shiga taya shi, nidai kaman na buɗe window na falfala da mugun gudu don kunya, tsabar wayo ne fah yasaka suka gaya mishi haka, wato *AUNTY NICE* na daɗe banga tsageru irin suba, kuma hattah yayah ishaq da yayah umar basu barsu ba, yanzu zasu haɗe su zaga su, halin sune yazo ɗaya shiyasa suke abota, kuma ko ƙaryah ɗaya tayi bazaki taɓa jin ɗayan ta ƙaryata ɗayar ba, sai dai itama ta tayata, gasu da shegen wayon tsiya, don ɗaya tana faɗan abu ɗaya take gane ina aka dosa, shidai A.G gaba ɗaya nishaɗi yake da shi a lokacin, muna haka har ma'aikatan suka kawo saƙon, bayan motan duk aka zuba musu, sannan A.G ya tayar da motan yana cewa, "wannan leda ɗaya kajin kune sai aka san muku tsiren kaɗan, don kada kuyiwa su Adda wayo ku cinye nasu, ɗayan ledan kuma na ummin mune, nasu Adda kuma yana hannun jama'an ta, tare dana hajiya ummah, kuɗin ku kuma zan zuba a acct ɗin Addan mu, haka yayi"? Kƴyalƙyala dariya sukayi lokaci ɗaya, hafsy na wani gyaran muryah tace, " yayan mu insha Allahu na maka alƙawari yau zan raba dare na tayaka da addu'an Allah ya baka mata ta gari wanda bazata hana mu zuwa gidan kaba, wacce zata barka kana mana abun duniya, kaga yayah muhammad da yayah Ahmad ae tsantsar addu'an da nake musu ne idan sun haɗani da abun duniya Allah ya amsa, kaga ae matan su nagari ne? Tou amma duk basu kai wannan aminiyata ɗin ba, don yayah umar yana kyautata mun, shiyasa nafi dagewa da roƙa mishi ta gari, kuma cikin ikon Allah sai ya samu Ummitah, ae ummitah mutum ce har da ƙari, matsalarta sai an dage ta bar yayah umar ya tara na kanshi, saboda bakinta baya hutawa da ciye-ciye, tou kaima ka shiga sahun addu'a na," dariya ummita ta sake ƙyalƙyalewa da shi tana duban hafsy tace, "Allahummah Ameen ƙawata, ae duk zamu saka shi cikin addu'a, amma nikan sai daga gobe idan Allah ya kaimu, don gaskiya yau kam naci naman nan bacci zanyi don na gajji, amma gobe kam idan Allah ya kaimu, zan maka addu'a Allah ya baka nutsattsiyar mace irim Addan mu, don yanayin ku ɗaya wallahi, akwai nutsuwa akwai alheri ". Ta faɗa tan turo kanta gaban motan, ni dai narasa dalilim da ya saka na haɗa hanya da su, don ni har wani jiri -jiri nakeji tsabar haushin su, a haka muka ƙarasu cikin gidan mu, inda A.G yake ce musu, "nagode da niyyan ku, ae ko bakuyi ba nagode, kuma Allah ya amsa bakin ku ya bani Addan na ku", ya faɗa yana ɗan maida idon shi kaɗan gefe na, shashun kuma haɗa baki sukayi suna wani ihun murna, ummitah nacewa, "wallahu kun dace, nifa ɗazu har mafarkin ido biyu nafara dana ganku, nace lallai za'a haifo yara ƴan gaske anan, wayaga kyau na dukan kyau, nutsuwa Na dukan nutsuwa, Allah dai ya tabbatar da alkairi, Allah yasa ka dace da samun zuciyata", murmushi yayi yana wani mun kallo da ya saka duk jikina fara rawa, ƴan tsiyar kuma sai wani smilling suke suna ƙara turo kawunan su gaban motan, ni da ma M.G ne ya kwashe su da nafi samun sauƙi, yana tsayar da motan na kai hannu zan buɗe sai naji ta lock, juyowa nayi na kalle shi, "yayah xaki fita bayan baki amsa musu addu'an su ba?" "wallahi kam yayah, kuma ma banga ta baka acct ɗin nata ba hehehehh", hafsy ta faɗa tana wani dariyan iskanci, kallo na yayi yace bani acct ɗin kafin ki fita," sannan ya buɗewa su hafsy ƙofan yana ƙara musu godiya, sai wanidariyan daɗi suke yi suna mishi godiya, sannan ummitah ta ɗan leƙo ta glass tace mun, "Adda nikan zan ƙira mama nagaya mata anan zan

kwana, kuma a side ɗin ummie zamu kwana don kada mu takurako hajiya ummah ta takura mu, don tana ganin mu da ledan nan zata ɓoye nata ta saka ido a namu, gara muje wurin ummie, ita sai ma taci ta rage mana mu ƙara da safe, zamu ƙiraki zuwa anjima muji yayah labarin alert mai kukan tararar at", tana gama faɗin haka sukayi ciki da sauri suna dariya.

Tsaki nayi ban shiryah ba, hakan ya saka naji A.G ya wani ɗan tuntsire da dariya, a hankali yace, "kai yaran nan sun sakani nishaɗi, ballantana ma da suka haska mun ashe Adda tana son tsire mai ɗan ƙarago, ashe bazan sha wahalan wani sayan kaza ba" ya faɗa yana duban fuskana, turo baki nayi gaba, wanda sai lokacin bakina ya buɗe nace, "kai fa baka san kalan ƙaryan su ba fah? Maƙaryata ne na gasken-gaske, kuma wallahi wayo suka maka don ka saya musu nama da shawarma, haka sukeyi wa su yayah Ahmad, nidai babu ruwana", na faɗa ina maida fuskana kanshi da naji dai yau sai dariya yakeyi, "wayace miki ban fahimci wayon su ba, ae abun da yaringa sakani nishaɗi kenan har kika ga ina dariya, bakiji wayon da suka mun ba na maganan shawarman su na gobe"? Ya faɗa yana ƙara sautin dariyan shin, nima ɗan murmushi najyi kaɗan nace, "sun ɗauka ba'a gane sune ae, ni tsoro suke bani ma wallahi, harta masu son su basu ƙyale su ba", dariya ya ɗan sakeyi kaɗan yace, "nidai sun sakani nishaɗi, kin san mai wayo wani lokacin ɓuya yake a bayan wayon shi, bakiji sunce a tura miki kuɗin acct ɗinki ba, kinsan meye dalilin su"?

Dariyan naji ya ɗan zo mun, son nasan shima ya fahimce su.

Nima dariyan naji ya zo mun, sai na ɗan dakata da sauraren Ayshaa na ɗan dara, itama dakatawa tayi tana darawa, domin tuna lokacin da abun ya faru, gashi yanzu duk anzama iyaye.

Murmushi kawai yayi bai sake cewa komai ba, har na gajji da jiran naji me zai ce amma sai naga yayi shiru, duka hannayen shi yana kan stearing motan, idon shi na kallon gaban motan, "bari na bar ki kishigs gida, saboda bai dace na tsayar da ke a mota ba, insha Allah gobe zan shigo idan kina free, don jibi zamu wuce Abuja", juyowa yayi yana kallona, ko jira yake yaji mai zance? Ni kuma sai nayi shiru ban ce uffan ba, ƙoƙarin buɗe ƙofan nakeyi sai najiyo muryan shi yana cewa, "3weeks zanyi na koma, sai bayan six month zan gama insha Allahu, tsarabanki gobe zan shigo miki da shi insha Allahu,"

Buɗe motan nayi na fito waje, hannu na riƙe da handbag ɗina, fuska a ɗan ɗaure nace, "sai da safe mungode," banjira jin mai zaice ba nayi gaba zuwa side ɗin ummie nah don na mata saida safe, ina shiga na samu babu kowa a parlor, ɗakin ummie na wuce, ta fito daga toilet alaman alwala ta ɗauro, gaban mirron ta na ƙarasa inda naga ledan namanta akai, kallona tayi tace, "hafsy tace mun yayan ku A.G ne ya saya mana ko?" ɗaga kai na mata alaman hakane batare da nace uffan ba, "tou angode Allah ya musu albarka" a zuciyana na amsa sannan na mata saida safe, ko ta kan su hafsy ban bi ba, don nasan ina zuwa zasu ɓata mun lokaci.

A ɗaki na samu su zainab sun baza nama a plet kowa tana figan nata, gefe ɗaya kuma sun ajiye mun nawa a leda, hiran su suke tayi na sha'anin bikin da muka gama, nidai abunda yake damuna ya dameni, nayi mamakin M.G daya na sauƙe su ya wuce abunshi, don ina ganin ko cikin gate ɗin gidan bai shigo ba, daga waje ya ajiye su, ni bai isa ya mun shariya ba, don ko wallahi wurinta yazo, Allah ya bashi sa'a, haka na ci naman ba wai don ina jin daɗin shi ba, gaba ɗaya na rasa me yake damuna ne kawai, haka muna gamawa kowa tayi shirin kwanciya.

Washe gari duk shaƙiyancin su hafsy ban kula su ba, don ina ankare da su agaban ummie suke zabga rashin mutuncin su suna dariya, har suka saka hankalin ummi dawowa kanmu, alama kuma kaman ta fara zargin wani abu ne daga yana yin dariyan su, 50k ya tura musu na shawarma, kuma yadda ya bayar haka na saka musu 25k ma kowa, ganin hakan ne suka fara tiƙa dariya kaman wasu tumakai, nidai ban kula su ba na juya na bar ɗakin.

Hadiza ne da ta fito daga side ɗin su habiba take ce mana yau kam sun haɗu har sun gaisa, nan habiban take ɗan tsakura mata abunda yake faruwa, wai haka kawai Aliyu zai burkice mata yace shi bai taɓa son ta ba, kuma shi ni yake so amma don su cuce shi suka aura mishi ita, shi bai san ma yayah akayi ya rabo da ni ya koma mata ba, daga nan kuma idan ta tanka akan ae abunda yayi Ayshaa shi yayita, ae duk ɗaya ne yayi haƙuri itace ƙaddaran shi, ae kuwa nan zai kama dukan ta yana ƙiranta da mummunan ƙaddara dai, tana gayawa hadiza tana kuka, akan ita wallahi mamie ne ta matsa akan maganan, ita dai tasan yana burgeta amma ita ma batasan yayah akayi wannan al'amari ya faru ba, tayi -tayi ta kaucewa abun amma ta kasa, kuma mamie tace zata tsine mata idan ta bari abun ya fasu, hadiza tana gaya mana cike da tausayin habiba, "hmm kunsan babu abun da mushirikiyar uwarta bazata yi ba, yanzu haka ma ita ta maida hankalin habiba kai, gashi asirin ya karye aure baije ko ina ba, sai tsaraban ciki", zainab ta faɗa tana ya mutsa fuska.

Bayan sallan azahar zainab ta wuce unguwar su, hadiza kuma tace sai gobe da safe insha Allahu.

Ana sallan ishaa wuraren 8:00 sai ga ƙiran A.G, ina ɗauka naji yace , "ina waje", raina ne naji duk ya ɓaci, babu yadda na iya na fito parlor na gayawa hajiya ummah A.G yazo yana waje, bakinta kaman zai tsage tsabar fara'a tace naje na shigo da shi mana, haka na fita babu ko ɗan powder a fuskana, na daiyi wanka bayan magrib saboda bana sallah, dogon rigan material na saka, amma dai ina ƙamshi na gaske, gyalen material ɗin kawai na yafa na fita, yana tsaye a jikin motan hannun shi riƙe da wayan shi yana dannawa, ina isowa turaren shi mai suna *BVLGARI* yana tashi a jikin shi, designer ne mai ƙamshin gaske, yana sanye da blue jean, da red ɗin polo, yayi wani haske yayi kyau a idon masu ganin kyaun shi, sallama na mishi murya chan ƙasa -ƙasa, ban yadda mun haɗa ido ba lokacin da ya kallo ni, shiru yayi baice mun komai ba, naga muna ta ɓata lokaci a tsaye, sai na daure na ɗago kaina nace, "mu shiga parlon ummah" bai ce uffan ba sai ido da ya zuba mun, juyawa nayi na nufi hanyan parlon, ina jin shi ya rufe motan ya biyo baya na, a parlon muka samu hajiya ummah zaune ta ƙurawa T.V ido kaman gaske tana ganewa, don kuwa labarai ne ake yi a channel ɗin CNN, zama yayi yana gaisheta cike da sakewa a fuskan shi, itama da fara'arta take amsawa, sannan ta tambaye shi "ina M.G?" murmushi a fuskan shi yace, "M.G yaje neman aure, ya tafi hira", ya bata amsa yana ɗaukan remote ya rage vulome ɗin da madam ummah ta wani ƙure, dariya tayi na jin daɗi, "kaii kai kai abu yayi kyau, a gari yake neman auren kenan"? Ta tambaye shi, "ƙanwata autar mu yake nema, sunan ta Heedayah".

"kace yʼar gida za'ayi kenan? A ashe muktari yayi maka wayo, shi kam a gida ya samo, kaima ae yakamata ka nemo, sai a haɗa ku tare asha biki, don abun zai fi armashi", murmushi yayi ya ɗago kai ya dubeni, sanan yace, "ke baki iya kawo wa baƙo ruwa ba ko? Haka za'aje gidan ki"? Turo baki nayi na miƙe nayi hanyar kitchen ɗin, ina jin hajiya ummah nacewa, ae banida wayo ne ko kaɗan, wannan mijinta ae zai sha fama, sai dai Allah ya bata nagari kuma ɗan gida.

Maida kallon shi yayi kan hajiya ummah yace, "hajiya ae ni yakamata kibawa ita, kinga nima nasamo yʼar gida irin na M.G, sai ayi tuwona mai na ko", ya faɗa yana bina da kallo fitowa na daga kitchen, hararan shi nayi ina mamakin wayon mutumin nan, wato so yake ya ɗaureni kenan ko?.

Cike da murna hajiya ummah tace, "idan nice wallahi na baka, kuma nayi imani daga iyayenta har yayunta babu mai hanaka, kai dai gata nan sai ka nemi haɗin kanta, mudai fatan mu ɗa addu'an mu Allah ya haɗa kanku, Allah yasa ace gara da akayi, bari na baku wuri kuɗan zanta, Allah yayi albarka abu yayi kyau", haka ta miƙe tayi ɗaki tana bani sallahun idan mungama na kashe mata T.V kada ya zuƙe kuɗin Usmanun ta.

Murmushi yayi yadawo da kallon shi kaina bayan ta ƙarasa shigewa ɗakinta.

Nidai ban yadda na ɗago da kaina na kalle shi ba, amma a jikina naji shi yana kallona, chan kuma naji muryan shi, "naso M.G mutaho tare ae, amma yaƙi, wai shima zai gyara zaman shi ne a wurin yarinyar nan, gashi ni sai naga kinƙi sakewa da ni", ɗago kai nayi na kalle shi, a zuciyana nace kaji mun mutumin nan, wai M.G yaƙi rako shi, wato hiran ma M.G ne zai mishi, tou zaman auren fah? Ƙara ɗaure fuskana nayi, don so kawai nakeyi naji yace zai tafi, amma mutumin ki kam sai ya gyara zama, "ina su hadiza da zainab, ko suna ɗakine?" ɗago kai nayi na kalle shi a fakaice, sannan nace, "zainab ta tafi gida ɗazu, hadiza kuma sai gobe insha Allahu, tana ciki tana waya ne", na faɗa da ƙyar kaman an mun dole, shiru ya sakeyi daga nan baice komai ba, amma kuma idon shi yana kaina, nidai wasa kawai nake da gyale na, ina ji kaman nace mishi sai da safe, haba me za'ayi da mutum shiru, ni shiru shima shiru ae abun baiyi ba, gaskiya M.G bai kyauta mun ba, bayan nagama sakawa raina shi zaice yana sona, amma sai naji wani daban, kuma tsaban banida muhimmanci a fuskan shi nace kada ya nemi sister A.G shine yayi kunnen uwar shegu yaje ya nema, nima daga yau na cire shi a raina, bazan sake tunanin shi bama, nima zan dage da addu'a Allah ya fito mun da wanda nake so, don wannan kam sallaman shi zanyi, ɗago da kai nayi ina kallon shi jin yana mun sallama akan zai tafi gida, da jin daɗi na amsa mishi da "nagode sai da safe" na faɗa ina miƙewa, ganin shima ya miƙe tsaye zai fita, har jikin mota na rakashi, tsayawa yayi kaɗan yana kallona, "me zancewa mummy"? Ɗago kai nayi da hanzari don jin abunda ya ke faɗi, "ka gaisheta" na samu bakina da faɗi, murmushi yayi mai ɗan sauti sannan yace, "inji waye zance mata"? hararan shi nayi a fakaice ina mutsul -mutsul da baki, kafin nace wani abu sai naga an buɗe gate, zuciyata ne naji ya yanke lokaci ɗaya, domin motan Abba ne ya shigo, daga ni har A.G bin motan mukayi da kallo har sukayi parking, ganin haka A.G ya dubeni da murmushi a fuskanshi, "bari ni naje na gaida surukina yasan ni waye yanzu a wurin shi, ki jirani" ya faɗa yana karasawa inda Abba yake fitowa daga motan, kaman an dasani a wurin kuma nakasa tafiya, ina ganin Abba ya miƙa mishi hannu fuska cike da fara'a, amma A.G yaƙi miƙa nashi ya duƙa yana gaida Abba, kafaɗan shi Abba ya ɗan buga yana amsa gaisuwan shi, idon Abba kuma akaina da nake tsaye jikin motan A.G, ganin haka ya saka na ƙarasa inda suke tsayen, hannu Abba ya miƙo mun na ƙarasa jikinshi, "sisto yayah akayi? Ina sauran ƴan'uwankin?" na'amsa mishi da suna ciki, sannan yace ya muka bar A.G a waje bamu shiga ciki da shi ba, ina ganin A.G yana wani sauƙe smilling, sannan yace, "Abba ta shigar da ni parlon hajiya ae, yanzu na fito ne zan kuma gida, saboda Daddy ya shigo gari ina so mu gaisa da shi", cike da farin ciki sukayi sallama da Abba nah, nidai duk a hargitse nake jin kaina, Abba na wucewa na mishi sallama, shidai murmushi yakeyi ya wuce motan shi.

****

Washe gari da wuri hadiza ta kama hanyan Tafawa ɓalewa, sai naji duk gidan babu daɗi, ga ummitah ma ta tafi gidansu tun jiya, hafsy kuma tayi gidan Aunty Rakiya, haka na wuni tare da ummie nah, da la'asaar na shiga side ɗin Mamah don mu gaisa, abun mamaki ina fitowa sai muka haɗu da habiba da raliya zasu fita, daga gani kuma habiba babu lafiya ne, don duk fuskanta ya wani hau, wani zuciyan yace na tsaya mu gaisa, wani zuciyan kuma yace kedai wuce babu ruwanki, ina kallon ta muna haɗa ido tayi mun murmushi, nima sai na maida mata na wuce, duk sai naji ta bani tausayi, gaskiya Aliyu bai kyauta mata ba, da ƙaramin shekarunta ya maida ta bazawara.

Ana sallan ishaa na lallaɓa na koma ɗakin Hajiya ummah, don nasan A.G zai zo, kuma bana son ummi ta fahimci komai, haka ko akayi ana idaar da sallah kuwa sai ga wayan shi, tsaki na ɗan ja a hankali bayan na ɗauka yace mun yana waje, kallon hajiya ummah nayi nace, "Hajiya A.G zai shigo" murmushi ta fara tace, "kice dai yaro ya ƙyasa yʻar kyakkyawar jikata, dama raina ya kwanta da shi wallahi, don kullum addu'a nake ko shi ko mai fara'an nan Allah ya baki ɗaya, ashe wannan mai yana yin basaraken ne rabo, aiko bari na wuce ɗaki kafin ya shigo, kada yace tsohuwar banza kullum tana gaban television", tana faɗa kuwa ta wuce ɗakinta, nidai kaɗa kaina kawai nayi nafita.

Gaisuwa mukayi sai kowa yayi shiru, ganin bazai ce komai ba sai kallona,kawai sai na tashi na shige kitchen na kawo mishi ruwa, ina zama ya tambaye ni ina hajiya su gaisa, kallon ƙofan ɗakinta nayi nace, "yau bata jin son fitowane nake ga, ko kuma ma ta kwanta", ina faɗa ya dube ni yace, "ko kuma baki so mu gaisa ba, don jiya na lura bakiji daɗin gaisawan da nayi da Abba ba", baki na buɗe ina kallon shi cike da mamaki, sai kuma na turo baki gaba saboda irin kallon da naga yake mun, "mummy tace idan nazo na haɗaku ku gaisa, zan iya ƙiranta yanzu"? naji muryan shi.

Da sauri na buɗe baki ina kallon shi, "nikan bazan iya ba kunya nakeji", kallo na yayi sai kuma yace, "kedai baki son ɗanta shiyasa baki son gaisheta, don ma kada ta saka ranta akanki, bari na ƙira sai nagaya mata ba zaku gaisa ba",

nidai ido na zuba mishi har ya ƙira suka fara magana da shi, sannan ya tashi ya miƙo mun wayan naji yana cewa, "tou first love ga princess ɗin", baki a buɗe na ɗago kaina, amma sai naga ya miƙo mun phone ɗin, da sauri na karɓa nasaka a kunne, muryanta naji cike da farin cike tace, "my doug yayah kike? Yh mutanen gida"? Ni dai sake miƙa mata gaisuwa nayi cike da rusunawa kaman ina gaban ta, wani sakewa dani tayi tana tambayana karatu, sannan kawai naji tana tambayana, A.G bai ɓata miki ko"? Nidai ɗan murmushi kawai nayi ban iya nace komai ba sai ɗaga ido nayi ina kallon shi, giran shi duka biyu ya ɗaga mun, hakan yasaka na mai da kallona ƙasa, chan kuma naji Heedayah ta amshi wayan cike da karaɗi take gaishe ni, har tana ce mun ae M.G yace zai kawota ta gaishe ni, nidai murmushi

kawai nakeyi har muka gama gaiswa dasu ya karɓi wayan shi, idon shi na kaina yace mun, "ina son mummy sosai, hope zaki tayani sonta da bata kulawa na musamman"? Kallon shi kawai nayi na sunkuyar da kaina, a zuciyata nace, kama jira kaima a baka kulawan tukun kafin ka nema mawani, haka dai hiran ya ƙare, sallama ya mun zai tafi, yauma har mota na rakashi, anan ya buɗe motqn ya fito mun da tsaraba, bai sauƙe ba parlor ya wuce dasu ya ajiye, sannan ya dawo mukayi sallama, godiya na mkshi ya harare ni na wasa ya shige motan shi ya tafi, ina dawowa parlon na samu hajjaju ta fito, haka ta buɗe kayan tana ta saka albarka, ni dai ban kalli me takeyi ba, sai da naji tace gobe zata nunawa iyayena tukun na juyo na kalleta, baki a buɗe nace, "waya aike ki ki gaya musu"? Harara na tayi ta rufe kayan tace sai ki ɗinke bakina ko ki ɗaure ƙafana.

Da safe na tashi da wuri domin naje na gyara side ɗin ummie, sbd hafsy bata nan, a parlor na sameta tana sauraren karatun sheikh Ahmad sulaiman, cikin karatun shi na suratul YASEEN, har ƙasa na tsuguna na gaisheta, parlon na fara gyarawa sannan na wuce ɗakinta, ina cikin gyaran na jiyo muryan hajiya ummah na buga bayani wa ummie na kayan, mai gadin mu tasaka ya ɗauko mata kayan, sai bayani ta keyiwa ummie na zuwan da A.G yakeyi, abunda ya kamata da wanda bai kamata bama duk tayi dalla - dallah wa ummie, kayan takaici kaman tana mana laɓe har da cewa wai A.G tsabar so kaman zai haɗiye ni, bayan ta gama jaddada komai, tayi hanyar waje, bayan ta jawa ummie kunne akan kada ta bari ko da wasa mamie ta fahimta, shima Abba tace zata ja mishi kunne, a haka ta fita ta bar ni cike da kunyan fitowa, ina gama gyaran ɗakin na wuce kitchen, ko da na fito parlon ban kalli inda ummie ta ke zaune ba, sa kai kawai nayi na wuce ciki, ina gyarawa ina haɗa breakfast, dama yau ba girkin ummie bane, don duk mai girki tana saka na hajiya ummah, saboda haka ko bamu tashi ba ummie muna samu tayi abun breakfast, sai dai muyi lunch da dinner, ina gamawa na zuba mana a filet ɗaya da ita na fito da shi parlon, ƙasa ta sauƙo kan carpet muka fara ci, gefe ɗaya kuma na haɗa mana tea ina ta gauraya nawa don yayi sanyi, wannan ɗabi'a nane bana iya sha tea mai tsananin zafi, amma kuma da tafasheshshen ruwa zan haɗa, chan kaman daga sama na jiyo muryan ummie, "tun yaushe kuka fara magana da shi A.G ɗin? Dawowan shi yanzu ko tun kafin ya yi tafiyan"? A burkice na ɗago kai cike da tsarguwa ina zare ido, kaman ban fahimci tambayan ba nasake tambayan ummin da, "me kikace ummie"? Kallo na tayi kaɗan, sai kuma ta cigaba da abinda takeyi, bata ɗago kai ta kalle ni ba sai ta sake cewa, "ki kula da kanki da tarbiyan ki, ki ɓoye neman wa ƙawaye da yan'uwa har sai komai yayi ƙarfi, ni dama na daɗe da addu'an Allah ya baki miji mai nutsuwa ɗan mutumci, kuma Alhamdllh wannan yaron yana da nutsuwa, don ko nasan sai mai nutsuwa ne tafiyan su zai zo ɗaya da yayanku, Allah ya sanya alkhairi".

Tana gama faɗin haka sai naji duk abincin ya fice mun a rai, ni narasa meyasa suke farin ciki da maganan nan,.

Wunin ranan nayi shi duk a tsarge, komai sai naji yaƙi tafiya mun yadda naci buri, gashi zuciyata cike da haushin M.G take, haka dai nayita ƙunci na.

Bayan sallan magrib sai ga iran shi nan, bayan mungaisa naja nayi shiru, har zuwa wani lokaci sai yayi murmushi yace, "wato ko sannu da hanya bazaki ƙira kimun ba ko? Na ƙira ɗin ma bazaki tambaye ni yayah hanya ba kp?".

Hararan wayan nayi na murguɗa baki kaman yana gani na, a xuciyata nace , "kai daka ga zaka iya ae ka ƙira", kaman wanda yaji mai nace, sai naji sautin muryan shi yace, "nikan da na damu ae na ƙira", gwalo na mishi na sake hararan wayan, "yaya tou meye labari?" naji ya tambaye ni, murya ƙasa -ƙasa nace, "ni ban iya labari ba", murmushi yayi yace, "tou ni nabaki labarin"? Nidai shiru nayi ban bashi amsa ba, jin nayi shiru sai naji yace, "samari nawa kika taɓa yi? Mutum ɗaya dai nasani wato mijin habiba Aliyu ko"? Buɗe baki nayi cike da mamakin yayah akayi ya sani? Murmushi yayi yace, "kina mamaki ko? Tsabar son jin labarin da ya shafeki ne watarana Barr dana dame shi kina da samari? Sai yace mun shi bayaga ma kina kula kowa, don tun wani dayace yana sonki ko baku fajimci juna bane? Sai ya koma habiba, abun ya mun daɗi nace gara mishi ae da yayi gaba saboda Ayshan ta Aminu ce",

"Aminu"? Naji bakina ya furta ban ankara ba, murmushi yayi mai sauti naji yace, "sorry ban taɓa gaya miki full name ɗina ba ko? *AMINU GARBA INUWA* (AG) mummy ne ta saka mana tun muna yara nida M.G, har yanzu kuma sunan ya bimu, saboda haka sunan mijinki maigaskiya".

Tura baki nayi gaba haushin ya ƙira kanshi da sunan mijina.

"saboda haka bayan shi gaya mun su waye suka taɓa cewa suna sonki"?

Gyara zama nayi nace, "nada ko kuma har da na yanzu"? A ɗan ɗage naji muryan shi yace, "ban gane ba Eeshaa, kina nufin kina da wasu samari da kike kulawa?..... Kuma kina hira dasu?..... Akwai wanda kuma kike so?" duk naji shi a furgice yana tambaya na, dariya ce taso ƙwace mun babu shiri, ganin na samu abunda zai saka na bashi haushi sai nace, "a unguwan mu mutum biyu ne kawai, sai unguwa su zee mutum ɗaya, amma duk bana kula su, a school ne kawai nake kula wani lecturer mu da wani student da yake final year a masters, su biyun ina son su....." ae ban ƙarasa bayanin ba naji shi da sauri da kuma ɗan ƙarfi kaɗan ya buɗe muryan shi yace, "kada kimun haka Eeshaa, ina da kishi sosai, nifa ban taɓa kula wata ba, ban taɓa ganin wata nace ina sonta ba sai ke". "ni kan yanzu ma naga wani yana brgeni, addu'a ma nakeyi yace yana sona", na faɗa cike da mamakin kaina yadda bakina ya buɗe don na ƙular da shi ko zai haƙura.

"Eesha Allah bazai nufa ba, ke nawa ce ni kaɗai, zan dawo gobe insha Allahu, ya kamata Daddy su turo wurin Abba, zan samu Barrister yau muyi magana" ae ko da sauri nace, "nifa wasa nake maka, wallahi bana son kowa, kuma bana kula kowa", "Eeshaa hankali na ya tashi tsoro nakeji, idan kikaje kika fara fah? Zan dawo goben insha Allahu ayi abun da ya kamata", ae ban ɓatawa kaina lokaci ba nayi wuff nace, "please mana yayah A.G, don Allah kada ka wahalar da kanka, ba aiki kaje yi ba? Don Allah ka zauna ka ƙarasa, wallahi wasa nake yi, ka tambayi yayah ma ba'a barin mu any how muna kula samari", ajiyan zuciya ya sauƙe mai ɗan ƙarfi, muryan shi alaman aɗan shaƙe yace, "Tsoro nakeji Eeshaa, amma promise me bazaki kula kowa ba"? Murguɗa baki nayi saboda haushin wai bazan kula kowa ba, ama don kada ya dawo mun nayi sauri nace, "ehh nayi", "kinyi alƙawari ke nawa ne ko? Alhmdllh amma duk da haka zanyi magana da barrister, don komai yazama manya sun shiga ciki, don kinga nan da 2weeks zan koma, yakamata komai yazama manya sun shiga."

Nidai cike da jin haushin shi naja bakina nayi shiru, ganin da yayi babu wani haɗin kai da zan bashi ayi hiran ya saka ya mun sallama.

****

Ƙarshen satin da muke aka kawo kayan aure da nasaka ranan raliya, murna da ɗaga wuya a wurin mamie kaman yayah, gashi babu ƙarya an zabga mata kaya kam, sai wani hura hanci itama raliyan takeyi, ita dai habiba babu um babu uhuhm, don Abba ya saka ta dole kullum da yamma tana fita tana ɗan zaga haraban gidan, cikin tan bai wuce wata biyar ba amma ta wani hau kaman ajiƙa yeast, yawancin ranaku idan tafito ita kaɗai, mukan haɗu har takan mun murmushi, nima nakan mayar mata.

A.G dai bai samu dawowa bauchi ba sai ana saura 2dys ya bar ƙasan, domin wani case ne ya riƙe shi a Abujan, gashi M.G kuma ya fita china shi da Daddy su A.G, kuma yasamu yayah Ahmad da maganan, har Alhaji inuwa yazo shi da wani abokinshi wurin Abba, sunyi magana akan a bari sai idan A.G ya gama ya dawo a saka rana, sun dai yi maganan su na manya kawai, kuma abun mamaki Abba bai

sanar a cikin gida ba, illah daga shi sai Aunty Rakiya da Ummie, don ita hajiya ummah dama ita ta kawo shawaran hakan, ko Mamah da bata da matsalah Abba bai sanar mata ba, hattah hafsy bata da labari, don Abba yacewa ummie ko danginta tayi shiru sai lokaci yayi, A.G bawai mutum mai tsananin ƙiran waya bane, zai ƙira da safe, zai ƙira da dare, shiyasa abun yake bani haushi, inaga yadda maryam kafin tayi aure take shan waya, ni kuma sai wannan duskum ɗin, haka dai ya shigo bauchi shi da yayah Ahmad, idan wannna ƙarshen wata yayah Ahmad yazo, wani ƙarshen watan kuma yayah Auwal sai yazo, haka sueyi, don kada su bar chan babu kowa.

Nasan ana idar da sallan ishaa zaizo yadda yace, ina shiga sallan magrib nayi wanka na saka skirt da riga na atamfah batik, banyi wani kwalliya ba ko cika jikina da turare ba wani Humrah ne kawai na shafe jikina da shi, Fatima ce da mukaje bikinta ta bani shi mai sanyin ƙamshi, haka kuma ban wani ɗaura ɗan kwali ba sai na yafa gyale *SHANTALI* a kaina, sharr dani kuwa na fito.

A Parlor na samu ummie da Yayah Ahmad sai hafsy zaune, Ƙasan carpet na zauna daidai ƙafan yayah Ahmad, hannun shi ya ɗaura saman kaina yace, " Eeshan Gwani kin fito ne"? Turo bakina nayi gaba cike da shagwaɓa, dukkansu dariya sukayi, hafsy shugaban yan sa'ido tace, "yayyah sunan shi Gwani kenan? Hala Gwanin iya soyayyah ne ko yayah"? Ta faɗa tana wani ƙyalƙyala dariya, shima dariyan yayi yace, "wannan ae Gwani ne a koto, don idan ya tsayah ba'a samun mai kada shi, kullum winning yakeyi shiyasa aka saka mishi GWANI ɗin, tou soyayyah kuma ae na lokaci ɗaya ne zai cinye wasan", ya ƙarasa dukkansu suna dariya har ummin, ummie ce tace, "yaron ae gaskiya babu laifi, yana da nutsuwa sosai, sai dai ita Ayshan ne banga ta wani zafafa ba akanshi kaman yadda naga su rasa kunya suna kulawa da nasu", ummi ta faɗa tana pointing hafsy, "gaskiya kam ummie mukan muna son namu bamu wani nuƙu - nuƙu, kaso mai sonka, kabashi kulawa kafin wata chan daban ta maka wuff da shi ta barka baki buɗe", ta faɗa tana guduwa zuwa ɗaki tana dariya, ummin ma dariyan ta sukayi ita da yayah Ahmad, sannan yayah ya kalloni ido a waje yace, "Eashan Gwani akwai matsalah ne? Idan akwai ki gaya mun tunda wuri, amma dai kam a sanina kafin ki samu nutsatstse irin A.G akwai wuyan gaske, baida problem ko kaɗan, gashi mai son gaskiya da riƙon amana, amma idan bai miki ba ki faɗa tun wuri".

"wani irin bata son shi, ae ni dai banga makusa a tare da shi ba ko kaɗan, yaro mai kyau da ilimi, gashi ya fito a zuriya masu daraja, nidai addu'a na Allah ya tabbatar da alkhairi a wannan tafiyan, "

Ummi ta faɗa, shidai yayah Ahmad ƙara jaddada mun idan bana so na faɗa da wuri, nidai bance uffan ba kawai na sunkuyar da kaina ƙasa, a haka aka ƙira sallan ishaa, fita yayi mu kuma muka shige ciki don yin sallan, anan na samu hafsy ana ta shan soyayyah a waya, ko kula takanta banyi ba na ɗauki hijab na fara sallah, don

nasan tsantsan iskanci ta ga na shigo ne take wani karairaya murya tana, "Baby tou me kachi tun ɗazun? Amma dai yayah umar bai kyauta ba da bai nema maka wani abu da zaka ci ba, ae yasan ciwo yana kan kowa, sorry Baby nerh", ina jinta ta na ta wasu ƙalƙala a harcenta, nidai na maida hankalina nayo sallah na, na idar tana ta kan wayan, hararanta nayi nace, "idan kin haɗu da walakiri sai ki gaya mishi zabgegen Baby ne ya hanaki sallah akan lokaci", dariya ta kwashe da shi tana gayawa yayah ishaq abunda na faɗa, sannan ta kashe wayan ta shige toilet, na kai mintuna talatin a zaune a wurin ina wuridi, don har hafsy ta idarr tayi nata wajen ina zaune a wurin.

Muryan A.G naji da yayah Ahmad a parlor, A.G suna gaisawa da ummie nah, dafa saitin zuciyata nayi domin wani bugawa yake mun, babu daɗewa kuwa sai ga yayah Ahmad ya shigo ɗakin kallona yakeyi fuskan shi cike da seriousness, "kifito AG yana Parlor idan kuma kinga baki ra'ayi tou ko gaya mun yanzu zan sallame shi ko zai samu attack ne, ni nafi son farin cikin Eesha na akan nashi", sunkuyar da kaina nayi ina murmushi, shima murmushin yayi ya juya ya fice.

Tashi nayi ina dariyan maganan yayah Ahmad, wai kada yasamu attack, tou akan me? Haka dai na fita zuwa parlon, samu nayi hafsy ta ajiye mishi zoɓo da cin-cin a gaban shi, ina fitowa kuma ta wuce tana ƙunshe baki ta shige ɗakin ummie, wanda nake jin muryan yayah Ahmad a ciki, na daɗe da zama tukun na gaishe shi murya chan ƙasa, ajiyan zuciya yayi sannan naji yace, "mummy tana gaishe da yꞌarta Eashaa, Eeshaa beauty", ya faɗa ƙasa-ƙasa kaman baya so wani yaji, don ni ma kaɗan kaɗan naji shi, ɗago kai nayi na kalle shi, don naji kunya da ban tambaye shi yayah take ba? amma da sauri na maida kaina ƙasa saboda ina ɗago kai yana ɗaga mun giran shi sannan ya kashe mun ido ɗaya, tura baki nayi gaba ina gunaguni, domin bai san kunyan da yake sakani ba idan ya wani ɗaga giran nan ko ya kashe mun ido, gashi dama wasu irin ido yake da shi masu sani jin ɗumi a jikina, "I luv u kike faɗa mun ƙasa -ƙasa"? naji shi yana faɗa, nan ma da sauri na ɗago kaina na dube shi baki a buɗe, "nifa cewa nayi sai kai ta ɗagawa mutum gira bakajin kunya", dariya yayi yace " kuke fah, ba gashi kim buɗe baki kin gaya mun idona suna gigita ki ba", kallon shi nayi nace, "nifa bawai nace suna firgitai bane, kawai dai naga da kunya mutum ya dinga kashe ido yana ɗaga gira, ni kunya yake sakani",

Idon shi ƙurr akaina yace, "tou nima ki mun naji yayah kikeji, ina so nima naji kinyani ko kaɗan ne", ya faɗa still yana sake ɗaga mun giran na shi, kukan shagwaɓa na fara mishi ƙasa -ƙasa ina ƙunƙuni na, dariya yayi kaɗan ya taso ya dawo kujeran kusa dani, "Eeshaa nah don Allah kada ki susutani a parlon ummin mu, wallahi idan baki bar kukan nan ba zan tayaki,"

Ɗago kaina nayi da sauri jin yayi ƙasa da murya kaman zaiyi kukan, kallon shi nayi ido waje nace, "nifa ba kuka nakeyi ba, please ka kuma chan kada yayah ya fito".

Ajiyan zuciya kawai yayi ya ƙura mun idon shi duka da suke lumshe, "Eeshaa kina da kyau sosai, banda ni banga wanda yafi ki kyau ba a duniyan nan, idon ki masu kyau kawai nawa ne yafi naki kyau", hararan shi nayi ina kallon shi nace, "kafini kyau?" ɗaga kai yayi alaman haka yake nufi, hararan shi nayi nace, "nafika dogon hanci fah," murmushi yayi yaa kan kallo na da lumsheshhen idon shi, bai ce komai ba sai idon daya kura mun yana wani smilling, hararan shi nayi na sauƙe idona ƙasa, don gaskiya ne yana da wani mahaukacin kyawawan ido, tun ba yau da ya matso kusa dani kuma yayi maganan kyaun ido yasaka na kalle shi da kyau, ga idon manya da su amma baya iya buɗesu dukan su, "nidai ka koma chan", na faɗa ina kawar da kaina gefe.

Hancin shi ya ɗan shafa kaɗan yana kallona, "Beuty kinsan kyaun hanci na kuwa? Baki san yafi dogon hanci kyau ba, kalla kiga hancin mu fa kusan iri ɗaya ne fah dake, don kema naki daidai ne mai kyau, don har ya kusa iso nawa a kyau", dariya ne ya ɗan suɓuce mun, "ni ban taɓa jin mai yaba kyaun shi ba sai kai, kuma har kana tunanin ina mace ka fini kyau" na faɗa ina maida kallon na fuskanshi, marairaice mun fuska yayi cike da alaman shagwaɓa yace, "Allah akwai wata yar Eathoupia da muke course ɗaya da ita, kullum sai ta ɗauki photo na idan ina zaune, har friend ɗinta yar India ce ita kuma, wata rana ta daure tazo har inda nake ta zauna, chan sai tace, "an taɓa gaya maka irin baiwar kyaun ido da kake da shi"? Kallon ta nayi shiru bance komai ba, sai ta cigaba, "friend ɗita AFRAH kana mata kyau, tana so kuzama friends da ita, amma ta kasa gaya maka", tou ni tunda ga ranan na ƙara yadda ni mai kyau ne, saboda yan eathoupia da india har suka ga kyau na, ae kuwa kyaun nan ya kai inda ya kamata ya kai", ya ƙarisa faɗa yana wani shafa fuskan shi, ido shi kuma akaina.

Lokaci ɗaya naji wani mumunan ɓacin rai, wanda har akan fuskana ma bai ɓuya ba, kallon shi nayi ya ƙura mun ido nace, "kuma kayi accepting ɗinta kun zama friends ɗin"?

Girgiza kai yayi alaman a'a, sanan ya buɗe baki har lokacin cike da wani basarwa yana wani ya mutsa fuska yace, "ina zan accepting mata? Kalan duk ranan duniya ta dinga kallona tana yaba kyau na? Ko amsawa friend ɗin nata banyi ba, tashi nayi na wuce room ɗina, a zuciyata nace, "wallahi baku isa ba, sai nazo naji daga bakin Beauty nah, idan haka ne tou sai naji gaskiyan batu, idan bakiga kyauna ba kuma sai na koma nayi accepting ɗinta, don ima son naji ance ina da kyau, da kyaun ido", ya faɗa yana kara shigar da idon shi cikin nawa.

Ajiyan zuciya mai ɗan Ƙarfi na sauƙe, wanda har sai da yasaka shima ya sauƙe, "ita ɗin tana da kyau ne"? Na tambaye shi, ɗaga kai sama yayi alaman ehh, ɓata rai nayi nace, "kenan dai ta maka kyau"? Girgiza kai yayi alaaman a'a , harara na

aika mishi da shi, "mekake nufi tou? Nasan ae ta burge kane shiyasa baka manta fuskanta ba", na faɗa ina tura baki gaba, du raina ya ɓaci.

Buɗe baki yayi ya saka hannu a haɓan shi yace, "nifa ke kaɗai nake ganin kyaunki, kawai ina so ke danafi so da ganin kyaunki naji daga bakinki kafin wasu kuchakai su dinga gaya mun, nafi son jin nako, ina da shi ko bani da shi"? Ya faɗa muna ara haɗa ido da shi.

Yamutsa fuska nayi sannan nace, "kana da shi kaɗan, amma dai baka wani fini ba", na faɗa ina kallon yatsun hannun shi da yake ɗan lanlanƙwasa su.

"Nifa nayi tunanin nafiki kyau wallahi, tou idan na koma zanje na samesu sumun bayanin yadda zan fahimci nawa kyaun, don ni tunani na nayi irin sosai ɗin nan ne".

Da sauri nace, " ba sai ka sake neman bafa, kana da kyau sosai, idonka ma mai kyaune sosai, kada ka sake kula su, kaga ance kai mutumin kirki ne kada kuma azo a ga kana kula mata", na faɗa kaman zan masa kuka.

Dariya yayi sosai yana lumshe ido, sannan ya ɗan sunuya sosai da kanshi yace, "dare yayi zan gudu wurin mummy, gobe insha Allahu zanzo muyi sallama, sai naji sauran bayanim, don ma ɓoye miki ne, tave ma tana sona, amma nafi so naji daga gareki, idan sonki yafi burgeni, tou xanyi warning ɗinta, idan kuma ke baki sona sai na duba yayah natan yake", ya faɗa yana miƙewa tsaye, dama sanye yake da wasu jean da shirt mai layi layi, ya mish kyau sai ƙamshi yakeyi, nima tashi nayi tsayen don jin da nayi yace bari dai ma na koma sai na ƙirata mu gaisa a waya don kada tace na shareta, kin san sun bani number wayan su".

Ɓata rai nayi nayi gaba don rakashi zuwa bakin ƙofan fita, hanya na bashi ya fita, yana fita ya tsaya ya maida hannayen shi cikin aljihun wandon shi ya karkatar da kanshi gefe kaɗan ya ƙura mun ido, duk narasa mai yake mun daɗi, a hankali na kalle shi fuskana cike da damuwa nace, "ka ƙirani idan ka isa zan gaya maka wani abu", risinar da kanshi yayi kaɗan yace "angama Beauty nah, inaga muna gama waya da ita zan ƙiraki, ko kuma sai munyi da ke"?

Bansan lokacin dana fara buga ƙafana a ƙasa ba, "nikan bana so ka ƙirata, ka Ƙirani sai nagaya maka tukun", na faɗa ina shirin mishi kuka.

Matsowa yayi kusa dani yace "mummy kawai na miki alƙawarin zan kula a duk matan duniya sao na ƙiraki, ko sister na yau ta kalle ni sai na ranƙwasheta ballantana ta mun magana, ina shiga ɗaki ke zan ƙira ranki ya daɗe".

Dariya ya bani babu shiri na juya cikin parlon da sauri, shima ina jin sautin dariyan shi.

Ina shigowa kuwa na haɗu da yaya Ahmad wanda fitowan shi kenan daga ɗakin ummie, kallo na yayi yana murmushi yace, "barrister ya tafi kenan?" murmushi nayi na ɗaga kaina sama alaman ehh, murmushin ya sakeyi yace, "A.G mutumin kirki ne ayshaa, ki so shi xakiji daɗin zama ɗa shi, dattijo ne sosai, kuma bayida hayani, idan Allah yasa yazama mijinki zakiji daɗin zama da shi", murmishi kawai nayi ina zama akan ɗaya daga kujerun parlon, muna haka ummie ta fito hannun ta ɗauke da filet, da sauri na miƙe na karɓa na wuce kitchen, sallama sukayi da shi ya wuce gidan shi.

Ina fitowa naga ummi bata parlon, wucewa nayi har ɗakinta na sameta suna shirin kwanciya ita da hafsy, don ɗakinmu sai da baƙi sosai a gidan muke kwana, ɗakin ummie hafsy ke kwana ni kuma ɗakin hajiya ummah, sai da safe na mata, sannan na wuce side ɗin hajiya ummah, bayan ummie ta biyoni domin rufe musu ƙofa.

Wuraren 10:00 na dare kuwa sai ga ƙiran shi ɗan halak, dama na shiga ɗakin hajiya umma ɗaya wanda muka mai da shi namu, a zuciyata nake maganan shi akan yaƙi ƙira, hala ma ya ƙira wancan ɗayan ne, tsaki naja bayan na kashe wutan ɗakin na hau zan fara addu'a, kawai sai ga wayan shi ya shigo, ido na zubawa wayan yayita neman agajin ɗauka ban kula shi ba, yana katsewa wani ƙiran ya sake shigowa, shima har ya kusa yankewa tukun nasaka hannu na ɗauka.

Ajiyan zuciya ya sauƙe mai ɗan sauti, shiru mukayi dukkan mu babu wanda yayi magana, amma kowa yana sauraran sautin bugun zuciyar ɗan'uwan shi, mun ɗauki sama da mintuna goma babu wanda yayi koda tari ne, har nayi niyyan kashe wayan, amma kuma kaman wanda yake duba sai naji muryan shi a ɗan shaƙe yayi magana, "beauty na dawo gida, mummy ta ɗan tsayar da ni muna hira", ajiyan zuciya na ɗan sauƙe a hankali, sannan nace, "bakayi wayan ba kenan"? Shiru yayi kaman mai tunani, don shi gaskiya a gefen shi ya manta da maganan wata da yayi bayan Eeahan shi, chan kuma abun ya faɗo mishi a rai yace, "ni na isa na ƙira wata bayan na miki alƙawarin ke zan ƙira? Heedayah ma tana gaishe ni nayi kaman ban san tana wurin ba, ganin haka itama tayi ta kanta".

Dariya ne ya suɓuce mun, "ni fa bance maka har da sisters ɗinka kada ka kula ba", na faɗa ina riƙe dariya na, don yanayin yadda yayi maganan ya sakani dariya, "ok tou nagane, banda su heedayah, tou ƙirgamun wanda baki son na dinga kula su beautyn A.G".

Gyara kwanciya na nayi nace, "wannan yarinyar da friend ɗinta", ina jin shi yace, "one",

Murmushi nayi nace ko wacce mace idan ba yan gidanku ba ko kuma tsufaffi, har yan office ɗinku", ina gama faɗa na saka hannu na toshe bakina, "insha Allahu zan

kiyaye beauty, sai dai ina neman alfarma guda ɗaya a wurinki", ya faɗa da mugun nutsuwa a muryan shi, ban amsa mishi ba naji yafara mun bayani, "Eesha ni mai tsare kaina ne sosai, kuma zan ƙara fiye da yadda nake a baya, ni lawyer ne dole wasu matan zasu neme ni akan damuwan su, insha Allahu na miki alƙawari daga abunda ya haɗani da su babu wani abu da zai biyu baya, sannan Ina da family both side, mummy da daddy nah, kuma akwai mata, insha Allahu zan tsaya dai dai da yadda shari'a ya umurce mu dayi, wata mace insha Allahu bazata ga dariya na ko murmushi naba idan bake ba, sai dai a bisa kuskure, zan tsare miki kaina yadda bakiyi zato ba, amma kema bana son ki kula ko wanni saurayi please."

Wani irin nutsuwa ne yazo mun a zuciyata, wanda bansan meye dalili ba, "ni ae bana kula samari, ni basu ma burgeni," na faɗa ƙasa-ƙasa da murya, "amma dai ni ina burge ki ko"? Naji muryan shi yana tambaya na, runtse ido na nayi, sannan nace, "ni tausayinka kawai nakeji".

"Alhamdulillah" naji ya faɗa, sannan kuma naji yace, "Eesha kin gama mun komai a rayuwata, duk macen da take tausayinka tou ba ƙaramin so zata maka ba, Allah na gode maka", ya faɗa da ɗan ɗaga muryah.

Zaro ido nayi ina rufe bakina da hannu ɗaya, "nifa ciwon kanne yake sani tausayi bawai sonka.....", sai kuma nakasa ƙarasawa, saboda yau ɗaya kawai naji ina jin kunyan nace bana son shi, haka dai mukayi ta hira wanda bansan ma 12:00 am yayi ba, sai da naji yace nayi haƙuri ya jani muna hira har 12, sallama mukayi kowa ya kashe wayan shi.

****

Washe gari yazo amma a parlon hajiya ummah muka zauna, sallama ya mun akan gobe zai wuce Abuja, don tanan zai tashi, yau banji yana jana da hira ba kawai shiru yayi ya ƙura mun ido, har narasa yadda zanyi da kallonshi, duk ɗago kaima kuma sai ya ɗaga mun giran shi sama, haka dai har 9:00 tayi sai yace nayiwa hajiya umma magana suyi sallama zai tafi gida, tashi nayi naje ɗakin na mata magana, sallama sukayi tana ta saka mishi albarka, da alƙawarurruka Kaman itace mai auren shi, bunch na 500 ya ajiye mata ya fice, tana ta zabga mishi addu'a, nidai nabi bayan shi, muna fita yace muje yayiwa ummie sallama, haka naja tsummukaran ƙafana jiki a sanyayae na raka shi har parlonta, suna tare da hafsy da yayah Ahmad, hannu ya miƙawa yayah suka gaisa, sannan ya gaishe da ummie, nidai gefen hafsy naje na zauna kaina a ƙasa, hira suka ɗan taɓa kaɗan, sannan yayiwa ummie sallama akan gobe zasu wuce tare da yayah Ahmad, flight na ƙarfe 9:00am zasu bi, hafsy ya ƙira sukayi waje, chan sai gata ta dawo, hannunta riƙe da envelop an saka 100k wa ummie, sannan tace mun naje yana jirana a waje, ni dai tashi nayi na fice, ina jin ummie nayiwa hafsy faɗan meyasa ta karɓo, ita kuma tana

cewa, ko da wa ita yabayar karɓewa zatayi wallahi, tana faɗa tana dariya abunta, haka dai na wuce nayi waje.

A jikin motan na tsaya hannu na riƙe da murfin motan, shi kuma yana zaune a driver sit, ƙafan shi ɗaya a waje ɗaya a ciki, hannun shi akan stearing motan, dukka ida nun she a zube a kaina, munyi shiru babu wanda ya tanka a cikin mu, chan dai nayi ƙarfin hali nace, "kana ta hidima dasu ummie da hajiya ummah, an gode Allah ya ƙara buɗi", baice uffan ba sai ido dai da yaci gaba da zuba mun su, ɗago kaina nayi muka haɗa ido da shi, "Beauty zakiyi mssn ɗina"? kawai naji ya faɗa ido a lumlumshe, Girgiza kai nayi alaman a'a, da sauri ya daga kanshi yace, "shiyasa nakeso nayiwa yarinyar nan tambayan gaskiya, idan ta amsa mun kawai zanyi haƙuri na amsheta".

"tambayan me zaka mata"? Na tambaye shi, "ko da gaske tana sona, idan har da gaske ne zan bawa kaina haƙuri kawai ayi da ita", ya faɗa yana wani ya mutsa fuska, sama na ɗaga kaina kawai ia kallon taurari, batare da na sauƙe kaina ba nace, "idan ta amsa maka kuma zaka sota? Bayan kache mun bazaka sake kula wata mace ba"? Kallona na mayar kanshi jin yace, "tou ae kene beauty, ni so nake kawai a soni, ke kuma kin nuƙe kin ƙi ki soni", ya faɗa idon shi na kaina, idona cikin nashi ina jin yadda zuciyata take wani irin mugun harbawa, a hankali na ɗauke kaina saboda yadda nake jin wani irin yanayi idan muna kallon juna, baki na tura gaba nace, "tou ni dai bama son kayi magana da ita, bana son ma ka koma school ɗin", "tou please Eeshaa ki soni", ya faɗa kanshi tsaye, shiru nayi ina tunani, chan kuma sai nace, "shine zai saka bazaka so wata ba" ido na akan shi, lumshe ido yayi ya ɗan ɗaga mun kai alaman ehh, "tou zanyi tunani, amma..... Sai kuma nayi shiru ganin Yayah Ahmad ya fito, ƙurawa Yayah Ahmad ido nayi, _Sai da ya Kusa isowa inda muke sai nayiwa A.G sallama na wuce, anan suka ɗan tsaya kaɗan, sai kuma naji tashin motan kowan su.

Washe gari suka wuce Abuja, zuwa dare kuma jirgin su A.G ya ɗaga, kafin ya wuce ya ƙirani munyi waya, washe garin ranan tafiyan shi kuma ya ƙirani wuraren ƙarfe shida na asuba akan sun isa lpy, daga wannan ranan kullum sau biyu a rana sai munyi waya da shi, wataran ma sau uku zuwa huɗu, amma bamu wani dogon hira da shi, M.G kuma shiru banji ko sau ɗaya ya ƙirano a waya ba, nima haka sai na share shi.

****

Kwanci tashi asaran mai rai haka dai rayuwa ta lula damu har december, har satin bikin raliya, wanda har zuwa lokacin mamie bata san da maganan aure na ba, ana sauran 2weeks auren raliya kuma Aunty j ta haihu, itama ɗa namiji aka samu, wanda yaci sunan Yayah Auwal, wato *MUHAMMAD AUWAL* amma suna ƙiran shi da Affan, a zuwan mu sunane nasan M.G yana ƙasan yana Abuja abun shi, domin ranan sunan ma hafsy tace mun sun haɗu da shi, yace ta gaishe ni suna saurine zasu fita da yayah, nidai naji haushi, saboda meyasa M.G ya wani ƙaurace mun, babu waya babu ziyara, gaskiya Alƙawari baice haka ba, haka dai nima na share batun shi, mun dawo kuma bikin raliya.

Mudai babu ruwan mu da wani rawan kan bikin, yayun mi dai duk sunzo daga Abuja, kuma har da Aunty B da Areef, maijego kawai aka bari da wata yar'uwar ta, Adda ma tazo, Aunty ma'u ma tazo, gida dai ya cika da dangi sosai, ranan da za'ayi walima, da safe hadiza suka zo da yan'uwa na chan, zuwan tane ma ta jani muka shiga side ɗin mamie, anan naga habiba, tayi wani irin ƙiba, ga cikin ya fito sosai, tana zaune a ƙasa tana shan kankana, gaisawa sukayi da hadiza, ni kuma ta kalleni fuskan ta ɗauke da fara'a, murmushi na mata, itama ta maida mun da gaggawa, sannan naga ta kalli gefen da mamin ta take zaune, ganin bata ganinta sai ta mum alaman nazo nasha kankanan, murmushi nayi na mata alamamn na gode tasha kawai, haka dai tayita ƙureni da idon ta, har muka gama muka fita fatar bakin mu bai furtawa juna komai ba, tausayin ta cike da zuciyata.

A haraban gidan mu akayi haɗaɗɗen walima, wanda yafi na habiba ƙayatuwa, amaryah tasha kyau sosai, tayi shiganta mai kyau, sit ɗaya muka zauna da ni da hadiza da maryam, domin tazo mana, hafsy da ummita suna chan cikin friends, don raliya bata tsoron mamie irin habiba, ita da taga bikinta ya matso kusa sai ta jawo hafsy ajiki suka cigaba da sha'anin su, duk ɗaga kna da zanyi sai mun haɗa ido da habiba, kuma sai ta mun murmushi, nia sai na mayar mata, har magrib tukun aka watse, washe gari aka ɗaura aure, akayi wuni, bayan la'asaar aka kai amaryah ɗakinta, naji ance bayan 1week zasu koma kaduna da mijin, don achan yake da zama, mudai washe gari muka bi Adda da Aunty ma'u muka ga gidan amaryah, gida yayi kyau sosai, don da muka fito naji Adda da Aunty ma'u suma hiran wannan karon mamie ta samu yadda ta keso, don Abba ya sakar mata kuɗi sosai bakaman na habiba, shiyasa tayi bushashanta son ranta.

Rayuwa tana ta jan mu da gudu har muƙa shiga watan Febuary, wanda yana daidai da saura 2month A.G ya gama ya dawo, alokacin idan kin kalli habiba sai ta baki tausayi, duk haskenta ya ƙaru tayi bauu ga kumburi da ƙafafunta da jikinta gaba

ɗaya sukayi, wata ranan laraba ta tashi da wani azababben naƙuda, mamie har side ɗin ummie ta shigo ranan a ruɗe ta gaya mata, haka aka ɗunguma akayi asibiti da ita, *RIMI CLINIC* Mamie da iyalenta suke zuwa, saboda haka chan suka nufa, bayan ummie ta umurce mu da mu ɗaura abinci nida hafsy, babu nutsuwa a tare dani muka shiga kitchen ɗaura abincin, chan wayan A.G ya shigo, a tsatstsaye na ɗauka na mishi bayanin aiki nakeyi, a cikin muryana ya fahimci akwai matsalah, tambaya nayi me yake faruwa, nan na gaya mishi habiba ce zata haihu, kuma tana shan wahala, rarrashi na yayi da kalamai masu daɗi, inda har yake ce mun saura mu, nida shi, yasan shikan duk ranan da zan haihu sai an mishi Alluran bacci, dariya nayi na mishi sallama.

Wuraren 12:00 mun gama haɗa komai, hattah flask da akace mu sake cika guda biyu mun cika, driver ne ya ɗauke mu tare da mahma muka bi bayan su, isan mu kuma babu wuya akace Abba ma ya taso daga Abuja yana hanya shi da yayah Auwal, har ɗakin da take muka shiga muka duba ta, nidai sai da nayi hawaye irin wahalan da naga tana sha, mahma da ummie suna riƙe da ita akan tasha ruwan ɗumi, ita kuma mamie tana tsaye daga bakin ƙofa, idan anjima kaɗan kuma ta fita tayi kiran waya, abu dai har wurin magrib babu haihuwa, ana haka Abba suka iso, bayan ya dubata ne suka shige office ɗin Dr don suji ko yayah ake ciki, nan Dr yace idan ta cika zuwa 8:00 bata haihu ba zasu mata C.S, haka su Abba suka wuce mosque sukayi sallah, har sai da sukayi ishaa tukun suka shigo, mu dai muna tsaye cirko -cirko a bakon ɗakin, shigan Abba bai daɗe ba naga mamah ta leƙo ta Ƙirani, jikina yana rawa nabi bayanta.

Muna shiga na kalli habiba rungume ajikin Abba tana kuka duk ta galabaita, "Abba na roƙeka ka umurci mamie ta bani izinin magana da yʻar'uwata kafin na bar duniya, Abba ina son magana da Ayshaa kafin na mutu, Abba mutuwa zanyi", ta faɗa tana ƙara kukan da takeyi, Abba ne ya dube ni sannan yace, "Ni nabaki daman kiyi magana da yʻar'uwarki, ae da nasan duk tsawon lokacin nan ta hanaki zumunci da yʻar'uwarki wallahi da na ɗauki mataki, kuma yanzu ma bai ɓaci ba zan ɗauka akan kowa, da wanda ta hana da wanda sun san an hana basu gaya mun ba, Allah dai ya sauƙe lafiya habiba nah".

Kallon mamie tayi cike da rauni tace, "mamie ki gafarce ni na mata magana"? Ɗaga mata kai tayi tana share hawayen ta, hannu habiba ta miƙo mun, ni kuwa ban ɓata lokaci ba na ƙarasa jikinta, rungumeta nayi hawaye na zuba a ido na, "sisto na kiyafe mun duk abunda ya faro, wallahi ɓa'a son raina nake ƙin kula ki ba umurni nake bi don na rabauta, amma kullu kina raina, ki yafebmun aure miki Aliyu da nayi sisto", hannu na nasaka na rufe bakinta hawaye na yana zuba babu kakkautawa, itama hannu ta saka ta riƙe nawa dana Abba tace, "Abba kazama shaidah duk abunda na haifa na bawa sisto duniya da lahira, idan mace ce a saka sunan sisto,

idan kuma namiji ne sunan ka nake so Abba, ina kwaɗayin su yi rayuwa da halaye irin na ko, duk duniya babu abun da nake so irin kai da sisto na", sannan ta dawo da kanta kaina tace, "kicewa Aliyu na yafe mishi duk abunda ya mun duniya da lahira, kuma ku haɗu ku riƙe mun abunda zan haifa idan mai rai ne", azaban ciwo ne yasaka ta ɗan yunƙura kaman zata sauƙo, nan kuma likita ya shiga yace mu ɗan fita daga waje zai dubata.

Muna waje ina rungume ajikin Abba inata kuka yana rarrashina, gefe ɗaya kuma mamie ce ta sunkuya tana ta share hawaye ummi na bata baki, ita dai hafsy sunyi tagumi ita da mama da yayah auwal da hajiya ummu suna zaune a ɗan gefe kaɗan.

Muna nan har wurin 1hr likita bai fito ba, chan kuwa muka jiyo kukan jariri, wani zabura nayi zanyi ciki Abba ya riƙoni, ita ma mamie tashi tayi tsaye, sai Ummie ta hana ta shiga, duk jikima rawa yakeyi narasa murna nakeji ko kuma me nake ji, muna haka har bayan mintuna kusan ashirin sai ga nurse ɗaya ta fito hannun ta riƙe dababy a farin showel, da sauri na nufeta hannu na miƙa ita ma sai ta saka mun babyn fuskanta da fara'a, da sauri na buɗe ina kallon fuskan babyn mai tsananin kama da su jamilah, sai dai farine sosai kaman yan gidan mu, murmushi da fitan hawaye ne a fuskana, ina jin nurse ɗin tace an samu ɗa namiji, godiya wa ubangiji duk aka fara, Abba yana tambayan mai haihuwan fah, nan naji tace Dr yana duba ta, na daɗe ina kallon fuskan yaron ina jin wani irin ƙaunar shi a zuciyata, hannu Abba ya saka ya karɓi yaron, babu yadda na iya na miƙa mishi, addu'a ya mishi sosai, sannan ya miƙawa yayah Auwal yana zolayan su da nikan bazaku bani yar budurwa bane kam na cika ta huɗu? Kowa sai ya sulluɓu ƙaton saurayi munana, dariya su mamah sukayi suna mu ae haka yafi mana, ayita haiho mana mazaje, ita dai mamie dariyan yaƙe ne a fuskanta, amma duk hankalinta yana ga ɗakin da habiba take, yaron yana rie a hannun ummie Dr ya buɗe ɗakin da habiba take ya fito, Abba ya miƙa mishi hanni suka sake gaisuwa, Abba yana tambayan shi yaya jikin ita mai haihuwan? Share zufan goshin shi yayi sannan yace wa Abba, "Munyi iya ƙoƙarin mu mubata kariya ta haihu lpy, amma tana haihuwa wanda yafi mu sonta ya amshi abunshi, sai dai nace kuyi haƙuri wanda yafi mu son habiba ya amshi abun shi", nidai abu biyu kawai naji bayan magana shi, shine naji muryan mamie da ƙarfi tace, "Karya kakeyi likita, habiba bana bata mutu ba", sannan naji muryan hajiya umma tana "innalillahi wa'inna ilaihir raji'un, wannan wani irin mummunan labari ne"? Daga nan ban san me ake ciki ba, sai farkawa nayi na ganni a ɗakin ummi na akwance, gefe ɗaya kuma yayah Auwal ne yayi tagumi hafsy na gefen shi tana ta share hawaye, da hanzari na miƙe zaune nace, "Yayah mummunan mafarki nayi, ina ummie nah"? Riƙo ni yayi da yaga ina ƙoƙarin zurawa waje a guje, Yace "ina xakije Ayshaa"?

Da sauri nace "zanje parlor ne ummie ta rakani na duba yayah habiba take, mafarkinta nayi wai ta haihu.....", sai kuma naji tsoron Ƙarasa faɗin sauran, hafsy ne naji ta fashe da kuka ta taso ta rungume ni, "Adda ba mafarki bane da gaske kin rasa yar'uwar ki yau", kallonta nayi baki a buɗe nace, "kuma kinga ta haihu? Yaron namiji mai kama da su jamilah"? Ɗaga mun kai tayi tace, "Adda ae har kin ɗauki yaron ma kafin a faɗa mana rasuwan".

Juyawa nayi na kalli yayah auwal, muryana yana rawa nace, "yayah rakani na ganta", hannu na ya riƙo muka fita har side ɗin mamie, muna shiga a parlor na hango mamah da sai hajiya umma a zaune a saman kujera, sai wasu daga cikin yan uwan Mamie a parlon, ga mahaifiyar mijin raliya da wasu daga maƙotan mu, daga ɗaki kuma ina jin sautin kukan mamie da ake ta bata haƙuri, ido na na mayar wurin dinn<ng ɗin mamie da aka matsar da kujerun aka kwantar da habiba a ƙasa, ga wasu yan'uwan mamie da suke zaune a gefen gawantan, juyawa nayi na kalli yayah Auwal bakina yana rawa ina nuna gawan habiba nace, "Habiba ce wannan yayah"? Ɗaga kai yayi alaman itace, "bakaga ana sanyi ba ne yayah aka kwantar da ita a ƙasa"? Hawaye na bin fuskana, bai amsa mun ba sai ya juya ya fice a parlon, ɗakin mamie na shige na tsaya a bakin ƙofan ina bin su da kallo, idon ummi yana kaina ni kuma ina raba ido na, chan na hango babyn a kwance akan gado, kallon mamie nayi da take ta kuka naji na ƙira sunan ta da ƙarfin da bansan murya na yana da shi ba, "mamie kinga abunda kikayi ko? Ashe yar'uwata bazata daɗe ba, bazamu goyi yaran mu tare ba? Kin raba mu, bayan tace mun duk ranan da ɗaya ya haihu zamu kwana muna kallon babyn mu saka suna mai daɗi, muyi wa junan mu takwara, mu so yayan, zata so nawa kaman nata, zan so nata kaman nawa, amma kin raba mu, ashe ma Allah a kusa zai raba tsakanin mu, kukan me kikeyi? Nice nan kuka ya same ni", na faɗa ina buga kƙirjina, da gudu mamie ta taso ta rungume ni tace, "dukkanmu kuka ya same mu Aysha", runtse ido nayi saboda kukan da naji babyn yana yi, juyawa nayi na fita zuwa parlor, direct wurin gawan habiba na nufa.

A gaban gawan yar'uwata habiba na durƙusa, hannuna toshe da bakina, saboda bana son yi mata kuka akan gawanta, hannu nasaka na yaye mayafin da aka rufe fuskanta da shi, kyakkyawar fuskanta mai kama da na Abban mu shinfiɗe da annuri, ga wani fari da tayi na alaman babu jini a jikinta, fuskanta a ɗan kumbure kaɗan, wani abu ne naji ya bugi zuciyana, sai na dinga tunata a yadda muke da kafin komai ya lalace a tsakanin mu, wai yau habiba ce shimfiɗe a gabana tazama gawa? Duk sai naji nakasa riƙe kaina, ina kuka ina mata addu'a, har wani lokaci aka zo aka mata wanka aka shiryata, duk dai ina wurin, addu'a Abba ya shigo yayi mata, ranan dai kwana mukayi a zaune babu wanda ya samu daman runtsawa.

Washe gari dukkan yayun mu sun iso, yayah umar ne kawai ba'a bar shi yazo ba, zuwa lokacin duk nayi laushi bana iya komai sai dai hawayen da yake zuba mun, ina ganin mama tayi wanka a babyn habiba, ta bashi madaran da tun jiya ummie ta

aika aka sayo da su glucose, ana bashi madaran hafsy ta goya shi a bayanta, ita dai mamie babu abun da take iya taɓukawa, wuraren tara na safe raliya suka iso, inaga daga ita har su yayan mu ko da asuba suka kamo hanya oho, shigowan ta ne ya sake hargitsa mu, domin rungume gawan tayi tana kua kaman ranta zai fita da ƙyar yayah muhammad yajata zuwa ɗakin mamie, ganin su ya saka mamin sake fashewa da kuka, shima yayah muhammad kukan ya fashe da shi yana zama a bakin gadonta.

Ana shirin fita da ita ƙarfe goma saura, sai ga Abba sun shigo tare da Aliyu, har gaban gawan Abba ya rakashi, ina kallon shi cike da jin haushin shi, yana ta share hawaye hannun shi riƙe da hanky, addu'a sosai ya mata, sannan naji yana cewa "habiba na yafe miki, Allah ya miki rahma, ya raya abunda kika bari, haƙurin ki da halayenki nagari, ya miki jagora har cikin aljannatul firdausi" daga nan ya fashe da kuka, har sai da Abba ya umurci yayah Ahmad ya fita da shi, gefe ɗaya kuma Mummyn shi ce zaune da wasu daga cikin yan'uwan shi mata, Addu'a sosai Abba yayiwa habiba shi da wani abokin shi da yayan mamie, Abba ya ƙurawa gawan ido na wani lokaci sannan yace, "haƙiƙah mutuwa xafin ta nada ciwo, mutuwa irin na ƙuruciya, habiba Allah ya gafarta miki, Allah ya baki ikon amsa tambayoyi, Allah yasa kinyi shahada, ni Usman mahaifinki na yafe miki duniya da lahira, ballantana ma baki mun komai ba, haƙuri da son zumunci duk naki ne habiba, Allah yasa kin huta," juyowa yayi idon shi akaina yace, "Aysha Allah ya ƙara miki haƙuri, tabbas kinyi rashin masoyiya, kinyi rashin twin sister ki", ta shi nayi da gudu na rungume Abba ina kuka, shima Abban kukan yakeyi, da ƙyar aka riƙeni lokacin da naga ana ɗaukan gawanta, yayuna ne da Aliyu da wasu daga dangin mu suka ɗauke ta, nidai farkawa nayi na sake ganina a ɗakin hajiya ummah, wato suna na sakeyi da aka fita da habiba.

Hawaye nima na share, ganin yadda Aysha take kuka kaman a yanzu ne aka mata wannan rashin, jikina duk a sanyaye na miƙa mata ruwa, karɓa tayi tasha sosai, sannan ta dube ni da idonta da suka chanja kala, tsabar rinewa da sukayi saboda kuka, "Aunty nice rasuwar habiba yana daga cikin mutuwa masu ciwo da aka mun a rayuwata, naji ciwon rashin yar'uwata, naji ciwon rashin masoyiyata, har gobe ina kokawa wannan mutuwan", ajiyan zuciya nayi na kalleta, "hajjaju ae mutuwace mai ciwo, rashin ɗan'uwa ae babban rashine, ballantana ke zafin har da raba tsakanin ku da akayi, Allah ya mata rahma", na faɗa, "Ameen ya rabbi, nagode Aunty nice, naji an fara ƙiran sallah, bari mu tashi muyi sallah, sai mu cigaba kafin nan ma zuciyata ta ɗan yi sanyi", miƙewa nayi na mata jagora har bedroom ɗina, tana shiga toilet na shimfiɗa mata sallaya na fice.

Bayan ta idar da sallah ne na kawo mata abinci, fuskan ta ɗauke da murmushi tace, "Aunty nice abincin nan zai samu shiga kuwa"? Nima murmishin nayi nace, "ae ko idan bakici ba bazan ji daɗi ba, gara ko kaɗan ne ki taɓa nasan dai kinci",

Rausayar da kanta tayi sannan ta jawo coolern abincin ta zuba kaɗan, nidai bance mata uffan ba, don halin da take cike Allah ne kawai ya bar wa kanshi sani, fuskanta da murmushi ta dubeni, "tare zamuci ko"? Murmushi nayi na gyara zama mukaci taren, bawai don ina jin yunwa ba, kawai dai ta samu sukunin ci, muna gamawa na tattare komai, wannan lokacin a ɗaki muka zauna, tana duba na da murmushi a fuskanta ta cigaba.

Bayan na tashi zaune na muka haɗa ido da Aunty Rakiya, Zama tayi a gefe na , "sannu Ayshaa, sannu ko", naji tana ta jero mun, ido na sun mun wani nauyi na riƙo hannunta, "Aunty an binne habiba ko"? Na faɗa idona suna zubar da hawaye masu zafin gaske, hawayen ta share itama, bata ce mun uffun ba ta jawoni kawai ta rungume, munyi kuka ba kaɗan ba, har zuwa wani lokaci tukun ta tashi ta haɗa mun ruwa mai zafi tace na shiga nayi wanka, bayan nayi wanka nayi brush, na ɗauro alwala na fito, tea mai zafi ta miƙa mun, kaɗa kai nayi alaman bazan sha ba, harara na tayi ta ɗaure fuskanta tace, "maza karɓa ki shanye ki bani cup ɗin," ganin fuskanta ya saka na karɓa ina hawaye na shanye, ina sha kuwa cikina naji yana wani uban kuka, haka dai na miƙa mata cup ɗin, sannan na wuce na saka kaya, chan ta dawo tace mu fita parlor.

Duk familyn su Abban mu suna zaune a parlor tare da hajiya ummah da taci kuka kaman yayah, sai cewa take, "usmanu na an mishi mutuwa, usmanu yayi rashi", haka dai duk muka gaisa dasu ina ta daurewa, amma kukan da hajiya ummah ta fashe da shine ya sakani sake fashewa da kukan, da ƙyar aka rarrashe mu, sannan na wuce parlon ummie na, achan na samu so zainab, hadiza, hafsy, ummtah da maryam da tun safe tazo, gefe ɗaya kuma Aunty B ne zaune tare da su Aunty j, gaisuwa mukayi sannan na wuce wurin ummie na, akan gadon ta na zauna gefenta, ɗago kai nayi don na gaisheta amma muna haɗa ido kawao sai na kasa, rungumeta nayi ina kuka, kuka mai ciwo da zafi nakeyi, bata hanani ba sai buga baya na da takeyi a hankali, da ƙyar nan ma Goggo maman zainab ta rarrashe ni, ban fita parlon ba sai na naɗe a jikin ummie kawai na kwanta, a hankali ina share hawayen da suka kasa tsayuwa.

Muna idar da sallan magarib muna zaune dukkan mu a parlon ummie, sai ga Yayah Ahmad da M.G sun shigo tare, nidai kallo ɗaya na musu na maida kaina ƙasa na

cigaba da jan chasbi na, ummie aka ƙira suka gaisa, sannan ya matso har inda nake ya ambaci sunana, ban iya na amsa mishi ba sai kukan da naji kawai yazo mun, wanda ban san meyasa ba ko sunana aka ƙira sai dai naji kuka yazo mun, wai habiba dai, habiba tawa ce babu yau a duniya? Wayyo Allah mutuwa, ashe haka ciwon ta yake? Haƙuri sosai ya dinga bani, bayan ya mun gaisuwa, sannan yace mun Goggo tana mun gaisuwa insha Allahu gobe zasu shigo tare da Mummyn A.G, kai kawai na ɗaga mishi alaman amsawa, amma ban ɗago Kaina na dube shi ba, ya daɗe a wurin kafin ya miƙe ya fice.

Washe gari kuwa su mummyn A.G suka zo, macece yar gayun gaske, duk da ta fara nanyanta amma bazaki taɓa cewa ta haifi A.G ba, Abaya ce a jikinta baƙa marar kwalliya, sai glass fari a manne a idonta, daga gani na ƙara ƙarfin kallo ne, gefe ɗaya kuma Goggo ce, farar bafulatana, ita ta zama dattijuwa, duk da girma ya kama goggo amma akwai farin fatan nan da kyaun fuska, daga ganin ta macece da lokacin ƙuruciya tayi jiki da tsayi, masha Allah, yau kam naga inda M.G ya samo kyaun shin nan, don babu ƙarya Matar akwai kyau, ga fara'a,

mummy ko ina ganin idon ta sai da na runtse nawa idon, da sauri na sunkuyar da kaina ƙasa, domin sai naga kaman idon ,A.G na kallah, duk da Mummy baƙace, amma kyakkyawar mace ce, ga ido kaman wanda ta cire nata ta mannawa A.G, hattah lumshewan da yake dashi irin nata ne, sai dai hala farin fatan shi na mahaifin shine, doguwace kuma bata da wani jiki sosai, gefe ɗaya kuma Heedayah ce, itama kyakkyawa ce amma dai bata kama ƙafan A.G ba, duk da dai suna kama da A.G, amma ita bata kai shi fari sosai ba, amma sunyi kama, don hattah idonta irin na Mummy ne, irin na shi, haka kawai naji haushinta a zuciyata, wato akan wannan M.G ya share ni ko waya baya mun, sai naji bana son kallon fuskanta.

Bayan mun gaisa da sune dukkan mu a parlon ummie, sai mummy take miƙo mun wayanta, "Ga A.G ko dougter", a kunya ce na karɓi wayan, "Eesha sannu ko, sorry beauty, sannu da rashin da aka mana, wayan ki akashe tun ranan bana samunki, M.G kuma yace mun yazo kina ta kuka shiyasa ya kasa haɗamu, kiyi haƙuri Eesha, addu'a take buƙata, Allah ya jiƙanta ya raya abunda aka bari,", ina jin muryan shi sai naji rauni na ya ƙaru, hawaye kuma suka soma mun sintiri, ban san lokacin da bakina ya ambaci sunan shi ba, amma murya chan ƙasa wanda nayi imanin ko maryam da ta ke gefe na bata iya jiyo maganana, "A.G na rasa habiba, ta tafi ta barni da amanan babynta, bansan yaya zanyi na bashi kula ba, bansan yayah zanyi da ciwon rashinta ba, kadawo please", na faɗa sautin kuka na yana fita, a hankali naji hannun mummy shi ta rungumo ni jikinta, shi kuma daga wayan naji yana magana, haƙuri yake ta bani kaman zai mun kuka, a haka na miƙawa mummy

wayan ina ƙara fashewa da kuka, rungumeni tayi sosai tana rarrashina, gefe ɗaya kuma su hafsy suna ta share hawayen su.

Ranan uku su Aliyu suka shigo bayan anyi addu'a tare da Yayah Ahmad da su M.G, ashe kullum da su ake zama bansani ba, sai lokacin naji su Aunty B suna faɗa, akan yadda Aliyu yayi laushi sai kuka yakeyi, hattah mummyn su jammy rasuwar ta bugata, gashi ƙannen mamie naji fir sunƙi basu yaron su gani, ganin kada abu yazama abun magana Mummyn ta share bata tanka musu ba, hatta Aliyun sun hanashi har sai da Abba ya musu jan ido tukun aka miƙa mishi ya mishi huɗuba ya mishi addu'a, tunda na ɗaga ido muka haɗa ido da su ban ƙara ɗaga kaina ba, don ko gaishe mu da sukayi idona yana ƙasa, kuma a washe gari M.G ya tafi, don naji Yayah Ahmad yana gayawa Ummie M.G zai koma gobe insha Allahu.

Nidai banje naga babyn ba sai ranan da akayi bakwai, wato ranan da aka raɗa mishi suna, kuma yaro yaci sunan Abba wato *USMAN* nan ma sai bayan magrib na shiga side ɗin mamie, wanda tun ranan da akayi rasuwan ban ƙara marmarin shiga ba, haka na daure muka shiga tare da su Aunty B, domin zasu mata sallama gobe zasu wuce idan Allah ya kaimu, zama nayi a ƙasan carpet da muka shiga parlon mamie, don dukkansu suna zaune a parlon, yaron yana hannun raliya tana bashi madara, kallo ɗaya na mishi na kawar da kaina, nayi-nayi na iya buɗe baki na gaida mamie amma na kasa, har sai da ita don kanta ta miƙo mun hannu, kuka naji yazo mun, wanda itama kukan ta fara, sannan raliya ta miƙo mun babyn tana cewa, "Adda gashi ki mishi addu'a ki zaɓa mishi sunan da za'a ƙira shi da shi," ta faɗa hawaye yana bin fuskanta, "wato Aunty nice idan kikaga mamie da raliya a lokacin zakiyi zaton har abada duk wani gaba yaƙare a tsakanin mu, amma ina kibar zuciyar da babu Allah a cikinta, " hannu na saka na amshi babyn da ya buɗe idon shi tar yana kallo, babu abun da yabari na kamanni da mahaifin shi, hatta baƙin fatan na Aliyu ne, don duk da jariri ne bai yi wani fari ba, ido na zuba ina ƙare mishi kallo, gefe ɗaya wani ƙaunar shi da tausayin shi na cika zuciyata, "SABEER" na ambace shi da shi muryana yana ɗan rawa, kuka mamie ta sake fashewa da shi tana furta, "Allah yasa ƙazamo mai haƙurin irin mahaifiyarka, Allah yasa ka amsa wannan sunan ɗan albarka", miƙewa nayi da shi a hannuna har gaban mamie, ƙasa na durƙusa na furta, "Mamie ki amince na tafi da shi don cika umirnin sisto", bata bani amsa ba sai sunkuyar da kanta da tayi ƙasa tana share hawaye, yayarta ce ta bani amsa da, "Aysha kiyi haƙuri ya ɗan ƙara tasawa, sai ki karɓe shi, yanzu idan ya tashi kuka da dare yayah zakiyi?" ido na ƙura mata bance komai ba, amma abun mamaki sai naji muryan mamie tace, "ta tafi da shi tunda ae ba nono za'a bashi ba, kuma nayi imamo da Allah ummie zata taimaka mata", tana rufe baki mahaifiyarta ta amsa da

"a'a bazaiyiwu ace yarinya ƙarama ta riƙe ba, kawai ta dinga zuwa da safe tana amsan shi, amma bamda a tattara shi a miƙa mata, ke mai zaki gani zuciyarki tayi sanyi bayan shi"? Ta faɗa tana kawar da kanta gefe, babu musu na miƙa shi hannun sister mamie muka musi sallama muka fice a parlon.

Kullum safe kuwa sai na shiga side ɗin mamie na ɗauko ɗana, gashi mai haƙuri baida rikici, wuni mukeyi tare da shi, har su raliya suka koma kaduna, idan zanje makaranta ne kawai na kan bar shi hannun mamie, wataran ma mamah ce ko ummie suke riƙe shi, ita dai mamie har zuwa lokacin a sanyaye take.

Habiba tayi arba'in aka raba gadon abun da ta bari, sannan a ranan Aliyu da iyayen shi suka sake zuwa gidan mu gaishe da su Abba, a wannan ranan kam an bar su sun ɗauki sabeer, don har video call sukayi da jammy, duk da munsha video call tana ganin shi, Aunty nice zaki sha mamaki idan nace miki sanadin yaron nan har video call munayi da A.G? Murmushi nayi ina kallonta cike da mamaki, itama murmushin tayi ta cigaba da bani labari.

Ranan farko da muka fara, na dawo daga sch yana ta kuka, an rasa me ya same shi, sai na ɗauke shi inata jijjiga shi, lokacin wayan A.G ya shigo, a rikice na ɗauka, jin kukan da sabeer yakeyi yasa yace bari ya ƙirani video call ya rarrashe shi, hummm abun mamaki indai akan ɗa nane zan iya komai, ae babu shiri na ɗauki wayan da ya sake ƙirana video call, duk nayi sukuku doni, matso mishi da fuskam sabeer nayi, shi kuma yanata rarrashi, ranan naga ikon Allah kawai sai yaro yayi shiru yanata sauƙe ajiyan zuciya, murmushi A.G yayi yace, "yarona yana missing ɗinane, ko kuma Ammin shi bata iya bashi kulawa ba, yafi son na Abbin shi", tura baki nayi cike da shagwaɓa, sanan ya umurce ni na saka mishi yatsa a baki , ina saka mishi kuwa ya riƙe yana tsotsa idon shi a kaina, a haka har yayi bacci, ajiyan zuciya na sauƙe na maida kallona kan A.G, ido ya kashe mun yana murmushi, "yakamata na dawo na baku kulawa sosai ke da ɗanmu, don naga wannan rikicin uwa da ɗan duk A.G ne zai iya shanyewa," Murmushi na mishi lokacin, sannan nace, "saura kwana nawa kadawo"? Idon shi cikin nawa yace, "saura 2weeks oum sabeer", daɗi nake ji idan ya ƙirani da wannan sunan, amma sai na wani harare shi, dariya ya ɗanyi.

Lokacin da su Aliyu suka zo da mummyn shi takeyiwa Ummie maganan ya kamata su turo manya akan maganan Aliyu, ita dai Ummie bata ce komai ba sai murmushi da tayi, bata kuma gayawa kowa yadda akayi ba har bayan sati biyu da maganan, ana saura 2dys A.G ya dawo, iyayen Aliyu suka zo wurin Abba da maganan Aliyu ya

dawo da maganana, a haka ma basu san da wasiyan Habiba, kawai da so da ƙauna da Aliyu yake mun da iyayen shi ne, anyi dace kuma ranan da sukazo Yayah Muhammad yana nan, don yazo weƙend.

Bayan Abba ya gama sauraron su sai yayi murmushi ya gyara zama, "ALHAMDULILLAHI Naji daɗin wannan batu na ku, don duk inda akace yʻar'uwa ta rasu tou daɗin zama ya kansa a sake neman auren yʻar'uwarta, duk da ansamu saɓani a tsakanin su har ta kai ga batun saki, tou naji daɗin zuwan ku, don alama ya nuna Habiba ɗiyata bata zalunci ɗanku Aliyu ba a zaman takewar su, don nayi imani da Allah da ace ta zalunce shi ko ta cutar da ku, babu wanda zanga ƙafan shi a ƙofar gidana don neman auren ɗaya daga cikin yʻayʻana," gyʻaɗa kai kawai iyayen Aliyu sukeyi, Abba ya cigaba bayan yabi kowan su da kallo, "Habiba, Ayshaa duk abu ɗaya ne yayi su sannan yʻayʻa nane mafi soyuwa a zuciyana, sanadin halayen su Allah ya saka mun ƙaunar su a zuciyata, yara ne dattawa, masu haƙuri, yarah ne masu albarka, Allah ya jiƙan habiba", Abba ya faɗa da wani yanayi a fuskan shi na jimami,

"Kunzo da maganar neman auren yʻar'iwarta, wanda da ko ba ayi zaman lafiya ba Albarkacin wannan jariri zan iya amincewa da buƙatanku, tou amma gaskiya banji daɗin riƙon da Aliyu da ku iyayen shi kukayi wa habiba, tabbas banji daɗi ba, amma komai ya wuce zamuyi zumunci a tsakanin mu ko dan albarkacin wannan jariri, amma maganan aure da Ayshaa abune ba mai yiwuba, don a yanzu akwai maganan aurenta da wani yarona, har an saka rana, kunga kuwa duk dattijon arziki baya magana biyu", Abba yana kaiwa nan ya miƙa musu hannu suka sake gaisawa, sannan yace su gayawa Aliyu duk lokacin da yaji yazo ko shi ko iyayen shi da yʻan'uwanshi ganin yaro ƙofa a buɗe take, amma maganan bashi ɗa kuma kada ya saka a ranshi, don ya wufantar mun da yʻa da abinda ke cikinta, bai san lafiyan su da komai da suke ciki ba har sai da Allah yayi ikon shi tukun na gan shi gidan nan, bawai na riƙe shi bane a zuciyata, a'a kawai zanyi abun da nake ga shine dai-dai, nagode da zuwanku neman sake haɗa iri dani a karo na biyu".

A kunyace ɗaya daga cikin ƙanin baban su Aliyu ya ɗan risina yana yiwa Abba godiya, sannan dukkansu suka sake bawa Abba haƙurin abunda ya faru, don gaskiya ne sun san basu kyauta ba, lokacin da Aliyu yayi saki babu wanda ya biyo bayan habiba, haka dai suka fita duk jiki a sanyaye,

Gida suka wuce wurin mummy, bayani dalla -dallah suka mata, gaba ɗaya ran mummy ya ɓaci, a fusace tace, "tou ae dama tun farko Aliyu baice yana son habiba ba, kuma bamuce habiba tana da aibu ba, kawai naƙita saboda halin mahaifiyar ta ne, don Aliyu ba'a hayyacin shi ya furta ya amince da auren ta ba, kuma lokacin da ya dawo hayyacin shi ya nuna baya sonta, amma ae dana san habiba tana raya baza'a taɓa barin ya auri ayshaa ba ae ban nuna komai ba, amma

da habiba ta rasu sai naga akwai dama da Aliyu zai maye gurbin habiba da yʼar'uwarta, wanda dama tun farko itace zaɓin mu da shi baki ɗaya", cikin ɓacin rai ta ƙarasa maganan, su dai haƙuri suka bata suka tashi suka fice, cike da ɓacen rai ta ƙira Aliyu ta zayyane mish komai, dama yayi tafiya baya gari, "mummy wani maganan aure aka tsayarwa Ayshaa da shi? Kawai munafurcin uwar habiba ne ta hana komai, ki ƙira ita ummie kiji komai daga gareta", sallama sukayi mummy ta ƙira ummie a lokacin, nan dai ummie tayi namijin ƙoƙarin sanarwa mummy akwai maganan aure akaina, wanda zan aura ma cikin satin nan zai gama ya dawo, "duk da haka dai ummin su a duba al'amarin Aliyu, yana son Ayshaa sosai fah, kuma ashirye yake daya haƙura da wancan maganan auren idan Ayshaa zata amince,"

Murmushi ummie tayi tace, "gaskiya koda zai auri ayshaa bazan so a fasa maganan auren shi da yarinyar da ta ke matsayin yʼa a wurinki ba, ga magana kuma yayi nisa, kawai dai mu ƙara addu'a, Allah ya zaɓa abunda yafi alkhairi a tsakani", badon mummy taso ba tayi sallama da ummie akan idan Aliyu ya dawo zaizo ya samu ayshaa suyi magana a tsakanin su.

Zuwa dare Abba ya ƙiramu nida ummie zuwa parlon hajiya ummah, achan muka same su harda yayah muhammad, nan Abba ya gaya mana yadda sukayi da iyayen Aliyu, kuma ya sake jaddada bai hana Aliyu yazo ya ga ɗanshi ba, amma su yayah muhammad su zama shaidah har abada bazai bashi riƙon yaron habiba ba, dom sakamakon izayan da suka yiwa habiba kenan, nan hajiya ummah ta tafka salati hannu riƙe da bakinta tace, "amma dai Aliyu da iyayen shi anyi sokayen banza, yoo sokaye mana, ku wahar da habiban don babu kunya a idonku kuzo kuma neman auren yʼar'uwarta? Da shegen baƙar fuska kaman na boss ɗin indian film ya kwaso ƙafa yana zabgegen bazawari yace Ayshaa budurwa wanda zata auri saurayi yake so? Tou haram wannan shirmen ba'a gidan Usmanu na ba, don ko Gwamnah ne mahaifin shi bai isa yaja da kai ba usmanu, nera yafi ka ko suna a gari"? Dariya ne ya kubcewa yayah muhammad yace, "ballantana ma besty kam bata son wani Ali black, A.G ɗinta kawai tace sai shi, bawai don farin fuska bako besty"? Ya faɗa yana duba na da murmushi a fuskan shi, sunkuyar da fuskana nayi ina duban fuskan Sabeer da yake rungume akan cinyata yana bacci, ido na ƙura mishi ina jin wani irin son shi alokacin kaman zai fasa mun ƙirji na, ummie ce cikin murmushi take zayyana musu yadda sukayi da mummyn Aliyu, nan ma hajiya sake rabka salati tayi tace, "amma kuwa sun tabbata manyan sokaye, daga uwar har ɗan", ta maida kallonta kan Abba tace, "ae wannan satin ne dawowan Aminun ko?" Abba ya ɗaga mata alaman haka ne, "tou kayi aniya sati na sama a sambaɗa auren nan", tayi ƙasa da murya har tana sunkuyowa kaɗan tace, "gama zafin uwar shinnan da yadda tafi ƙarfin Hauwa da zuriyarta da suka shahara a yawon bin malamai, tou itama bazata gaza bin bokaye ba, tou bokaye mana, don itama ae Hauwan su tabi ta jawo hankalin Aliyun ya bar Ayshaa ya dawo kan nata yʼar, amma da yake na uwar Aliyun sun fi shahara ae kaga abun baiyi lestin ba, tunin yayi espiya", ta faɗa tana watsa hannu.

Ɗago kai Abba yayi da sauri ya maida kallon shi kan ummie, "dama bada amincewar ayshaa ya fara neman habiba ba ne"?

Ita dai ummie bata ce komai ba, sai kallo na da ta ɗanyi ta kawar da kanta gefe, "dama baka da labari ne? Lallai khadijah kin cika cikakkiyar bafulatana, kawaicinki yakai duk inda ba'a zato, tou Ayshaa ya fara gani a bikin yʻar'uwarshi Ƙawarsu, ya kware yana sonta, ita kuma marigayiya ban san ya akayi ba, don bana ce taci amanar yʻar'uwarta ba tunda ƙasa ya rufe idanunta, kuma da kunya ga idon ɗanta na faɗi wani mummuna akanta, tou haka dai muka samu zance ya juye ya koma kan habiba, amma dai ba wai da yardar Ayshaa ba yadda suka tsara maka, juya kanshi akayi ya bar kan Ayshaa, daga wannan rana kuma uwar habiba ta raba tsakanin ayshaa da habiba, Allah dai masani amma shu'umancin uwarta na shige da fice wurin bokayen da baka son afaɗa ne ya tabbatah, shi kuma Aliyu bayan aure Allah ya kuɓutar da shi uwarshi ta tashi tsaye ta lalata ɗan ƙaramin shirkan Hauwa, don daga ganin idon uwar Aliyu gwaska ce, tou komai dai ya karye Aliyu ya dawo hayyacin shi yace baiji ba bai gani ba baya son habiba, don ba ita yace yana so ba, ita kuma marar kunyar ƙanwar tatah Raliya ta tsayar mishi rashin kunya ya labga musu uban na jaki, kaga asalin ƙiyayyan shi da ita marigayiya kenan, sharrin rashin da ce da uwa ta gari".

Abba ido ya zuba mun kaman bazai sake furta komai ba, chan kuma sai yace, "Aysha ki yafewa yʻar'uwarki, nayi imani ko da laifin habiba tou babbar mai laifin uwartace, don Allah ina roƙon arzikin ki kiyafe mata, taci darajana"!

Hawaye na saka hannu na share, "Abba ni ban taɓa rike habiba da zuciya ba ɗaya ba, kuma ni tun farko ban so Aliyu ba, shiyasa ma ni banja ba, amma ni ban riketa da komai ba tun farko, Allah ya jiƙanta da rahma", na ƙarasa ina share hawayen da bansan ranan daina shi ba.

Addu'a sosi Abba ya mana na alkhari gaba ɗaya yʻayʻan shi , sannan ya umurce ni da na je na cigaba da kula da yaro na, tashi nayi ima rungume da Sabeer na fice, ina ganin hajiya ummah da ummie suna ta share hawayen su.

Ranan friday da 6:00am jirgin su A.G ya sauƙesu a garin lagos, 9:00am kuma suka tashi zuwa Abujah, amma A.G bai shiga bauchi ba sai ranan saturday da yamma, don basu samu flight me zuwa bauchi ba, dole suka bugu mota sai bauchi, ya iso ya samu gidan a cike, ga Hudah ga Heedayah da suke ta girke-girke don isowan big

broh, twins ɗin ta suna ta shawagi a tsakani, hatta Daddah ranan a gidan ta wuni tare da goggo, suna dakon isowan A.G, suna isowa kuwa su hudah sukaje suka rungume shi suna murnan dawowan shi, ranan dai ya ɗan sake musu har yana zolayan heedayah washi take girkin nan ko dai wa M.G ne? Rufe ido tayi takasa bashi amsa sai dariya da takeyi, haka dai suka kasance cikin farinciki, mummy kaman ta goya ɗanta, gashi wannan dawowan yayi kyai sosai yayi fari ya ƙara jiki, don har M.G na tsokanan shi ya samu kan Ayshaa ne yasaka ya nutsu bakaman farkon tafiyan shi ba, shidai murmushi kawai yakeyi baice komai ba, anyi sallan ishaa duk suka koma parlor suka zauna, bayan M.G ya mayar da su Goggo da Daddah, ido ya zubawa M.G dayaga ya wani share shi yaƙi kallon shi, ganin bazai kalle shiba ya sa ya aiki heedayah ta bar Parlon, harara M.G ya jefe shi da shi yana gyaɗa kai, alaman zamu haɗu, share shi A.G yayi, sai ya tura mishi text, "wai me kake nufi ne da bazaka rakani wurin beauty ba"?

Dariya M.G yayi yaƙi maida mishi reply, chan sai A.G ya dubi mummy yace, "mummy key ɗin motan ki please"? Ido ta zaro waje tace, "haba son yau ɗaya kam doug ta mana haƙurinka mana, muna marmarin ganinka ae", kunya ne yaji ya rufe shi, tun bama da M.G ya kwashe da dariya ba, "mummy ba wurinta zanje ba fah, phermacy nake son zuwa na duba wani magani", ya faɗa yana zaro ido, M.G yayi wuf yace, "Indo pharmacy ba", dariya dukkan su Parlon suka saka, Shima dariya ƙaryan da yayi ya bashi, haka dai ya daure ya zauna da su har zuwa 9:30pm, a maraice ya dubi mummy yace, "zanje na huta mummy", murmishi tayi tace, "hakan na da kyau son, jeka huta akwai gajjiyan karatu ae", bai jira shaƙiyancin da M.G yake mishi ba ya wuce side ɗinsu, da sauri ya rarumo wayan shi ya zabga wa Beautyn shi ƙira.

Tun ɗazu da Aliyu ya ƙira wayana, wai yaji lafiyan sabeer nakejin zuciyata babu daɗi, ni ban san ma na tsane shi ba sai yanzu, da baya burgeni ne kawai, yanzu kuma daya wahalar da habiba sai naji haushin shi nakeji, gashi yau ana magrib mamie ta aiko mai mata aikin side ɗinta ta karɓi Sabeer, sai naji haushin sun mun yawa, don na lura kwana biyu idan naje ɗaukan shi ta ringa mun wasu kwane - kwane, ko tace ya tashi da mura ko tace yana bacci, ni dai naƙi yin zuciya saboda ina ji a raina ɗana ne habiba ta haifa mun, anzo an ɗauke shi babu daɗewa Aliyu kuma ya ƙirani, gaya mishi nayi ya ƙira mamie Sabeer yana chan, haka dai ya ɗan taɓa kame -kamen shi ya barni, don ina jin shi har da cewa tsaraban me nake so idan zai dawo, darajan jammy yaci da na kashe wayana a lokacin, amma na daure mukayi sallama.

Ɗaukan ƙiran A.G nayi duk babu wani walwala a tare da ni, jin muryana wani iri sai yayi ƙasa da muryan shi yana tambayana, "waya taɓa beauty ne"?

Turo baki nayi kaman yana gani na nace, "mijin habiba ne ya ɓata mun rai", "lallai ya maida hankalin shi, don darajan habiba ne da yaron mu zai saka na ɗaga mishi ƙafa, sbd haka kada ya sake", dariya maganan shin ya bani, haka dai baya son yawan maganan amma yaja ni da hira, har 11:00 muka kai muna hira, yawanci ma nike bashi labarin, rayuwar mu na ƙuruciya da habiba yawanci nake bashi, wani yayi dariya wani ya tayani alhinin mutuwan Ayshaa, da ƙyar dai yayi sallama dani, don sai da yaji na fara jera hammah tukun ya barni.

Washe gari kuwa ana idar da sallan ishaa suka zo tare da M.G, bayan sun gaida ummie parlon hajiya ummah suka wuce, nima achan naje na same su, gaba ɗaya sai na samu kaina da jin kunyan A.G, gashi tun da na shigo idon shi suke zube akaina, ko kunyan M.G da keta zolayan shi baya ji, nidai sai sunne kai nakeyi kamar wata munafuka, abun mamaki M.G kaman bai taɓa sona ba haka yayi ta acting, irin dai kawai ni wanda amininshi ɗan'uwan shi zai aura ne, nima ganin yadda yayi kawai sai fuske, muna zaune kuwa sai ga wayan Aliyu ya shigo, ido na zubawa wayan har ta gama ringing ina kallo ban ɗaga ba, a karo ta biyu da ta sake shigowa sai A.G ya ƙura mun ido, ganin haka sai M.G yace, "ki ɗauki wayan mana, ko ba important call bane"? Ɗaga kai nayi alaman hakan ne, shidai A.G ido kawai ya ƙura mun, jin kusan 5mnt ba a sake ƙira ba sai hankali na ya kwanta, amma da yake Aliyu jarababbe ne sai ya sake ƙira, haɗa ido mukayi da A.G, bai buɗe baki ba yayi mun alaman na ɗaga wayan, ganin fuskanshi ya ɗan chanja sai na ɗaga wayan, sallama mukayi daga nan muka gaisa, tambaya na yayi Sabeer, gaba ɗaya naji haushi yakamani, har ban san lokacin da nace, "bayan magrib nae maida shi wurin mamie, ka dinga ƙiranta kana jin yayah yake mana", murmushi yayi yace, "haba ayshaa ae tunda ba nono yake sha ba kidinga barinshi a wurinki mana, ae inaga kwana ma zai iya a wurinki, ni ina so ya buɗi ido baisan kowa ba a matsayin uwa sai ke",..... ban jira ya ƙarasa shirmen shi ba nace, "sai da safe ina tare da baƙi", kashe wayan nayi na ajiye, ina ajiyewa muka haɗa ido da A.G, ƙura mun ido yayi kawai, duk sai naji babu daɗi, a ɗan ruɗe nace, "mijin habiba ne, yana so yaji yayah sabeer yake"? "ok shirmemen mutumin da Barrister ya bani labari wai don shirme ya turo mamyan shi wai a bashi ke madadin habiba ko? Tou ya manta irin uƙuban da ya bawa habiba ne? Baida hankali ae".

Da sauri A.G ya maida kallon shi kan M.G, har muryan shi na ɗan shaƙewa yace, "yaushe haka ya faru"? Tsaki M.G yayi yace, "ae inaga maganan nan bai wuce 2weeks ba, yafa saki habiba kafin ta haihu, amma don rashin hankali wai a bashi Aysha, sai da Abba ya fito musu a mutum tukun suka haƙura", M.G yace.

Idon shi ya dawo dashi kaina, batare da ya kalli M.G ba yace, "bai haƙura ba",

Kallon shi M.G yayi sannan yace, "kaman yayah? Kaji sun sake dawowa ne"?

Fuskan shi a matuƙar murtuke yace, "dama ae wancan ɗinma daga kai har ita babu wanda ya sanar dani, ballanyana har naji a wani wurin, salo ya chanja, meyasa zai ƙira wayanta? Yaron ya isa magana ne"? Ajiyan zuciya na sauƙe na maida kallona kanshi, harara ya aiko mun da shi, hakan ya saka na buɗe bakina da sauri nace, "tou ae Abba ya dakatar dasu",

"duk da haka kin gaya mun"? Naji A.G yana faɗa, ganin haka yasa M.G ya miƙe tsaye yace, "bari na ɗan miƙe ƙafana kafin ka fito", shima A.G miƙewa yayi tsaye yace, "muje kawai, nima zan leƙa gidan Daddah", murmishi M.G yayi mun sannan yayi sallama ya fita, nidai ban tashi ba kuma kaina yana sunkuye, ɗaure fuskana nayi naƙi kallon inda yake, ganin haka yasaka ya kasa fita, dukka hannayen shi ya zuba cikin aljihun wandon shi, ido ya ƙura mun har na zuwa wani Lokaci, ko ya fahimci raina a ɓace ne yasaka ya ƙaraso gaba na ya tsaya, shiru naji yayi hakan ya saka na ɗan ɗago kaina na dube shi, ganin kallona yake yasa na murguɗa bakina na maida kaina ƙasa.

Tsugunawa yayi dai-dai saitin fuskana, sannan naji yace, "tou meye ne kuma Eeshaa"? Murguɗa baki na sakeyi na ƙara hararan shi, kawar da kaina gefe kaɗan nayi, wani ƙamshine mai nutsuwa yake tashi daga jikin shi, hakan ya saka naji na sake kallon shi, kallo shi kuma na sakeyi, ya wani marairece fuska kaman zaiyi ihu, "tou ni meyasa zan gaya maka maganan da baida wani muhimmaci a gare mu, kana Exams fah lokacin", na faɗa ina maida ido na cikin nashi, idon nan a lumshe an zuba mun su kaman zai lashe ni, "bana son ƙiran da yakeyi Eeshaa, please ki daina ɗauka, idan yana so yazo gidan yaga ɗanshi, shima bake zaki kai ba, yaje wurin kakar yaron please".

Ɗaga mishi kai nayi alaman naji, "tou ki sake fuskan ki bar fushin", ya faɗa still yana tsugune a gabana, kallon shi nayi nace, "tou meyasa zaka tafi yanzu"? Tashi yayi ya zauna a kujeran da yake gefe na yace, "an ma fasa tafiyan nan, dama M.G nake yiwa wayo ya fita".

Dariya ne ya kubce mun babu shiri, "ka dai chanja ne, ae ɗazu fushi kayi", shima dariyan yake yace, "ae danaga naki fushin yafi nawa tunin na daina, shi kuma M.G abun ya hanani tafiya wai sai yayi gaba irin na biyo shin nan, tou anƙi wayon, so yake mu kuma yaje yaga wannan mummunar budurwar wanshi, ni kuma yasaka nayita kallon bango".

Dariya sosai A.G ya sakani, wato idan ya samu wuri shima bakin shi buɗewa yakeyi ko? Wato har zolaya ya iya?

Ido ya zuba mun yana murmushi, gaba ɗaya yayi kyau sosai, har wani rausayar da kanshi gefe kaɗan yayi yana kallo na, a hankali na dakata da dariyan na kalle shi, "waya gaya maka Heedayah mummuna ce? ae da kai take kama fah, kuma ta fika ma kyau don ita mace ce", na faɗa ina kallon shi da murmushi a fuskana, kwaikwayon yadda nake tura baki yayi, "waya gaya miki mace tafi namiji kyau? Kema ae baki fini kyau ba ballantana heedayah, ku daina saka kwalli, da shafa powder da jan baki kuga idan ba ace munana bane ku, ke kinyi sa'a fah", ya faɗa yana shafa fuskan shi.

Hararan shi nayi cikin wasa nace, "yanzu kai kana ganin kafini kyau ne"? Ɗaga kai yayi yana kallon cikin idona, jijjiga kai nayi na kawar da ido na.

"kijira muyi aure, wanzami zan saka ya miki aski tal kwabo, ranan zaki banbance nida ke wayafi kyau, nima zanyi askin".

Ya faɗa yana kashe mun idon shi.

Aeko bansan wani irin dariya bane yazo mun, amma na saka hannu na rufe bakina, dariyan yayi yace "kin yadda nafiki kyau?"

Kai na girgiza alaman a'a, "tou sai mun haihu, me kama dani da me kama da ke, zakiji ance kai mai kama da Aminun yafi kyau" ya faɗa yana ɗaga mun dukkan giran shi.

Tura baki nayi dukka gaba nace, "ni duk masu kama dani zan haifa".

"Haba? Dayawa zaki haifa mun"? Ya faɗa yana sunkuyo da kanshi dab da fuskana, rufe fuskana nayi ban ce uffan ba, chan da na gajji da zolayan shi sai nace, "suɓutan baki ne fah", dariya ya fara yana miƙewa tsaye yace, "aeko ni A.G na dinga saka ki suɓutan baki, da ido a sai kin mun suɓutan zance, yʼan mata tashi kimun rakiya kada M.G ya zaune miki ni yau,"

A mota muka samu M.G ya kwantar da sit yana ta waya, harara yabi A.G da shi, shi kuma A.G ya wani ɗaure fuska kaman bashi bane yanzu yake ta ɓarin zance, ni dai murmushi kawai nakeyi ina kallon su, har sai da suka shige tukun A.G ya kallo ni, "gobe insha Allahu da yammah zan shigo, zanzo naga yarona ko"?

"gara da kache kai, don gobe saloon zan kai Giwata, ba zanyi wani rakiya ba azo ana fito da ni waje da wayo", murmushi nayi nace, "tou yayah M.G a gaida giwar", sannan na juya da sauri nayi cikin gida.

Ina shiga na wuce direct ɗakin Ummie, anan na sameta ita kaɗai, tambayanta nayi hafsy, "tana ɗakin ku tana jaraban wayan kun nan", nidai murmushi nayi na zauna a gefen gado kusa da ita, zayyene mata yadda Aliyu yake damuna da ƙira nayi, da kuma yadda yau mukayi har ran A.G yaso ɓaci, ido ta ƙura mun tayi tagumi tana saurara na, har sai da nagama tukun ta sauƙe ajiyar zuciya, "kada ki ƙara ɗauka, insha Allahu da safe zamuyi magana da yayinki, abunda muka tsayar kuma zamu gayawa Abban ku, amma in banda neman fitina an ce musu da maganan aure akan ki, shi kuma zai dinga damunki da ƙira? Gaskiyan Aminun ne ae, yazo har gidan yaga ɗan na shi mana, ae Abban ku bai hana su ba, ko kuma ya ƙira mamin ta ku yaji yayah yake mana? Shirmen banza dama ya damu da abunda ke cikin ne ya wofintar da uwar yaron"?

Muna maganan sai ga hafsy ta fito, zama tayi tana ta zabga masifah nidai ido na ƙura mata nayi tagumi ina kallon bakin masifan nan, sai da tayi iya yinta sannan ta dube ni tana wani murmushin shaƙiyanci, "Adda nace yayah A.G bai kawo mana wani tsaraba bane? Ina sauri ae naje muyi gaisuwa na musamman sai aka ƙirani a waya, dama turare nake sha'awa wallahi, idan bai sayo ba kuma sai ya ɗan zaga damu gari su ganmu muma mu gansu, don naga wata sabuwar mota sukazo da ita, nace harka taci uban tada kenan"?

Hararanta ummie tayi tace, "wallahi naga kinje kin tambayi wani tsaraba kiga yadda zanyi gutsi-gutsi da naman bakinki, ke ni hafsy meyasa kunya ya miki ƙaranci ne kam"?

Tana Dariyan ummie tace, "haba mumsy bawai kai tsaye za'a fito ba ae, kwane - kwane akeyi ae, bayan gaisuwa sai a sauƙe dabaru, kin san kuɗin nan fah kaman na banza suke da shi, ba wai daɗin shima suka sani ba", ta faɗa tana dariya.

Dariyan nayi nace "kin ɗauka ranan bai fahimce manufanku bane keda ummie ko? Tou bayan kun fita dariyan ku yayi tayi, har ya ƙara mun haske akan halin ku".

 Baki hafsy tariƙe tana dariya, "kin fasan barristocin nan Allah ya musu ɗam banzan wayo, bakiga yayah Ahmad bane, duk shirun shi wayon tsiya yake da shi kina shirin cutar shi yake ganoki, kuma sai yabi diddigi kafin ya baki abu, shiko yayah

muhammad bawan Allah yayanmu madadin ubanmu, kana faɗa zakaji tararar a account ɗinka, baya ma bin ta kanka wallahi, tou inaga da M.G ne buris zaiyi damu yayi ta labta mana abun duniya, shi ko A.G nan daga ganin idon shi wayone da shi, idan bakiyi da gaske bama Adda sai yaci naki", ta faɗa tana wani ya mutsa fuska, ita dai ummie kallon bakin ta kawai take tana mamakin halin hafsy, nima dariyan ta nakeyi, "aiko zan gayawa Yayah Ahmad abunda kiƙa faɗa, tou na hannun damanki fah"? Na faɗa ina dariya, don nasan sharrin da zata zabgawa yayah umar.

Aiko baki ta riƙe da hannunta, "dila kike ji, ae ba banza ba hajiya umma take ce mishi diƙa sarkin wayo, ae yayah umar sai da yaci naka, don ni har yanzu yana ƙwaƙile mun account ɗina, kullum alƙawari yake mun idan yayi kuɗi ni zan fi kowa morewa a gidan nan, a wayon shi wai ko ummie bazata ci kuɗin shi ba irina".

Aiko daga ni har ummi dariya muka kwashe da shi, ummie tace, "amma duk da kinsan wayo yake miki ae ko kullum ƙusƙus ɗinku tare ne,"

Dariya hafsy tayi tace, "tou ummie yayah na iya da saurayin kakata ummah? ni bana so mu rabu ne saboda duk gidan nan nafi jin taisayin shi, saboda baiyi dace da mace ba, don wallahi ummitah ɗan banzan wayone da ita ga son abun duniya, kedai kawai ummie godiyarki ga Allah da kika haifi su yayah Ahmad masu tausayinki, sai kuma da Allah ya baki ni, don ido na akan ummitah yake, tana samfe yayah umar zan samfe yayah ishaq, kema ki dongwali arzikin yayya, tou ina zan saka ido ana zuƙe miki ɗa acan side ɗin nima nakasa zuƙe na wasu ɗan", ta faɗa tana wani tura baki gaba.

Dariya kaman zan faɗo a kan gado, ummie na kallon drammer hafsy tace, "nidai tashi kije kiyi alwala kizo kiyi shirin bacci, ae Allah yaga halin ku ɗaya ne ya haɗaku ƙawance, mazajen ma ya baku daidai da ku, halinku ɗaya da umaru a wayo, shiyasa kuke son junaku, kinga Ayshaa ae da yake halinsu ɗaya su uku sai naso yazo ɗaya, shiyasa ma mijinta bai da fitina irin halinta Allah ya bata".

"yanzu ummie kina nufin yayah ishaq baida halin ƙwarai kenan"? Hafsy ta faɗa tana wani zaro ido waje.

"nikan ki rufa mun asiri hafsy, bance kije ki gayawa ishaq nace wani abuba, ae ishaq inda hali ake bi ae bazaku haɗuba, shima masha Allah, kedai tashi ayi shirin kwanciya", haka mukayi sallama cike da farin cike a zuciyar kowa, har bakin ƙofan parlor ummie ta rakani, tana tsaye har na ƙarasa ƙofan parlon hajiya ummah, hannu na ɗagawa ummie itama ta ɗaga mun, ina shiga na samu hajiya ummah zaune a parlor, harara take bina da shi, dariya nayi nace, "ke kuma matar umaru hararan na meye"?

Tsaki tayi tace, "kin tattare kinje wurin mahaifiyarku, babu kunya ta zauna tana ta hira da ƴayƴan cikinta, ae da kuka gama hiran da A.G ɗin sai kizo muyi shawar -wari, amma bawai kawai ki wuce wurin uwarkiba, itaga ga mai ƴayƴa ta wani riƙe ki a chan",

Dariya nayi nace, "ke idan Abba ko Aunty Rakiya sukazo kada ki kula su, ki dinga sharesu su zauna su gajji su tafi, ni kuma muna tare ne da hafsy bawai ummie ba", na faɗa ina ɗaukan ruwa nasha.

"Wato ƴayƴan nawa kike so nabarwa duniya su? Tou baki isa ba, kinci uwar ƙarya kuwa, ita kuma hafsy take kowa? Munafuka baka ganin ƙafan ta anan sai isiyaku yazo tukun zata ishe ni da iyayi, ta dinga jele kenam kaman wutsiya", tana faɗa kuwa na kwashe da dariya.

Waya nane ya fara ringing, ganin A.G ne ya saka na tashi nayi hanyar ɗaki ban kula ta kanta ba.

Kwanciya nayi saman gado tukun na ɗauki wayan, shiru dukkan mu mukayi babu wanda yace uffan, har kusan mintuna biyar, "hmmm yarinyar nan wato sai na sauƙe abunda yake mun yawo a kaina na tanka tukun ki amsa mun ko"? A.G ya faɗa bayan shirun da mukayi na wasu lokaci, murmushi nayi nace, "tou ae kai ke nema, kaga bansan me zaka ce ba kada na maka shishshigi", "kedai kika sani, yayah meye labari"? Duk yadda naso shareshi bai yadda ba, haka yayita jana da hira har zuwa wani lokaci tukun mukayi sallama, ya kuma sake jaddada mun kada na ɗauki wayan Aliyu, nidai da tou kawai na bishi, sallama mukayi nidai nayi shirin bacci.

Yadda yayi alƙawari kuwa da yamman yazo, parlon hajiya ummah na kaishi, bayan sun gaisa ta shige ciki ta bar mu nida shi, gaishe shi nayi sannan na tashi na fice domin ɗauko Sabeer.

Tunda na shigo rungume da Sabeer ya ƙura mana ido, da ƙyar naja ƙafa na zuwa gaban shi, hannu biyu ya saka ya karɓi Sabeer, shiru yayi mai ɗan tsawo yana kallon fuskan sabeer, kaman wanda yake ƙididdige abubuwan fuskan shi ya daɗe a haka, sai chan ya ɗago ya kalle ni, "masha Allah, Allah ya rayashi da imani, Allah ya jiƙan mahaifiyar shi yasa tayi shahadah",

"Ameen ya rabbi", na faɗa ina duban shi yadda ya riƙe babyn.

Ɗago kai yayi ya kalle ni yamun murmushi, "girls nake so ki haifa mun masu kama da ke, two, or three, idan kina son boy tou mai kama dani amma ya tafi ana uku" dariya nayi mai ɗan sauti kaɗan, ina kallon shi yadda ya wani ci serious, "tou idan kuma duka boys ne fah"? Na faɗa ina mishi dariyan zaro idon da yayi waje, gaba ɗaya girman su sua bayyana, "a gidan M.G insha Allahu za'a haifa mishi boys, nikan girls nake so, boy ɗayan ma nafasa, sabeer ya wadatar, idan kin matsa kuma sai M.G ya bamu ɗaya a nasu muƙara",

Fuska a ɗaure ya faɗa, daga gani kuma iya gaskiyan shi ne, murmushi nayi na girgiza kaina, "idan ya baka boy ɗaya zaka bashi naka girl ɗaya ne"?

Harara na yayi "haba Eesha, yara ukun ne zamu bawa wani? Tsaya kiji iya maganan gaskiya, ni ko hutu yʻata baxata je ko ina ba ballantana nayi kyautan su".

Kallon shi nayi cike da mamakin son kanshi, "amma kai kuma zaka ɗauki ɗan wasu? Tou idan ummie ko mummy sukace a basu ɗaɗɗaya fah"? "wayyo beauty ki rufa mun asiri kada ki haɗa abunda bazai yiwuba, yara biyu ko ukune kike zancen mu bayar da su? ko hutu baza suje musu ba ballantana kyauta, ni zan kula da yʻayʻana idan bazaki iya ba", dariya maganan shi ya bani, ga mamakin maganan da yakeyi, duk da dai shi maganan shi murya a ƙasa take amma dai yana iya mu hira, wanda duniya ta shaidah dagani sai M.G ake ganin yayi dogon hira da su, M.G kamma wataran baya amsa mishi, amma ni a rayuwar shi sai ya iya good 2hrs yana mun hira, some times nice ma ke nuna gajiyawa, kallo kuma a rayuwar shi har mamakin baya iya gajjiya da kallona nakeyi, "tou mu haifi 5, ɗaya mu bawa mummy, ɗaya wa ummie, sai mu rie 2girls 1boy, mu haɗa da Sabeer sun zama 4 mue dasu".

Harara na yayi yace, "ke Eesha nifa ko goma kika haifah bazamu bawa kowa ba, yauwa gari ki sani, ke ummie tayi kyautan kine ko ni mummy mai tsananin ƙulafucin yʻayʻa ta bayar da nine? Muma mu zamu riƙe namu, kuma 3 ne insha Allahu".

Dariya nayi kawai na bar mishi zancen a haka, "wawan nan ya sake ƙiranki kuwa"? Naji muryan shi yana tambaya na, kai na girgiza mishi alaman a'a, "jiya nagayawa ummie yadda mukayi da shi, kuma tace zata samu yayah muhammad akan maganan, duk yadda sukayi zata gaya mun".

Ajiyan zuciya ya sauƙe, "Allah ya sakawa ummie da alkhairi, gaskiya naji daɗin shawaran da ummie ta bayar, mungode Allah ya saka da alkhairi",

Babu daɗewa yace na ƙira hafsy a waya, shigowan hafsy na ɗan harareta ƙasa-ƙasa ganin kallon da take mun tana ɗan iskan smilling, "yauwa hafsy zuki sha da yaro nan sai ki dawo,"

Miƙa mata sabeer yayi ya ɗaura mata 50k a kanshi, "kisaya mishi madara da pampers ko? Murmishi tayi ta fita da sabeer, kallon shi nayi bance komai ba, har hafsy ta dawo naga ya miƙe yace mata suje waje, gwalo ta mun da tazo fita.

Basu wani daɗe ba ya shigo, zama yayi ya ɗan ƙura mun ido, kunya naji nayi ƙasa da murya nace, "mungode Allah ya ƙara buɗi", shirun da naji yayi ne yasaka na ɗago ido na kalle shi, abun ko da nayi tunani ne ya faru, idon shi ne dai a zube a kaina, "idan uba yayiwa ɗan shi abu sai a mishi godiya"? Naji muryan shi yana faɗa, ɗago da kai na nayi ina duban shi kaina a ɗan langaɓe, "nidai nagode Yayah A.G, Allah ya ƙara buɗi", "bana son yayan nan, a bani wani sunan special, yayah ae Ahmad ne da M.G.

Bai wani daɗe ba ya mun sallama, rakashi waje nayi har jikin mota, bayan ya tafine na wuce wurin ummin mu, a ɗaki najiyo muryan su, har chan na samesu, ina shiga kuwa hafsy tayi charaff tace, "yauwa Adda gara da kika shigo, dama har haƙurina ya kusa ƙarewa, kaman zan leƙa waje nace ki dawo, ga tsaraban da nake ta ɗoki an kawo, buɗe mugani, ummie ta hanani buɗewa", ta faɗa tana wani washe baki, ummie na hararan ta "amma dai hafsy ke kam ko wa ke aka kawo kayan nan sai a hankali", murmushi hafsy tayi tana jawo babban jakan da yake kusa da ita, tana dariya tace, "ummie ae abun Adda na mu ne, yanzu hala ƙaramin jakan ma nawa tsaraban ne, bari mu fara na ma'in ɗin muga meye da meye a ciki"?

Buɗewa tayi nidai ido kawai na ƙurawa bag ɗin, dogin riguna ne kusan kala biyar, masu kyaun gaske, sai jean skirt kusan kala uku da riguna masu kyau, sai holland guda biyu super guda biyu, lace guda biyu masu kyaun gaske, sai gayyan takalma designers masu kyau da wasu handbag masu kyau na yayi, sai turaruka da dai cusmetics sosai, idona na ƙura akan wani agogo mai kyaun gaske, ƙasan kayan kuma kaya ne kusan set 10 na Sabeer da takalmin babys guda uku masu kyau "tou ni khadijah, duk wannan tsaraba ne? Shi dayake da haɗa kayan aure a gaban shi ya kawo wani tsaraba mai yawa haka"? Ummie ta faɗa, na buɗe baki zanyi magana sai naji ƙaran shigan txt a wayana, Aliyu ne ya turo mun txt, tsaki nayi ko karantawa banyi ba na goge, ido na mayar kan ɗayan jakan da hafsy ta buɗe Leda na asama an rubuta ummie, ɗaukowa tayi ta buɗe, turmin zani ne holland guda ɗaya sai turare guda biyu, miƙawa ummie tayi tana dariya tace, "ummi gana ki tsaraban, sannan ta ɗauko leda na biyu, English ne a ciki sai wani flat takalmi mai ɗan laushi an rubuta Hajiya ummah ajiki, ajiye shi tayi a gefe ta ɗauko wani da aka saka shadda 10yrd fari da turare guda biyu a ciki, an saka Abba, dariya hafsy ta ƙyalƙyale da shi da ta ɗauko ledan gaba jiki na rawa ta buɗe saboda ganin sunanta akai, lace ne mai kyau a ciki, sai tarkacen, bags, shoe, cusmetics kala-kala a ciki, ga wani riga da skirt mai shegen kyau a ciki nata ma har da wani agogo mai kyau a

ciki, rungume ledan tayi tana "Yaya A.G Allah ya baka Adda duniya da lahira, Allah yasa a aljannah a rabon kace", "Ameen ya rabbi" ummie ta faɗa tana kallonta da farin ciki, "hankalinki ya kwanta ko"? Ummie tace mata, tana wani jaririn dariya tace, "ae ummi bakiji yadda kayan nan suka sakani farin cikiba, gaskiya Yayah A.G duniya ne".

Harara ummie ta mata "tou maza rufe komai sai Abba ya gani tukunnah", ummie ta faɗa tana miƙewa zata fita, "ummie kada fa Abba yace no", hafsy ta faɗa, "bazai faɗa ba auta, amma abinda ya kamata kenan ayi", ummie na fita mutuniyata ta matso kusa dani, "Adda gaskiya kinyi dace da Ɗan gaske, don wallahi mutumin nan duniya ne, kiga wasu arnakun laces masu zafi? Wannan kam hala ma ya haɗa kayan shi achan, kuma ya tambayeki size ɗin takalman mune Addah"? Hafsy ta faɗa tana jin wani farin ciki domin ya nuna a fuskanta, nafi kowa sanin hafsy da son abun duniya, gashi dai akowani lokaci daga Abba har yayun mu cikin hidima suke mana, amma ita bata gajjiya da abun duniya, murmushi nayi na miƙe don jin an fara ƙiran sallan magrib, "nifa tun farkon tafiyan shi sister shi Heedayan nan ta tambaye ni size ɗin takalmi na dasu bra, ni na ɗauka ma mummyn su ce ta sakata, sai ana sauran kwanaki ya dawo ya mun wayo, don sai yanzu nagane, ya tambayeni nida ke wayafi tsayi nace kin ɗan fini kaɗan, shine yake ce mun kenan zaki fini tsayin ƙafa, ban fahimta ba nace mishi a'a size ɗaya mue sawa 39, kuma fah sai da yace kice hajiya ummah ma bazata wuce 39 ba nace mishi 38 take sakawa, ashe wayo yamun", dariya hafsy ta ƙyalƙyale da shi tace, "kai kaji ɗan bariki" harara na juyo na mata cikin wasa, "ae mijin nawa ne ɗan bariki? Ba laifin ki bane na bar shi ne har ya miki tsaraba", da sauri na shige toilet jin dariyan da hafsy ta sheƙe da shi, ima jiyota tana, "ashe fah kema Adda idan kin samu wuri duniya ce ke"? Ina toilet ni kaɗe ina smilling, wai nice ke ƙiran A.G da mijina ko kunya bana jin, haka nayi alwalan na fito na ɗaure fuska don kada ta kawo mun rashin mutunci, hannu ta saka ta rufe bakinta ta wuce toilet ɗin itama.

Abba bai wani yi faɗa sosai ba , kawai dai yace kayan sunyi yawa ne, ummie na taya shi, ƙiran wayan A.G yayi ya saka a speaker, ina jin muryan A.G na sunkuyar da kaina, godiya Abba ya mishi ya kuma mishi faɗan shi dayaje karatu kuma ga hidima a gaban shi ya kashe kuɗi haka? Shidai A.G godiya yake tayiwa Abba kaman wa shi akayiwa kyautar, daga jin voice ɗinshi risinawa yakeyi,haka ummi ma ta karɓa tayi godiya ta kuma ce ya gaida mummyn shi, itama godiya yayi ta mata, haka Abba ya sallame ni bayan ya tambayeni babu komai ko? Anan ne ummie ta ɗauko mishi maganan Aliyu da takurawan da yayi mana, ai kuwa Abba inda ya shiga bata nan yake fita ba, ɗaukan waya yayi ya ƙira yayah muhammad, ya

umurce shi daya nemi Aliyu yaja kunnen shi, ya tabbatar mishi shifa bai manta riƙon da yayiwa habiba ba, sannan kuma ya gaya mishi ya tsayar wa yar shi da ranan aure, kada ya shiga hurumin da bana shi ba.

Ummi da kanta ta kaiwa hajiya ummah kayanta, ranan kuwa A.G yasha yabo a wurinta, har da cewa ba'a taɓa saya mata takalmi mai kyaun wannan ba tunda tazo duniya, ita dai ummie murmushi kawai bata tanka ba, sai da hajiya ummah ta gama murnan ta tukun tayi ƙasa da muryah tace, "tou kayan shi jaririn wa matsafiyar za'a kai ? Kada fah taje tayi wani surkullen ta ɓata maganan auren"? Murmushi ummie tayi tace, " babu abunda ta isa tayi akai hajiya, insha Allahu babu abunda zatayi yayi tasiri, za'a kaimata yau ɗinnan".

Haɓa hajiya ta riƙe tana ya mutsa fuska tace, "tou duk yadda kuka gani, amma nidai da za'a bi shawara na da kada a kaimata, amma yanzu idan an kai babu bayanin matsayin shi, kawai abokin Ahmadu ne",

"hajiya ae yanzu da maganan Aliyu ya taso tasan da maganar aure, amma dai bata san waye ba, don ko lokacin rasuwar habiba, yayansu ne ya haɗashi da ita awayan shi suka gaisa, inaga ae rasuwan nan ya rikitata bazata yi wani abun ba", ummie ta faɗa tana miƙewa, ya mutsa guska hajiya tayi tace, "a naki zucuyar imanin ba, don Hauwan da nasani ko mutuwa tayi ta dawo taga abun mugunta zata aikata, saidai Allah ya tsare".

****

1month da dawowan A.G aka ska ranan auren mu, 3month mai zuwa, rana ɗaya dana M.G, zokiga rawan kai a wurin M.G, sai wani tsare-tsare yakeyi, sai da yagama A.G ya gwale shi, buɗan kai da reception kawai A.G ya amince zaiyi, haushi kaman zai kashe M.G, daga baya ne ma da A.G yaga ya tayar da hankalinshi ya yadda da maganan hawan da za'ayi, sai lokacin M.G ya ɗan sake, idan bani ba babu wanda ya isa ya ce ga ɗokin da A.G yakeyi, amma ni yakasa ɓoye mun farin cikin shi, photonan gidajen da zamu zauna bauchi da Abuja yake ta nuna mun, ya matsa wanne yafi mun kyau, babu yadda na iya dole na nuna mishi na bauchin yafi mun kyau, kallo na yayi yace, "Abuja yafi tsaruwa, kawai don baida girmane, shi 2bedroom ne, na bauchi kuma unguwa guda ne, side ɗin shi da ban nawa daban, 3bedroom ne nawa, ga parlor babbah, gidan yana kallon na M.G.

Abuja kuma A haɗe suke Gate ɗaya.

Kwanci tashi asaran mai rai, duk abunda aka saka mishi lokaci saurin zuwa ne da shi, yau saura 3weeks bikin mu, daga gefen mun har nasu A.G da M.G shiri akeyi sosai, abun mamaki yan'uwan M.G da suka haɗa mahaifi tare, wato yayan Alkali sai shirin biki sukeyi babu kunya, Aunty umatiti har ashobi ta fito musu da shi wai na familyn su, da yake ita da Aunty safiya sunayi da shi sosai, don karatun yayan umatiti duk yana kanshi, shidai alƙawari yayi ƙafan shi bazai leƙa cikin gidan da aka wulaƙanta shi ba, amma komai ya kama idan baifi ƙarfin shi ba zai musu, gashi yadda Allah ya bunƙasa mishi dukiyan shi abun har abun mamaki.

Gidan mu kuwa zuwa wannan lokacin mamie hali ya fara dawowa, don sabeer ma fir ta mun hali akan ɗaukan shi, wai yanata laulayin haƙori, sbd haka abar shi jikn babu lafiya, haka ba a son raina ba na haƙura, amma kullum sai naje na duba shi, gashi da ƙiwuya, amma idan ya gani ya dinga wangale baki kenan yana dariya, hanani ɗaukan shi da tayi sai danayi ɗan ƙaramin zazzaɓi, sai da hajiya ummah ta watse ni tukun na haƙura wa raina.

Gyara sosai ake mun a side ɗin ummie, akwai wata ƙawar ummi mai suna hajiyan basakkwata, itama ta na unguwar mu na G.R.A, ita take mun gyara mai sunan shi gyara.

A week ɗin aka kawo kayan aure gidan mu, kaya ne da ya amsa sunan shi kaya, set biyu na akwatuna A.G ya haɗa, M.G ma komai iri ɗaya aka yi, colour ne kawai yake banbanta, wai ranan zokiga mita a wurin mamie akan ba a gaya mata za'a kawo kaya ba, an maida ita meye a cikin gidan? Haka ta ringa bala'inta babu wanda ya kulata.

****

Gidan su Aliyu kuma haka Mummy tayi ta fama da shi har ya sake amincewa da auren yar sister ta, shima jamy ne ta nunawa Mummy abun da sukayi bai dace ba,

itafa bataga laifin Ayshaa da iyayenta ba, saboda son da akeyiwa jammy ya saka mummy ta fahimceta, har ta ƙira ummie ta bata haƙuri.

Shirye-shirye mukeyi sosai na liyafa a ta gefen ummie, don zainab ta tattaro tun ana saura 2weeks ta dawo gidan mu, haka hadiza ma ana saura 1week ta dawo, kowan su itama an saka mata rana, kuma satin auren su yayah umar zasiyi passing-out, gashi ya matsa sai ummie taje mishi, mudai dariyan drammer su muke tasha, domin ita ta kafe saidai Aunty Rakiya idan zata tafi mamah ta bita, shi kua fir yaƙi yace shima ummie yake son gani a ranan, koyaya za'ayi Allah masani.

Yayuna sun mun akwatin kayan fitan biki, babu ne kawai babu a kayan, don gaskiya sun mun kaya na kece raini, ga furnitures yan gaske da aa mun Abuja da bauchi, kuma ko ina an saka mun gadaje, Abuja duka ɗakuna biyun Abba ya saka mun gadaje, bauchi kuma sise ɗina ɗaki ɗaya ne ba'a saka ba, gado uku su yayah suka mun, ɗaya aka kai side ɗin A.G, ranan da akaje akayi jere shima an sha daga da mamie dn har da kukanta, akan ana mata rashin adalci, Abba dai kacha-kacha ya mata ya barta, dayake ana gobe passing-out ɗin su yayah su Aunty J Da Aunty B suka haɗu da Adda da Aunty ma'u da ta sauƙa Abujan sukayi, kuma ranan su ummie suka sauƙa Abujan, da yake mamah tana Abuja lokacin tare da Abba, tou duk tare sukaje wurin bikin fitan su Yayah, ga hafsy da ummitah ansha sabbin ɗinkuna taya masoyan su murna duk sunje, mu da su hadiza da Maryam da Goggonta aka bari a gida, sai mamie da take gefenta ita da raliya da tazo ranan da su ummie suka tafi, tayi wani kyau daga gani tana hutawa, sai dai bangan alaman taa da ciki ba, don naga daga Fatima har maryam suna da ciki, don maryam lokacin ma tana kwance cikin laulayi sosai, don sai da mukaje muka duba ta ana gobe su ummie zasu tafi, don a gidan suka ɗauki ummitah ma da zasu tafi, duk tayi wani iri abun tausayi.

A.G ma ranan suka shigo bauchi shidah M.G, don sun baro masu jere sunje, zuwa dare ko ya iso gidan mu, parlon hajita ummah muka zauna, hadiza da maryam sunzo sun gaisa, da yake hadiza yar barkwanci ce ta saka shi a gaba da zolaya babu yadda ya iya dole ya amsa mata, ita dai zainab yar shiru ce daga gaisuwan ma wucewa tayi ɗakin hajiya ummah, don idan baka fahimce ta bafa zaka ɗauka mugun halinta ya kai inda ba'a zato,, koni da muna yara haushinta nake ji, don idan tazo gidan mu tayita haɗa rai wa habiba, shiyasa na tsaneta, don wataran ni ko bin ta kanta banayi har tayi kwanakinta ta tafi, sai yanzu nake ɗan fahimtan wasu

halayenta, ita ba mai son hayaniya ba ce, sannan kuma ba kuwa hankalinta yake ɗauka ba, idan baka mata tou ko za'ayi yaya da ita bata bin ta kanka, abunda na lura kuma yɗan'uwan ummie suna jin haushin abunda mamie take yi mata, shiya jawo bata son habiba ko kaɗan.

Itama hadiza tashi tayi ta bar mu nida A.G, kallo na namayar kanshi lokacin da ta wuce ɗaki wurin su zainab, gira ya ɗaga mun duka biyu yace, "meye sirrin wannan ƙamshi da kyau da kikayi Eeshaa? Sai wani zabura nakeyi ni kaɗai, Allah ma ya taimaka su hadiza sun zauna, anya zan sake dawowa kuwa"? Ya faɗa yana kashe mun idon shi na jaraban nan, tura baki nayi gaba cike da shagwaɓa nace, "haka ma fah akeyi, har sai ranan auren fah ya kamata ka ganni".

Tasowa yayi ya dawo kueran da yafi kusa dani ya zauna, ya buɗe baki zaiyi magana mukaga an ɗago labulen parlon, namie ce ta shigo, zuciyata naji yayi wani mumunan yankewa, gashi wani kallo ta bi A.G da shi sannan ta dawo da idonta kaina, "amma saboda Allah ayshaa har an shiga satin aurenki baki taɓa tunani ko ke ko mamanki ba ku saka mai auren ki yazo ya gaishe ni ba? Ko don ni Allah ya ɗauke tawa yɗar kuke nuna mun haka? A hakan kike zaton na baku riƙon sabeer bayan mai riƙewan bai san girma na ba"? Da sauri A.G yafara gaisheta, rai a ɓace ta amsa mishi, ni dai bance komai ba na sunkuyar da kaina ƙasa ina mamakin ta a zuciyata.

Hummm ta furta bayan ta nemi wuri wa kanta ta zauna, hankalinta ta mayar kan A.G, "kasan tun suna yara mahaifiyarta ta hanata raɓa na, gashi Allah ya haɗa tsakaninta da habiba yɗar wurina, tou meyɗe aciki idan sunyi zumuncin su da Allah ya haɗa su na mahaifi ɗaya? Sai muyi namu kishin daban mu bar yara suyi zumuncin su, amma da yake ana ganin ni bani da haƙuri ina faɗin gaskiya sai duk kowa yaƙi jinina a gidan nan, tou gashi dai wacce ake husumar yanzu bata raye, basai a bar komai ya wuce ba, ae dai ko sau ɗaya za'ace kazo ka gaishe ni," ta faɗa tana share hawayen fuskanta, duk nidai jikina sai rawa yakeyi na abun da tayi, mamaki ne ko tsoro ta bani ohoo, "don Allah kiyi haƙuri, insha Allahu zamu gyara, zamuzo nida ɗan'uwana na musamman mu gaisheki, ita kuma ayshaa zata gyara na miki alƙawari", A.G ya faɗa yana wani risina mata, haka ta miƙe ta fice tana, "Allah yasa su barka, don ni bansan faɗin gaskiya yana saka kayi baƙin jini ba".

Ido ya ƙura mun yana murmushi, ganin duk fuskana ya chanja yasaka yace, "me kuma ya faru? Gaskiya ta faɗa ae beauty, yaka mata ko sau ɗaya kice muje mu gaisheta ae, tuda ita mamah muna gaisheta a chan Abuja, amma ba komai na miki

uzuri ke yarinya ce ay be bakiyi tunanin ayi haka ba, insha Allahu zamu gyara", ya faɗa yana kallona cike da murmushi.

Ajiyan zuciya na sauƙe ina cike da mamakin mamie, bance mishi komai ba kada ya ga mune da gaske bamu son a zauna lafiya, tunda shidah ba sani zaiyi ba, haka dai muka gama hiran ya tafi, koda ya tafi ban gayawa su Hadiza ba , gudun kada suyi magana hajiya ummah ta samu mamie, daga nan kuma ban san me zata zo tagaya mishi ba, haka dai na bar komai a zuciyata nayi shiru.

Ranan da su ummie na suka dawo, bataliya guda suka dawo, son har dasu yɗan'uwa na da matan su, da gudu na fita naje na rungume yayah umar, duk sai naga ya zama wani ƙato da shi, dama yafi su yayah muhammad siffan girman jiki, dariya yakeyi yana ta wani juyawa da ni, nima dariyan nakeyi nace, "yayah congratulation, Allah yasa kungama a sa'a", Ameen kowa ya amsa har da shi da yake cike da farin cikin ganina, "sisto na gama na dawo ke kuma zaki gudu ki bar ni da mai rusheshen kan nan"? Ya faɗa yana dariya, kowa yasan da hafsy yakeyi sai yayah muhammad yace, "mudai babu ruwan mu kunfi kusa kai da mai rusheshen kan", ya faɗa yana miƙa mun hannun shi, wurin shi naje na rungume shi ina "oyoyoyo best broh" shima oyoyon yayi mun, inda nabi su 1 by 1 Ina musu oyoyoyo, daga yayuna har matayen shu, su ummie dama sun wuce ciki da su goggo, Aunty Ruƙayyah da Aunty ma'u sun wuce tare da yayah ishaq, akan zuwa dare zasu shigo, gida dai ya cika sosai, nan suke cewa gobe Abba da mamah zasu taho insha Allahu, flight zasu biyo, nidai murna da daɗi nakeji a zuciyata, nan su Zainab da hadiza suayi wa yayah umar murna, hannu ya miƙa musu suka tafa, yana tsukanan zainab, "dunkum ae ina ta Allah- Allah kizo ko soja zasu ɗauke ki sunga irin su", dariya aka yi ita kuma tana hararan shi tace, "ina zuwa sallaman ka zasuyi suce wannan maganannen sojan a sallame shi a ɗauki asalin sojar", haka dai akaita raha, hadiza ta taya goggo jera musu abinci, nidai dama Goggo ta hanani komai a gidan iyakata naci nayi wanka a mun gyara.

Yayah Ahmad ne ya ƙura mun ido, "kai matar barrister wannan shinning ɗin da kike tayi ya kamata barrister fah ya ƙara sadaki, don 2million zan karɓa", ya faɗa cike da zolaya, "amma yayah ae karage mata, irin kyaun nan da tayi ae gida da mota zai ƙara", yayah umar ya faɗa shima da zolayan, nidai na tura baki gaba ina kallon yayah muhammad cike da shagwaɓa, hannu ya miƙo mun yace, "rabu da su bestyn besty, zo muyi wani ƙus-ƙus ɗin mu ni dake", matsawa nayi dab da shi na zauna ina hararan marenin wayo na, shi kuma yana kai loman abinci yana wani kaɗa mun kai irin alaman zai haɗu dani.

Kus-ƙus ɗinmu mukayi nida yayah na, duk yadda yayah Ahmad yake turo kai su Adda dasu Aunty J suna mishi dariya bai ji mu ba, chan kuma wayan shi ta fara ƙara, "wannan jarababben mijin naki ya dameni da nazo, nifa ya kama kanshi ni yanzu ba abokin shi bane yayan shine", ya faɗa yana ɗaga wayan, ido muka zuba mishi nida yayah muhammad, fuskan yayah muhammad ɗauke da murmushi, "barrister yyh ake cike ne? Ka matsa mun fa bayan madam ta hanani fita", baki Aunty J ta riƙe tana zare ido, shi kuma dariya yayi yace, "tou basai na saka a ɗaga ɗaurin auren ba, kasan nine alwali, wancan yayah m ne yayi na marigayiya, ni ko don ka kama kanka ma zancwwa Abba don Allah abani", bamuji me A.G ya faɗa ba amma ganin dariyan da Yaya Ahmad yake bayan dariya ba al'adan shi bane yasaka kowa ma ya dara, nidai sum-sum na tashi na bar wajen, jin yayah Ahmad nace mishi bazai bashi ba idan bai ƙara sadaki ba, ko me A.G yace naji Yaya Ahmad nacewa "tou ka taimaki kanks, ina ɗaya susususaccan angon"? Banji yayah suka ƙare ba na wuce chan ɗakin mu, anan na samu Aunty B kwance, don hafsy na tare da Areef a ɗakin ummie.

Ranan da sukaje jere washe garin da wowan su ranan su Abba suka dawo da mamah, babu wanda ya aiki mamie ta wani je gidan jere, bata daɗe ba ta dawo da wannan bala'in, nan Abba yayi mata kacha-kacha, ganin idon yayah umar da yayah ishaq ne ma da suka fito ya saka ta koma side ɗin ta , amma inaga taso abun yafi haka, don babu rahma a tattare da ita, kusan dab magreeb Mummyn Aliyu suka shigo ita da ƙawarta, gudumawa sosai na wasu manyan bedsheets guda biyu ta kawo masu kyaun gaske, tura hafsy tayi a ɗauko mata sabeer ta ganshi, amma fir mamie ta hana, koda aka zo aka gaya mata bata ce uffan ba bayan murmushi da tayi, hira suka cigaba dayi basu bi takan mamie ba, har akayi sallan isha sai ga yayah umar ya shigo, cike da isa da iya bariki mummy ta kalle shi, "yauwa ɗana soja, nace ko zaka taimaka ka kawo mun ɗanku na wurin Aliyu na ɗan ganshi"? Cike da gadara yayah umar yaje ya amso shi kuwa, kar ɓan shi tayi ra kalle shi daga nan ta mishi addu'a ta miƙawa ƙawarta, pics sosai suka mishi sannan suka yi sallama da ummie suka miƙawa hafsy akan ta maida shi.

Basu daɗe da tafiya ba hafsy ta shigo baki a zunɓure, kallonta ummie tayi ta ɗaga kanta, goggo ce ta tambayeta me ya faru? Bako a ture a gaba tace, "wannan matar da yarta wallahi yan rainin wayo ne, tsabar ni ta rainani bani na karɓo yaron ba ina maida shi ta wani rufeni da zagi tana zagin ummien mu, wallahi darajan Abba taci yau dana gaya mata maganan da har ta mutu bazata manta ba,"

"kul naji wannan ranan, babu ruwanki da su", ummie ta faɗa, "tou ummie ta isa tayiwa yayah umar ne? Itama raliya har da tsoma ruɓaɓɓen bakinta wai, ko wani

abu akayiwa yaron da aka ɗauke shi? Allah ya kare musu yaro, " hafsy ta faɗa ta na wani cika kaman zata fashe.

"Baki naushi bakin marar kunya ba"? Zainab ta tambayi hafsy, ita dai hafsy na kallon ummie tace, "na ajiye mata kykkyawan warning, idan ta sake shiga sabgata kafin ta tafi zan zane ta, ina faɗa na fito na barsu da baƙin ciki", ta faɗa tana juya ido

"Allah ya kyauta, ki zaneta kiga matakin da mijinta zai ɗauka akanki" ummie ta faɗa, dariya hadiza ta saka tace "haba ummie ita mai miji soja har za'a gaya mata ɗaukan mataki"? Dariya hafsy ta kece da shi tana, "gaya musu dai Adda hadiza, yanzu yayah ishaq yasaka yarinyar da mijinta tsallen kwaɗo wlh".

Har ummie dariya muka saka, wallah hafsy bata kunyar hiran yayah ishaq da ummie, don har ƙiranshi mijinta takeyi a gaban ummie, nikan bazan iya ba kunya nake ji Aunty nice.

Murmushi nayi ina kallon hajiya Ayshaa, hannu ta miƙa ta ɗauki goran ruwa tasha kaɗan, sannan ta cigaba.

Sai da naga duk sun fita tukun na gayawa ummie abunda mamie taje ta mun a gaban A.G, ido ummie ta ƙura mun, har wani lokaci tukun tace, "tou meye nufinta da zuwa wurin shi? Kuma me takeso yayi mata idan yaje gaisheta? Tou aniyarta ta bita, bazai je ba, kada ki yadda ki kulata balle ki kaishi", haka mukai ta hiran mu da ummie tana ɗan ƙara mun haske a rayuwa da kuma kula da mutane.

Su Aunty j duk sun wuce gidajen su tun magrib da mazajen su, ummie tace kowa taje ta huta, A.G bai sake shigiwa gidan mu ba don sanin a cike yake da mutane, amma waya kam har mamakin yawan ƙiran da yake yi nakeyi, a haka ranan alhamis aka zo aka zizara mun lalle da kitso, tun daga maiduguri Aunty Bintu ta saka fatima su taho da mai lallen, wednesday suka zo, fatima da ɗan ƙaramin cikinta wanda yayi mata kyau cif da ita, ba irin na maryam ba da yake wahalar da ita sosai, fatima da kitsonta da lallenta tazo, saboda haka washegari ni dasu hadiza da su hafsy mukayi, sai wasu feiends ɗinmu da muka haɗu da su a A.T.B.U da suka zo, babu kunya da yamma raliya ta aiko wai mai lallen idan tagama don Allah tazo ta mata, hararan yƙar aikan zainab tayi, "kice bata da wannan kuɗin da zata mana iko irin haka, ta nema a ɗauko mata wata daban", yƙar aikan tana fita hafsy ta sheƙe da dariya tace, "sai Adda jebo, ae da gangan ana gama yi mun na wuce side ɗin su, tana gani ta wani taso tana rangwaɗa wai don Allah hafsy ina kika samu aka miki wannan haɗaɗɗen lallen? Shine nagaya mata from maiduguri Aunty B ta ɗauko mana mai yi, har da kitso wa amaryah, shine wai ae bata sani ba ko itagama

zata zo ta mata, wai wallahi mijinta yana son lalle da kitso fa, nidai na isar da abinda ya mun na fito na barta, shine hakima bari ta aiko? Tou ta haɗu da Adda jebo yau".

Dukkan mu ɗakin dariya muka saka, don gaskiya hagsy tsiyarta yana da yawa, ita kanta mai lallen dariya take yi.

Ana gama cire mun na koma gefe na ɗauki wayan A.G, duk da nace mishi lalle fah ake mun amma bai fasa ƙira akai akai ba, ima ɗauka kuwa ya wani ajiye ajiyan zuciya, "Beauty", kawai iya abunda ya faɗa yayi shiru, murmishi nayi don nasan me yake nufi, ya gama gajjiya da galabaitan rashin jina yau, saboda yanzu maganan shi ɗaya nasan me yake nufi, idon shi ma idan na duba nasan meye yake so, "sai yanzu aka gama ne fah", na gaɗa mishi don ya kwantar da hankalin shi, "ina son ganinki", zaro ido nayi kaman yana ganina nace, "amma kasan gidan fah acike yake, yayah za'ayi ka shigo? Bakajin kunya ne"? Ajiyan zuciyan shi na sake ji mai ɗan ƙarfi, da kuma jin sautin numfashin shi kaman babu lafiya, a hankali nace. "kasha magani? Ko kasha wani abu mai sanyi ne"? "Eeshaa ni ke nake son gani", ya sake faɗa yana jan numfashin a hankali, duk sai naji babu daɗi amma ni bansan yayah zanyi ba, shiru nayi ina sauraron numfashin shi da yake fita da wani irn sauti, "Beauty", ina jin shi amma nakasa amsa mishi, shima daga nan shiru ya sakeyi, "zanzo" ajiyan zuciya nayi sanan nace, "Allah ya kawo ka lpy, ka kula da kanka".

Daga nan muka ajiye wayan, amma duk sai najini babu wani kuzari a tare dani.

Ina idaar da sallan magrib na shige kitchen ɗin ummie na ɗaura tea mai haɗe da kayan maiduguri na ƙamshi, bayan na tafasa na jure a flask ƙarami, sannan na ɗebi cake na saka a takeaway na wuce ɗakin mu da shi, kan mirrow na ajiye na shige wanka.

Isowan shi kenan ya ƙira wayana, lokacin kuma yayi daidai dana idar da sallan ishaa, haka na tashi na ƙarawa hijabin da nayi sallah turare kaɗan, dama an turara shi da kabbasa, ko kula tambayan da hadiza take na ina zanje banyi ba, ɗaukan flask ɗin nayi da take-away dana saka cake a ciki nayi na fice, ina ji suna ta tsokanana, ina isowa jikin motan kuwa ya buɗe mun ƙofan gefen shi, shiga nayi na

zauna, duk hankalina yana kanshi, domin ya kwantar da kanshi akan stearing motan yayi shiru, duk hankali na naji ya tashi, zama nayi na ajiye ɗan basket ɗin dana sako komai, "Yayah. A.G" na samu kaina da ambatan sunan shi, shiru bai amsa mun ba sai ɗan numfashin shi da sautin yake fita da alaman baya jin daɗin shi, "don Allah ka ɗago kanka" na sake faɗa, shiru kaman bazai ɗago ba, har na fara tunanin na ƙira yayah Ahmad, sai kuma ya ɗan juyo ya dubeni a hankali batare da ya ɗaga kan shi akai ba, "Eeshaa nah" ya ƙira ni a hankali, ajiyan zuciya na sauƙe a hankali, "ko asibiti za'aje? Na ƙira yayah Ahmad"? Tasowa yayi sosai ya zauna yana kallo na, "sun ganni ae tun da yammah a haka, amma basu damu ba, sai hidiman su suke tayi, M.G wai har dacewa ya kusa samun sauƙi ya huta, shiyasa nazo wurinki"

Dariya ce tazo mun amma nayi saurin mai da ita nayi murmushi, don yadda ya marairaice mun kaman wani baby yana magana cike da shagwaɓa, "nikan wallahi da duk kabani tsoro, yanzu irin wannan shagwaɓa kaman baby zaka iya kulawa dani kuwa"? Na faɗa ina kallon gefe don kada dariya yazo mun.

"Beauty ni ae baby ne a wurinki, gaskiya ki shiryah sosai, don kulawa zaki bani kaman baby ɗin, ina son kulawa sosai beauty", ya faɗa yana wani kashe mun ido.

Da sauri na kawar da kaina gefe, a hankali nace, "tou ni wa zai bani kulawan"?

"duk ni zan baki, akwai inda dole na naware na baki, amma lokuta da dama aikin kine, kinga ko bacci zanyi sai kin lallaɓani kafin na iyayi", ya faɗa yana ƙura mun ido, ae kam ban shiryah ba dariyan nan ya kubce mun, ido ya ƙura mun yadda nake ta ɓalɓala dariyan, ɗaga ƙarshe dole shima ya dara kaɗan, "me ya baki dariya"?

Ido na dukka suna zube akan shi nace, "tou ba namiji bane yake lallaɓa mace, kai kuma kace ni zan lallaɓaka, har kayi bacci, tou yayah kake bacci da?"

Ɗan ya mutsa face ɗinshi yayi ya wani tura bakin shi gaba, irin sakalun yaran nan yace, "ina yaro mummy ke lallaɓani nake bacci, tana shafa kaina tana ɗan bubbuga bayana a hankali har nayi bacci, dana girma kam da ƙyar nake baccin, ina da bashin bacci sosai akaina, sai munyi aure zan biya, zaki lallaɓani baby"? ya ƙarasa faɗi yana wani langwaɓar da kai kaman zaiyi kuka, kunya naji maganan shi ya bani, kawai sai na share shi na ɗauko cup na zuba mishi tea, zuma na saka ina gauraya mishi a hankali, shidai ya wani ƙura mun ido, nidai ban sake bi takan shi ba na cigaba da juya tea ɗin har ya mun yadda nakeso, miƙa mishi cup ɗin nayi, bai sa hannu ya karɓa ba sai ido da ya wani lumshe yana ƙare mun kallo, "ka karɓa sai na miƙo maka cake ɗin" na faɗa ina wani mummunan jin kunyar shi, "ki bani a baki nikam" ya faɗa kaman bashi ba, "don Allah ka karɓa bazan iya baka ba, ina jin kunyan hakan", na faɗa still ido na yana kan cup ɗin tea ɗin, hannu ya miƙo na bashi tea ɗin, da ƙyar na juya na miƙa mishi, idon shi akan lallai na, "woow beauty hannun ki ya ƙara kyau, baby kinyi kyau sosai", ya faɗa yana karɓan tea ɗin, nidai ban kula shi ba na ɗauko cake guda ɗaya na miƙa mishi, kai A.G duniya ne, ashe dama haka yake? Baki ya buɗe wai na bashi, hararan shi nayi nace, "plz mana

A.G" matsu da kanshi yayi kusa da ni murya chan ƙasa -ƙasa yace, "Eesha numfashi na zai ɗauke, plz ki bani", da sauri na kai cake ɗin bakin shi, shi kuma ya datsa kaɗan bai sake ba yana kallon ido na, ganin ni dai bazan iya wannan kallon ba kawai na kawar da kaina, ina jin shi a hankali ya dinga gutsura yana shan tra ɗin, yana cinye wa na sake ɗauko wani, a haka yaci har uku, sannan ya shanye tea ɗin, "thanks" naji ya furta, nidai ban iya na kalle shi ba, kaina a ƙasa nace, "za'a je asibitin ne?" "zaki rakani ne"? Juyowa nayi na kalle shi da sauri, "eh mana, saura 2dys fah ki zama tawa".

Share shi nayi ban iya cewa uffan ba, chan naji yace, "beauty ɗazu numfashin nan ya takura ni fa, har sai da mummy ta mun allura, M.G yana ta mita da akace ya ɗan jira ni na huta" , ya ƙura mun ido, nima ƙura mishi nayi kaɗan, "baby ina son ki kula dani sosai, kada ki gajji da A.G ki plz".

Runtse ido nayi sannan na buɗe su akan shi, ganin har yanzu irin kallon yake mun yasa na kawar da kaina gefe, "Eeshan A.G zata kula da shi har sai ya manta akwai wata kulawa a duniya wanda ba'a mishi ba", na faɗa cike da jin kunyan shi, " Eeshan A.G", ya furta a hankali, sao duk mukayi shiru babu abinda yake tashi sai sautin numfashin shi, wasa nakeyi da zoben hannu na kaina a sunkuye a ƙasa, jikina kuma ya bani idon shi yana kaina.

Aran wayan shi ne ya saka na ɗago kaina a hankali na dube shi, handsfree ya saka yayi shiru, "A.Gn mummy ina ka shiga ne? Ya ɗan lafah maka? Kazo kachi abinci ko", dukka naji mummy ta jeho mishi tambayan lokaci ɗaya, idona yana kan fuskan shi ganin yadda ya ya mutsa fiska kaman zaiyi kuka, "kai mummy na girma fah da tambayan nazo naci abinci, nifa ina wurin Eesha kuma ta ciyar da ni, am ok mummy" ya faɗa yana maida kallon shi kaina, ina jin ta tayi ɗan dariya kaɗan tace, "ahh tou masha Allah tunda har ka fita wurin doug, ka gasheta tou sai ka dawo", miƙo mun wayan yayi bata gama maganan ba, jiki na rawa na karɓa nafara gaisheta, cike da jin daɗi ta amsa tana ƙara mun godiya, nidai bam wani iya sakewa ba na miƙa mata wayan, kashe wayan yayi ya kwantar da kan shi akan stearing motan,

Chan kuma ƙiran M.G ya shigo, ɗauka yayi ya saka a handsfree, "Kai ƙaton sakali ba'a sallamu ka bane har yanzu"? M.G ya faɗa yana dariyan shaƙiyanci,

"Nakasa sallamuwa ne ƙaton banza, fargaban dawowa nake na kalli mummunar fuskan ka nan, bayan naga kyakkyawan halittah a gabana".

Dariyan mutane dayawa naji, wanda alama ya nuna handsfree suka saka suma, kuma daga ji abokanan su ne, zare ido yayi kaɗan yace, "mutanen mu sun iso kenan"? Ya faɗa yana wani sosa kai, M.G yana dariya yace, "za'ayi fitinannen ango

marar haƙuri, tou kadawo ba mutanen mu ba har yɗan Gombe ma sun iso, ga Babban yayanka ma mai baka matar yana jin ka, kabarta ta huta kaz kagaisa da ƙattin munana da suka taro",

Murmushi yayi yana shafa gemun shi, baice komai ba ya kashe wayan ya juya haba ɗaya yana kallo na, "Beauty naje"?

Murmishi nayi bance komai ba, "Eeshan A.G", ya sake ƙirana, nidai ɗaga mishi kai kawai nayi alaman eh, "tou ko sallameni" juyowa nayi na kalle shi, "saida safe Allah ya ƙara sauƙi", na faɗa ina ɗauko basket ɗin da yake ajiye.

"No baby ba haka ba, ki gaya mun wani word da zai mantar dani ganin mummunar fuskan gardawan da zanje na tarar",

murmushi nayi ina ƙara mamakin buɗewar bakin shi,

"zan gaya maka ta waya", "naƙi wayon baby, ki gaya mun yanzu, idan ba haka ba bazan iya tuƙa kaina ba",

Kallon shi ina jin tausayin shi a zuciyata, "Allah ya kaika lpy angon Eesha, yasa har waye gari har ranan da zan zama mallakinka kada mummunar fuskar M.G ya dameka, ko wani lokaci ka dinga tunawa da kyakkyawar fuskar Eeshan A.G".

tafi naji ya fara yana, "masha Allah yɗar aljanna, madallah da kykkyawar mace mai daddaɗan lafazi, baby goodnyt", buɗe motar nayi ban ko iya juyawa na kalle shi ba na wuce cikin gida, duk kunya da mamakin kaina ya rufe ni, har sai da na daɗe da wucewa tukun ya tafi.

****

Washe gari friday mukayi kyakkyawan liyafa a haraban gidan mu, nayi kyau iya kyau, anyi shi kuma ya ƙayatar, dayake bikin gida mu babu african time, dayawa an hallarah, hatta dangi ango da wuri suka iso, komai yayi babu laifi, haka akayi taro lafiya aka watse lafiya.

Da daddare Abbah ya ƙirani zuwa parlon shi, ina zuwa na same shi tare da Ummie, Yayah muhammad, Yayah Ahmad, Yayah Umar, gefe ɗaya ga Aunty Rakiya da Hajiya ummah kusa da shi, wucewa nayi wurin yayah muhammad na zauna a ƙasan

inda yake, a hankali duk na gaishe su, shiru nayi kaina a ƙasa, chan naji Abba yace, "malam muhammadu buɗe mana taro da addu'a ko".

Addu'a sosai yayah muhammad yayo ana binshi da Ameen, bayan ya gama Abba yayi gyaran murya tukun yace, "Ayshaa ɗago kanki ki kalle ni", haka na ɗaga kai na kalli Abba, "kinsan meya taru mu yau duka anan"? Girgiza kai nayi duk jikina a sanyaye, ƙura mun ido Abba yayi kaɗan har zuwa wani lokaci, sannan ya buɗe baki yace, "sallama da nasiha, sallama bawai na rabuwa ba, a'a, sallama wacce take da fa'idah, take da daraja take da muhimmanci, amma a ƙasanta mai ciwo," ina jin ya faɗi haka na maida kaina kan ummie danaga gaba ɗaya yanayin ta ya chanja, a hankali na maida kaina kan Abba, "munyi farin ciki da murna da Allh ya nuna mana wannan kyakkyawan rana na gobe da za'a ɗaura miki aure, wanda shine sanadin sallaman da zamuyi dake bawai don mun ƙosa da ke ba, ko gajjiyawa, sai dai yadda haka addinin mu ya umurta da muyi, Ayshaa da ace uba yana aurar da yar shi, kuma ya basu wurin zama su zauna a cikin gidan shi, a al'adance, tou wallahi Ayshaa kece irin yar da irin uba irina zaiyi, tabbas ke yace mafi soyuwa a zuciyata saboda halinki da ɗabi'un ki, ni mahaifinki ina miki albishir da cewa na yafe miki a zaman da nayi dake daga ranan haihuwar ki danayi har zuwa ranan da zaki bar hannuna, har ranan ƙarshen rayuwarki, ke yar albarkace wacce ta fito a tsatson yar aljannah, kinyi dace da mahaifiya ta gari, wacce ta baki tarbiya na gari, wanda shi nake fata Ayshaa ki nuna a gidan auren ki, ki nuna ke yar Nana khadijah ce, ki nuna ke tarbiyar Nana khadijah ce, yadda kika zauna lafiya damu, na roƙe ki ki zauna lafiya da mijinki da ahalin shi, yadda kika mana biyayyah kiyi sama da shi wa mijinki, yadda baki taɓa kawo mun ƙorafin kowa ba a gidan nan, don Allah kada ki kawo mun ƙorafin mijinko, don tabbas zan iya ƙinshi, ko mahaifiyar kice kika kawo mun ƙorafinta wallahi zan ƙita a zuciyata ballantana mijinki, ke yace lafiyayyah mai mutunta kowa, ina so ki mutunta yan'uwan shi da iyayen shi Ayshaa, don Allah kada akawo mun sukanki, kiyi haƙuri ba haƙurin cutarwa ba, idan akwai abunda ya sha miki gaba, ga mahaifiyar ki da yar'uwata Rakiya ki tun karesu da shi, na yadda dasu ɗari bisa ɗari zasu baki shawara, kada ki cinye abu a zuciyarki ya illataki irin yadda ya illata yar uwarki", yana zuwa nan ya sunkuyar da kanshi ƙasa, yayi shiru.

Nidai dama tunda ya fara nake kuka na ƙasa-ƙasa, amma yana zuwa wurin sai sautin kuka na ya ƙaru, hannu yayah muhammad ya ɗaura akaina yana shafa mun, "Eyyah usumanu kada ka raunana zuka tanmu, wannan rashi na habiba ya ƙone ka muma ya ƙone mu Usmanu, ga tafiyar baiwar Allan nan da yazama na farin ciki amma kullum fargaba nakeji a zuciyata na kewan da zaka shiga usmanu am," ta faɗa tana share hawayenta, ɗago kaina nayi don jin muryan yayah Umar yana, "haba ummie ku da zaku mata nasiha da fatan alkhairi cike da farin ciki shime zaku ɓuge da kuka,? Aunty Rakiya don Allah kuyi haƙuri", ya faɗa yana ƙara basu haƙuri.

Shiru parlon yayi na lokaci mai tsawo, sannan Abba ya dakatar da shirun, "Allah ya jiƙan habiba da rahma, Allah ya raya abunda ta bari da imani" gaba ɗaya aka amsa da "Ameen" banda ni kaɗai da na amsa a cikin zuciyata, "Allah yasa duk abubuwan da nagaya miki kiyi amfani da su Ayshaa, Allah yayiwa sabuwar rayuwar da zaki shiga albarka, Allah ya baki zuriya nagari masu albarka," "Ameen" kowa ya sake amsawa, Hajiya ummah Abba yace ta yi mun nasiha, amma fir ta kasa, "usmanu am me zance wanda baka faɗa ba, har ma abunda ni bazan iya ba duk ka faɗa, fata na dai Allah ya zaunar da ita lafiya yadda mahaifiyarta ta zauna da kowan mu lafiya, ae magana ya ƙare tunda tayi dace da uwa tagari irin khadijah, duk da dai dace da miji nagari adali ne ya zaunar da ita lafiya, don babu irinka a duniyan nan usmanu, mahaifin ka sak kabiyo a halin kirki," ta ƙarasa tana ta share hawaye da jan majina.

Ummie Abba ya bada dama ta mun nasiha, amma ummie yau kaman ba ita ba, cewa Aunty Rakiya kawai tayi ta mun, haka kuwa akayi Aunty ce ta mun nasiha da jan kunne sosai akan riƙe sirri, da kiyayan ƙawaye da shawara da su, daga nan Yayah muhammad yayi mun, yayah Ahmad ma ya mun, kowa cike da saka mun albarka, amma aminin hafsy da Abba yace saura shi, gyara zama yayi sosai ya ƙira sunana da ɗan ƙarfi, har sai da na ɗaga kai na dube shi, "Abin ƙaunar kowa da kowa a gidan nan, nidai abun da zan gaya miki shine, HAƘURI! HAƘURI!! HAƘURI!!!

BIYAYYAH! BIYAYYAH!! BIYAYYAH!!!

TSAFTA!

KULA DA GIRKI!

IYA MAGANA!

SUN DANGIN SHI!

wanda duk nayi imani da Allah kin samu training akan su sosai, na ƙarshw duk wanda ya ɗaga iki yatsa ki sanar dani, idan baiyi hankali ba sai na harbe shi, don da a taɓa mun ke, gara a ɗaga garin bauchi da kewaye, atou gara a san da haka", ya ƙarasa kowa yana ƙyalƙyalewa da dariya, ranƙwashi Ummie da ke kusa da shi ta kai mishi tana cewa, "kaji sarkin hankali babban kobo kawai".

Dariya shima yakeyi yace, "tou ummie nah idan ba haka nayi ba duk kun raunana mana zuciya, nida nake soja ƙarshe nayi abun kunya na ɓuge da rabza kuka, don ina ganin Abba namijin ƙoƙari yayi bai fashe da kuka ba", duka dariya sukeyi banda ni dana kwantar da kaina akan cinyar yayah muhammad inata share hawaye nah.

"aiko zuciya ta sanyaya kaɗan umaru ɗan albarka, ae ni ba yan pamilyn mijin nake so ka harbe wa ƙafa ba," sai ta ɗanyi ƙasa da murya tace, "hauwa munfukar gidan nan zaka harbewa ƙafa don ranan har parlor na ta biyo A.G tana kai sukar uwarku, laɓewa nayi a jikin ƙofa da naji alaman shigowarta, amma da yake Aisha tayi kalan sokaye shiru naji bata gaya mun abun da ya faro ba, shiyasa naƙira ƙanina kawun

babanku masaka ayita sauƙan qur'ani, duk sharrinta ya koma kanta, ita ta sani munafukar kawai", hajiya umma ta faɗa tana ƙasa da muryah.

Abba ne yace "shine ba'a gaya mun ba"?

"Tou wani abu zaka iya wanda bakayi shi ba abaya usmanu? Kawai nagama koai tunda na haɗata da Allah, kuma zaiyi maganinta", ta ƙarasa tana hararan Abba da yayi shiru baice komai ba.

Haka dai muka tafi muka barsu a parlon shi da su yayah muhammad.

****

Washegari saturday

A babban masallacin ƙofar fada aka shaidah ɗaurin auren

AMINU GARBA INUWA (A.G) DA AYSHATU USMAN UMAR (U.U)

sai kuma

MUKHTAR GARBA (M.G) DA HEEDAYAH GARBA INUWA

Runtse ido A.G yayi a zuciyar shi ya furta. "*ALHAMDULILLAH*"

ido suka haɗa da M.G, murmushi yayi mishi, shima M.G ya mayar mishi murmishin idon shi cike da ƙwallah, amma fuskar shi ɗauke da murmushi, lumshe ido yayi ya cigaba da sauraran abun da akeyi, Daddy ne mutum na farko daya miƙa wa A.G hannu suka gaisa, yana congratulating ɗinshi, sannan suka haɗa hannu da M.G, sun kuyowa A.G yayi saitin kunnen M.G yace, "yayah kaman kafin ɗokin wannan rana? Naga har hawayen farin ciki kake shirin zubarwa" M.G bai iya yace mishi komai ba har jama'a suka fara miƙa musu hannu ana taya su murna, daga nan suka wuce inda zasuyi recieption.

Alhamdulillah komai ya tafi musu yadda sukayi fata, ana idar da sallan azahar suka shiga gida da abokansu suka gaida Mummy da ƙawayenta, ghotographer ya musu pics sosai, nan A.G ya haɗa rai wai M.G da tashi amaryar shi kuma tashi tana gidan

su, haka dai suka gama daga nan suka ɗunguma sai gidan Goggo, nan ma sun haɗu da dangin M.G na fannin goggo da na baban shi da suka shigo, nan ma anyi photona sosai, daga baya suka dingayi da yayunshi da iyalen su, don hattah yayah auwal yazo ƙasan da matan shi da yaran shi, auren autan su mukhtarin goggo.

A gefen mu tun safe nasha wanka da ado da wata super ta mai kyaun gaske, an mun ɗauri mai kyaun gaske, gefe ɗaya kuma an kawo mun sabeer ɗina mun sha gayu sai photona mukeyi, dawowan su yayah daga ɗaurin aure suka mun chaa da tsokana har sai da nayi kuka, yayah muhammad ne ya rarrashe ni ya saka naje na ƙara chanja kaya, shaddah na saka gedzner mai kyau, tasha adon ɗinki sosai, photona mukai tayi wuri dayawa ina rungume da sabeer, duk rauni ya cika mun zuciyata, haka akai ta hoto har da su Abba da familyn shi da suka zo, daga baya Abba ya ƙora kowa na gidan akayi family picture a parlon shi, hannu na ɗauke da sabeer ɗina.

Ana idar da sallan la'asaar akace a fito kai amaryah, don dama an shiryah don Abba yace ana idar da sallah za'a tafi, suna da buɗan kai da hawa.

Atamfah ta holland mai ktau nasaka, sannan aka nannaɗeni da lafayan da Aunty B ta kawo mun wani fari mai ratsin Red ajiki, atamfah ta kuma red ce.

Goggo da Aunty rakiya sai Adda ne suka kaini ɗakin ummie, inda take tare da yan'uwanta da ƙawayen ta, har ƙasa na durƙusa a gabanta, Bayan an buɗe taron da addu'a Aunty Rakiya tace, "tou matar yayah ga ɗiyata na kawo miki kuyi sallama ki saka mata albarka, ki yafe ta kimata fatan shiga gidanta lafiya", murmushi ummie tayi ta dube ni, a hankali muryanta na rawa tace, "tou ni me Ayshaa ta mun a rayuwan danayi da ita? Albarka na kuma kullum ae yana tare da su", kaina na mayar kan cinyarta na kwantar ina sheshsheƙan kuka, abun mamaki kawai sai aka ga ummie na kuka, "haba Addah ke da zaki rarrashe ta kuma sai ki ɓuge da kuka"? Goggo ta faɗa tana ɗago ni tsaye akan mutafi, hannun ummie na riƙe, ina jin ta itama ta riƙe ni gam-gam, haka dai aka lallaɓa mu muka fice.

Side ɗin hajiya ummah mukaje itama kukan dai tayi tayi tana saka mun albarka, daga nan sai wurin mamah, itama ban kwana na mata tayi ta jero mun addu'a da saka albarka, daga nan aka wuce dani ɗakin mamie, achan najiyo sautin kukan

sabeer, sai naji duk zuciyata babu daɗi, haka na daure na tsuguna a gabanta, itama yadda akayiwa su ummie haka aka gaya mata, hannunta ta saka ta riƙo duka hannaye na ta riƙe su gam acikin hannayenta, addu'a take mun da fatan alkhairi, amma gaba ɗaya jina nake kaman na zabga ihu, saboda wani irin matse mun hannaye da tayi da ƙarfin gaske, wanda har sai da naji hannayen mu suna fitar da zufa nida ita, saboda babu space ɗin da iska zai shiga, adda'a tayi ta ja, daga baya kuma ta miƙar dani ta rungume tana muyafi juna, hannu Aunty Adda ta saka ta ɗago ni a jikinta muka fita, hannu na kai sai tin hanci na nashaƙi wani warin da naji yana mun kaman na jan miski, ni tun asalina bana son warin shi, sai naji kaman miski kaman kuma wani ƙarni-ƙarni yake mun, muna shiga parlon Abba na goge hannun a jikin cottons ɗiɓ parlon da dabara, amma dai har jikin lafayyah na ina jin yana warin abun.

Muna shiga naje na durƙusa a gaban Abba, kuka nakeyi sukuma sunata mun addu'a da nasiha, a ƙarshe Abba yace muwuce kada mu ɓata musu lokaci, kafaɗu na ya riƙo na miƙe tsaye, hannun shi ya saka ya riƙoni muka wuce har waje, motan da aka kawo na ɗaukan amarya Abba ya umurci su goggo da wasu a family su shiga, motan shi ya saka yayah muhammad ya matso mishi kusa da mu, baya ya buɗe ya saka ni, sannan shima ya shiga, ya umurci Aunty Rakiya ta shige gaban nashi motan.

Duk yan kai amarya ya saka suka wuce, muka bi su abaya, ashe kafin mu isa yasaka yayah Ahmad ya taho tare da A.G, masu rakiya dukka side ɗina suka wuce, mu kuma muna isa A.G suka fito a parlon shi suka tarye mu shida yayah Ahmad.

Muna shiga A.G ya rusuna yana nunawa Abba wurin zama, kujeran da Abba ya zauna ya manna ni a gefen shi na zauna, shi kuma yana rungume dani a kafaɗan shi, daga nan duk su Aunty dasu yayah suka nemi wuri suka zauna, shiru parlon ya ɗauka bayan an gama gaisuwa, ƙurawa A.G ido Abba yayi har zuwa wani lokaci mai tsawo, har sai da A.G yayi kaman ya koma ƙasa ya zauna, saboda ƙasa zai zauna Abba ya hanashi ya saka shi dole ya zauna kusa da Yayah Ahmad, duk sai A.G yaji kallon ya na tayar mishi hankali, har sai da Abba ya gama kallon shi na wani lokaci mai tsawo tukun yayi gyaran murya yace,

"Aminu"!

Ɗago da kai A.G yayi a nutse ya amsawa Abba da "na'am ranka ya daɗe"!

Ya maida kanshi ƙasa yana ƙara risinawa, ido Abba ya maida kan Yayah Ahmad yace "buɗe mana wurin da addu'a", addu'a sosai yayi daya gama, Abbah yayi gyaran murya yace

"A.G ga Ayshaa yʻata da ka nemi aurenta akan ka ganta ta maka kana sonta, ka zaɓeta akan ta zame maka uwar yʻayʻanka abokiyar rayuwarka right"? A.G ya ɗaga kai ya amsa da ehh, "a'a ka buɗe bakinka ka amsa mun" Abba yace mishi, "hakane Ranka ya daɗe, Allah ya ƙara girma," A.G ya faɗa.

"good, nakawo maka Ayshaa da hannu na ba saƙo ba, na kawota na danƙa amananta a hannun ka Aminu, na kawo ta na baka amanan yʻata mafi soyuwa a zuciyata, yʻata da idan an taɓa tou tabbas an taɓa zuciya da rayuwar usman" Abba ya faɗa yana nuna kanshi da hannun shi, hakan yasaka dukkan su suka sunkuyar da kansu ƙasa suna jijjiga mishi kai.

"Ayshaa amana ce a wurinka Aminu, haka kaima amana ne a wurinta, kuma na jaddada mata ban yadda ba ban yʻafe ba idan tayi wasa da amananka da yake kanta, ban yadda ba ta ƙunsa ma baƙin ciki, ban yadda ta ɓata maka ba sai a bisa kuskure, haka kaima,

Nakawo maka Aysha ne da sharaɗin ban baka aurenta don ka wulaƙanta mun ita ba yadda dayawa maza sukeyiwa matayen su a yanzu, ban yadda ka dakar mun yʻa ba, ban yadda ka kashe mun ita da baƙin ciki ba, idan Ayshaa tayi kuskure ka hukunta ta yadda addini ya tsara, amma dis time around duk wanda na bashi auren yʻata ya tozarta tou wallahi zanyi mishi hukunci daidai da abinda yayi, idan mutum yaji yʻata ya gajji da ita, tun wuri ya ɗauko ta a mutunce yadda nakawo mishi ita ya kawo mun abata,babu duka babu zagi".

Sannan ya tausasa muryan shi ya cigaba, "Aysha ta samu tarbiyan da nayi imani da Allah ko bayan ranmu bazata bamu kunya ba, haka kaima nake kyautata maka kyakkyawan zaton na bawa yʻata miji nagari ɗan manyan mutane, na roƙe ku ka haɗa kanku ku zauna lafiya, daga nan Abba ya dinga haɗamu yana mana nasiha mai ratsa zuciya daga ƙarshe Aunty ma tayi mana, inda take gayawa A.G, bawai Abba bai yadda da tarbiyan shi bane ya kawo ni har yaja mishi kunne, a'a yayi hakane saboda karin magana da hausawa suke cewa, *IDAN MACIJI YA SAREKA.....* idan kaga tsumma dole ka kiyaye, saran da Aliyu yayi mishi ne yake firgice da shi, nan A.G ya nuna shi hakan ma yayi mishi, kuma ya ƙara jin aranshi Diamond mai tsananin daraja da tsada ya ɗauko, kuma yayi alƙawari da ƙarfin shi da lafiyar shi da komai nashi zai kare Ayshaa, insha Allah sai kowa yace gara da akayi.

Tashi Abba yayi tsaye ya ɗagoni muka tsaya, nidai ban da kuka babu abinda nakeyi, domin nasan Allah ya mun komai na rayuwa, ya bani gata na iyaye nagari, yʻan'uwa nagari , dangi nagari, kuma duk maso ƙaunata, gashi yanzu ya bani miji Nagari, mijin marainiya mai ƙaunata, Abunda zan nema kawai Allah ya zaunar dani da shi lafiya ya bamu zuriya ta gari, hannu Abba ya miƙawa A.G, da sauri ya ƙaraso gaban Abba amma yakasa bada hannun shi, har sai da Abba ya rungumu shi, hannuna ya cire a nashi ya ɗaura akan na A.G, ae kuwa da hanzari ya riƙeni sosai, "Aunty nice nidai aduniya ban taɓa jin wani halittah na ɗa namiji daya taɓa riƙe hannu na bayan

Abba dasu yayye na, gashi dai ɗabi'ace ta yayuna su rungumo mu, especially ma ni, Abba ma idan munje gaishe shi sau dayawa hannun shi yake miƙowa mu gaisa, amma ko yayah ishaq bamu taɓa riƙe hannun shi ba saboda kiyaye wa, amma nidai ban taɓa jin hannu mai laushi ba irin na A.G, har tsoro naji a zuciyata nace, hala taurin nawa hannun zaiji, saboda laushim da hannun shi yake da shi banyi tsammanin akwai maza irin haka ba a duniya", Nidai murmushi nayi ina bin hajiya Aysha da ido, matse hannuna yayi cikin nashi, ina jin yadda hannun shin yake rawa, a haka Abba ya sake jaddada mishi amanan da ya bashi, sannan ya umurce shi daya sada ni da ɗakin shi, ina jin Abba yana zame hannun shi ajikina na zabura zan chafko shi, amma sai naji A.G yasaka dukka hannayen shi ya riƙe ni, ae kuwa da sauri na ƙara fashewa da kuka murya a sama nace, "Abba na kada ka tafi ka barni," amma sai abba ya dafa kaina ya ƙara saka mana albarka yayi hanya fiya daga parlon, aeko da ƙarfi na ɗaga murya nace, "Abba sisto ka zaka bari da wani"? Tsayawa Abba yayi chak a bakin kofan, ganin haka Aunty Rakiya ta ƙarasa ita da yayah Ahmad suka riƙe shi suka fice a parlon batare da ya juyo kaina ba, maida kallona nayi kan yayah muhammad da zaibi bayan su nace, "besty kada ku tafi ku barni tsoro nakeji", shima ɗan murmusawa yayi kaɗan bai kai chan ciki ba ya juya yayi waje batare da yace uffan ba, da sauri na maida kaina kan A.G, bakina har wani ɗan ɓari yakeyi nace, A.G nikan kabar ni na biso, tsoro nakeji",

Hmmm A.G duniya ne, kawai Jawo ni yayi ya buɗe ƙofan ɗakin shi ya shige dani, muna shiga kuwa ya rungumeni tsaf a jikinshi bai bani amsa ba tanbayan da nake ta mishi na ina zai kaini ne? Kuka na fashe dashi kawai mai ƙarfi, idan banyi ƙarya ba yakai sama da mintuna Goma muna a haka, har sai da aka ƙwanƙwasa ƙofan tukun naji muryan shi ƙasa -ƙasa yana tambayan waye? "Hudah ce yayah", ajiyan zuciya ya sauƙe, bai kuma ɓalle jikin shi da nawa ba yace, "meye ne kuma Hudah"?

"Mummy tace amaryar ka kaita za'a shiryata saboda buɗan kai, su Yayah M.G duk sun shiryah", tou kawai ya amsa mata da shi ta juya ta fice.

Ina jin shi yayi tsaki yace "duk fitar M.G ne wallahi da wasu bidi'a, an ɗaura aure an kawo amaryah kuma meya saura ne nikan? Basai a haƙura da bidi'an da baida wani dalili ba? Hala Y'an rakiyan kawo amaryan ma Abba ya kafa su sun tafi".

Nidai da sauri nace, "wallahi suna nan, ina jin muryan su ma" shiru yayi baice uffan ba, kuma bai sake ni na tafi ba.

A tsorace na sake cewa, "mummy tace mu shiryah da wuri fa", still dai bai kulani ba, shidai ya manna kanshi a saman kafaɗa ne, chan naji shi kaman mai barci yace,

"ko na ƙira Abba ne nagaya mishi suna nan basu tafi ba, don nasan yanzu zai umurcesu su tafi, mummy kuma babu matsalah Daddy ya isheta ta ƙyale mu da maganan bidi'an nan".

da sauri na har da fashewa da wani sabon kukan nace, "wallahi nayi burin bikina ya zama akwai buɗan kai da hawa, udan ba'ayi ba za'a mun dariya, kuma bazan taɓa daina damuwan rashin yin ba", aiko ina faɗin haka da sauri ya juyo dani ina kallon shi, dukkan hannun shi zube akafaɗa na, tsoro naji yadda naga udon shi a lumshe kaman bazai iya ganina ba, a raunane ya buɗe baki yace, "zan shirya muje, zanyi abun da kike so, ai naji ance ba haramun bane ma, amma don Allah ana gamawa su tafi kinji beauty", da sauri nake ɗaga mishi kaina alaman naji, nan kuwa ni kaɗai nasan wani irin masifaffen tsoron da nake ji a ƙasan zuciyata, har ƙofan da zai fitar da ni daga sashen Shi ya rakani, yana riƙe da dukkan hannaye na ya ƙira Hudah, tana zuwa yace ta wuce dani side ɗina na shiryah, da sauri kuwa ta amsa mishi, dukka hannayenta ta saka ta riƙoni muka fice, a parlor na muka samu su Aunty Rakiya da sauran yan'uwa, nan ta riƙe ni muka wuce ɗakina, inda aka fara mun shirin fita wurin buɗan kai da za'ayi a haraban gidan su A.G.

Wurin buɗan kan ya cika maƙil da yan'uwa da abokanan arziki, gefen mu M.G ne zaune da amaryar shi, sun sha ankon blue shaddah shida A.G, haka wurin ɗaurin aure sunyi ankon white shaddah, gefen shi Heedayah ce zaune fuska a rufe, nima gefen A.G aka zaunar dani,

M.G ne yafara buɗe fuskan amaryar shi, bayan ya liƙa mata kuɗi ya koma ya zauna, sannan A.G ya tashi ya biɗe nawa fuskan, ina jin shi yana liƙa mun kuɗi yana ɗan taka ƙafana a hankali, haka na share shi dai ban motsa ba.

yan uwana da nashi suna ta aikin liƙa mana kuɗi, gefe ɗaya ma yan'uwan M.G suna ta liƙa musu, Yayah Ahmad ne ya shigo shida wani aboki, M.G suka fara liƙawa, sannan suka dawo kanmu, liƙa ma A.G yayi, amma daya dawo kaina key ɗin mota ya ɗaura mun a tafin hannu na, aiko gaba ɗaya fili ya ɗauki tafi, har sai da A.G ya miƙe tsaye ya rungume yayah Ahmad, M.G ma tashi yayi ya rumgumeshi fuskan su duka cike da farin ciki, hannu A.G ya miƙo kan cinya na ya ɗage key ɗin, aljihun shi ya saka, gaskiya buɗan kan ya ƙawatar, ko dan motan da nasamu abun ya mun daɗi sosai.

Daga nan motoci ne suka ɗauke mu zuwa kallon hawa da zasuyi, shima hawan babu laifi yayi kyau sosai, ni dai dayake bai dame ni ba ko kaɗan, so ba wani burgeni sosai abun yayi ba, A.G nah yayi kyau da shigan da yayi, a ido na ma kaman yafi kowani namiji a wirin kyau.

Zuwa ƙarfe 10:00pm na dare dukkan jama'a sun watse, kowa ya kama gaban shi an gajji da ganin gidan amaren, haka ƙawaye da dangi duk sun tafi gida, daga ni sai

hadiza da zainab, sai hafsy da Aunty j da suke jiran yayah Ahmad yazo ya ɗauke su, sun ƙara gyara gidan sun saka turaren wuta, ko ina ƙamshi mai daɗine yake fita, nima daidai lokacin na fito a wanka, Aunty j tana tayani kintsawa sai ga yayah ya ƙirata akan su fito yana waje, batayi saurin fita ba sai dana shiryah acikin wata doguwar rigar atamfah mai kyaun gaske, ta gyara mun fuska da ɗan light make-up, ta yafa min gyale ya rufe mun fuska bayan ta fesa mun turare duka jikina, ina jin su duka suka fita suka barni ni kaɗai, nidai ban iya nace musu komai ba sai hawaye na da nake sharewa, ga wani irin fargaba da nakeji yana cika zuciyata, bayan wasu yan lokuta masu ɗan tsawo sai naji an buɗe ƙofan ɗakin baki cie da sallama, A.G ni ya shigo ina jin shi ya mayar da ƙofan a hankali ya rufe, ya ɗan daɗe kaɗan abakin ƙofan, daga baya kuma sai naji takun tafiyan shi yana shigowa cikin ɗakin, duk wani sautin takun shi haka nake jin sautin bugun zuciyata, kafin ya ƙaraso na haɗa wani uban zufa kaman nayi gudun ceton rai.

Zama yayi a bakin gadon ya ƙura mun ido, chan kuma ya saka hannun shi ya yaye lulluɓin kan, runtse idona nayi naƙi kallonshi, ajiyan zuciya ya sauƙe mai ɗan ƙarfi kaɗan, sannan ya sunkuyo da kanshi saitin fuskana ya sumbaci goshina, "*MARABA DA KYAKKYAWAR SALIHAR MATANA, MARABA DA RAYUWAR A.G, MARABA DA HASKEN ZUCIYA DA GIDAN A.G, MARABA DA ƊAWISUN A.G*"

ya ƙarasa faɗa yana haɗa fuskanshi da nawa, nidai har lokacin ido na duk suna kulle, sai hawaye ne kawai suke bin kumatuna, harshen shi ya saka ya fara lashe hawayen, hakan da yayi ya sakani fashewa da kuka, shiru yayi ya dakata da abun da yakeyi, muryah a hargitse yace, "Eeshan A.G meyake faruwa? Kukan kewan su ummie ne ko kuma na farin cikin kasancewa da A.G? Idan na kewa ne nima na koma gefe nayi tagumi na kewan mummy nah, idan na farin cikine don Allah ki jirani muyi tare".

Ido na duka na buɗesu akan shi, wai kukan farin cikin ganina a gidan shi? Lallai ma, shi bai san kewan yan'uwana da iyaye na nakeyi ba ko? Rufe idona na sakeyi na ƙara sautin kukan, rungumoni yayi jikin shi sosai ya na lallashi na, da kyar dai ya samu nayi shiru, daga nan ya kamo hannu na muka fita zuwa parlor.

Kan kujera ya zaunar dani ya kunna mun T.V, sannan ya dawo gefe na ya zauna hannun shi riƙe da nawa yace, "kiyi kallo zanje nayi wanka na dawo, zaki bani labarin abunda kika kallah, ko zaki rakani nayi wankan"?

Juyar da kaina gefe ɗaya nayi na ƙi kallon shi, murmishi yayi ya miƙe ya wuce side ɗin shi, yakai kusan 45mns kafin ya dawo parlon cikin wasu white kayan bacci, three quater ne da riga armless, sai wani ƙamshi a hankali da yake tashi a jikin shi,

kitchen ya wuce ya ɗauko ledan da ya bansan lokacin da ya kai kitchen ba, a saman tray ya ɗauro da filet da cups, ƙamshin kajin ne ya cika parlon wanda jin hakan yasaka ni wani mummunan faɗuwar gaba, wanda har sai da naji alaman kaman fitsari ya ɗan biyo jikina, ɗan gyara zama nayi ina mamakin tsoron da nakeji mai sakani mummunan faɗuwar gaba irin haka, duk yadda yayi naci naman nan kasawa nayi, daya takurani ma kuka nasaka mishi, haka ya haƙura yaci naman yasha jus ɗin shi, daga nan ya tattare su ya wuce ya kai kitchen.

Bayan ya dawo ne yazo gabana ya miƙo mun dukka hannayen shi akan na miƙo nawa ya tayar dani tsaye, kawar da kaina gefe nayi na tashi tsaye ni kaɗai, hannu ya saka ya riƙo ni, muryan shi chan ƙasa yace, "Beauty kina tsoro nane? Kini cin komai? Tou muje narakaki ki chanja wannan kayan ki saka na bacci a ɗakina," ɓata rai nayi ina kallon shi nace , "zan iya zuwa ni kaɗai," idon shi cikin nawa yace, "kayan suna ɗakina ne, su nake so ki saka bana son musu", shiru nayi kaman ina tunani sai kuma na bishi, duk jikina a tsarge da fitsarin da naji kaman yana shirin zubuwa.

muna shiga ɗakin shi naji kaman an kwaɗa mun guduma a tsakar kaina, dole naja ƙafana na tsaya na dafa kan, a ɗan furgice yace, "kan yana miki ciwo ne"? Kai kawai na ɗaga mishi alaman ehh ban buɗe baki ba, kuma hannun yana dafe da kannawa, kamoni yayi yana shirin zaunar dani a bakin gadon shi sai naji wani sarawan kan ya ƙaru, dole na ja na tsaya naƙi, "bana son zama kaina yana ciwo sosai,"

"shiyasa nake son ki zauna ae princess, ina son ki ɗan ji sauƙin ciwon kan ne"

Raina ne naji yana ɓaci, ga wani tafasa da zuciyana yakeyi lokaci ɗaya, ƙwace hannu na nayi na fice a ɗakin da sauri, ina jin idan ban gita ba zuciyata zata buga, da sauri na koma side dina ina harhaɗa ƙafafu, ina shiga ɗakina na wuce direct zuwa toilet, ina cire panta ɗina sai naga period ɗinane ya dawo, abun sai ya ban mamaki domin banfi 9dys dagamawa ba aka ɗaura aure na, yanzu dai inaga 10dys ne ko 11dys da gamawa, dama babu abun da basu saka mun a toilet ɗin ba, sbd haka gyara jikina nayi na cire kayan na ɗaura towel, domin ganin ya ɓata mun har dogon rigan da nasaka, ɗakin na dawo na ɗauki kayan bacci mai riga da wando na saka, shafa jikina nayi gaba ɗaya da humrah, ina juyowa naji ya buɗe ɗakin ya shigo, gaba ɗaya sai naji kaina ya sake sara mun, gefen gadona naje na zauna na ɗaure fuskana, takowa yayi ya zauna dab dani, "nikan ka tafi ɗakinka bana son ganinka, kaina ciwo yakeyi sosai idan na ganka,", na faɗa mishi ina jin wasu hawayen ɓacin rai suna zubo mun, ido ya ƙura mun sannan yace, "beauty don Allah

kidai na kukan nan, wallahi babu abinda zan miki da babu yaddan ki, kizo muje gobe zan kaiki ki sake ganin ummien",

"ummimato" da iya ƙarfina naji bakina ya buɗe na furta mishi, wanda tsabar firgitan da yayi sai da ya ja baya, har wani hakki nakeyi na tashin hankali nace, "kafita ni bana son ganinka, wari kake mun, kafita kaina zai gashe idan ina ganinka", na faɗa murya na cike da ihuu mai ƙaran gaske, wanda har sai da ya toshe kunnen shi ya miƙe tsaye.

Kuka na fashe da shi na baƙin cikin ganin ya ƙi fita a ɗakin, Aunty nice a cikin ɣan lokuta kaɗan naji babu abinda bana son gani irin A.G, gashi wani wari mai ƙarni nakeji yana mun, don har zuciyata tashi takeyi, shi kuma gaba ɗaya hankalin shi tashi yayi sosai, "Eeshaa don Allah akwai laifin da na miki ne da na shigo? Ko tafiyan danayi na barki zuwa wanka ya ɓata miki rai ne baby"? Ya ɗan ƙara matsuwa kusa dani kaɗan da nufin rarrashi na, aiko na taƙarƙare na zabga uban ihuu mai ƙaran da sai da ya miƙe da sauri yana furta, "innalillahi, Ayshaa me na miki ne please? Ko gida kike son na kaiki ne"?

Harara na zabga mishi nace, "kalan ace banida hankali yau ankawo ni na dawo gida? Kawai ganinka ne bana sonyi, kuma kana tare mun numfashi mai kyau, kawai ka fita kada na mutu", na faɗa da ƙarfi sosai ina miƙewa tsaye ina zare mishi ido.

Hannu ya ɗan ɗaga mun alaman rarrashi, "tou shikenan Eeshaata zan fita amma don Allah kiyi addu'a ki kwanta, kada kiyi kuka kiyi bacci", hararan shi nayi wanda ban taɓa tunani a rayuwa zanyiwa wani ɗa namiji ba ballantana A.G dana samu kaina dumu-dumu a ƙaunar shi, don kawai bana so a gane irin son da nake mishi ne kawai nake sharewa, amma sai yanzu nagane ashe M.G hiran shi da kulawan da yake nuna mun ne ya ja hankalina da shi, amma zuciyata A.G take muradi, haka yafice a ɗakin cike da damuwa yana waiwayo wa yana kallona, yana fita naji nutsuwa yazo mun, har wani ajiyan zuciya na sauƙe a lokacin, sannan kuma chan ƙasan zuciyata inajin ban kyautawa A.G ba, amma kuma a zahiri kuma ina jin kaman lafiya na samawa kaina, haka dai cike da damuwan abunda na mishi na kwanta.

Baccin da na kwanta ba mai daɗi bane ko kaɗan, domin wani mafarki nayi marar kan gado, mafarkinayi na ganni cikin wani forest mai ɗan duhu kaɗan ina tafiya ni kaɗai, ta baya na kuma ina jin taku mai ɗan ƙarfi a bina a baya da na juya sai naga wani narkeken mutum ne ke biye da ni, babu riga ajikin shi sai gajeren baƙin wando, gashi dogo a murtuƙe, wuyan shi da sarƙan mai ɗauke da hutun doki a jiki, ganin yana nufoni sai nayi sauri nayi gaba na ɓuya a jikin wata bishiya, ina kallon shi har yazo ya wuce bai ganni ba, ina ganin yayi gaba yana ta dube-dube bai ganni ba sai na fito na koma da baya na fita a cikin bishiyoyin, ina fitowa kuwa sai na

haɗu da mamie da ƙawarta surkuwar raliya da ƙanwarta sun saita ni da bindiga a hannun su, juyawa nayi zan koma ciki kuma sai naga zabgegefn mutumin tsaye ya ƙura mun munanan jajayen idanun shi, a daidai nan na farka a firgice, duk da A.Cn da yake aiki a ɗakin amma na haɗa uban zufa a fuskana har zuwa wuya na, tashi nayi na zauna cike da tsoro, waiwaya wa nayi na ƙarewa ɗakin kallon amma banji alaman komai ba, naso na koma na kwanta amma naji ajikina pad ɗina ya ɓaci, haka na lallaɓa na shige toilet na gyara.

Da safe tun kafin 7:00am na tashi na gyara ɗakina na shige nayi wanka, dogon rigan lace cotton na saka a jikina mai ruwan ganye, ɗinkin yayi kyau sosai ya kuma zauna ajikina, turare na saka na wuta a cikin burner na koma na zauna cike da zulumin yadda zanyi na fito zuwa parlon, ina haka har wurin 9:00am sai ga driver gidan su da wata yʻar'uwan mummy sun kawo mana breakfast, har ɗakina ya shigo ya gaya mun na fito mu gaisa da matan, jiki duk a sanyaye na yafa gyale nabi bayan shi, cike da fara'a a fuskanta ta amsa mun gaisuwan, sannan tace mummy na gaishe mu, nima cike da girmamawa na mata godiya, inaji tana gayawa A.G zasu shiga gidan M.G ne su miƙa musu nasu, har wajen parlon na rakota, anan na tsaya nace ta gaida mummy.

Ban daɗe da zama ba naga ya shigo ɗakina, a bakin ƙofan yaɗan dakata, fuskan shi cike da damuwa da alaman rashin bacci akai, murya ƙasa-ƙasa cike da rauni yace, "morning my dear", kunya naji ya ɗan rufe ni, kaina na sunkuyar ƙasa sannan ni na gaishe shi, "fito kizo muyi breakfast ko, idan babu matsa kafin mutane su fara sintirin zuwa"? Cike da jin kunyan shi da abunda na mishi jiya na miƙe nabi bayan shi, zama mukayi akan dinning muka fara break tare, duk kunya lulluɓe dani muka ƙarasa karyawan tare, nidai tunda nayi ƙasa da kaina ban yadda na ɗago ba har muka gama, gashi ban iya na ci wani abun kirki ba, baice mun uffan ba ya ci abincin shi sosai, ina ankare da shi peppesoup ɗin yafi maida hankali akai, muna gamawa na tattare komai nayi kitchen da su, wanke abubuwan da muka ɓata nayi, sannan nazo na ɗan goge parlon na saka turaren wuta, fitowa na baya parlon shiyasa ina gamawa na koma nawa parlon na kunna t.v na zauna, nidai ba kallo nakeyi ba tunani kawai na tafi mai dogon zango, ban san shigowan shi ba sai zaman shi a gefe na kawai naji, a razane na kalle shi, murmushi yayi mun mai kyau a fuskan shi, "M.G ya angonce yabar twin brother shi da kwanan fargaban me yayiwa amaryah take ihuu da kuka haka?"

Sun kuyar da kaina ƙasa nayi ina wasa da zoben hannu na, don duk maganan shi sai tasaka naji kunya sosai.

"Any way babu matsala idan amaryah ta furgice a rananta na farko a gidan ta, sai dai hankalina ya tashi daga nin irin razanatan da nayi, har sautin muryanki fa ya chanja gaba ɗaya kaman bake ba", ya faɗa yana kamo hannaye na da nashi hannun, ban iya nace komai ba sai kallon yatsuna da suke sheƙin lalle a hannun shi.

"Beauty akwai wani abu da ranki bai so bane wanda na miki shi a jiya"? Najiyo muryan shi yana mun tambaya, duk kunya ta lulluɓeni na girgiza kaina alaman a'a, lumshe idon shi yayi ya tashi ya matsu kisa dani sosai, hannun shi yasaka ya ɗagoni dukka na ya ɗaura a saman cinyan shi, ban neme tashi daga jikin shi ba sai dai fama da na fara da faɗuwan gaba da kuma sarawan kai, a hankali yakwantar da kanshi a kafaɗa na yana murza mun hannaye na da suke cikin nashi hannun.

"Beauty ina so ki buɗe baki kigaya mun duk wani abu da baki so na miki marar kyau a zaman takewar mu, sannan me kika fi so a zamanmu da zamuyi tare? And nima kuma zan gaya miki meye nake so meye bana so, fatan zaki bani dukka hankalin ki wurina"?

Ɗaga kai nayi na kalle shi, sai naji son shi da tausayin shi sun cika mun zuciya, narasa dalilin dayasa jiya na mishi abun da na mishi.

Dukkan hankalina da nutsuwata na maida shi kanshi.

"Eesha ima so muyi zama na mutunta kai da amana, zan baki dukkan ƙaunata, kulawata, yarda ta, amanan kaina, kema haka naƙe so ki bani naki, duk wani abu dana miki bani so ki doshi kan kowa sai ni, idan kinga abin yafi ƙarfina kona kasa tsayawa akai ne zaki doshi iyayenki da shi, bana son 3rd party a tsakanin mu beauty, bana son tarukucen ftiends saboda gujewa matsalaloli, bana son aro da bayar da aro na sutura, bana son chin bashi, ina son ki girmama iyayena da yan'uwa na, ni kuma zan tare miki duk wasu fitina da zasu iya fitowa daga gefena, Eesha ina son biyayyah da girmamawa, ina son kula sosai, kuma bana son ƙaryah akan komai" yana faɗa ya ƙura mun idon shi, sunkuyar da kaina ƙasa nayi ina maimaita abunda ya faɗa a ƙasan zuciyata , "ina sauraronki Eesha".

"Nidai bana son ka wulaƙanta ni ne kawai, ina so ka soni har tsufah na, kuma...kuma..", sai nayi shiru ina murmushi, shima murmushin yayi yana kallona, "kuma bako son kishiyako"? Ya ƙarasa yana dariya sosai, nima dariya nayi ina juya kaina alaman a'a, "nifa bawai kada ka ƙara aure bane bana so, idan Allah yasa bani kaɗai zaka zauna dani ba ae dole sai kayi, amma ni nafi so ka soni sosai kafin lokacin da zaka so wata", na ƙarasa ina ɓoye fuskana a ƙirjin shi, dariya sosai yakeyi ya rungume ni gaba ɗaya ajikin shi, mun daɗe a haka jifa -jifa ina jin sautin murmushin shi mai kaman sautin dariya, "Eesha na ina sonki sosai, ina roƙon Allah idan akwai rabon auren wata mata a tare dani kada Allah ya kaini wannan ranan,

ina roƙon Shi daya zama ke kaɗai ce rabona duniya da lahira," da sauri na ɗago kaina na dube shi, "nifa bance kada kayi ba, idan ni kuma na mutu fah"? Haɗa goshin shi yayi da nawa, hancin mu ma suka haɗu, "sai na zauna ni kaɗai, idan da yaran mu sai na basu kulawa sosai", lumshe ido na nayi ina sauƙe numfashi a hankali, "a'a zamu rayu tare insha Allahu", na faɗa mishi muryah a hankali,, shima shiru yayi bai sake cewa komai ba, sai chan wayan shi ta fara ringing, handsfree ya saka bayan ya ɗauka,

"morning Babban yayah, nace ko za'a barka kafito muje muyi sallama da mutanen mu, sai muƙara sa mu gaida su mummy dasu goggo da bangajjiya ko? Har gidan su Ayshaa zamuje kafin baƙin namu sutafi ko"?

Ajiyan zuciya ya sauƙe bayan yaji dogon lissafin da M.G ya mishi, "mutumin banza yau kuma nine ka yadda nadawo babban yayah ko? Tou ni dai ba'a bani izinin fita ba, amma kaɗan yi jira na ɗauki permission, duk abunda beauty tace shi za'ayi", yana gama faɗa ya kashe wayan, sannan a hankali ya maida kanshi saman nawa ya kwantar, shiru banji yace zai fita ba, sai nine nayi ƙoƙarin cewa, "yayah baka tashi ba"? Ƙara matseni yayi cikin jikin shi sosai yace, "sai abun da kika ce ranki ya daɗe, ina jiran umirnin ki ne", miƙewa nayi yana taimaka mun har na tsaya, murmushi na mishi ina gyara tsayuwana, "amma zaka chanja kaya ko"? Kallon kayan yayi yana yamutsa fuska yace, "dole na ae yadda kika ya mutsani nida kayan ae na chanja, don wannan ɗan sharrin idan ya ganni dasu zai kunce mun zani agaban yayah na", ya faɗa yana wucewa ɗakin shi, nidai dariya yabani wai na ya mutsa shi,.

Cikin shiga mai kyau ya fito, hannuna ya riƙo mukayi hanyar waje, har jikin motan shi na raka shi, kafin ya shige yayi mun kiss a goshi yana buɗe motan ya shige, "tsaraban me zan kawo miki beauty"?

Ɗan lumshe ido nayi nace, "kadawo mun da kanka gida lpy", idon shi a ɗan lumshe yace, "alƙawarin yau babu ihuu da faɗa ko? Kinga daga jin muryan ƙaton banzan nan ya zama cikakken ango ya barni"?, juyawa nayi da gudu cikin gida, shi kuma murmushi yakeyi har ya bar gidan.

Ana idar da sallan la'assar su Aunty B suka zo dukkansu, fitan A.G kuma babu daɗewa wasu daga familyn maman shi suka zo tare da Hudah, mun kai 1hr tare dasu suka mun sallama sukace saura su shiga gidan heedayah, cike da mutuntawa muka rabu, na haɗa musu tsaraban biki na basu, don sunce mun gobe zasu koma, yan matan cikin ma basu kayan kwalliya da su panties, ina ganin Hudah sai farin ciki takeji sosai, don har fuskanta ya nuna hakan.

Kallo nah hafsy takeyi tana ta ƙunshe dariya, dana gajji na tambayeta meye takewa dariya, aiko sai ta kunce da dariyan gaba ɗaya, hadiza ce ta koreta tace ta tashi suje su gyara kitchen ita da ummitah, suna tura baki gaba suka wuce, hira sosai muka sha tare dasu Aunty B, sai wurin 5:00 suka tafi, har lokacin kuma A.G bai shigo gidan ba, amma dai ban zauna ni kaɗai ba, idan wayyan nan sun tafi tou wayyan chan zasuzo, haka har akayi magrib sai ƙafa ya ɗauke, don ko abincin rana da aka kawo baƙi ne suka ci, hafsy sun mun wanke -wanken duk abunda aka ɓata, zuwan su kuma dama diffent jus Aunty b da Aunty j suka kawo mun, aka shirga su a babban friedge ɗina, duk wanda suka zo akwai abunda za'a basu da kuma cake da cin-cin dasu diblan, ganin bana sallah hafsy sai da takasa shiru tace, "Adda yaushe kika gama period? Naga baki daɗe dayi ba kuma gashi yanzu ma kina yi"? Hararanta nayi nace, "a'a wannan na ƙaryah nakeyi munafuka", dariya duk suka fara, har sai da zasu tafine Aunty B ta riƙo hannuna muka tsaya a ɗaki, "kada ki damu Ayshaa, sau da dama irin haka yana faruwa da amare, sai kiga lokacin period ɗinsu bai kai yadawo ba amma ya dawo, majority tsoro ne wasu kuma kayan gyaran mata da suka sha ne sai kiga period ya dawo, kada ki damu komai zai daidaita, kedai don Allah tsaftan nan dana sanki da shi ki dage, don yanzu zai dinga yawan shige miki ne, ki dage ko sau ɗaya kada yaji ƙarnin jinin nan, duk da nasan ke bada ga nan ba a kula da jiki amma plz ki ƙara beatyn besty", rufe fuskana nayi ina murmushi, Aunty j na tsaye a gefen Aunty B itama tace, "gaki dasu humrah da miski sisto plz kada kiyi wasa da ƙamshi a jikin ki, kuma kada kiƙi bashi haɗin kai ku kwana wuri guda duk yana ƙara shaƙuwa a tsakanin ku kinji"? Kai na ɗaga musu ban yadda na buɗe fuskana ba, "idan akwai abunda ya rufe miki baki gane ba, gani ga jeeddah, ko wacce acikin mu babu shamaki ki ƙira mu wayar miki da kai kinji bestyn mu, saboda dukkanmu gobe monday zamu koma", Aunty B ta faɗa, buɗe ido na nayi ina kallon su kaman zanyi kuka, "amma dai su yayah zasu zo mun kafin ku tafi ko?" dariya Aunty j tayi tace, "tare ma duk zamu zo idan za'a wuce airpot".

Har waje na rakasu suka tafi.

Bayan nayi wanka na saka wani rigan material ɗina wani pink riga da skirt, humrah na shafe jikina gaba ɗaya da shi, dayake duk kayana su fatima da Aunty B sun turara mun, sai yazama humrah nake shafawa kiji kaman yanzu akayi kabbasa, wasu oils masu daɗin gaske da Aunty ma'u ta kawo mun irin na saudin nan duk na shafe jikina dasu, hatta gashi na yasha nashi haɗin ɗan borno, ana idar da ishaa A.G ya shigo, daga ganin shi duk a gajjiye yake, ina biɗe mishi ƙofa ya buɗe mun dukka hannayen shi alaman nazo, nidai kasawa nayi na nuƙe kaina ina murmushi, ganin haka ya ƙaraso da kanshi ya rungumeni, duk da wunin da yayi da kayan amma ƙamshin shi mai sanyin daɗin nan ne ke tashi a jikin shi, "baƙauyiyar amaryata mai gudun miji, yau kin sakani duk naji kunya a gaban abokane na, kowa ya gane bana fallin angwaye yadda M.G yake tayi, abu kaɗan zaka ganshi yana ta ɓallewa da dariya, har naji haushi nace ya tashi ya tafi, wani abokin mu ɗan Gombe ne yace yaga alaman A.G yana ruwa kenan, ko an kulle ƙofa an barni da sintirin

parlor ko kuma baƙon mata ya hallara, sai da barrister ya dakatar dasu suka barni asha iska."

Sunne kaina nayi a ƙirjin shi bance komai ba, murmushi yayi ya ɗago fuskana yace mun zaije yayi wanka, har ɗakin sh yaja ni muka shiga domin yayi wankan, bakin gadon ya ajiyeni ya wuce toilet, nidai da ƙyar na daure nayi mintuna kusan uku zaune a ɗakin, bana so yaga kaman ina gudun shi ne tun shigowan mu ban juya na fita ba, don wannan mummunan ciwon kanne naji ya sake sauƙo mun, bayan na zauna kuma sai nafara jin kaman numfashi yana mun ƙaranci a ɗakin, amma duk da haka na daure na zauna ina ta haɗa uban zufa, chan sai naga kaman inuwa ta gefena ya wulga, da sauri na juya inda naga wulgawan abun, amma banga komai ba, chan naji kaman an wulga ta gab dani, ai babu shiri na miƙe nayi waje, ina fita kuma na sauƙe ajiyan zuciya, saboda sai naji wani ni'imah ya sauƙa mun lokaci ɗaya, wurin dinning naje na Ƙara gyara filet ɗin abincin da aka kawo mana, ina zaune a parlon shiru ni kaɗai, chan sai gashi ya fito jikin shi da wasu kayan bacci blue masu kyaun gaske, suma shot wando ne da riga armless shigen irin wanda yasaka jiya, sai ƙamshin shi mai daɗi da yakeyi.

"yarinyar nan ya zanyi ma cire miki wannan kunya da tsorona ɗin nan da kikeyi ne kam? Wato baki son ganin fitowana haka ne yasa kika gudo nan ko"?

Murmushi nayi don jin bai gane abun da ya fito dani ba, bai ce komai ba ya miƙo mun hannun shi na kama ya miƙar da ni, dinning mukaje mukaci abinci, dayake gudun kurna ne aka kawo mana yasha naman kaji rugu-rugu a ciki, "beauty wannan abincin yana ɗaya daga cikin favourite ɗina, sai ki kula da duk abincin da mummy zata na aikowa har tsawon 1week, don duk abunda nake so takeyi mum, tun daga breakfast, lunch, dinner".

Ɗaga kai nayi alaman naji, sannan muka ƙarasa, muna shan kunun aya, shima ƙura mun ido yayi yace, "ina son kunun aya sosai, yaji kwakwa da madara Eesha", murmushi na mishi ina ƙara maida hankali akan duk abunda yace yana so, a haka muka gama na tattare kayan nayi kitchen dasu don wankewa, shikuma inaga ya wuce ɗakine don ya wanko bakin shi, ina gama wankewa kuwa na wuce nawa side ɗin, nima baki naje na wanke sosai, daga nan na ɗauki wani cwemgum da Aunty ta bani mai ɗan karen ƙamshi nasaka a bakina, na ɗan ƙara shafa humrah kaɗan a jikina, ina zama a bakin gadona ban daɗe ba sai gashi ya shigo, kaina na ɗago na dube shi yana ƙarasowa kusa dani, wato Aunty nice ina son A.G a zuciyata, idan na kalli yadda idon shi suke a lumshen nan sai naji kaman na saka ihun daɗin mijina ya haɗu, ya haɗu mun irin yadda nake so miji ya kasance mun, amma ina wannan banzan tsoro da kunyan da nake ji sun hanani zuwa ga mijina, kyakkyawan mijina ma aji.

gefe na ya zauna, sannan ya saka hannun shi ya matso dani jikin shi, kaman wanda nake jiran hakan kuwa na lafe sosai a jikin shi na kulle idona, "beauty kin gudo kin barni, a ɗakin nan kike so mu kwana ne"? Naji ya faɗa, nidai ban ce uffan ba ina lafe a jikin shi mai taushi da ƙamshi kaman bana namiji ba, "ki chanja kaya ki saka na bacci tou beauty, wannan yanzu ae kin gajji da shi ko? Gashi A.Gn Eesha yana son ganinta da kayan bacci", murmushi nayi, bayan na ɗan ja lokaci na daure nayi namijin ƙoƙari na tashi na wuce na buɗe walldrove na ɗauki kayan baccina masu ƙamshin daɗi, riga da wando armless pink colour, haɗawa nayi da wani hijab tsayin shi ya kai gwaiwa na, wucewa nayi zuwa toilet, ina shiga wani zuciyar yace mun na sake yin wanka, haka na haɗa ruwa mai zafin gaske nayi wankan, pad na chanja bayan nashafa mishi misk ajikin shi, ina saka kayan na shafa misk ajikina da wasu oils dana riƙo su a hannuna, hijab ɗin na ɗaura akan kayan da suka amshi jikina, wando bai ƙarasa chan ƙasa ba sosai, rigan kuma armless ne, tsaraban daya kawo munne, tun lokacin naci alwashin saka kayan ranan farkona, saboda sun mun kyau a ido da kuma jikina sosai, fitowa nayi zuwa ɗakin da ƙyar, ina buɗe Ƙofan ya maido da kallon shi kaina, amma lokaci ɗaya ya ɗaure fuskan shi, "kada ki ƙaraso mun da wannan abun a jikin ki, bana son haka beauty", ya faɗa babu sassauci a fuskar shi da muryan shi, babu yadda na iya haka na daure na cire, jikina har rawa yakeyi saboda kallon da naga ya bini da shi, ƙafa yana sassarɗewa na wuce na maida hijab ɗin walldrove na ajiye, zan juyo kenan naji ya eungume ni ta baya, ajiyan zuciya yake saukewa da sauri da sauri, ni kuma ɗakin ne naji ya mun dummmm, ga lokaci ɗaya naji kaman na cika ɗakin tam, sai zuciyata da ta fara tafasa kaman ana hura mun wuta, bakin cikin daya ƙaru mun kuma jin sautin muryan A.G da ada yake mun daɗi, yanzu kuma naji shi babu daɗin sauraro yana ta jera ƙiran sunana kaman yaron da yake neman uwarshi ta shayar da shi, "Beauty! Eeshaa!! Baby nah!! Plz ki barni ajikinki", ai babu shiri naji zuciyata zata fashe, bansan ina da wani masifaffen ƙarfi ba sai da naji nayi jifa da A.G yayi taga-taga kaman zai kai ƙasa sai kuma ya dafa bango ya tsaya, idon shi da suke masifan lumshen nan duk naga ya buɗe su lokaci ɗaya ya ƙura mun su, "haba bawan Allah me kake nema dani ne kam? Ka kama hanya kabar ɗakin nan kafin na murɗe wuyanka kowa ma ya huta, wani irin fitinane haka"? Na furta ina jin kaman bakina zai yage da nake maganan tsabar girma da kaurin muryana, da sauri A.G ya runtse kunnen shi da hannun shi duka biyu, hattah idon shi a kulle suke yana tsaye wuri ɗaya, ni kuma gefe ɗaya sai hakki nake sauƙewa babu kakkautawa, kaina nayi saurin kawarwa lokacin danaga ya buɗe idon shi da duk sukayi ja yaƙura mun su, "Eeshaa ta na miki laifine kam? Kina period babu abunda zamuyi kawai nazo jikinki ne na ɗan samu relief a zuciyana, plz Eeshaa nah plz", ya haɗa dukƙa hannayen shi guri guda yana roƙo na, hanyar waje na nuna mishi bada son raina ba, "ka fita ko nayi jifa da kai", jaka nasamu kaima da gaya mishi cike da tsawa, amma baiji ba sai ya ƙara takowa kisa dani, aiko yana zuwa na zabga wani uban ihu da ƙara na kai mishi duka da yaguni, da ƙyar ya iya haɗani wuri ɗaya ya matse ni, kokiwa muke tayi har ya samu ya kwantar dani akan gado, duk ya haɗa zufa lokaci ɗaya ga numfashin shi dayake ta

sama da ƙasa, alaman abun shi yana kusa, ganin naƙi barin kukuwan yayi sauri ya ɗagani, hannu yasaka a aljihun shi ya ciro Inhela ya shaƙa, duk sai hakki yakeyi, ni kuma ina ta zabga kuka ina kwance, zama yayi gefe ɗaya ya kama kanshi yana ta sauƙe numfashi a hankali, zuwa wani lokaci abun ya ɗan lafa mashi kaɗan, ina ganin shi ya tashi yaje ya buɗe ɗakin ya fita, sai a lokacin naji normal kuka ya taho mun, duk sai naji tausayin A.G a zuciyata, ni kam mai yasa nake mishi hakane? Bawan Allah nan ko auren dole aka mun dashi bai chanchanci haka da ga wurina ba ko don darajan yayah Ahmad, ballantana Allah ne kawai yabar wa kanshi sanin irin so danakeyiwa A.G, shiru zuwa wani lokaci naga bai dawo ba, sai naji babu daɗi, tashi nayi nabi bayan shi, ko ma ciwon shi ne ya tashi ban sani ba?.

Parlor na nafito kawai sai na ganshi ya haɗa Uban tagumi yana zaune a parlon, ɗaguwa yayi ya kalle ni yadda na tsaya ina ta rera kuka, kallona yayi sannan yace, "kije ki kwanta tunda haka kike so, zan barki har sai ranan da tsoron ya bar jikinki, don naga alaman an razanaki da maganan aurene kawai beauty", kallon shi nakeyi ina share wasu hawayen da suka gangaro mun, "tou ae naga kaman numfashinka yana wani iri,"

Murmushin dole yayi yace, "yalafa kije ki kwanta".

Na daɗe tsaye a wurin ni ban tafi ba ni banje inda yake ba, shi kuma ko sake kallona bai sake ba, dana ga nafara jin bacci a tsayɘe sai na koma cikin ɗakin na kwanta, yiwa dai irin najiya ne, ina kwanciyar wani mummunan mafarkin na fara, wannan karon ihu nasaka a cikin baccin, in farkawa naga A.G riƙe dani yana tambaya na meye ya faru?.

Ajiyan zuciya na samun nutsuwa na sauƙe, a hankali nace mishi, "mafarki ne nayi", tashi tsaye yayi yace, "bakiyi addu'a ba ko? Ko kuma kina tunanin zan biyo bayanki ne"?

Girgiza kai nayi alaman a'a, sannan na gyara kwanciya na, shiru yayi a tsaye yana kallo na, chan yace, "beauty meyasa kike tsoro nane"?.

Buɗe ido nayi na dube shi, don lokaci ɗaya naji kaina yana wani sarawa, girgiza kai nayi alaman a'a, ba tsoron shi nake ba, "tou ki daure na kwana ɗaki ɗaya dake mana", tura baki gaba nayi kaman zanyi kuka, ganin haka yasa ya jiya ya fice a ɗakin.

Washe gari wurin ƙarfe 3:50pm sai gasu yayah Ahmad da iyalensu A.G ya musu jagora har parlor, ae bansan lokacin dana felfelo da gudu na rungume yayah muhammad ba, daɗi nakeji kaman nayi shekaru bamu tare, dukkan mu dariya muke yana rungume dani, yayah Ahmad na kallo yana gefen A.G, ae da sauri shima naje na rungume shi ina dariyan jin daɗin ganin su, "chaɓ yau munaga wariyan launin fata, wato baki maraba da mu sai yayunki ko"? Aunty B ta faɗa tana kama haɓa, kunya naji na rufe fuskana da hannun yayah Ahmad, shi da A.G sai dariyan abunda nayi sukeyi, haka naje na musu oyoyoyo dukkansu, duk da Aunty B ta wani kawai da kai, hannun areef na riƙo muka wuce kitchen, drinks na zuba saman tray na juyo zan fito sai ga A.G, shigowa yayi ya karɓi tray ɗin ya ajiye a gefe, buɗe hannun shi yayi yace, "zoki mun nawa oyoyoyo ɗin ko kuma mu kwana a kitchen ɗin nan," tsayawa nayi cike da mamakin shi, ganin bazai bani janya ba yasa na rufe idona naje na shige jikin shi, aiko rungume ni yayi a jikin shi sosai yana juyi dani a hankali, chan nace, "tou bari na kai musu ruwa plz A.Gn Beauty",

Sakeni yayi yana murmishi yace kawo A.Gn Eeshaa ya ɗauka, ke ki huta ko"? Ban ja maganan ba na miƙa mishi, na koma na haɗa cake dasu chinchin na fito da su, kallona yayah muhammad yake cike da murmushi a fuskan shi, nima murmushin nayi na koma gefen shi na zauna, bayan angaisa ne yayah muhammad ya sake mana nasiha sosai da ƙara mana shawarwari na rayuwa mai kashe jiki, daga nan yayah Ahmad yake cewa su tashi a wuce, turo baki nayi gaba ina "yayah tafiya kuma"? Dafa kaina yayi yace "ke da nan da 2weeks zaku dawo Abujan? Sai kin gajji da gani ae, inaga kullum ma ina gidanki", dariya matan suka mishi suma lallai kuwa A.G yasan ya auro yar gatan ƙanwa, shima dariyan yayi muka rakasu har mota, driver ne yake jiran su, hannu na riƙe dana yayah muhammad, ina kallon yayah Ahmad ina ƙara mishi godiyan motan daya bani, "albishir sisto"? Da sauri na kalle shi nace "goro kyakkyawan yayah na mai nasarori", dariya sukayi har da A.G daya wani kafe ni da ido yana murmushi, nasan bai taɓa karo da ganin dogon hira na bane, "Yayanki ya biya muku makkah ku uku, ummie, Aunty B, ke," ƙara nayi na rungume yayah muhammad, dariya ya fara yace "bai miki ɗayan ba ae? Shima ya biya mana ni da shi da jeedah shi, bana mu shidah zamu ƙetara insha Allahu," inji yayah muhammad da maganan shi ba mai tsawo bane sai takama, duk da shirun yayah Ahmad yafi shi magana, shi kaman A.G ne sai ta ɓaci kakanji su, hawaye na fara narasa waye zan kuma je gare shi, ganin haka yayah muhammad ya jawo A.G ya manna mishi ni yace, "mu zamu wuce sai kayi aikin rarrashi, maganan makkan naji barrister yace ya nemi izinin ka ko"?

Murmushi A.G yayi yace, "ranka ya daɗe ya gaya mun mungode Allah ya ƙara girma, ya mun gaggawa ne ae, naso ni nafara kaita, amma yanzun ma bai ɓaci ba tunda babban yayah ne, muma tare za'aje damu, nida M.G da wife ɗin shi", "masha Allah abu yayi kyau sosai, Allah ya zaunar daku lafiya, zamu wuce sai kun iso", haka mukayi sallama A.G na riƙe da hannu na har suka wuce, juyowa yayi ya kalle ne yana murmushi, "hajiya Eeshan A.G", juya ido nayi na mishi fari da su,

"Alhaji A.Gn Beauty" kiss ya kai mun kan lips ɗina yana murmushi, hannu na ya kamo muka shige gida.

Daren yau ma dai abunda ya faru haka ya faru, ranan kam da ƙyar numfashin shi ya daidaita, har naji tsoro nayi tunanin neman taimakon M.G ko zai kai shi asibiti, hanawa yayi ya shaƙi inhelan shi kawai, kuka sosai nayi ranan, don har hannu na nasaka na shaƙe wuyan shi, da ƙyar ya ƙwace kanshi a lokacin, kwana biyu ya biyo bayan ranan bai sake gigin cewa zamu kwana ɗaki ɗaya ba, ni duk sai naji abun babu daɗi, amma ya na iya, tsoro nake ji sosai, kuma wannan ɗabi'un ban san ina yin su ba, lokacin kawai suke zuwa mun, kuma ko nayi ƙoƙarin na hana kaina yi abun sai yaci tura.

Sati ɗaya da yin auren mu da daddare bayan an idar da sallan ishaa sai ga M.G da Heedayyah sun zo, nidai har ranan period ɗina bai ɗauke ba, kuma ni 4dys nakeyi amma wannan karon tsabar tsoron da nakeji abu yaƙi tsayawa.

Da fara'a sosai na karɓe su bayan ya buɗe musu ƙofa sun shigo parlon yazo ya mun magana, rungume ni heedayah tayi tace, "Aunty Aysha ina ta son leƙowa mu gaisa amma bai barni ba sai yau, gashi nasan yayah ba zai barki ki fito ba nasani," murmushi nayi bayan mun zauna na gayar da M.G, ya amsa yana ta murmushi, ya wani ƙara mun ƙiba a ido yayi haske, sai wani fallin angonci yakeyi, kallon A.G nayi sai naga kaman ya mun baƙi ma, duk sai naji tausayin shi ya rufeni, gaisawa mukayi da heedayah sai tace " Aunty muje parlon ki mu gaisa da kyau", ta faɗa yana wani riƙo hannu na, "bana son gulma da faɗin abun da bai dace ba kinji ko Heedayah, don naga wani sabon falli kike ji dashi" muryan A.G ne ya doki kunnen mu, duk sai naji kunya ya kamani, don nagane mai yake faɗi, ita kuma zaro ido ta fara ta kasa cewa komai, sai M.G ne dayake dariya yace, "jeki Giwata kuyi hiranku keda Auntynki," ya juyo kan A.G kuma yana "don Allah a daina firgita mun Giwata" nidai ban ji mai A.G yace ba, hannunta na jawo muka wuce, don ya wani haɗa girar sama da ta ƙasa.

Muna zama na ɗauko mata drinks da ɗan abun taɓawa, hannunta ta dafa a ƙirjinta tace, "Aunty nifa hala baifi sai ɗaya ko biyu naga yayah A.G yana murmishi ba, dariya kam hala bantaɓa gani ba, amma tsawan shi yafi sau million yake mun, gara ma Adda Huda suna ɗan zama suyi hira, ballantana da aka fara sayyayyan auren ku

kullum zakiji shi ƙus-ƙus da ita, dama shirun su iri ɗaya ne, nikan haushi na yakeji tun farko saboda yawan magana na, na ɗauka yanzu tunda na girma har da miji zai sarara mun tunda abokin shine, ashe abu kam bazai chanju ba, dafah fita zanyi da gudu da naji tsawan shi, tou ganin Giwa na yana wurin ne fah na ɗan kama kai", dariya ta bani wanda har yasa na ɗan dara, wato dai halin su ne yazo ɗaya da M.G shiyasa Allah ya haɗa su, "yana murmushi da dariya mana heedayah", na faɗa ina dubanta, ya mutsa fuska tayi ta ɗauki coke ta buɗe ta ɗan kurɓi kaɗan ta ajiye, "Aunty yanzu yana iya ce miki I Luv u kuwa"? Dariya sosai maganan ta ya bani, ina kallon ta yadda tayi wani tagumi ta ƙura mun ido, nace mata " bai miki kama da wanda zai faɗan bane ko"? Ya mutsa fuska tayi tana lumshe ido ciki irin nashi, don na lura dukkan su ukun suna da wannan ɗabi'an, kuma dukkan su suna kama, amma yafi kama da ita sosai, haline shida Huda yafi zuwa iri ɗaya, amma ita Huda tana da fara'a, don kuna haɗa ido zata maka murmushi, amma babu surutu sosai, "Aunty ae kam bai mun kama ba, nasan dai kam zaki na shan doka da umurni, ko ba'a miki tsawa ba kam zaki sha aika, da umirni, ke kam sai dai kiji ko kiga ana cewa wasu I Luv U", ta faɗa tana riƙe haɓa, nidai murmushi nayi na sake wannan maganan na tambayeta yayh mummy? Tana lafiya ta gaya mun, inda tace mun idan ana gobe zamu tafi chan zataje ta wuni ae, shine nace zan tambayi A.G nima sai muje tare, amma bazan wuni ba zanje na ƙarasa a gida, kallo na tayi tace, "Aunty kema A.Gn kenan kike gaya mishi? Aiko gara ki sama mishi wani special suna wanda zaiji ya banbanta shi da wanda ya saba ji",

Juya ido nayi nace, "kinsan shi special ne, sunan shi ma special ne, bawai ina so kunnen kowa ya ji bane", dariya ta kwashe da shi tana tafa hannu, "Adda kawai ki faɗa babu kunya, bakiga shi ko agaban mummy da daddy Eeshan shi ko beauty yake faɗa ba? Ranan fah har daddy ya manta yace mishi ina yaje ya daɗe ko yana wurin beauty ne"? Kowa sai da yayi dariyan daddy, shine rana na biyu da naga murmushin shi, kinga kema ako ina yakamata kada kiji kunya, bakiga Giwana ko gaban waye ba Giwa yake ƙirana ba"? Muryan A.G naji yana ƙiran ta tafito su tafi, baki ta turo gaba bayan ta amsa tace, "yanzu fah shine zai kore mu don a barshi ya hole da amaryan shi bawai Giwana bane zaice mu tafi, kawai bazai bar mutum ya ɗan yi hira ba", ta faɗa tana miƙewa tsaye, nidai murmushi nakeyi ina gyara gyalen jikina, "Aunty yaushe zaki shigo kiga nawa gidan"? Ta faɗa tana fita da sauri jin ya sake zabga mata ƙira, na bayanta nabi da sauri ina murmushi, a parlor muka same su suna tsaye suna magana, M.G ne ya dube ni fuska cike da fara'a yace, "tou amaryar babban yayah mun gaishe ku munga wuri yayi kyau, muna sa idon ganin ku muma", ya faɗa yana miƙawa A.G hannu, hararan shi yayi suka fice waje, bayan su muka bi muka raka su har bakin namu Gate ɗin, bayan sun fita ne ya rufo Gate ɗin ya juyo inda nake tsaye ina jiran shi, kallona kawai yayi ya wuce ciki, a baya na bishi amma duk sai naji babu daɗi da yayi gaba ya barni.

Parlon shi nima ma zauna ganin ya zauma yana rage volume ɗin T.Vn, "yaushe zaki gama wannan abun?" ɗago kai nayi na kalle shi, ganin yayi magana amma kuma

idon shi yana kan T.V, shiru nayi bance komai ba, har ya gajji ya juyo ya kalle ni, sunkuyar da kai ƙasa nayi nace, "na ban sani ba, 3dys yake yi ko 4dys, amma wannan naga har yanzu", shiru yayi yana kallona, chan yace, "saboda kin sakawa ranki tsoro ne Eesha ta, dom Allah ke yanzu heedayah basu baki sha'awa ba? Yakamata ki saki jikin ki dani, nifa ba dodo bane, and kuma bazan taɓa cutar da ke ba beauty, kinsan yadda na damu da ke kuwa? Kin san yadda abun nan yake hanani bacci da chin abinci kuwa? Don Allah ki daure ki cire tsoron, ni bazan miki komai ba sai abunda kika amince, nidai naga kin sake dani kin daina wayan nan ihun da dukan da kikeyi kawai".

Hawaye na share na haushin kaina da nake ji, saboda Allah meye amfanin abunda nakeyi, ni wallahi wannan period ɗin da bai ɗauke bane ma yafi bani haushi, don insha Allahu idan ya ɗauke ko mutuwa zanyi zan bashi kaina, "kayi haƙuri A.G nah insha Allahu idan ya tafi zan daina jin tsoron, kuma zan dawo ɗakinka",

"why not tun yanzun ki dawo mu saba kafin ya tafi? Na miki alƙawarin bazan taɓa miki wani abu da bako so ba ko da babu yardar ki a kai kinji beauty nah", ya faɗa yana dawowa gefe na ya zauna, hannun shi duka biyu ya saka ya riƙo nawa cikin nashi, hawayena suƙa zubo mun a fuskana, bana komai ba sai najin ciwom sabon halina da nakeyi yanzu, ina jiran naji wannan chanjin yanayin halin nawa yazo mun amma sai naji shiru, shima ina ankare da shi, ganin shiru baiga ina wasu idun ba ya saka ya matso jikina sosai, Allah sarki A.G jikin shi wani rawa yakeyi kaman zan ƙwace mishi ne, Rungume ni yayi sosai ajikin shi, nidai ban hama shi ba, haka ya ringa zuba mun kisses kaman zan cinye ni, har zaman kujeran ya gagare mu muka faɗo ƙasan carpet ɗin dukkan mu, har a haka yana rungume dani bai sake ni, ido kaɗan na buɗe jin hawayen shi da yake taɓa mun fuskana, tausayi sosai ya bani, gashi banji wannan tsoron ba amma kuma ina jini, laluɓeni ya fara yi babu nutsuwa a tare da shi, sai wayan shi tafara ringing, a hankali ya buɗe odon shi ya diba mai ƙiran, ido ya zubawa wayan bai ɗauka ba bai kuma kashe ba, ganin shirun da yayi ya ƙurawa wayan ido yasaka na miƙe da ƙyar na wuce nawa side ɗin don nayi wanka na chanja pad ɗina da nakeji duk ya ɓaci, ido ya bini da shi har na kusa wucewa tukun naji yace, "M.G ne, ko me yake so bayan yanzu suka bar gidan"? Juyowa nayi na kalleshi, duk kunyar shi lulluɓe dani nace , "tou ka ɗauka mana, ko akwai abunda ya manta ne", na faɗa ina kallon shi, ga hawaye kuma kan fuskan shi, "ok, zaki dawo yanzu ko na biyu ki"? Murmushi na mishi murya a hankali nace, "wanka zanyi, zan dawo insha Allahu".

Shima murmushin yayi ya ɗaha mun giran shi duka biyu, sannan ya ƙira M.G, nidai wucewa nayi ina jin yana masifan "wallahi bazan buɗe ƙofa ba, ƙaton bamza yarinya ƙarama tana juya ka kaman waina, sai da safe ta aiko a ɗauka mata, tun da har yanzu sakara ce tana jefar da abu a unguwa", nidai dariya nayi a zuciyata nace, "shi ae juya shi akeyi, kao kuma kuka ma ake saka ka, gara shi yasan daɗin abunda yasa ake juya shi, kai hanya kawai ka ɗan kama amma aka saka ka kuka, ranan da

ka ƙarasa kam ina ga sai maƙota sun taru rarrashi", na faɗa ina shigewa toilet, wanka nayi da ruwan mai zafi sosai, bayan na fito na shirya cikin wani three quater da riga armless fari sol, cotton ne mai kyaun gaske, gashi na nasaka a wani hula mai net mai kyau na bacci, bayan nagama kintsawa na ɗauki chwemgum na jefa a bakina, hijab har ƙasa na ɗauka na ɗaura akan kayan na fice, parlon shi na shigo naga baya ciki, a zuciyata nace ya shige ɗakin shi don yayi wanka, hanyar ɗakin na miƙa, buɗe ɗakin nayi na shiga, baya ciki sai dai ina jin ƙaran shi a toilet yana wanka, ɗakin yayo sanyi A.C akunne ga ƙamshi daya kama ɗakin sosai, chan kan kujeran dressing mirrow na je na zauna ina jiran fitowan shi, ban daɗe ba kuwa ya fito ɗaure da wani farin towel a jikin shi, sai ƙamshin shower gel da yayi wanka yakeyi, kallona yakeyi fuskan shi ɗauke da murmushi, ganin haka na sunkuyar da kaina ƙasa ina wasa da yatsuna.

Ina jin shi a gaggauce ya shiryah, ƙamshin danaji ya cika ɗakin mai daɗin gaske ne yasa na fahimci ya gama shiryawa, amma duk da haka ban ɗago fuskana ba, har gaba na ya ƙaraso ya tsaya, "Eesha kinyi kyau sosai", naji sautin muryan shi a kaina, ban ɗago ba amma nayi murmushi kaɗan ina bin yatsun ƙafan shi farare sol da kallo, hannun shi ya saka ya riƙo nawa, jin haka yasa na ɗago kaina na dube shi, aiko da sauri ya sake ni ya ɗan ja baya da sauri ya ɗan saki ƙara kaɗan, tashi nayi tsaye da sauri ina kallon yadda yake yarfe hannun shi, a hankali nace, "wani abune ya sameka"? aikuwa babu shiri najo yayi ƙasa da sauri yana toshe kunnen shi, bakin shi kuma yana furta, "innalillahi wa'inna ilaihir raji'un", matsawa kisa da shi nayi da sauri nima na durƙusa ganin ya riƙe kanshi da dukkan hannayen shi yana runtse ido, "A.G na lafiya"? Na faɗa duk jikina yana rawa, ihuh ya saka iya ƙarfin shi yana cewa, "ki matsa a kusa dani bana jin numfashi sosai, ki matsa ana shaƙe mun wuya na, wayyo Allah subhanallahi", da sauri na matsa a kusa da shi jikina yana rawa, birgima ya farayi yana jan numfashi da ƙyar, ganin haka ya saka na fice a ɗakin da sauri, parlor na naje da gudu na ɗauki wayana, rasa wa zan ƙira a wannan lokacin nayi, wani zuciyar yace na ƙira M.G, kuma nayi tunanin bai kamata ba, tou ko gidan mu zan ƙira? Nan ma nayi tunanin me zance? Kawai sai naji na fashe da kuka, zama nayi a bakin kujera hannu na riƙe da wayata, ban daɗe ba sai na ganshi ya fito daga ɗakin shi ras da shi, binshi nayi da kallo ganin ya wuce kitchen, tashi nayi nabi bayan shi, friedge ya buɗe ya ɗauki ruwa, kafa kai yayi ya shanye duka goron, nidai har lokacin kallon shi nake idona na zubar da hawaye, a jiyan zuciya ya sauƙe sannan ya fito zuwa parlon, yadda bai mun magana ba haka nima ban ce da shi uffan ba, three sitter yaje ya zauna ya ƙura mun ido, "beauty meyasa kike chanja muryoyinki kala-kala ne? Ɗazu gaba ɗaya kin maida muryanki kaman na wata tsohuwa, daga baya kuma ki ka mayar kaman na wani namun daji, babu daɗi sauraro ga wani irin zafi kaman wuta da jikinki yayi, nikan baki sonane"? Hawaye ne suka zubo mun a ido na sharrr, buɗe baki nayi zan bashi amsa kawai sai naga wani shadow yabi ta bayan kujera da sauri, aiko tsalle na daka na faɗa saman cinyan A.G babu shiri, hannu na saka na toshe bakina da na zabga ihun tsoro, a

razane shima ya kallen yace "lafiya Eeshaa tah"? Waiwayawa nayi na kalli hanyan ƙofan kitchen don jin kaman an buɗe ƙofan an kuma rufe, "A.G na, naga kaman an wuce ta jikin kujera, kuma sai naji an buɗe kitchen an rufe, ni wallahi tsoro nakeji", rungume ni yayi yace, "babu komai beauty, kice kike firgita kanki da kanki, ni bansan waye ta baki wannan shawara na jin tsoron ba? Gashi bayan kina tsorita kanki har nima kin fara bani tsoro wallahi, ɗazu fah....." Sai kuma yayi shiru bai ƙarasa ba, chan yace "tashi muje ɗakina", girgiza kaina nayi alaman a'a, "ɗakinki zamuje"? Ɗaga mishi kai nayi alaman ehh, aiko ɗaga ni yayi chakk ya kashe wutan parlon muka wuce chan cikin bedroom ɗina babban, kwantar dani yayi saman bed ɗin ya sumbaci goshina da hanci na da saman lips ɗina, nidai ido kawai na bishi da shi ganin ya wuce zuwa kashe wutan ɗakin, ƙatt naji ƙaran ya kashe wutan ɗakin, sannan ya juyo ya nufo inda nake kwance, aiko uban ihuu na rabza, domin ganin ya rikiɗe ya koma mun mummunan baƙin mutumin nan da nake mafarki da shi, ga wasu labta labtan haƙura da ya buɗe baki yana mun dariya, ihun da nake yi ne yasa ya koma da sauri ya kunna wutan ɗakin, jikina yana rawa na ɗago kai na dube shi, "A.G kada ka kashe wutan ɗakin please, ka barshi tsoro nakeji," ido ya zuba mun na tsawon wani lokaci baice komai ba, chan kuma sai ya juya ya fice a ɗakin batare da yace mun uffan ba, kuka na fashe da shi ina maida kaina saman ƙafufuna, nidai ranan ban san yaya akayi bacci ya ɗauke ni ba.

Tun daga wannan ranan bai sake nuna zai zo inda nake ba, zamu zauna muci abinci tare, idan baƙi sunzo zamu karɓe su tare, idan dare yayi zamu zauna a parlor ɗaya muna kallo muna ɗan hira jefi -jefi, amma bao sake kusanto da kanshi kusa dani ba, a haka har ya saura kwana biyu ne tafiyan mu Abujah, da dare muna zaune a parlon shi muna kallo naji yace, "Eesha na gobe ki shiryah zakuje kuyi sallama da mummy da su goggo da gidan Dadda, sai kuma chan gida wurin su ummie" Farin ciki naji sosai saboda zan fita nima, gashi jiya da hafsy tazo take ce mun wai raliya zata tafi da sabeer, amma Abba ya hana ta, gashi yanzu yaron yana ta laulayin haƙori, sai zazzaɓi da gudawa yakeyi, da ta tafi dashi wani kulawa zata iya bashi," duk dama hankalina yana kan na ga yaron ne wallahi, shine babban farin cikin zuwa na gidan kuma, don zanyiwa Abba magana yaushe zan ɗauke shi? Don Abuja muna gama hutu zan dawo bch, zai sama sai anyi hutu naje, A.G ma zuwan shi zai zama ba akai akai ba, yaron zai ɗebe mun kewa, ranan nayi bacci cike da farin ciki, kuma Aunty nice nifa wannan period ɗin har ranan bai ɗauke ba, sai dai yawan zuban shine ba sosai ba.

Washegari tun 9:00am nagama shiryawa, A.G kuma don gadara har lokacin bai ma tashi a bacci ba, sinasir nayi mai yawan gaske, don tun an idar da sallan asuba nake aikin yin shi, ga miya nah mai daɗi da kyaun gani a ido, duka gidajen da zamuje n

zuba musu a cooler daban -daban, akwai dambun kaza da aka mum, shi kuma na nemi ɗan madaidaicin bucket na zubawa Daddy ɗaya, ɗaya kuma na kakane, wato Alhaji Inuwa.

Ɗakin shi na shiga na samu ya wani ƙura A.C ya duƙunƙune yana bacci, zama nayi na yaye duvet ɗinna ƙura mishi ido, jin sanyi na ratsa shi ya sa ya ɗan buɗe lumsassun idanun shi kaɗan yana kallo na, marairaicewa nayi alaman don Allah ya tashi, jawoni yayi na faɗo kanshi, duvet ɗin yaja ya rufe mu ruf da shi, hannu na saka na sake yayewa, buɗe idon shi kaɗan yayi yana kallona, "baby muyi bacci please", ya faɗa yana ƙara jawo duvet ɗin, ban barshi ba ya rufe ba na saka hannu na yaye duka nace. "please mana A.G na ka tashi mu tafi, nifa na musu abun karyawa ne fah, kada su riga su karya kuma", na faɗa ina turo mishi baki gaba, kiss ya manna mun a lips ɗinnan sannnan ya tashi zaune da ƙyar, juyar da kaina gefe nayi saboda bana son ganin tashin shi, duk da jallabiya ce a jikin shi, amma shi yanzu ya koyi rashin kunya, a gabana sai ya cire kaya, "yarinyar nan baki son zaman lafiya wallahi, breakfast ɗinma sai kin wahalar da kanki kinyi har da su? Hmmm amma aikin miji kam an kasa sauƙewa, sai na sarakune" Ya faɗa yana ɗan dariya kaɗan, hararan wasa nabi shi da shi har ya wuce toilet, gyara mishi ɗakin nayi tsaf na feshe shi da turare, bayan na fita a ɗakin naje shiryah duk abunda zamu tafi dasu, kunun gyaɗa na fari sol na cika flask biyu da su, ɗaya babbaɓ wanda zamuyi break agidan su A.G nah, ƙaramin kuma na ummie nane, don tana son sinasir da kunun gyaɗa.

Tayashi ɗaukan komai nayi muka kai mota, yana ta mitan an hana shi breakfast wai sai munje gida, nidai ko kula shi banyi ba na shige mota ina ta dariyan shagwaɓan shi, gidan mu yafara zuwa ya tsaya a Gate, ɗaure fuska yayi sosai bai kalle ni ba, ƙiran hafsy yayi a waya ta fito, coolern na ummie da flask ɗin kunu ya bata, yace ta gaishe da ummie sai mun shigo anjima, gwaliyo take ta mun har ta koma gida, kallon fuskar shi daya murtuƙe kawai nakeyi, nasan don kada nace zan sauƙa ne yasa yayi haka, daga nan unguwar winti mukaje gidan kakan shi, nan ma a waje ya barni ya ɗauki cooler da ɗan ƙaramin bucket ɗin dambun ya shige dashi, bai wani daɗe ba ya fito ya miƙa na gidan goggo, sai da muka ɗauki hanyar gidan su tukun ya juyo yana kallona fuska a sake yace, "yan mata na mai tsoron aure yayah kike"? Hararan shi nayi cikin wasa na juyar da kaina, murmushi yayi ya saka ɗayan hannun shi ya matsa chinya na yace, "Eesha wai yaushe period ɗin nan naki zai ɗauke ne kam? Nifa na matsu fah, haba M.G sai wani kallon banza yake mun kullum wanda na rasa dalili".

Dariya nayi ina ture hannun shi da yake wani matsa mun cinya kaman mai shirin matsan gyaɗa, "ni ae ban san yayah zanyi bane"? Na faɗa ina sunkuyar da kaina, bai juyo ya kalle ni ba yace, "ki daure ki cire tsoro na a ranki zai ɗauke", shiru nayi

bance uffan ba, gannin haka ya juyo ya ɗan kalle ni kaɗan, dai dai maigadi yana buɗe mishi gate da yayi horn a lokacin, muna shiga muka hango motar M.G a parke, murmushi A.G yayi yace, "wayaga bita zoi-zoi M.G har an hankaɗo shi ya iso", ya faɗa yana wani munfukin murmishi, wanda nayi imani iyakan ta nan cikin mota ne, muna fita zai koma kaman ba shi ba, muna parking ya juyo ya kalle ni, "wallahi kada naji kina ziban zance a gaban ƙananun yaran nan, don bana son raini, idan sun raina mun mata ni suka raina kinji ko"? Ɗaga mishi kai nayi alaman naji, ganin haka ya ɗan sunkuyo ya sumbaci lips ɗina, murmushi ya mun nima na mayar mishi, sannan muka buɗe motan muka fita tare, taimaka mishi nayi muka ɗauki kayan da muka zo da su.

Muna shiga parlon na hango M.G zaune Shi da Daddy, T.V kunne yana aiki, su kuma Suna hira, lokacin kuma mummy ta fito daga hanyar kitchen heedaya na biyota a baya hannun ta ɗauke da filet da soyayyen ƙwai sai cup da tea a ciki, direct dinning muka wuce muka ajiye kayan da yake hannun mu, ɗan ihu kaɗan heedayah tayi tana mun oyoyoyo, hararanta da A.G yayi ne taɗan nutsu, amma idon ta nakaina tana murmushi, nima murmushin nayi idona yana kanta, "har kun iso kenan"? Na tambaye ta bayan na ajiye abunda yake hannu na na juyo hannu na riƙe da handbag ɗina, "ai ina ga da ƙyar idan ba a ƙofan gidan nan 8:00am ta musu ba, gashi ni tunda tazo bata barni na huta ba", mummy ta faɗa tana dungure kan heedayah, Murmushi nakeyi na ƙarasa har parlon inda mummy suka ƙarasa da A.G suka zauna, har ƙasa na je na tsuguna na gayar da Daddy, amsawa yayi cike da jin daɗi, haka itama mummy na gaisheta tana amsa cike da jin daɗi, M.G na gayar, murmushi ɗauke a fuskan shi ya amsa da, "yauwa matar babban yayah, kun samu iso ko"? Nidai murmushi nayi bance uffan ba, hararan shi A.G yayi ya kawar da kai, bayan heedaya ta gaishe da A.G ne ta mun alaman mu wuce ɗakinta, ban wani ja ba nabi bayanta muka wuce, "Aunty naje na soya miki egg ɗin ne ko zamu ci wannan na zubo miki tea"? Murmushi nayi nace, "ga abun breakfast na taho mana da shi, kada ki wani wahalar da kanko, ci kawai ke kaɗai", dariya tayi tace, "aiko naga kuloli kawai ban isa nayi wani rawan kai akai bane tunda tare kuka zo da yayah, amma ae dana biɗe na fara ci, yanzu sai sun gama hirarrakin su tukun ace mu fito" ta faɗa tana hararan tea ɗin hannun ta, nidai murmushi nayi bance mata uffan ba, aiko baifi wasu mintuna ba mummy ta ƙwala mana ƙira, da sauri muka fita zuwa parlon.

A dinning muka same su dukkansu suna zaune, fuskanta cike da farin ciki ga murmushi a kai tace, doug ashe hidima sosai kika mana haka? Gaskiya abu yayi kyau Daddyn kuma sai yabawa yake tayi", ta faɗa tana zubawa daddy a filet, shima Daddy godiya yayi har yasa naji kunya a lokacin, kallon mu tayo bayan ta zubawa mijinta da kanta yadda zai musu, ta cika musu cups da kunun gyaɗan tace, "tou kowa tazo tayi saving kanta da mijinta, kuna na kuma kada a zuba dayawa, a saka

dai-dai a bar wa mijina sauran," ta faɗa kowa yana mata dariya, da sauri heedayah ta matso zata zuba, hararanta A.G yayi yace, "ke matsa a wurin don Allah, ki bari wanda ta hanakanta bacci tayi ta fara zubawa, ke ae haka kika bar kanki da mijinki don lalaci da shirme kika taho", aiko baya taja ta tsaya, daga Daddy har Mummy dariya sukeyi, shi ko M.G hararan A.G yakeyi baice mishi komai ba, mayar da kallon shi yayi kan matar shi yace, "dawo nan kafin ya kai miki naushi a kyakkyawan fuskanki, su gama zubawa mu ko sauran nasu ne bamu da matsala zamu ci," ya faɗa ya na maida ita gefen shi ta tsaya, ni dai cike da kunya na zubawa A.G na, gaban shi na ja filet ɗin da cup na ajiye, sannan na zuba ƙwaya biyi anawa filet ɗin, ban zuba kunu ba nace, " heedayah ki haɗa mun tea mana" mummy ne rayi charaf tace, "a'a doug bazaki sha kunun bane? Ko kinfi son tea ɗinne"? Ina murmushi na amsa mata da ehh, dama nayi saboda sune kunun, ni nabar nawa a gida ae, tea ɗin heedayah taje ta haɗo mun, sannan tazo taa zubawa M.G na shi a filet ɗin, kunu ta zuba mishi ta miƙa misho, ta ɗauko cup zata zuba A.G ya dakatar da ita, "kema ki zuba tea ɗin yadda kika ga ita ma tayi karan barwa Daddy, idan kunun kike so idan kin kuma gidanki ki dama", dariya sosai mummy da daddy sukayi, inda Daddy yace "godiya nake ranka ya daɗe, ita bata kawo ba zata shanye mun kununa mai daɗi" ya faɗa yana kurɓan kunun, mummy kuma cewa tayi, "ni banga ta inda wani abu zai shiga cikinta bama idan ba fitina ba, shigowan ku fa ta gama soya egg ta haɗa da tea, shiyasa daga ita har mijinta suke labta uban ƙiba, tsabar cinsu yayi yawa, sun bar mun kai da matar ka baku ƙara ko taki ɗaya ba, sai ma ramewa da kuka sakeyi", kunyar maganan mummy naji har na ɗaga kai na kalle shi, shima kallo na yayi ya mun alaman ae duk nine na jawo.

"Daɗin abun ma ae an bawa mijinta, kuma bazai shanye duka ba zai bar mata ko Giwata? Kuma muna zuwa gida zan zo na karɓe na matar ka data ajiye a raba musu", ya faɗa yana duban A.G yana dariya, harara A.G ya zabga mishi sannan yace "ke jata kuje ɗakinki zata fi sakewa ta ci sosai, saura kuma ki cinye naki kici nata", ya faɗa yana ƙara mun sinasir biyu akan wanda na zuba, ita dai heedayah ta tura baki gaba, parlon kuma duk dariyanta sukeyi, haka muka wice ɗakinta wanda hakan kuma wallahi ya fi mun daɗi.

Muna shiga kuwa tace, "kaii Allah ya baki fitinannen miji wallahi Aunty, kuma akwai sauran kunun ne a gida kika bari"? Nidai murmushi nayi na zauna akan lazy chair da yake garkame a ɗakin nata ƙwaya ɗaya, "akwai amma baifi cup 2 ba, wa mijina na ajiye dama ba wa kaima ba, saidai ku raba ke da shi idan mun koma", na faɗa ina fara kai sinasir ɗina baki, "chaɓɓ sai dai kawai na lallaɓa daddy anjuma idan babu kowa ya sanmun, amma cup biyu kam bazai bani ba, kinsan yadda yake shan kunu kuwa shi da Daddy? Ae yafi son kuni ma akan tea, Giwa ne kawai yake son tea, amma mijinki kam dama kunu ya sameki, nima ina so, idan na dama baya kyau ne kawai yasa banayi," ta faɗa tana zama a bakin gadon.

Bayan su daddy sun gama sun kuma parlor ne na fita na samu mummy zata tattare, hanata nayi na kwashe nakai kitchen, ina jin A.G ya ƙwalawa heedaya ƙira ta fito da sauri, nuna mata hanyar kitchen yayi ya juya, shigowa tayi muka wanke komai muka gyara, tambayanta nayi mai zamu ɗaura na rana? Ya mutsa fuska tayi tace, "don Allah Aunty fito mu tafi, akwai fa mai yiwa mummy girki, breakfast ne kawai ta keyi da kanta, don Allah fito bacci nakeji, yanzu ina fita mijinki zai koroni",

Dariya nayi nace, "gaskiya yai mu zamiyi abinci, nemi wuri kawai ki zauna, idan zaki iya ki fakaici idon shi ki wuce, haka ko akayi ficewa tayi ta gudu, dariya ma ta bani sosai.

Friedge na buɗe na ɗauki mama na wanke na ɗaura akan gas, sannan naga akwai markaɗaɗɗen kayan miya shima na fito da shi, ina haka sai ga mummy ta shigo, "doug kaii jeki huta akwai wacce zata zo ta ɗaura" ta faɗa tana ƙarasa shigowa, "mummy yai kam ta huta, babu komai zan yiwa Daddy abinci da hannu na yasaka albarka", na faɗa ina ajiye kayan miyan, "doug wanda kika kawo mana for breakfast ma ae ya saka albarka, Allah ya muku albarka gaba ɗaya, Allah ya zaunar daku lafiya a gidajenku," haka dai na ribace ta tabari na ɗaura, muna zaune ta ɗauko shuwaka ta gyara, ina ganin haka nagane tuwo takeso ayi kenan, haka na zage na tuƙa tuwon shinkafa mai kyaun gaske, muna hira da mummy da taja kujera ta zauna, duk abinda na nema sai ta nuna mun, haka na haɗa miya ne wanda yaki cyryfish da egusi da stockfish ga nama sosai, muna ciki A.G ya shigo, "ina wannan malalaciyar ita kuma take"? Mummy na murmushi tace, "don Allah amata haƙuri ta kwanta bacci ne"

"mummy ita ba mace bace da ku zaku fito kuna aiki ita kuma taje ta kwanta don son jiki? "

Mummy tana murmushi tace, "kasan kowa da yadda abu yake zuwa mishi, ita na lura ciki ta samu na gaggawa, kuma yazo mata da bacci da yawan ci, wata macen ranan da aka kaita ranan take samun ciki idan an dace, tou inaga yar'uwaka haka nake tunani, saboda haka kayi haƙuri kaima naku da irin na shi salon zaizo" kunya naji ya kamani, don kuwa yace mun ita fah Mummy bata jin kunyar watso zance, saboda haka idan kinje kiyi haƙuri ki saba da haka, sunkuyar da kaina nayo, amma kawai sai naji A.G da wani zance, "mummy ita wannan ae ban san meye matsalanta ba, tunda aka kaita fah har yau period ɗinta bai tsaya ba, ke da yake tsohuwar ma'aikaciyar jinya ce may be zaki san meye matsalan"?

Shiru nayi tsabar kunya naji kaman zan nitse a ƙasa, murmushi mummy tayi tace "shikenan son babu komai, insha Allahu zamu yi magana da ita, zanje koma menene," "yauwa mummy idan kuma tsoro ne ta saka a ranta please ki hanata ni wallahi....." sai kuma yayi shiru yana kallon mummy yakasa cewa komai.

Dariya tayi tace, "babu komai son zamuyi magana da ita, bari ta gama abincin mu shiga ciki, idan akwai matsala ma zan sani idan babu ma duk zan sani, ka gajji kuma tou kayi haƙuri, kasan mata da matsala iri-iri", murmushi yayi ya juya ya fice, nidai ji nayi bazan ma iya juyowa na kalli mummy ba wallahi, kai amma A.G bai san meye kunya ba naga alaman shi wallahi, har wa mummy yake iya irin wannan bayanin? Gashi yana magana kaman zai mata kukan nan na shi na jaraba, naga alaman shima idan a kusa da ita yake shagwaɓaɓɓene.

Yana fita kuwa ta sauƙe ajiyan zuciya mai ɗan ƙarfi, nidai kawai kasa sakewa nayi da ita, ita dai sai ɗan jana da hira takeyi nakasa sakewa, ana ƙiran sallah kuwa ta wuce ɗakinta, amma sai da tagaya mun, ina tuƙa tuwa kuwa ya shigo kitchen ɗin, ɗan hararan shi nayi na juyi na cigaba da tuƙawa, haɓan shi ya ɗaura a kafaɗa na bayan ya saka dukka hannayen shi akan kunkumi na, "beauty zanje nayi sallah", dakatawa nayi da tuƙin nace, "A.G nah ya kamata ka iya gayawa mummy wannan zance? Tou yanzu idan ta tambayeni mai zan iya cewa"? Dariya yayi mai ɗan sauti kaɗan, "ki ƙirani zan mata bayani, don ni kam a hargitse nake, ina buƙatar matata", dakatawa nayi da abunda nakeyi cike da mamakin shi nace, "don Allah ka wuce masallacin kada mummy ta shigo", "alwalan ne baby ya lalace" aiko ji nayi kaman na nutse a wurin, gaskiya ashe A.G bai da ta ido, Allah ya taimakeni sai naji muryan Daddy yana neman shi, da sauri ya fice a kitchen ɗin, ajiyan zuciya na sauƙe, na furta "Allah ka taimakeni har mu bar gidan nan kada A.G ya sake kunyata ni, ni dama ashe haka yake ne"? Na faɗa wa kaina da kaina, ina gamawa na wuce ɗakin Heedayah lokacin mummy ta tashe ta tayi sallah, tana yamutsa fuska irin an tashe ta tawuce toilet tayi alwala, bayan tayi sallah ne tace mun zataci abinci sai muje gidan su goggo, haka ko akayi suna gama cin abincin muka wuce gidan Goggo, na ɗauka mummy zata mun magana sai naga bata ce komai ba, gidan Dadda mukaje aka gaisa, mun kai good 1hr a gidan muna hira, godiya sosai Alhaji da Dadda suka mana da zamu tafi, suka mana addu'a sosai, gidan Goggo muka shiga da chan, mun samu goggon kwance babu lafiya, mura da zazzaɓi ne ke damunta, haka muka zauna a parlonta, godiyan sinasir ita ma tayi mun sosai, daga baya ta mana nasiha na zaman lafiya sosai, anan take gayawa M.G mai aikin gidan Alƙali zuwan ta biyu tana so taje gidan shi taga matar shi ta mishi murna, dariya yayi yake gayawa Goggon ya sayi wani ƙaramin gida nan kusa da su na wasu magada ɗaki biyu ne a ciki sai ɗakin girki da ƙaramin store, zai bata ta koma ciki insha Allahu, albarka sosai goggo ta saka mishi, "Aunty nice idan baki manta matar ba, itace wacce ta zabgawa M.G itace a bayan shi Lokacin da yaje gidan alƙali yin waya yana yaro", jijjiga kai nayi alaman na tuna labarin matan, ana sallan la'asaar A.G ya ɗauke ni muka wuce gidan mu, har parlorn ummie ya shiga suka gaisa, ya daɗe zaune a parlon tunda Abba baya nan, hajiya ummah bata nan sunje gaisuwan rasuwa itada Aunty Rakiya da Mamah chan garin su Abba, bayan ya tafi ne nida hafsy muka je na duba jikin sabeer a chan side ɗin mamie, tunda muka shiga take wani bina da kallo daga sama har ƙasa, gaisheta mukayi na duba jikin sabeer da

yake bacci, Allah sarki duk ya zabge har abun tausayi, ganin irin kallon da take bina da shi yasa hafsy tace, "Adda muje ko", hararanta mamie tayi ƙasa-ƙasa, muna dab da zamu fice najiyo muryanta tana, " Ayshaa auren sati biyun ne ya wani zabgar da ke haka? Ko baya baki irin abinda ake baki a gida? Ko yafi ƙarfin kine a auratayyah duk ya figar da ke haka"? Nidai murmushi nayi bance mata komai ba, ganin bazanyi magana ba yasaka ta ja tsaki tace, "tou Allah ya rufa asiri, hala a jininku ne keda habiba rashin dace da aure", "ajinin habiba dai, Adda kam ae banga wanda yakaita dace da miji ba a gidan nan, sai dai muce Allah yasaka a madadin su, miji ya ganka yana sonka kam ae duniya ne, idan har ba tura mishi kai akayi ba kam ae kayi dace babba" habiba ta faɗa tana riƙo hannu na muka fita, ina jin mamie na aika mata da zagi, amma ko ajikinta har muka fita ina mamakin halin hafsy na rashin barin sai ta kwana.

Ɗakin ummie dukan mu muka ƙule, daɗi nakeji kaman zanyi yayah, sai ina ganin gidan ya dawo mun sabo, sai shiri ummie take mun na kayan marmari kaman ba kwanan nan tagama na auren ba, har kilishi ta saka aka mana, ga dambun kaji da ta saka aka sake mana, daga ni har su yayah ta haɗa mana kaya rigijib, hira sosai mukeyi har aka ƙira sallan magrib, anan hafsy tace na shiga nayi alwala, "bana sallah hafsy" kallo ta bini da shi cike da mamaki, chan tace "wani irin baki sallah Adda? Yaushe naje gidan ki nasamu bakiyi? Sau uku kikeyi wannan watan kenan"?

Girgiza kai nayi ba tare da nufin komai a raina ba nace, "tun wancan bai ɗauke ba, kusan 2weeks fah? Har tsoro nakeji kada jinina ya ƙare", na faɗa ina maida kaina kan ummie da ta shigo lokacin, "ummie kiji wai Adda mensis ɗinta 2weeks bai tsaya ba amma take zaune bata ce wa Yayah A.G suje asibiti ba, sai jininta ya ƙare mu shiga uku", ta faɗa tana wani harara na kamar nice ƙanwar ita kuma yayar.

Kallona ummie takeyi cike da mamaki, "tun yaushe kika fara sokancin ɓoye mun abu irin haka eyyeh ayshaa"? Ummie ta tambaye ni, "ummie wallahi na ɗauka zau ɗauke danaga ya rage zuwa, amma kullum sai naga akwai yananan, ni ummie tsoron aje asibiti ace wani allura za'a mun nakeji", kallona ta tsaya tanayi, chan kuma sai tace "hafsy tashi kije kiyi sallan", tashi hafsy tayi ta fice, sannan ummie kuma ta mayar da duban ta kaina, "yanzu shi A.Gn bai ce miki komai ba? Tun angama bikin ku da kwana nawa ya dawo miki"? Ummie ta faɗa, tura baki nayi gaba saboda nasan yanzu za'ace asibiti, "ummie ni baice komai ba, amma yau da mukaje gidan su naji yana gayawa mummy, inaga tunda tsohuwar ma'aikaciyar asibiti ce zata san yadda za'ayi", ummie ni tun ranan da aka kaini yazo mun, yau kusan 15dys ko 16 ne ma" na faɗa ina duban ummin.

Shiru ummie tayi tana kallona, sallaya riƙe a hannunta, "Ayshaa ni wallahi ban san ina zaki kai rashim wayo ba, ae komai kiga baki gane ba sai ki ƙira ki gaya mun, Allah ya rufa asiri, bari muji me ita mummyn zatace tukun, idan abun bai yiwuba sai

ki daure kuje asibiti kicire tsoron nan", kaman an taɓo mun abunda yake damuna, "ummie ni tsoron gidan ma nakeji, kinsan abubuwan da nake gani kuwa a gidan"? Kʻawai nasamu bakina da gayawa ummie duk abubuwan da suke faruwa, ido ta zare tana kallona, chan tace, "innalillahi wa'inna ilaihir raji'un, shine kuma da ga ke har A.Gn baku gayawa kowa ba? Tou ae wannan kam akwai matsala babba a gidan, hala ma wani matattaran shaiɗanu akaje akayi ginin shine suke damun ku? Gaskiya wannan ba abun da za'ayi shiru bane, bari nayi sallah na ƙira mummyn shin, ae sai suje su sauƙar miki da jininma suce kunzo musu gidan su, gara ayi sauƙan qur'ani kafin abun yayi yawa", tana gama maganan ta fara sallah.

Shiru nayi ina tunanin abubuwan daya faffaru a gidan, ko dai aljanu ne a gidan na faɗa a zuciyata, sai naji zuciyata ya yanke lokaci ɗaya, kada fa sune suka shiga jikina har nake jin abunda nakeji akan A.G? Hankali na nane naji duk ya tashi, a haka hafsy ta shigo ta sameni, "Adda kinyi azkhar ne? Naga kinyi shiru kina tunani"? Lokaci ɗaya sai naji hankali na ya ƙara tashi, tunda naje gida na kuwa nayi azkhar ko karatun qur'ani? Hala ko addu'a idan zan kwanta ma na manta ranan da nayi, ko alwala idan zan kwanta kuwa inayi? Sai naji ƙwaƙwalwata ta kasa tuna inayi kp banayi, sai kawai nabar tunanin na fara azkhar ɗin da hafsy ta tuna mun, ima idar wa na karanta surutul mulk.

Ummie tana idar wa ta juyo kaina, "aysha kima addu'a kuwa"? Shiru nayi kaman zanyi kuka na ƙura mata ido, "hmm Allah ya kyauta, hala daga ke har A.G ɗin kunje kuma wasa da addu'a", nidai bance mata komai ba, wayanta ta ɗauka ta ƙira mummy, ina jin su suka fara magana akan matsalan da nagayawa ummie, nan itama mummy take mata bayanin ae tun ɗazu da A.G ya mata maganan period ɗin ta samu sister ta sukayi magana, suma dama sunyi tunanin ko jinnu ne, don bayan A.G ya kawo ni daya koma ta ajiye shi sunyi magana sosai, inda duk abunda yake faruwa sai da ya gaya mata, nan Mummy tace tou zata samu Daddy ta gaya mishi A.G ya wuce aikin shi chan Abuja shi kaɗai, ni ka abarni a bauchi a gwada magani agani, itama Ummie tace yanzu kuwa zata gayawa Abba, duk yadda ake ciki zuwa safiya zataji ta, bayan sunyi sallama ne ummie ta titsiyeni da wasu abubuwan da mummy ta gaya mata, kawai sai naji kuka yazomun, kuka na ringayi ummie na mamakina, chan dai ta rabu dani ta ƙira Abba ta gaya mishi, amma Abba sai yace wai babu matsala idan anyi hakan, amma ba shi ko ummie bane suke da hurumin nema mun magani, saboda gudun zargi ta barni a gida na ko wurin surukuwata suyi mana magani, don shi Abba cewa yayi yʻat'shi lafiyanta qalau sai dai matsalan daga A.G ne, amma kafin ayi komai shi yafi so muje asibiti akan issue ɗin jinin, haka dai ummie ta rabu da shi don tasan halinshi, ba lallai bane dama ya yadda da maganan wasu iskokai, sai wurin 9:00pm A.G yazo ɗaukana, aikuwa ummie ta haɗamu ta

mana kacha-kacha akan addu'a, da kuma zama da alwala, kanshi kuwa ya sunkuyar yana ta bada haƙuri, domin ta nuna mishi dole amatsayin shi ma namiji kuma babba ya dinga hankaltar da ni, har mota hafsy ta rakamu, naso maje naga sabeer, amma ummie ta nuna mun hanyar waje, haka na wuce hafsy tana dariya don ita ta kitsa komai.

A mota babu wanda yace komai daga no har A.G duk munyi shiru, a haka muka tsaya ya sayi Bread da nama sai yougouth muka shige gida, a parlor ya zauna ya ƙura mun ido, "Eeshan A.G kin san ni duk mummy ta razanani da gidan nan? Kinsan nifa mutum baya bani tsoro, don ko ɓarawo ne sai muyi gaba da gaba da shi banji tsoro ba, amma aljani? Gaskiya ina tsoro," ya faɗa yana nuna mun ledan naman wai na ɗauko filet da cups muci, kallon shi nayi baki a buɗe nace, "ni kaɗai zanje kitchen ɗin? Gaskiya ni tsoro nakeji, kawai kazo muje tare", ido ya ƙwalo mun yace, "me zai sameki? Ga wuta ga komai, jeki nima ae dare nake tsoro ba wai yanzu ido naganin ido ba," zama nayi ina kallon shi, ganin da gaske yake bazai rakani ba, "A.G na bazaka raka Eeshan kaba"? Na faɗa ina rausayar da kaina, miƙewa yayi yace, "wuce muje kin cika tsoro," bayan mun ɗauko na zuba mana tare babu yadda na iya, don ni wallahi kunyar cin abincin tare da shi nakeyi, amma yadda ya takura ni haka nake daurewa nake ci, "ina ga gobe tafiyan nan ba zai yiwu damu ba beauty.

Washe gari da safe mummy ta ƙira A.G, bayan sun gama wayan ne yake cemun mummy tace yau na maida ki gidan ta, ni kuma mu wuce tare dasu M.G, kinaga babu matsala

komawanki wurin mummy"?

Hararan wasa na mishi nace, "akan mummyn batawa bace kenan da zai zama matsala don na zauna a wurinta"?

Murmishi yayi ya girgiza kan shi , "mummyn muce, ni na ɗauka zasuce kije wurin ummie don zaki fi sakewa".

"Mummyn ma zan sake, ae mama nane itama, kuma a haka ne ma zamu saba idan mun zauna wurina ɗaya, ummie ae ta ɗanani tunda ga haihuwa, yanzu kuma turn ɗin mummy ne" na faɗa fuskana ɗauke da murmishi, jawoni yayi jikin shi ya rungume, daidai saitin kunne na yace, "ni kuma yaushe nene turn ɗina"?

"forever" na faɗa murya chan ƙasa, shiru mukayi har zuwa wani lokaci, kiss ya mun akan lips ɗina, sannan ya ɗago fuska na muka haɗa ido, murmushi mukayi wa junan mu, murya ƙasa-ƙasa yace " muje na tayaki haɗa kayan ki, ki ɗauki duk abunda kike so", hannuna ya kama muka wuce ɗakina, jaka ɗaya na zuba duk abunda nake buƙata, tunda a gari nake idan basu isa ba zan iya shigowa na ɗauka, haka muka lalace a parlor muna ririta junanmu kaman zai bar ƙasan ne ba garin ba,

kuma abun mamaki duk rungume ni dayake yi abun da nakeji shiru, shima taya shi haɗa kayan da zai tafi da shi nayi, danbun da aka mun nayi mishi packaging ɗin shi, haka dai na dinga jin kewan shi tun bai tafi ba.

A gidan mummy mukayi lunch, har aka yi sallan la'asaar muna tare dukkan mu a parlorn ta ana hira tare, bayan sun dawo daga mosque ne M.G shi kaɗai ya shigo, idon shi a kaina yace, "matar babban yayah kije yana miki magana, yana side ɗinmu na da", ido na mayar kan mummy, amma sai naga hankalinta baya kanmu, kallon Heedayah nayi na mata alaman ta nuna mun ɗakin, dariya tayi ta miƙe ta riƙo hannuna, har ƙofan parlon ta rakani, fuskanta ɗauke da murmushi tayi ƙasa da muryanta irin na gulman nan tace, "ki fa bar shi ya fito akan lokaci matar yayah", murmushi nayi nayi nocking ƙofan, sannan na buɗe a hankali na shige batare da na bata amsan maganan ta ba, itama tana dariya ta juya da sauri ta koma cikin gida.

Pralon babu kowa sai ƙaran t.v da A.C kawai, ƙofan dana gani a buɗe na nufa, don ƙofa uku ne a parlon, ɗaya yana kallon ɗaya a gefen dama idan kashi go, ɗaya kuma yana yamma da parlon, alama wannan ƙofan kitchen ne, wayan nan kuma ɗaya na A.G ɗaya na M.G, shiga nayi kai tsaye, a kwance na ganshi akan gadon yayi ruf da ciki, tsayawa nayi a bakin ƙofan ban ƙarasa shiga, ba don ganin daga shi sai gajeren wando, bai ɗago ya dubeni ba naji yace "shigo ki rufo mun ƙofan", banja ba na shige na rufe mishi ƙofan, har bakin gadon naje na zauna a ta gefen shi, shiru yayi na wani lokacin kafin ya mirgina ya tashi zaune, hannu ya saka ya matso dani jikin shi, idon shi a lumshe kaman baya kallona, amma nasan kallona yakeyi, murmishi nayi jin ya jawoni gaba ɗaya jikinshi, ajiyan zuciya dukkan mu muka sauƙe, "Eesha Allah yasa idan kunje asibiti ace komai lafiya qalau tsoro ne kawai, idan sunce maganin islamic ɗin ma za'ayi Allah yasa komai lafiya ne Eesha nah".

Ajiyan zuciya na sauƙe a zuciyana nace "Ameen"

A fili kuma nayi murmushi na saka dukka hannayena na rungumeshi, "A.G nah banji daɗin irin matsalolin da nake tare da su ba, nasan har....." sai kuma na kasa ƙarasa wa nayi shiru, murmishi yayi ya rungumeni gam ajikin shi yace, "kin san har na ƙosa ko? Eeshaa na lafiyan ki da kwanciyar hankalinki yafi mun wani kwanciyar aure muhimmanci, yes ina so naga mun zamu abu ɗaya kodan naga mun Haihu tare, amma nafi son lafiyanki da kwanciyar hankalinki, kawai dai zanyi kewanki ne idan na tafi wlh, gaba ɗaya bana jin marmarin tafiyan ne da zanyi babu ke, nasan M.G ɓata mun rai zai tayi da gangan", dariya ne naji ya kufce mun, shima dariyan yayi ya sake matse ni ajikin shi, munfi mintuna goma a haka sannan ya raba jikin mu ya tashi ya shige toilet, wanka yayi ya zo ya kintsa ya maida wasu kayan, yayi kyau sosai, ya ɗauko agogon shi zai ɗaura nayi sauri na miƙe na ƙarasa inda yake, hannu na saka na riƙe ina tayashi ɗaurawa, ido ya ƙura mun har nagama ɗaura mishi, "Beautyn A.G zakiyi missing ɗin A.Gn ki"?

Murmushi nayi na juya kaman zan fuce a ɗakin, rungumoni yayi yana murmushi yace, "haba yar fullo a gaya mun mana naji daɗi", ina murmishi nace, "A.G na zaku makara fa, ya kamata muje", "hmmm beauty kenan", iya abun da yace kawai ya kamo hannuna muka fice, parlon muka koma muka samu M.G a tsaye yana magana da mummy, shigowan mu kenan ya kalle mu yace, "yanzu nake shirin ƙiranka na tuna maka flight ɗinmu fah 5:00 ne ya kamata by now mun fita daga gida", ɗan ya mutsa fuska kawai A.G yayi ya harare shi, ƙarasawa yayi har gaban mummy ya ƙarasa, hugging ɗinta yayi yana wani shagwaɓe fuska, "mummy nah" murmushi tayi ta ɗaura hannun ta akanshi tace, "yarona Allah ya tsare ka a duk inda kake, Allah yayiwa rayuwaeku albarka, Allah ya baka lafiya, Allah ya kaiku lafiya, duk inda ka shiga alkhairin Allah ya isar maka" ɗagowa yayi hannun shi yana riƙe da nata aka fita har haraban gidan, heedayah sai ya mutsa fuska takeyi tana kallon mummy, dariya mummy tayi tace, "auta yayah ne ne kam"? Juya ido tayi ta ɗan kalli A.G sai kuma ta tura baki gaba hawaye yana taho mata, kamo hannunta mummy tayi tana "haba auta kukan kuma na meye? Zanzo har Abujan insha Allahu na rako doug, kuma ke kam ma ga A.G ga M.G ae kaman kina gida ne, zasu kula mun da ke nasani" kwanciya tayi a kafaɗan mummy tana hawaye, hannunta A.G ya kamo yana rarrashinta, driver ne ya matso da motan har inda muke, kallona A.G yayi sai naji kaman zan rasa shine, kaman zai tafi wani nisan duniya ne, sai naji hawaye ya cika idona, amma na daure na mayar da shi, lumshe idon shi yayi ya buɗe gaban motan ya shige, M.G kuma da heedayah suka shige baya tana ta kukan shagwaɓa, gaba ɗaya M.G ya birkice ko kunyan idon mummy baya ji yake ta jawota jikin shi yana rarrashinta, tunda A.G ya shige motan bai ɗago ya kalleni ba, ƙure inda yake zaune nayi da idona, amma yaƙi kallona, haka nayi haƙuri na maida idona ƙasa, har suka fice a gate ɗin gidan tukun mummy ta riƙo hannu muka shige cikin gidan, duk yadda tayi ta jana da hira kasa sakewa nayi, sai yaƙe kawai nakeyi.

Lokacin da suka isa sun ƙira mummy sun gaya mata, fatan alkhairi ta musu suka wuce zuwa gida, yadda nakeji suna faɗa Yayah Ahmad ne da Aunty J, sukaje ɗaukan su.

Bamuyi magana da shi ba sai wuraren 9:00 na dare lokacin na fito a wanka, ɗakin mummy ta sauƙe ni, lokacin tama parlor tana waya da Daddy, saboda shima ranan da safe ya wuce lagos, shagwaɓa yayita mun a waya wai shi kaɗai ne a gidan babu daɗi, M.G yaƙi zuwa suyi hira ya wuce gidan shi, nidai dariya nakeji amma naƙi yi, hak nayita rarrashi har da ƙyar ya haƙura, sallama mukayi yace bari ya barni na kwanta tunda da wuri zamuje asibiti gobe.

****

Da wuri washe gari na tashi, gyaran ɗaki da wanke toilet na fara yi, sannan nayi wanka, saboda na leƙo naga an share parlon ana morping, kitchen na shige na ferw doya na soya mana, ganin akwai markaɗaɗɗen gyaɗa sai na dama mana kunun gyaɗa da peppesoup ɗin kifi dana gani a freazer, 9:00 na gama komai, bayan munyi breakfast da mummy muka wuce asibitin *NI'IMA CLINIC*

wani gueiny Dr muka gani a asibitin mai suma Dr Robbin son, ƙwararrene a fannin matsalolin mata, test kusan kala uku ya bamu, sannan ya mun wasu tambayoyi, duk na amsa mishi yadda ya kamata sannan ya mun scarning, shima scarning ɗin bai nuna akwai matsala ba.

Bayan 3dys muka koma lokacin dukka test ɗin sun kammalu, shima bayani ya mana akan babu matsalan komai, sannan ya rubuta mana wasu magunguna akan mu saya, bayan 2weeks sai mu dawo, mun dawowa Mummy ta ƙira daddy ta mishi bayanin komai, sai cewa yayi babu komai a jira 2weeks ɗin su cika a koma, idan baiyi daidai ba sai a fara na gidan, haka ko akayi, bayan 2weeks ɗin mukakoma asibitin, dama tayiwa Ummie da A.G bayanin yadda akayi da Daddy da kuma asibitin, suma basu ƙi ta Daddyn ba, nan ma ya sake chanja mana magunguna kuma, bayan wasu gwaje -gwaje da akayi again, nayi 1week ina sha A.G yazo, lokacin yayi 3weeks da tafiya, ɗaukana yayi babu kunya yayiwa mummy sallama muka wuce gidan mu, shi ya tayani muka gyara gidan tsab, har sai da akayi la'asaar tukun muka gama gyara ko'ina, sannan na ɗaura mana abinci, gudun kurna na mana wanda na ɓararraka kaza guda a ciki, sai daya dawo a sallah mukaci, daga nan na gyara wurin sauran na saka a container na saka a friedge, ɗauka na yayi mukaje gidan Goggo gaisheta, don har lokacin bataji daɗin jikin ba, anan muka haɗu da ɗanta Rabiu yayan M.G, mutum mai kirki da fara'a kaman M.G, hira sosai akan ball sukayi da A.G, ni kuma muna hira da matar shi, anan muka barsu muƙa wuce gidan Daddah, sun man alƙawarin zuwa gidan mu.

Dadda sai hida take tayi dani, ga shi ƙafa ya sakota a gaba amma bata zama, daga parlon mijinta zuwa nata ma bata ganin wuyanshi, bayan mun gaisa da Alhaji inuwa na dawo parlon Daddah muƙa zauna da ita, shi kuma yana tare da kakan shi a chan, har sai da akayi Magrib tukun muƙa fito, ina ganin shi yayi bauchi club da mu, bayan fitan shi bai daɗe ba ya dawo motan ya zauna ya ƙura mun ido, ganina kallon yayi yawa yasaka na mayar da kaina gefe ina kallon waje ta glass ɗin motan, hannum shi yasak ya riƙo nawa, ina jim shi duk da haka ban juyo ba, sautin murmishin shi kawai naji, nima murmushin nayi yadda yake matsa mun hannu na a cikin nashi, muna haka aka miƙo mana ledan naman, tada motan yayi mukayi gaba,

na ɗauka gidan mu zamu wuce sai naga yayi hanyar gidanmu, daɗi naji yau zanje naga ummie, a bakin gate ya tsaya, na juya zan buɗe motan da sauri na, kawai sai naji mota a kulle, juyowa nayi ina kallonshi, sai naga yana danna wayan shi, chann babu daɗewa aka ɗauka, "ki fito mun bakin Gate" iya abunda ya faɗa ya mayar ya kashe wayan, ido na ƙura mishi cike da mamakin shi, meyake nufi bazan shiga gidan mu ba?.

Isowar hafsy wurin ya sakani ƙara shiga mamakin shi, bayan ta gaishe shi ta glass ɗim window shi da ya sauƙe mata, tana dariya ta kalle ni tace "manyan mu barka da dare", harara na mata na mayar da kaina kan A.G, miƙa mata leda biyu yayi yace, "leda ɗaya na hajiya ummah, ɗaya kuma naki ne", ɣa faɗa bayan yace ta gaida kowa da kowa, hannu ta ɗaga mun alaman bye - bye, bayan ta mun gwaliyo, bansan lokacin dana fashe da kuka ba ganin yana shirin tayar da motan shi, kallo na yayi baki buɗe, "lafiya kuwa Eeshaa"? aikuwa kukan na fashe mishi da shi gaba ɗaya, ido na zube akanshi, dariya yayi yana kama haɓa, "lafiyar ki qalau kuwa"? Turo bakina gaba nayi nace, "zanje naga ummie ne", dariya yayi yana kallona cike da mamaki yace, "nono zaki sha ne"? Hararan na mishi ina ƙara sautin kuka na, yana dariyan yaga ina ta ƙoƙarin buɗe motan, buɗe mun yayi yana kallo na yace, "jeki gaisheta ki fito da wuri, ina jiranki", ganin ya buɗe yana dariya yasa na buɗe na fice da sauri, direct side ɗin ummie na shige, a parlor na same su da hafsy, ganina hafsy ta kwashe da dariya, Ko bin ta kanta banyi ba, wurin ummie na kawai na ƙarasa ban bi ta kanta ba, ido cike da mamaki ummie take duba nah, "lafiya na ganki"? Rungumeta nayi nace , "ummie ganinki nake sonyi", murmushi tayi tace, "tou kin ganni wuce ku tafi nasan bai yi niyyan ku tsaya ba, tunda ya ƙira mai kwaɗayin nan taje ta amso saƙo", ya mutsa fuska nayi nace, "ummie kin daina sonane kam"? Jawo hannuna tayi na zauna sosai a gefenta, bayan mun gaisa tace tou na tashi mu tafi, ina shirin miƙewa muksji sallaman shi, hafsy ce ta amsa mishi, ummie kuma ta gyara mayafin ta, bayan ya shigo har ƙasa ya sunkuya ya gaida Ummie, ɗan hira kaɗan sukayi ya tashi ya fice, alama ummie ta mun na tashi nabi bayan shi mutafi, parlon hajiya mukaje muka gaisheta, daga nan dole nabi bayan shi muka wuce gidan mu.

Sabon salo, bayan munci namu naman mun haɗa da tea, sai na wuce ɗakina domin nayi wanka, shima nashi ɗakin ya wuce, na fito a wanka nagan shi zaune akan gadona yana danne danne a wayan shi, ganin haka na daure naje mafara shirin kwanciya, ina gamawa jiki a sanyaye na juyo inda yake akan gado, abun mamaki sai naga A.G a tuntsire yana ta sharara bacci, abun mamaki ya bani, ganin irin kwanciyar da yayi kaman wanda yasha wani maganin mai ƙarfin gaske, ganin haka yasa na gyara ta ɗayan gefen na kwanta bakina alekum.

Bamu muka farka ba sai da hasken rana ya hasko idon mu, a firgice A.G ya farka, salati naji yanayi na buɗe idona da wuri, "Eeshaa wani irin bacci kenan mukayi haka? Har gari fa ya waye rana ya fito,", ƙarasa faɗa yayi yana shigewa toilet ɗin ɗakina, tashi nayi zaune cike da mamakin irin baccin da mukayi, nifa daga cewa bari na ɗan kwanta kaɗan kafin ya tashi shikenan sai da gari ya waye tangararan tukun muka farka?.

Yana fitowa na shige da sauri nayi wanka da brush, bayan na fito ne naga baya ɗakin, amma ga sallaya a shimfiɗe alaman anan yayi sallan, shiryawa nayi na fice zuwa kitchen, ina cikin aiki ya shigo, rungumo ni yayi ta baya, fuskan shi ya ɗaura a kafaɗa na, har ina jin hucin numfashin shi, murya chan ƙasa yace, "Beauty jiya kawai sai nayi bacci, wani bacci mai shegen daɗi, nayi mamakin baccin danayi baby", murmushi nayi ban ba shi amsa ba, haka dai na ƙara aikin nan yana manne da ni, bayan munyi breakfast ne ya sake tambayana naga wani chanji danake shan maganin? Girgiza kai nayi alaman babu wani chanji, "inaga dai kawai a nemi maganin gargajiyan aga ko zai tsaya, ni wallahi tsoro nakeji kada jininki ya ƙare", ya faɗa duk fuskan shi cike da damuwa, nima dai abun yana damuna, amma na ƙarfafa mishi guiwa akan insha Allahu za'a samu sauƙi, wunin ranan dai haka muka ƙare shi rungume da juna, ana sallan magrib Alhaji Inuwa kakanshi ya ƙira shi akan ya taho tare da ni yana neman mu, hijab na saka muka wuce gidan.

Muna isa gidan muka samu mummy agidan suna tare da Dadda a parlon Daddan,, gaishe su mukayi dukkan mu, nidai ina zaune a ƙasan carpet na lanƙwasa ƙafafuna duka, hiran jinya na naji sunayi da A.G da mummy wa Daddah, ita ashe sai yau taji da mummy ta ƙira da safe ta gaya musu, akan ko za'a sama mana mai maganin gargajiya ko na islamic, shine Alhaji Inuwa ya ringa faɗan meyasa ba'a sanar musu da wuri ba? An bar yara suna ta fama da damuwa, yanzu mai maganin ne yazo shine aka ƙiramu, nidai tunda naji sunce mai maganin yazo naji hankalina ya tashi, wani tsoro ma duk sai ya rufe ni, kadafa aje ina da wani matsala ne tuntuntuni.

A parlon A.G ya barmu ya wuce wurin Alhaji, nidai kaina yana sunkuye a ƙasa ina wasa da yatsuna, sukuma suna ta hiran su kaman uwa da yar'ta, duk sun ban sha'awa kaman ba surukune ba.

Alhaji inuwa ne ya ƙira wayan Dadda yace muzo parlon shi dukkanmu, da ƙyar na miƙe ƙafana na bi bayan su, duk inda ƙofa yake ajikina zufa yana fitowa, cike da tsoro da wani fargaba da ban san daga ina yake ba suka runtumo mun, a haka dai na cigaba da jan ƙafana har parlon Alhaji, da sallama a bakina na shiga parlon, su huɗu muka same su a zaune a parlon, Alhaji, A.G, sai wani dattijon mutum kan shi da rawani sai jikin shi da Alkyabbah, sai gefen shi kuma wani matashin dattijo ne, wanda a ƙallah zai iya kai shekaru hamsin, nan ma ƙasa na nema ta gefen mummy na zauna, itama mummyn a ƙasa kan carpet take zaune, A.G na a ƙasan naga ya zauna, Daddah ce kawai ta zauna akan kujera kusa da Alhaji, gashe da Alhaji nayi ya amsa mun fuskan shi cike da murmushi, ga annurin dattaku a fuskan shi, mayar da kaina nayi kan wannan Dattijo mai rawani aka nayi, sai naga shima gaba ɗaya fuskan shi a kaina, gaba nane yayi mummunan faɗuwa, saboda haka nayi saurin sauƙe idona ƙasa, murmushi yayi ya maida kanshi kan Alhaji yace, "naji dukkan bayanan ka Ahaji, amma kuma ko ma aljanine ya ke sakata haka tou aljanine na ture, domin daga shigowan ta naga inuwan shi yana mara mata baya, amma insha Allahu komai zai daidaitu", ɗago kaina nayi da sauri na dubi A.G da mukaji muryan shi yace, "Aljani kuma Ranka ya daɗe"? A firgice yayi maganan, daga dukkan alamu abun ya bashi tsoro, murmushi dattijon yayi bai bashi amsa ba, Alhaji kuma sai ɗaga kai yakeyi kawai, daga nan alaramman mutumin ya ƙira sunana "AYSHAA", ɗago kaina nayi ban iya amsawa ba, sai idona danaji suna cikowa da hawaye, alama ya mun dana taso naje gaban shi, ban tashi ba sai idona dana mayar kan A.G, shima kallona yake duk hankalin shi a tashe, Alhaji ne ya sake ƙirana da nazo gaban wannan dattijon, babu yadda na iya ne kawai ya sakani ƙarasawa gaban mutumin, kuma kada kiyi tunanin da ƙafana naje gaban shin, a'a samun kaina nayi da ja da gindi har na ƙarasa gaban shi, miƙawa matashin dattijon hannu yayi akan ya miƙo mishi jakan da yake gefen shi,

Tambaya ya fara mun game da ire-iren mafarkan da nakeyi, da kuma yadda jinin yake zuwa, akan da yawa ne ko kaɗan,? Buɗe baki nayi zan mishi bayani amma naji kaman an naɗe harce na, juyawa nayi da sauri na dubi A.G ko shi zaiyi mishi bayani, amma shima sai naga alaman jira yake yaji mai zance, juyowa nayi zan dubi mutumin kawai naji ya saka mun wani roban faro da yake ɗauki da wani ruwan abu kaman ruwan nono, fari mai ɗan kauri, amma azaban abun a hancina kaman an fasa mun bom a tsakar kaina, haka naji zafi da ƙarfin abun acikin kaina, nidai abunda zan iya tunawa shine naji na yi ihuu iya ƙarfina, sannan na miƙe zan tashi naji muryan mutumin yana umurtan A.G daya riƙeni, daga nan ban san meya faru ba, sai wuraren ƙarfe tara na dare na farka na ganni rungume a jikin A.G, mummy na riƙe da hannayena, Dadda kuma tana zaune a gefen mummy hankali duk a tashe, gefe ɗaya kuma Alhaji ne zaune da wayannan mutanen, farkawa na ne naji mutumin na hamdalah, sannan ya miƙe tsaye shida abokin tafiyan shi, sallama yakeyiwa Alhaji akan gobe idan Allah ya kaimu da safe ɗayan zaizo, ka duk yadda ake ciki su neme shi, haka Alhaji ya miƙe domin ya musu rakiya, A.G daga inda

yake zaune rungume dani ya ke yiwa mutanen sallama, godiya sosai naji su mummy da Dadda suna musu, a haka suka fice tare da Alhaji, tambaya na mummy tayi zan iya tashi mu wuce ɗaki? Juya kaina nayi gefe, da ƙyar na iya buɗe bakina nace, "mummy bana jin ƙafana a jikina", ido ta mayar kan ƙafana a ɗan tsorace tace, "doug ga ƙafan ki, ko kina jin suma miki ciwo ne"? Lumshe ido nayi ban sake magana ba, daga nan naji A.G ya saɓeni kawai yayi hanyar ɗakin Hajiya daddah da ni, lumshe idonayi saboda wani irin ƙunci da nakeji a cikin zuciyata, a haka yaje ya kwantar da ni a ɗakin kan gadon Daddah, zama yayi a gefe na yana tambayan abun da nake so? Nidai a cikin zuciyata bana jin ina son tankawa kowa magana, haka yayi ya gajji ya barni, Dadda ce tazo ta zauna a gefena ta ƙira sunana, ɗago kaina nayi na kalleta, ganin ina kallonta yasa ta tambayeni me nake son ci takawo mun? Kura mata ido nayi ban ce uffan ba, saboda wani iri nakeji a cikin jikina da kaina, dukkansu ukun babu yadda basuyi dani ba amma ban tanka suba, haka suka gajji kowa ya koma gefe ya zabga uban tagumi.

Washe gari da safe mutumin nan yazo, wuraren ƙarfe 11:00am yazo, Hajiya ummah kuma da Aunty rakiya tun wuraren ƙarfe 10:00am suka iso, saboda duk yadda akayi mummy ta ƙira ummie ta sanar mata, shiyasa sukayi smmakon zuwa dubani, suma babu yadda basuyi dani na amsa musu magana ba amma fir naƙi, domin wani mummunan ƙunci nakeji a zuciyata, ji nake idan na buɗe baki nayi magana zuciyata zata fashe,

Wanka Aunty Rakiya ta sakani na tashi mukaje tare da ita ta tsaya nayi, sannan ta bani wani roba da akasaka ruwan magani kuma naga an zuba wani turare mai ƙamshi a ciki wai nayi wankan da shi bayan nagama normal wanka na, haka dai badon rai yaso ba na karɓa nayi wankan, zani aka bani na ɗaura muka fito, kaskon wuta naga Dadda ta miƙo wa Aunty rakiya, sannan suka koma parlor suka barmu, wani garin magani ta zuba akan kaskon sannan ta sakani na tsuguna akai, bayan na gama ta saka na tashi ta bani pant data manna mishi pad a jiki na saka, nayi tunanin maina zan shafa, amma sai naga labarin ya chana, wani maganine daga gani mayukan islamic ne aka haɗa ta miƙo mun, hattah gashin kaina sai da na shafa mish, ina gamawa ta bani wata doguwar riga mai haɗe da gyalanta nasaka, duk yadda naso shafa turarena ta hanani,

lokacin da mutumin nan ne yazo jikina ya sake burkicewa, don maganin daya shigo da shi akan dole sai na shanye a lokacin ne ya tayar mun da hankali, wanda har sai da na ringa zabga mishi ihuu ina kuka yadda naso, A.G dai sai lallaɓani yake har saida nasha maganin, da ƙyar nasha, sannan ya bada wani magani akan na shafa ajikina sai nayi hayaƙi, aiko da daru da komai sai da nayi, bayan ya tafi ne naji yadda jiya aka ƙare da ni, lokacin mummy keyiwa su Hajiya ummah da Aunty

rakiya bayani, hajiya ummah sai zabga salati kawai takeyi, "jiya kam ai munga tashin hankali, ae mutumin yana shaƙa mata maganin ta miƙe a firgece zata gudu, shine ya saka mijinta ya riƙota, nan kuwa suka fara bayani a jikin ta, wai su biyansu akayi da jinin baƙin taure, baƙin agwagwa, baƙin kaza, baƙin yadi, baƙin zare, da tsiren gidan mashaya, kuma wai a hakan ma bai samu daman ƙarasawa jikinta ba, raɓanta yayi," mummy na musu bayani hajiya ummah ta sake zabga wani dogon salati tana kama haɓa, Aunty Rakiya ƙurawa mummy ido tayi, chan ta tambayi mummy "tou basu faɗi waya sayo su ba"? Mummy tayi ajiyan zuciya tace, "cewa sukayi wai wata mata ce baƙa mai ɗan jiki guntuwa, amma sunƙi faɗin sunanta, sun daice wai ta daɗe tana jefawa Ayshann sharruka basu kamata ne, wannan ma sunce tayi wasa da ibadunta ne da zama babu alwala yasa suka sameta," "ehhh babu shakkah zatona ya zama gaskiya, tabbas babu baƙa gajeruwa mummuna kaf a wanda na sansu sai Hauwa, kuma zatayi abunda yafi haka indai zuciyar da yake tare da Hauwa yana nan a ƙirjinta Usamanu bai taimaka an kaita ƙasar indiya a cire ba, don tabbas idan ba'a cire ba Hauwa zata kashe mutum idan ta samu sarari," hajiya ummah ta faɗa tana fashewa da kuka, ido Dadda ta ƙura mata na wani lokaci, kafin daga baya tace, "hajiya wacece hauwa? Akwai wacce kuke tunani zatayi wa Ayshaa irin wannan muguntan ne"? Ajiyan zuciya Aunty rakiya ta sauƙe sannan ta dubi Dadda tace, "matar babanta ce," sannan ta ɗaura da basu labarin abunda ya faru lokacin auren habiba, da wasu halaye na rayuwar mamie tunda aka aurota, ita dai hajiya ummah kukanta sosai tasha, haƙuri suka ringa bata, chan bayan tayi shiru sai ta maida kallonta kaina tace, "ni tsoron da nakeji ɗaya ne, dubi yadda baiwar Allah yarinya ƙarama take fama da sharrin kishiyar uwa ba nata kishiyar ba, dubi yadda Ayshaa tayi jigum taƙi tankawa kowa, tsoro na kada shegen aljanin ya taɓa mata saitin kanta, miji yaje ya gaji yace ya fasa aure, ha yaro sam barka da shi," sai kuma ta sake fashewa da kuka tana tsinewa mamie da zuriyarta kaff, haƙuri sukai ta bata, nidai ban san tafiyan su ba saboda baccin daya ɗauke ni, lokacin dana farka sai na samu sun tafi, A.G ma baya nan ya fita, daga ni sai Daddah, domin mummy ma wai ta tafi chan nata gidan, amma wai zata dawo jimawa.

Ranan monday jirgin safe A.G yabi ya koma Abuja, amma kafin ya tafi mun ɗan taɓa hira da shi sosai, don na ɗanji sauƙin ƙuncin da nakeji, lokacin da Alhaji ya kawo shawaran a dinga kunna mun karatun Al'kur'ani ina saurara.

Na kai 2weeks a gidan Dadda ana mun magani, kuma alhamdllh an fara gani sauyi sosai, domin kwanana tara ina wannan hayaƙin jinin ya ɗauke, yanzu abun da yake ɗan damuna shine rashin ƙarfi a jikina, wasu mafarke da bana iya tunasu idan na tashi, sai kuma rashin son dogon magana, a haka muka cika sati uku cif, sai A.G ya dazo, wannan zuwan tare da M.G suka zo, amma Heedayah an barta a chan, gaba ɗaya A.G yayi wani iri da shi, daga ka ganshi kaga baya cikin kwanciyar hankali, duk sai tausayin shi, da son shi suka cika zuciyata, suk inda yayi idona da hankalina suna kanshi, bayan na idaar da sallan ishaa ne naji Dadda tace na haɗa kayana nabi mijina idan ya dawo daga masallaci, ban ɓata lokaci ba kuwa na haɗa kayan wuri ɗaya, saida suka shigi shida Alhaji tukun muka musu sallama muka tafi, bayan Alhaji yayi mana dogon nasiha da shawarwari akan riƙo da ibadah, sannan aka ja kunnena akan shan magunguna na.

Muna shiga gidanmu nagan shi fes yana tashin ƙamshi, kallon A.G nayi da aman tambaya a fuskana, murmushi yayi yana dubana da kyawawan lumsassun idunan shi yace, "gaggawa da ɗoki irin na sabon ango yasaka nazo da wuri na gyara gidan, hafsy naje na ɗauko ta gyara miki ɗakunan da toilets ɗinki," murmushi nayi kawai na wuce hanyar nawa ɗakin, ina jin shi a baya yana biye da ni, tsaf kuwa nasamu ɗakin da toilet ɗin, kallo na yayi yace, "Eeshaa bari naje nayi wanka na dawo, kafin nan ma kema kinyi wankan, sai nazo musha maganin ko"? Murmushi na mishi kawai bance komai ba, bayan ya fice a ɗakin ne n shige toilet nayi wanka, shiryawa na farayi sai gashi ya shigo, magunguna na ya ɗauko mun dukka nasha, sannan na shafa na shafawa, magic charcol ya kunna nayi hayaƙi na, ina ganin shi yana ta hatishawa saboda asthman shi da baya son hayaƙi, bayan a gama na zauna warin hayaƙin ya ɗan bar jikina kaɗan, chan na ɗauƙo humrah zan shafa naji ya riƙe hannuna, "beauty yyh kuma da ɗauko turare"? Kallon shi nayi jiki a sanyaye nace, "zan sakane kada warin hayaƙin ya dameka", lumshe ido yayi ya ɗan buɗesu kaɗan yace, "hakan bazai yiwuba baby, idan Allah ya bamu lafiya zamuyi karaƙin shafa duk turare da muke so,amma yanzu kam ni *AMINULLAHI GARBA INUWA* na yafe, a haka nake son Eeshaa ta, kuma ni ƙamshin ki nake ji a haka.

Jiki a sanyaye na ajiye kwalban turaren a inda na ɗauko shi kan mirrow, rigan bacci na kawai na ɗauko nasaka, duk abinda nakeyi idon shi na biye da ni, ina gamawa ya miƙo mun hijab ɗin da nake sallah da shi, jiki na a sanyaye na saka, sannan ya miƙo mun socks ɗina na saka.

Sallah ya jamu raka'a biyu, bayan mun idar ya mana dogon addu'a na zaman lafiya, nidai Ameen nake bishi da shi, daga nan ya ɗauko mana cooler da wani cocounut

juice mai cike da ƙamshin flavour da madara, duk yadda naso ƙin cin naman kazan da akayi shi kaman danderu, amma bai barni ba sai da naci, a baki ya dinga bani har na ƙoshi, daga nan na shige toilet na wanko bakina sosai, bayan na fito na samu ya kwashe kayan zuwa kitchen.

Gado na hau na ja duvet na rufu, ko minti biyar ban cika ba ya shigo, ina jin shi yana tambayan yaya na rufe har kaina,? Nidai shiru ban amsa mishi ba, kashe wutan ɗakin yayi ya kunna bedside lamp, a haka ya hawo gadon yana jawo ni jikinshi, "Eeshan A.G shine baki jirani ba"?

Nidai bance komai, wayan shi aka ƙira ina ji yaja tsaki ya katse wayan, murya chan ƙasa yana mitan, "kaji mun munafukin yaro, kagama angwancewa tun shaiɗan yana saurayi, ni yanzu da nake niyyah zaka wani dameni da ƙiran tsakar dare", ya faɗa yana jan tsaki, nidai dariya ne naji yazo mun, ban shiryah ba ya kubce mun, shima ina jin shi yayi dariyan kaɗan ya kwanto a jikina.

Fuskanta cike da murmushi tana wani lumshe ido ta dubeni, "Aunty nice a wannan daren ne alama ya nuna nasamu lafiya, domin kuwa a wannan rana mai cike da tarihi, aminci, ƙauna, amana, da kuma soyayyah, A.G ya karɓi darajana da ƙima na, wanda wannan wata rana ce da bazan taɓa mantawa da shi ba a tarihin rayuwata,

Dare ne daya ƙullah abubuwa masu girman gaske a rayuwata da A.g, dare ne mai haske wanda ya haska duniyar mu da A.G, a wannan daren nagama zama A.G shima yazama Eeshaa", kallona tayi fuskan ta cike da farin ciki, sannan ta cigaba, "Allah sarki A.G wato ranan naga rawan jiki da ƙauna, don a wannan daren ya mun alƙawarin mota, kuma haka akayi, washegari kuwa ko idon shine ya rufe, yana idar da sallah ya ƙira mummy a waya, wato nidai naga takaina a wannan rana, don tana ɗauka kuwa yace, "mummy wallahi beauty ta warke, inaga gobe tare ma zamu tafi Abujah da ita", duk sai naji kunya ta lulluɓe ni, ballantana da tace mishi tana zuwa idan gari ya ƙarasa washewa.

Nidai dawowa nayi kaman wata sarauniya, don komai shiya mun, yadda kika san babu wata mace a duniya bayan ni, wato Aunty nice naga so, ƙauna, kulawa a rayuwar A.G, haka yayi komai ya gyara ni ya gyara ɗaki, wuraren ƙarfe 10:00am kuwa sai ga mummy, kayan breakfast ta haɗu mana rinkicicif, ga peppesoup Ɗin kaza daya sha kayan ƙamshi na gargajiya, haka dai itama ta lalace a tarairaya na, ga tonun sili da suka mun, don wallahi sai da ta ƙira ummie ta zayyane mana lafiya

ya samu, ita dai ummie murmushi ne nata da hamdala, mummy day sai da akayi sallan magrib ta bar gidan, bayan ta zayyana mishi Dadda tace babu inda zanje sai na ƙarasa magani na, kuma haka babu yadda ya iya, dole da zai tafi ya mayar dani, da zai tafi ƙin sake fuska yayi, ya haɗe kaman A.Gn da dana sani, don ko ni banga fuska ba ranan, ko da ya isa yaƙi ƙiran kowa, sai nice ma ya turo mun msg ya sauƙa lafiya, nima reply na mishi da Alhamdulillah na barshi.

Humm ranan friday sai ga Gwani A.G kam ya dawo bauchi, baki mummy ta riƙe tana kallon shi cike da mamaki, sharewa yayi kaman bai san me yake faruwa ba, daga nan kuwa ya shige ɗakin mummy inda nake kwance ina waya da Hadiza, ganin shi tsaye a bakin ƙofa ya ƙura mun ido yasaka na tashi zaune ina sallama da hadiza.

Ido na ƙura mishi ina kallon shi, shima idon ya zuba mun yana kallo na, "ki shiryah idan kin gama kallona ɗin mu wuce gida" ya faɗa yana wani harara na, dariya ma yabani , "nikan don Allah ka barni anan, bansan me zan iya gayawa mummy ba, ae zataga kaman bamu da kunya", na faɗa ina maida kallona ƙasa, don ganin irin yadda ya ƙura mun ido, hmmm naji yace, sannan ya matso ciki har bakin gadon ya tsaya, "anan kenan kike ga yakamata mu kwana ko"? Ɗaga kafaɗa yayi alaman babu komai hakan, "shikenan bari na sauƙe kayana sai mummy ta bamu wuri mu kwana anan".

Jin abunda yace yasaka na wani zaburo nace, "yayah kuma mu kwana tare da kai a ɗakin mummy? ae ko gidan nan bai kamata mu kwana tare ba ballantana kuma a ɗakin mummy", na faɗa ina sauƙowa da ƙafufuwana ƙasa.

"Tunda kinga hakan bai dace ba sai ki tashi baki alaikum mu wuce inda ya dace da mu, don wallahi yau babu wanda ya isa hanani kwana ɗaki ɗaya gado ɗaya da ke"..... Bai gama ba kuwa mukaji muryan mummy tace, "babu kam Barrister, ke kuma Ayshaa ɗauki kayanki ku wuce, kafin ya nuna mun shi baijin kunyan kowa, kedai ki kula da magungunan ki kinji ko", ta faɗa tana juyawa ta bar ɗakin, kunya

naji ya rufe ni, duban shi nayi kaman zanyi kuka nace, "haba mana A.G", hararana yayi yace, "kin tashi ko sai na ɗale gadon"?

Tashi nayi ina ƙunƙuni ƙasa-ƙasa na zuba magunguna na a wani leda, banda shi ban ɗauki komai ba sai handbag, ko sallama banyiwa mummy ba, don ta wuce parlon daddy duk da baya nan, shi kaɗai yaje yayi mata sallama, a tsaye a bakin mota ya sameni, kashe mun ido yayi bayan ya ɗaga mun giran shi duka biyu, nidai kunya ya bani na juyar da kaina kawai na shige motan.

A gidan mu nida shi muka gyara gidan, naso ɗaura a binci amma fir yaƙi barina, dole mukaje *MCDOWALS* muka sayo snacks, sai kaza gashin injin da yogouth, haka ranan ma muka lalace da nunawa juna ƙauna, wannan daren ma darene mai girma a wurin A.G, mun nunawa juna so da ƙauna, kulawa da A.G ya nuna mun har sai da naji kaman babu yani a duniya, ranan monday ya sake juyawa ya koma Abuja, ni kuma na koma gida wurin mummy.

****

Bayan 2month jiki yayi sauƙi sosai, sai lokacin mukayi shirin tafiya tare da A.G, satin da yazo ummie ta ƙirani inda hali na tambayi A.G nazo na duba jikin sabeer, domin yau sai da aka ɗaura mishi drip, hankalina a tashe da yazo na gaya mishi, kuma ana sallan magrib muka wuce gidan mu, muna shiga kuwa muka haɗu da su suna shirin wucewa asibiti da shi, duk sabeer ɗina ya fige yayi baƙi, hankali atashe muka bi bayansu akaje asibitin, *ALWADATA* wani private hospital na yara da yake Fadaman mada mukaje, muna asibitin har 10:00 na dare ana abu ɗaya, sai da mukaga an bsu ɗaki har an saka mishi drip yana bacci tukun muka tafi, duk zuciyata babu daɗi muka dawo gida.

Ƙarfe shida bayan mun gama azkhar munyi karatun qur'an, sai ga wayan ummie ta ƙirani, wani irin faɗuwan gaba sosai naji ya kamani, amma na daure na ɗauka, bakina yana rawa na gaida ummie, "Ayshaa" naji ummie ta ƙirani a hankali, da ƙyar na amsa mata, tambayana yyh A.G yake tayi, shima amsa mata nayi da yana lafiya, sannan cikin lumana da nasiha take gaya mun Allahn da yafi mu son sabeer ya karɓi abunshi, idan A.G ya amince nazo kafin a kaishi, kuka sosai na fashewa ummie da shi, wanda tayi sauri ta kashe wayan, da sauri A.G ya matso jikina ya rungumeni, bai tambayeni komai ba don volume ɗin wayana daya ke bayyane ya kai mishi komai, rarrashi na yakeyi har zuwa wasu mintuna, sannan yace na tashi na sake wanka muje, shima ɗakin shi ya wuce yayi wanka, bayan nayi wanka na saka dogon rigan atamfah ta soso, sannan na ɗauko hijab green kalan atamfar na saka, sai ga A.G ya shigo da cup ɗin tea a hannun shi, babu yadda na iya haka ya takura ni sai dana sha half na tea ɗin tukun muka tafi gidan mu, duk illahirin yan gidan sɲa parlon mamie, gaban ummie naje na zauna n kwantar da kaina a kan cinyanta ina kuka, tabbas naji mutuwar Ɗana sabeer, amma babban damuwa na na rabu da wani abu daya danganci habiba, don mutuwar habiba ne najishi ya dawo mun, kaman yau akayi rasuwan nakeji.

Ko kunya mutane mamie bataji ba lokacin da Aliyu da maman shi suka zo da yan'uwan shi, haka ta dinga fade -faɗen magana ana hana ta amma batayi shiru ba, har Allah ya isa saida ta musu, amma da yake mummyn Aliyu tafita bariki ko bin ta kanta batayi ba, ɗaukan gawan jikanta tayi ta mishi addu'a, shima Aliyu addu'a yayi mishi sosai yana share hawaywn shi, gefe ɗaya kuma amaryar shi tana zaune cikin yan'uwan shi, har ita mamie bata bari ba ta zage ta tsaf, lokacin da suka gama kuwa suka ɗauki gawan yaronsu suka gita domin ayi mishi sallah, lokacin kuwa Aunty Rakiya ne ta mata jan ido ta nuna mata bata isa ba sue da ƙarfi akai, gashi gida babu Abba babu mazajen gidan, mudai munga fitina da tashin hankali ranan, don ƙarshe sai da sukayi uwar watsiya da Aunty Rakiya da Mamah, don da abun yafara tsamari wai Abba yace tunda A.G yana gidan ya tsaya akan komai kafin su iso, ai kuwa inda ta shiga bata nan take fita ba, shine su mamah suka taso mata, don tana farawa ummie ta jani muka fice, hajiya ummah sai da ta kusan tsine mata albarka ranan, nidai ban sake komawa ba sai da zamu tafe A.G yajani muka shiga, nan ma sai da ta gaya mana abunda banji daɗi ba, ina ankare da A.G duk sai mamakinta yake tayi, jiki na a sanyaye uka wuce

Washe gari kuwa Abba da yayah muhammad suka zo, kacha -kacha Abba yayi mata ka yace kowa ma ya watse a zaman, kuma ya ƙira Raliya da itama ranan tazo yayi mata kacha-kacha yace kuma ta juya ta tafi, nima ya mana sallama da A.G yace mu wuce Abuja baice mu zauna ba haka ya isa, abarta da halinta, Allah yaga yaron jinin habiba ne, baida hakkin girban ayyukanta shiyasa Allah ya ɗauke shi batare da ya girma ya girbi baƙin ciki ba.

Hafsy da Huda ce suka mana rakiya zuwa Abujah, mun isa lafiya muka samu Aunty B da Aunty J sunzo, tare suka sake gyara mun gidana da Heedayah, mun samu an mana abinci, ga drinks kala-kala da suka mana, heedayah ce tazo ta rungume ni, ga cikinta da bai wuce 5month ba ya fito ɗas da shi, bayan ta sake ni ne taje ta rungume Hudah, hararanta A.G yayi sannan ya wuce ciki, gaskiya gidan yayi kyau kuma ya tsaru sosai, ga wasu kaya da aka saka mun a gidan kaman ma sunfi na bauchi kyau, da yake jirgi muka biyo sai babu gajjiya a jikin mu, abinci muka haɗu mukaci da su, M.G suna tare da A.G a parlor, hira sosai mukayi da su Aunty, daga baya suka ce zasu tafi, sun so su tafi tare da hafsy amma A.G fir yaƙi, daga Hudah har hafsy yace a gidan zasu kwana, don heedayah taso su tafi gidanta da Hudah, kallo ɗaya A.G ya mata ta risina, ita dai Hudah murmishi kawai tayi tace wa Heedayah ta bari kafin ta taɗi zata zo mata, "dayake mijin ta ne ya kawoki ko"? Ya faɗa yana hararan Heedayah, ita dai miƙewa da sauri tayi tana girgiza mishi kai alaman a'a, shi kuma M.G dariya kawai yake don yasan darun A.G.

Da wuri su Aunty B suka mana sallama suka tafi, dukkan mu uku muna zaune a parlor bayan tafiyan su M.G ma, amma shi kuma A.G ya wuce ɗakin shi, abun gwanin burgewa gidan, gashi dai 2bedrooms ne, amma a mugun sake gidan, don ɗakun A.G yana parlor, shima bawai ƙofan cikin parlor kai tsaye bane, zaki bi wani ɗan corrido ne daga parlon sai ki samu ɗakin shi, tou duk abunda ake a parlor bazai dame shi ba, haka shi bazai takura na parlor ba, imda dinning section yake nan ƙofan shiga kitchen yake, akwai store mai ɗan girma a kitchen ɗin, daga nan zaka fice ƙofan baya, wanda tanan ma zai sadaka da gidan Heedayah shima ta nata kitchen ɗin, amma tsakiyan su akwai wani ɗan boysquater mai ɗauke da ƙaramin parlor da ɗaki ɗaya da store, a parlor zaki bi wani ɗan dogon corridor zuwa ɗakina, ɗakine babban gaske, ga toilet ga kuma wani ɗan ƙaramin ɗaki a cikin ɗakin, kaman wurin da zaki ajiye wasu kaya haka akayi wurin, idan baki son shirgi a ɗakinki, may be ma wata zata iya mayar da shi ɗakin yara ma, don zai ɗauku madaidaicin gado da sauran tarkacen gado.

Fitowan A.G ne ya nuna mana an ƙira sallan magrib, ido ya ƙura mun yna maida links ɗin rigan shi, miƙewa nayi ina faɗin, "bari mu tashi muyi alwala, ashe an ƙira sallah"? Lumshe ido yayi ya sake buɗesu akaina, batare da yace mun uffan ba ya maida kallon shi kan Hudah, "babu buƙatan wani abu ko"? Sannan ya ƙure hafsy ma da kallo, jiran ko da mai buƙata a cikin su, murmushi hafsy tayi ta juya kanta alaman babu komai, sannan ta miƙe hanyar nawa ɗakin tana faɗin, "sai ka dawo Yayah", amsawa yayi sannan ya ƙure Hudah da ido, itama murmushi tayi tace,

"Yayah babu komai, komai da muke buƙata naga sun kawo, sai ka dawo Allah ya tsare", ta faɗa tana juyawa hanyar ɗakina.

Giran shi ya ɗaga mun duka biyu, alaman nifah? Murmushi nayi nace, "babu komai Jarumina, fatan kadawo mun lafiya kawai damuwa na", na faɗa ina kallonshi ina ɗan rakuɓewa gefe kaman munafuka.

"Jarumi ko"? Sannan ya lumshe ido ya buɗe, "Jarumin ki ko? Lallai da magana, bari na dawo kimun bayanin jarumtar A.Gn ki yarinya".

Baki na ɗan rufe kaɗan da hannu na ina dariya, "nifa bana nufin komai ranka ya daɗe kawai dai..... Kawai dai fatan ka dawo lafiya ne nima nayi maka", na faɗa ina dariyan shi, shima dariyan yayi mai kama da murmushi ya wuce waje, domin ƙiran shi da naga M.G yayi ta waya, bai ɗauka ba kawai ya duba ya mayar da wayan cikin aljihun shi.

Ɗakina su Hudah suke shirin bacci, ni kuma na gajji da mitan Hudah akan na tafi wurin ɗan'uwanta na bar shi shikaɗai, ita dai hafsy tana kwance rub da ciki tana ta wayanta da yayah ishaq, kaman munafuka ko muryanta baka tsinta, haka na shige toilet nayi wanka da ruwa mai zafi, bayan nagama na fito na shiryawa cikin wani rigan bacci red colour, rigan dogone ya ɗan wuce gwiwa na kaɗan, amma kuma hannun shimi ke gareshi, gaban rigan gaba ɗaya net ne, gashi yana da alaman gidan bra, magani na nasha wanda hudah ta sake jaddada mun, nasha nayi hayaƙi, na kuma shafa na shafawa, daga baya nasaka rikan bayan na jira ƙaurin jikina ya ɗan rage, hijab ɗina na ɗauka har ƙasa na saka, sai da safe nayiwa Hudah, hafsy kuma mari na ɗaka mata a cinyoyinta na fice.

Ido ya ɗago ya ƙura mun tunda na shigo parlon, nima idon na ƙura mishi bayan naja wuri guda na tsaya, ganin haka ya saka ya buɗe dukka hannayen shi, "ki matsar da wannan abun jikin kin kafin ki ƙaraso nan baby girl",

zare hijabin nayi idona yana kanshi, akan kujeran da yake gefene na ajiye, sannan na sauƙe ajiyan zuciya mai ɗan ƙara kaɗan ganin yadda A.G ya wani lumshe idanun shi kaman ba zai iya ganin mutum ba ya ƙura mun, hannun shi ya ƙara buɗewa

yana mun alaman na ƙarasa wurin shi, nidai cike da tsarguwan warin hayaƙin da jikina yakeyi na ƙarasa, kan cinyar shi ya zaunar dani, dama ya cire rigan shi sai wani white singilet ne ajikin shi, sai dogon wandon shi, zama nayi sosai akan cinyan shi, shi kuma yasaka hancin shi yana shinshina wuya na, abun har mamaki yake bani, ni da nake warin hayaƙi shi kuma yana wani shinshina ni, da ƙyar na samu ya iya tashi muka wuce room ɗin shi, muna shiga ya kwantar dani ya wuce toilet ɗinshi, ya daɗe sosai sannan ya fito yana ta zabga ƙamshin shwer gel ɗin dayayi wanka da shi, shiryawa yayi gaba ɗaya hankalinshi ya tafi kaina, hmmmm Aunty nice A.G nah nace miki duniya ne, babu wata yɑ mace inaga a doron duniya da tayi dace da miji mai tsananin sonta ba irina, gaskiya A.G ƙarshe ne a nuna so, ashe dam haka sirrin auren shiru -shirun namiji yake? Wato Aunty nice babu dare ko rana da A.G zai kasance dani bakiji yana kuka ba, kuka kuma da hawayen shi, wani sa'in har tsoro nakeji naga kaman suma zai mun idan yana kwance dani, kuma hakan sai na lura nima wani shauƙi sosai ya ke sakani, ji nake babu wata mace da ta fini dacewa da miji a duniya".

nidai murmushi nayi ina ƙara maida kaina da nutsuwana kan Hajiya Aysha mayar A.G uwar Nana khadijah (Mamah)

A zuciyata kuma nace naki kika sani nima haka nakeji nawa Gwarzon yafi naki iya nuna mun so da kulawa, don kawai ..... Kawai dai shikenan, na faɗa a zuciyata, a fuskana kuma na bita da murmushi, ina ƙura mata ido, idan kuma nayi ƙarya ku tambayi , *sahibata ummie yawale* nima tasan irin son da nawa mijin ya mun, wane wani A.G 😣.

Hudah da hafsy sun mana 2weeks, da ƙyar A.G yabar Huda taje gidan M.G tayi 2dys, Shima sai da yaga ran M.G ya ɗan ɓaci ne, don yace idan yana ganin gidan heedayah gidan ƙanwarta ne, wato shi ba yayan huda bane shi bare ne ko? Shi bai wani ɗauka ta wurin yayan shi mijinta ba, shima ae ɗan daddy da mummy ne, amma idan A.G ya cire shi babu komai Huda basai tazo gidan shi ba, ganin yau ɗaya M.G ya nuna ɓacin ranshi yasaka yace taje tayi 2dys, hafsy kam dama 5dys tayi a gida na ta ɓalle chan gidan su yayah, wai a cewar ta da zaran A.G ya shigo tou bata wani ƙara ganina, wai bana bata kulawa, kaji sharri irin na autar ummie, naji daɗin zama dasu wallahi, da zasu tafi duk sai naji kewar su ya ishe ni, amma babu yadda na iya haka suka tafi, tare da M.G da kuma yayah Ahmad suka tafi, mota suka bi a komawar su, A.G nah yana fita office kuwa heedayah take shigowa, biyar nayi take guduwa nata gidan, gashi cikinta mai ƙin yin girkine, Allah yasota M.G baida fitinan sai tayi kaza tayi kaza, bata ma yin girki banda breakfast, Ni nake

mana taci ta tafi da na M.G, gashi bai ma yawan zama a Abujah yanzu sosai, kullum yana hanyar lagos, yakanyi 2weeks a chan kafin yazo yayi 5dys haka a Abuja.

Bamufi 2month da dawowa ba nafara laulayin mai zafin gaske, gashi ya sakani wani irin shiru da rashin son cin abinci, A.G yayi fama dani akan abinci amma fir naƙi, saidai zan wuni ina shan ruwan tea, shima black tea, a haka har na shiga 3month, lokacin heedayah tana 8month, wata rana A.G ya fita da wuri shida Yayah Ahmad, kasa tashi nayi na mishi ko ɓreakfast, shima bai wani takurani ba, fita sukayi bayan ya jaddada mun nine nayi na tashi nayi wankan magani nasha tea, da ƙyar na amsa mishi ya fice, daga nan kuma Heedayah ya tattaro yace ta dawo parlor na ta zauna, idan nine yayi ta tasheni nayi wanka nayi break, haka doe tazo ta kwanta a parlor tana kallon dole, don ba gwanar kallo bace ita sai yawan son karatun hausa novel, inda muka ƙara ƙullewa da ita ma kenan, duk da A.G baya son karatun haka ya barni.

Bacci na nakeyi cike da wasu birkitattun mafarki, a haka nayi mafarki wai gani nan a garin bauchi ina kwance a ɗakin hajiya ummah, kuma alama ya nuna kaman ina gida lokacin banyi aure ba, amma ka ina kwance da ciki a jikina rusheshe, ina so na tashi amma kuma na kasa, chan sai naga ƙofa ya buɗe wata mata mai fuska a rufe da wani abu ta shigo, hannunta ɗauke da wani jaririn yaro fari sol an mishi kwalliya, kyaun yaron sai ya mun kaman fuskan A.G, duk sai naji hankalina da ƙauna na ya koma kan yaron, yana ta wasa da hannayen shi da ƙafafun shi, chan sai naga matar ta yaye abunda ya rufe fuskan ta, kawai sai naga fuskan mamie tana mun wani dariya har da hawayenta, tana kuma nuna mun fuskan kyakkyawan yaron daya ƙura mun ido yana kallona kaman ba baby ba, gashi fuskan sak na A.G, amma kuma yana so yayi kuka alaman wurina yake son zuwa, "kina son ki karɓi yaron ne"? Naji muryan ta tana tambaya na, daga bayanta kuma sisto na habiba ce take mun alaman a'a da kanta, ita kuma tana riƙe da ƙofa tana kokiwan shigowa amma sai naga an figo ta ta koma baya, chan saiga Raliya da surkuwarta sun shigo suma suma dariya, hannu na miƙa don na karɓi jaririn da yake ƙoƙarin miƙo mun hannunshi, kawai sai naga sun haɗu su uu sun koma mutum ɗaya amma da fuskan mutum uku, wato mamie, raliya, surkuwata, jeho mun babyn sukayi ya faɗo jikina, abun mamaki duk kyaun da nagani da fari a tare da yaron sai ya juya mun baƙiƙirin da suka jeho mun shi kan cikina, kuma hannayen shi duk sun watsu a jikina kusan guda goma ko fi, don ko ta ina sun manne a jikana, gashi ya wani ƙamƙameni yana ƙyalƙyalah dariya irin yadda suma sukeyi, aiko banbi takan nayi addu'a ba kawai sai na zabga wani rin ihuu mai ƙarfin gaske, daidai lokacin kuma naji na farka da wani uban ƙara a bakina, ga zufa daya gama wanke mun jiki kaman wanda nayi tsere,

ina tashi zaune kuma saiga Heedayah ta faɗo ɗakin da saurinta, jikinta duk rawa yake tazo ta rungumeni a jikinta.

Jinta a jikina nima nayi saurin rungumeta ina kuka, gashi gaba ɗaya illahirin jikina rawa yakeyi, inda mamie suka tsaya na ƙurawa ido, amma sam babu kowa ballantana komai, "meya faru Aunty kike ihu"? Heedayah da duk hankalinta yake tashe ta tambayeni, jikina da muryah nah gaba ɗaya rawa sukeyi, da ƙyar na buɗe baki nace, "zuwa sukayi suka bani tsoro da jariri", ina gaya mata abunda ya faru duk ta wani firgice, da sauri ta ɗauki waya ta ƙira A.G nah, sun riga da sun fita a gari shida yayah Ahmad, suleja sukaje Domin zasu gana da wani mutum daya nemi su, umurni ya bata da na tashi ta taimaka mun nayi wankan maganina, kuma ta tabbatar nasha tea da bread, kuma kada ta yadda su kunna kallo idan ba karatun qur'ani ba a gidan, haka akayi wanka ta riƙe ni akan na tashi naje nayi, ai kuwa kaman jira ake naje daidai ƙofan toilet ɗin sai naji wani iein mummunan murɗawan ciki mai azaban gaske, hannun ta na riƙo da ɗan ƙarfi na runtse ido na, chan sai naji abu shaaaa ya zubu mun ta ƙasa na kaman wani ruwan naƙuda idan mace zata haihu, dagani har uta muka ƙurawa ruwan da yake zuba kaman wani fitsarin sati guda na riƙe.

Sai da ya gama zuba tukun naji na fara jin wani azababben ciwo a marana, amma haka muka ƙuƙuta muka shiga toilet ɗin, da ƙyar na samu na tsaya, ai kuwa tana fita naji marana yayi wani mummunan ƙullewa, sunanta na ƙwala ƙira da ƙarfi, da shigowanta da ɓalluwan jini a jikina duk lokaci ɗayane, daga nan sai naga toilet ɗin yana mun duhu, ɗif kuma sai naji komai ya tsaya mun.

Lokacin dana dawo hayyaci na sai na samu kaina kwance a gadon asibiti, gefe na A.G ne zaune ya yi tagumi, yayah Ahmad kuma tsaye ya rungume hannayen shi a ƙirji, heedayah kuma zaune ta buga ubantagumi, da sauri A.G ya matso kusa dani, daidai kuma Aunty B na fitowa daga toilet ɗin ɗakin, "beauty sannu", naji muryan shi kaman wanda zaiyi kuka ya furta, matsowa yayah Ahmad yayi kusa damu, shima sannun ya mun, nidai ido kawai na bisu da shi, chan kuma na lumshe ido na nayi shiru, inajin yayah Ahmad nagayawa Aunty J a waya na farka, wanda daga dukkan alamu ita tana gida ne, gefe na Aunty B tazo ta zauna, hannun ta tasaka ta riƙe hannu na tace, "bestyn besty kin tashi? Sannu ko besty".

A.G Dr ya ƙira a waya ya gaya mishi, babu daƈewa nurse ta shigo ƈauke da tray ƈin sun nan, ita da Aunty B suka taimaka mun na tashi muka shiga toilet, wato daga dukkan alamu nasamu misscarrige, mummunan tashin hankali naji ya sameni, amma na ɓoye don kada su fahimta nai kunya, haka suka tayani nayi wanka, gyara jikina nayi da pad, muna fitowa Aunty B ta bani tea mai kauri wanda na samu heedayah na gaurayawa, hannu na saka na karɓa, ina zaune a bakin gaƈon ƙafana suna ƈaure akan kujeran da A.G da ya zauna,shi kuma yana zaune a gefe nah ya doka uban tagumi.

Allura nurse ƈin ta mun da wani magani , bayan ta gama ta fice a ƈakin.

2hrs na ƙara aka sallame mu, bayan mun shiga Dr yayi mun scarning, inda naji Dr yana yiwa su yayah da A.G bayanin cikin gaba ƈaya ya fice ba sai anyi wankin ciki ba, jiki a sanyaye A.G ya amsa mishi, sannan ya bamu takaddan maganin da zamu saya.

Gida na muka taho tare dasu, bamu daƈe ba Aunty J tazo tare da Areefh ta kawo abinci, suna nan a gidan dukkan su har 10:00pm, munyi waya da su ummie, Aunty Rakiya, mummy, hajiya ummah, hattah Abbana da Daddy sun ƙirani, a gidan Aunty B ta kwana da ni, kuma inaji hajiya ummah tace kada ta barni nasha ruwan sanyi kuma nayi wanka ko na sati biyu ne zuwa uku.

Washe gari kuwa Abba na ya shigo ya duba ni, inda yace daga lagos yake, kuma gobe zai wuce bch, idan yaje ummie zasu zo su dubani, nidai ranan farin cikin zuwan Abba na kaman zanyi yayah, da zai tafi kaman zanyi kuka yana riƙe da hannu na har jikin motan shi muka raka shi, a kunne ya sunkuya ya gaya mun "insha Allahu sisto zan dinga zuwa dubaki idan kinyi murmushi", ae kuwa dariya na ƙyalƙyale da shi, hakan kuma ya saka shi shima yin dariyan su yayah suna taya mu.

Bayan kwana 2 da faruwan haka kuwa sai ga su ummie da mummy, hajiya ummah da Aunty Rakiya sun zo, naji daƈin ganin du ainun, da suka shigo na rasa wurin wa zanje kawai sai na rufe fuskana da hannu na ina dariyan daƈi, don babu wanda yace mun zasu zo, mummy naje na fara hugging tana dariya na ita ma ta rungumo ni, hajiya umma ta turo baki gaba tana , "don Allah ja jiki da munfurcinki yarina, nidai ku bani wuri na zauna kada kayan takaici ya kaini bango, nasan da ba don ganin

idon surukuwar ki ba nuna mana zakiyi bamu taɓa haihuwa ba, uwarki zaki runguma, kaman mu bamu da yara Allah na gode mishi ma da ya bani usmanu, ɗaya tamkar da dubu" riƙo hannunta yayah Ahmad yayi yana zaunar da ita akan kujera, cikin muryan shi marar hayaniya yace, zaunawar ki lafiya uwar usmanu", dole ita ma tayi dariyan, bayan duk sun zauna na koma daf da Aunty rakiya na zauna akan cusion da yake ƙasa a wurin, gaishe su nayi ɗaya bayan ɗaya, sannan suma suka mun yayah jiki, duk ido na ya na kan ummie nah, itama muna haɗa ido take sakar mun da murmushi.

Shigowar heedayah ne ya mayar da hankalina kanta, tana tura ciki gaba ta rungume mummy tana dariya, ita daga alama bata san da zuwan su ba sai yanzu, abun karyawa Aunty B ta fito musu da shi, saboda isowan ƙarfe 9 sukayi, dayake flight ne, saboda kada uwar usmanu ta gajji a mota, ɗakina ta wucewa su mummy da ummie, Aunty Rakiya dai tace a barta tare da ummanta, A.G sun fita tare da yayah, ɗaki heedayah ta bisu, nidai ina xaune tare da su, nima tare da su mukayi break ɗin.

Naji daɗin zuwan su, duk da ummie na bata kwana gida na ba, chan gidan su yayah suka tafi tare da Aunty Rakiya, hajiya ne ta kwana mun duka biyun da sukayi, mummy ma kwana ɗaya tayi taje gidan M.G, duk da A.G yaso yi mata gardama amma tace ae chan ma gidan ɗanta ne, kuma ranan M.G ɗin ya dawo, babu yadda ya iya haka taje.

Ranan Laraba Suka koma, haka kuma bayan nayi 2weeks Aunty B ta tafi, naso na kara jin karfin jikina ba tare dana komawa A.G ba, amma kaman yana jiran tafiyan Aunty B ne ya ƙiya mun, dayake jinin baifi kwanki kaɗan ba ma ya tsaya, tou Allah ya so Aunty ta ɗan mun gyara ba mai tsananin yawa ba, dahuwar kaza na nonon raƙumi, da gumba sai wasu da zansha da nono ta saka wata mata yar sudan ta mun, ga kuma dahuwar wani kazan kaman gasa shi akayi da maganin ajiki, kaman dai irin anyi tukunyan nan da shi, haka kuwa nasha gumurzo a hannun jarumin mijina.

Babu wuya wurin ubangiji, ranan 10/08/2022 heedayah ta haifi ɗanta kyakkyawa mai kama da M.G, lafiyayyen yaro mai kyawawan ido irin nasu heedayah da jarumina, don idan ka kalli yaron zakace sak M.G, idan ka matsa kuwa sai kace

gidan su maman shi ya biyo, amma a zahiri farin shi da siffanshi, da kamanin hancin shi da komai irin na M.G ne, amma ƙwayyar idon shi sak nasu A.G da su heedayah ne, yama fi kama dana A.G, ranan farin ciki kaman zai huda zuciyar mu, A.G yaje bauchi akayi haihuwar, saboda haka ranan gaba ɗaya tarewa nayi a gidan bayan an dawo daga asibiti, kuma gaskiya daga Aunty B har Aunty J sunyi kara sosai wa A.G da M.G, don abunda zasuyi idan ni na haihu tou haka sukayi wa Heedayah, sun yi komai a mutumce, muna dawowa gida Aunty B ta ƙira wata yar'uwarta babbar matace da take zaune a suleja tazo har gida ta wanki yaro tsaf, fararen kayan sanyi aka sake saka mishi, sai naga ya ƙara wani haske da aka mishi wankan, nono aka saka heedayah ta bashi, da ƙyar ta yarda tasaka mishi nonon, don sai da Aunty j tayi da gaske da ita, yana kamawa kuwa ta fara kuka, nidai banda dariya babu abunda nakeyi, harara na Heedayah tayi tana jijjiga kai, "wallahi Aunty na lura tun kafin na haihu kike mun dariya, Allah kaɗai yasan ke me zaki aikata, gara ni ma halah", ta faɗa tana ƙara matse idonta don yadda babyn ya kama kamam ya shekara a duniya da ƙwarewa, nidai dariyan na sakeyi ina kallonta nace, "nifa kin san me yake sakani dariya ne? Tou matar da take cikin labour me ya kaita salati da kuma waƙa a lokaci ɗaya, ni shiya ɗaure mun kai, dama ana haka ne"? Na faɗa ina dariya, dukkan su dariyaɓ suka ƙyalƙyale da shi, hattah ita kanta mai haihuwar dariyan abunda tayi takeyi, "Allah ya nuna mana naki yarinya, hala ma pareri zakiyi" Aunty J tafaɗa tana zama bakin gadon, nidai karɓan babyn nayi na ƙura mishi ido ina murmushi, "ni wallahi kada ace nayi son kai, nidai yaron nan kyaun miji na ya ɗauko wallahi, jibi da ya buɗe idon nan kaman na Jarumi na, kai Masha Allah", na faɗa ina yiwa babyn kiss a fuskan shi.

"Chabb kaji wani zance, kina ga yaro ya ɗauko kyaun baban shi zaki wani haɗa shi da mijinki mai ɗaurarren fuska? Nidai ɗana kyaun Giwa na ya ɗauko", heedayah ta faɗa tana wani fari da ido, bakina a buɗe ina kallon ta, dariya su Aunty suke mana, wato kowa nata gwanin ne kyakkyawa.

(Na manta ko na gaya muku Aunty J ta haihu itama? Tana da yaro namiji, yanzu kuma dukkansu suna ɗauke da ciki ita da Aunty B, ita Aunty J lokacin da Ayshaa tayi ɓari cikinta ya kai 3month, so yanzu cikinta 5month, ita kuma Aunty B yanzu ne take cikin na, 3month, ita kuma ayshaa na maƙale da ɗan 2month, wanda daga ita har A.G alokacin basu da labarin shi, don tunda tayi miscarrige bata sake ganin period ba, so batayi tunanin ciki bane a lokacin, don bai nuna alaman komai ba da za'a gane).

Bayan 2dys A.G ya dawo, kuma ya dawo tare da wata umman mummy ce, wanda zata zauna da heedayah,matsayin kaka take a wurin du A.G, mace cr mai kirki, ga tsabta, ga ta da kazarkazar kaman mummy da heedayah, tunda tazo wancan matar da Aunty B ta kawo ta koma, Aunty j kusan kullun sai tazo duba heedayah, kuma takanzo da abinci, Aunty B dai cikinta da laulayi, so bata zuwa, bata ma sake zuwa ba sai ranan suna, shima sai yammah sosai tazo.

Ranan suna yaro yaci sunan *MUHAMMAD AUWAL* sunan babban yayan su M.G inda naji M.G yace yayan shi ne kuma Baban shine, a wannan ranan naga kara da zumunci na yan'uwanta ka, domin matar Yayah Auwalu ne kawai da basu ƙasan ba suzo ba, amma naga matar yayah sanie, rabiu, hassan da hussain, duk da dama Huda kam tamuce, babu wacce bata zoba daga inda ta ke, kuma ranan naga Yayah Auwal, domin ya ƙira video call don yaga takwaran shi, bawai ba'a taɓa mishi takwara bane, a'a yaji daɗin na wurin M.G sosai akace, domin shima gani yake yiwa M.G ɗane a wurin shi, babyn yana hannu na lokacin da M.G ya shigo da wayan, bayan sun gaisa da heedayah ne, M.G ya miƙo mun wayan yana cewa "Yayah ga matar A.G da takwaranka", kai so masha Allah, inaga duk yayan Goggo masu kyaune da farin fata, don ko yana xaune turai ne, duk da girma ya fara kama shi amma naga duk yafi su fari da kyaun, fuskan shi ɗauke da murmushi yana kallon fuskan babyn yace, "barka da ƙanwata, yyh Aminu yayah takwara na? Fatan yana cikin lafiya ko"? Sai da nasake ɗaga ido na dube shi, wai nan hausa yake yi, amma kaman turancin ne a bakin shi, ashe bayan M.G dana sani da mugun iya turanci ashe akwai wanda ya fishi a gidan su? Ko da yake duka yayan Goggo masu ilimine, don Yayah Sani yanzu professor ne, shima kuma yayah auwal ɗin hakane, twins kuma dukan su P.H.D suke da, Drs ne su duka, Yayah Rabiu ne kawai iya kaciɓ dhi degree ya kama ball, duk da nace kuma wai Yayah auwal ɗinne kawai ya fishi ƙwaƙwalwa, kawai dai nashi abincin a ƙwallo ne ba a boko ba, murmushi nayi na amsa mishi da komai lafiya.

Suna yayi kyau mun chakare abunmu, amma tun ranan sunan kuma zaman ƙafiya tsakani na da abinci ya ƙare, don tun da naji warin alale hankali na ya tashi, sai duk lokacin da zanci abinci sai naji warin a hanci ne, sai naji bazan iya ba, dole rayuwata ta koma daga tea, sai idan ka matsa nace zan sha garin kwaki.

Watarana naje gaida su Aunty B, don jikinta daya ɗan matsa, duk sai nakasa cin komai, da yayah muhammad ya matsa sai nace ni garin kwaki kawai nake so, jikin

shi na rawa ya fita nemo mun, daya dawo kuma ya taho mun da gyaɗa da ƙarago wai ya tuna yadda suke sha da a school, hakan kuma ya mun daɗi, sai naji na daka ƙaragon na kwaɗa kawai, aiko na kwaɗa na zuba albasa da attarugu, daga ni har duka Aunties ɗina muka dinga ci, muna cine naji Aunty B tace, "Besty cikin ki how many months kenan"? Tsayawa nayi da cin nace, "ciki kuma Aunty? Ni ae Aunty banida ciki, tunda nayi miscarrige ae har yau ban sake period ba".

Dariya suka kwashe ita da Aunty j, "tazarce kenan kikayi"? Aunty j tace, nidai tsayawa nayi ina binsu da ido, a zuciyata kuma ina mamakin wai ina da ciki, tou wani irin cikine kuma babu ciwo babu komai?

Shigowan yayah muhammad yaga suna ta mun dariya ni kuma ina zare ido ya tambaye su da lafiya kuwa?

Nan Aunty B ta mishi bayani, shi dai murmushi yayo kawai yace , "ae sai suje asibiti ayi test ko?inaga hakan zaifi kwanciyar hankali", nidai shiri nayi ina tunanin in da gaske cikine wani irin farin ciki Jarumina zaiyi? Sai naji gaba ɗaya asibitin kawai nake so muje mu tabbatar, basu ankara da ni ba na ɗauki waya na tura mishi message.

Aikuwa ko ƙwaƙƙwaran awa uku bai cika ba ya baro abunda yakeyi ya taho gidan, mudai kawai ganin shi mukayi yazo, kuma yace na taso muje asibitin, dariya sosai Aunty B ta mana ta kuma mana fatan alkhairi, garin kwaki na ta ɗauko mun, karɓa nayi muka wuce.

Scarning Dr ya mun, inda ya juyo yana duban A.G.

"Congratulation barr, madan na ɗauke da ciki na kusan 8weeks", fuskan Dr cike da murmushi, ɗaga hannu sama A.G yayi yana hamdalah wa ubangiji, nidai na sunkuyar da kaina ƙasa ina wasa da yatsu na,a hankali ya saka nashi hannun ya riƙo nawa, ido na ɗago na zuba mishi, idan banyi ƙaryah ba hawaye ne cike a idon shi, baiyi magana ba amma alama ya nuna mun da ido, na tashi muje, miƙewa nayi hannu na cikin na shi, sallama sukayi da Dr bayan ya bu wani paper da zamu sayi magani.

Har muka je pharmacy muka saya muka kama hanyar gidan mu baiyi magana ba, daga baya kuma dainaga ya juyo ya dube ni, "ko akwai wani abu da kike so kici"? Lumshe ido nayi na buɗe ina duban shi, "ina son cin kwakwa da soyayyan kifi", mirmushi yayi ya juya hanyar winti market, aiko leda guda aka ciko da kwakwa, kifi ma lodi guda aka sayo, kusan kala huɗu, sit ɗin baya ya ajiye ya dawo Sit ɗinshi ya zauna, "sai kuma me beauty na? Me unborn ke so? Me cwit heart ɗina take so?" yana faɗa hannun shi akan lafaffen cikina yana shafawa, turo baki nayi gaba nace, "boy ɗina dai, wacce irin takeso kuma, ni baby boy ne aciki? Buɗe idon shi yayi duka a kaina yana murmushi, "beauty insha Allahu girl ce, kin san yadda nake son yara mata kuwa? Duka girls zaki bani insha Allahu, ke ko ɗaya sai nayi ƙoƙarin baki tunda kina so", tada motan yayi muka kama hanyam gida, still hannun shi ɗaya yana riƙe da ni.

A parlon shi mukayi masauƙi, shi ya ɗauko ledojin, direct kitchen yaje ya jubge mun so, bai fito ba sai da ya ɓare mun kwakwa guda, ruwan ya juye mun a wani ƙaramin cup, kifin kuma ko wanne a ciki sai daya saka mun akan filet, inda nake yazo ya ajiye mun, idona akan shi ina jin wani azababben son shi yana ratsani, murmushi ya mun ya ajiye komai akan stool ya matsu mun da shi a gabana, kifin kuwa na dirawa, ko wanne sai dana ɗauki ɗaya aciki na taɓa, a ƙarshe na tsaya akan wani buɗaɗɗe kaman banƙararren kaza, shi sai danaci har biyu, bayan wanda naci a farko, tissue ya miƙo mun ma goge hannu na da baki na, sannan na ɗauki ruwan kwakwan nasha, hannu na ɗauka na ɗauko kwakwan, ina sakawa bakina na wani runtse ido tsabar daɗin da ya ratsa ƙwaƙwalwa na, murmushi yayi yana bina da kallo, "Eeshaa na baza a ɗan samma A.Gn Eesha bane"?

Kallon shi nake ina murmushi, "Jarumina ae kaine baka nemi zaman lafiya ba", na faɗa ina murguɗa bakina, murmushin shi ya faɗaɗa, "beauty me nayi kuma"?

"Kace baby girl ne, ni kuma boy nakeso don mu saka sunan M.G" na faɗa ina kallon shi ido cikin ido.

Dariya yayi ya tashi daga tsugunen da yake a gabana, gefen inda nake zaune ya zauna " beauty ina fatan Allah ya raya abinda ke cikin ki, idan tazo duniya sunanta *KHADIJAH* sunan ummie zan saka saboda ta bani farin cikin rayuwata, ita ta haifa mun beauty nah, ita ta bani kyauta mai girma da daraja a rayuwa na, ina so na faranta mata yadda ta faranta mun, ina son na girmamata sama da wanda ta haifi mai mun,

Na biyu kuma zan daka Heedayah, ina son ta sosai, ina ƙaunar ta, gashi kuma tana riƙe mun da farin cikin rayuwata, M.G, tunda aka haifi heedayah nake jinta kaman zuciyata, amma in kin cire M.G da mummy kowa gani yake Hudah ce tawa, ita nutsuwanta yake samu zama inuwa ɗaya Heedayah kuma hattah sunanta ni ma zaɓa mata shi,ni nayi kusan rabin rainonta, shi yasa naji daɗin aurenta da M.G.

Na ukun sai ki haifi naki boy ɗin, na huɗu kuma girl nake so, ita kuma RASHIDAT, (mummy) ce, auta ta da zan mata kauna na daban, ƙaunar da babu wani mahaifi daya taɓa yiwa ɗiyar shi irin shi, zan so ta sama da irin son da mummy tayi mun, xan so yarah na sosai beauty", ya faɗa yana kwantar da kanshi a kafaɗa na, ajiyan xuciya na sauƙe, "kaɗa fah ka so su sama dani", na faɗa ina kai mishi kwakwan bakin shi, murmushi yayi ya gutsuri kwakwan sannan yace, "hmmm beauty kenan, ni ae babu wani abu da zai zo yafi mun ke a rayuwan nan, bana fatan ganin hakan ma, amma dai kada fah ki fara kishi da su axo ana ƙin basu nono su sha, don zamu samu matsalah akansu fah yɑn mata na", dakata wa nayi da cin kwakwan na ɗaga anshi na ƙura mishi ido, "bangane magananka ba jarumi nah? Kana nufin akan su zanga ɓacin ranka? Kenan ma ka zaɓe su sama dani"? Na faɗa bakina a ture a gaba.

Rungumeni yayi yana dariya, sanann ya chanja topic ɗin, "Beauty next week zanje lagos, kuma inaga zamuyi 1week nida barrister, zamuje ko"? Tashi nayi nayi hanyan ɗakina don nayi wanka, kallon shi nayi ban ce uffan ba, shidai dariya kawai yake mun,don yasan na shaƙa ne game da maganan zaiso yaran shi da yawa, kaman ma sama da ni.

Cikina yana six month lokacin Aunty j ta haihu, wannan karon ma ɗa namiji, ta haifah, gashi kowani yaro kama yake da gidan mu, yaran nan babu abunda suka baro na yayah Ahmad, a lokacin kuma aka saka Date ɗin auren mutane na, Yayah umar da ummitah, yayah ishaq da hafsyn shi, gashi garin zaman su ya banbanta, shi yayah umar kaduna yake, yayah ishaq kuma Maiduguri, (october 2023) bikinsu, ni kuma zai kama na haihu da kusan 6month kenan,an saka date ɗin da nisa saboda zasu tafi wani training ne na six month, shi yasa aka kai shi wannan lokacin.

A cikin wannan watan da zamu shiga ne bikin hadiza, saboda haka nayi shiri sosai na zuwa bauchi, bamu samu zuwa a lokacin da muka so ba, sai ranan friday ɗin bikin muka tafi, don ma flight ɗinmu na safene, tafi da gidanka mukayi, don gaskiya duk yayuna sunyi kara, mun iso wuraren 10:00am, gida naso wucewa amma fir A.G

yaƙi amincewa, amma ganin Heedayah ma gidanta zata sauƙa sai abun ya ɗan mun sauƙi, gidan su muka wuce nida shi da M.G da kuma heedayah, inda su Aunty B ma da mazajen su da yaran su gidan mu suka shige, achan mukayi break, bayan munyi na matsawa A.G akan zanbi su Aunty B zuwa garinmu, inda achan zatayi event ɗinta.

Saida mukaje gidanmu ya ɗan gwangwaje ni yadda yaso tukun muka ƙarisa sir kashim, ina shiga kuwa nayi karo da ummie na ta fito daga ɗakinta xatayi kitchen, aiko banji nauyin cikina ba, banji kunyan su yayah da dukkansu suna parlon ba naje na rungumeta, murmushi cike a fuskanta tana kallon na cike da tausayawa irin na uwa idan taga yarta ɗauke da ciki, gashi kowa yayi mamakin bajewan dana ɗanyi, babu wanda yayi tunanin zanyi jiki haka, duk da dai ƙarfin cikin a cinyoyina ne, amma kuma shima ya ɗan tasa kaɗan.

Muna rungume da juna Su Aunty suna mun dariya, hafsy ka sai mita takeyi wai zan kayar mata da mahaifiya na fallashe ta, nidai ban bar jikin ummie ba ina ta murmushi ido na cike da ƙwallan daƒin ganina tare da ita, a haka A.G ya shigo parlon, ganin shine ma yasa ummien ɗan matsar dani a jikinta, dawowa tayi cikin parlon sosai ta zauna tana amsa gaisuwan shi, hira akan ɗanyi a parlon kaɗan, sannan yayah muhammad yace mutashi mu tafi kafin a fara shirin jumma'a , haka ko akayi, mota ɗaya aka ce zamu yi tafiyan da ita.

hajiya ummah ance tayi sati achan, tafiyan da mamah zamuyi, sai Aunty B, Aunty J, ni sai Hafsy kuma, mamie da ummie ance gobe zasu taho da su yayah yan ɗaurin aure, fitowan mu dukkan mu muka wuce side ɗin mamie don a gaisheta, nidai ina ta bayan yayah muhammad, kuda muka shiga muka samu Raliya da mamie zaune a parlor suna cin abinci suna hiran su ƙasa-ƙasa, ban fito fili yadda zata ganni sosai ba, gaisheta mukayi tana wani bin mu da kallo kaman taga kashi a zube a wurin, yayah Ahmad ne ke tambayan Raliya dama tazo ne?

Kafin ta bashi amsa mamie tayi charaf tace, "taxo tun ranan laraba, ina xaku sani kun watsar da ita kaman ita ba ɗaya take da su Ayshaa ba a wurinku, tou ina zaku sani tunda ita ta dawo bare a cikinku,

Ta faɗa tana wani banzan kallo wasu Aunty B da suke miƙewa domin barin parlon, shi ma A.G miƙewa yayi yabi bayan su, nidai ina manne sosai ta bayan yayah muhammad, don ni ko cikin bana so ta gani, don ma ummie ne tace na biyu su mu shigo tare amma da banyi niyyan zuwa ba.

Murmushi yayah muhammad yayi sannan yace, "mamie kenan Allah ya rufa asiri, amma ita inaga ko number ɗaya daga cikin mu bata da shi, ba'a taɓa mana haihuwa ta ƙira wani tayi barka ba ballantana taje suna, ina kaduna ina Abujah"?

Sunkuyar da kai ƙasa Raliya tayi alaman ta ɗan ji kunya, don yaushe ma su yayah muhammad suke magana ballantana har du nuna maka abunda kayi ya ɓata musu rai ko baiyi daɗi ba a wurin su?

"Tou ae ganu tayi baku damu da ita bane, waye a cikin ku ya taɓa bin inda take? Don kunga ita Allah bai bata haihuwa ba ko? Don ma yanzunaga alaman sun zama biyu, don ga ita Ayshann ma abokiyar auren ta har ta haihu amma ita shiru, anyi biyu kenan a gidan magadan mamah, Allah dai yasa ba maman suka gado ba".

Miƙewa mukayi dukkan mu, yayah Ahmad ne ya bata amsa da, "insha Allahu suma zasu haifi nasu, fatan da muke musu kenan", ni dai fit nayi na fice a parlon, gaban motan na shige na xauna, inda mamah da Aunty B suka zauna a tsakiya, chan baya kuma Aunty J da hafsy suka zauna, yara kuma dama Aunty j ta ajiye su a gidan su, daga Areefh har Ameer ɗinta, babynta Ammar kuma yana riƙe a hannun Yayah Ahmad, sai da ta shiga tukun ya miƙa mata shi, addu'a sosai suka mana, A.G dai babu ko kunya yana tsaye a ƙofan da nake zaune, sai da driver zai tashi ya ɗan sunkuyo kaɗan yace, "ki kula mun da baby nah plz beauty", murmushi nayi na mishi alaman ummie fah naganin mu, itama ummin kaman tasan magananta nakeyi sai ta juya ciki, lumshe mun ido yayi bayan ya kashe ido mun ido ɗaya, murmushi nayi na ɗagawa su yayah hannu, da fatan sai sun shigo goben idan Allah ya kaimu.

Hadiza taji daɗin zuwan mu sosai, achan muka samu zainab da maryam besty nah, aiko munsha chaftah ranan, suna ta zolayana da cikin A.G, maryam har da cewa, "yanzu yadda A.G yake wani ciccin magani yana basarwa haka ya juye wa yar mutane ciki babu kunya"? Dariya da kan mu mukayi, bakina baiyi shiru ba nace, "yadda Dr Abduol babu kunya ya juye miki nashi haka shima Jarumi na ya juye mun nashi", na faɗa ina juya ido ina rausayarwa, dariya duka mukayi Anan kuma aka ƙira fatima itama aka zolayeta, sannan aka ƙira jammy aka sha dariya da ita don video call akayi da su dukkan su, haka kuma sukayita zolayana, Allah sarki ƙarshe sai da nafara kukan tunawa da sisto na habiba, kai rayuwa ina jin mutuwan habiba kaman zai fasa mun zuciya idan na tuna, habiba tana son taji ana labarin rayuwar aure tsakanin mata da miji, ana farawa zakaga ta matso tana munafukin dariya, gashi yau babu ita a duniyan, kukan da nafara ne ya kawo ƙarshen rahan mu,

dayake a side ɗin matar yayanmu babban wan su hadiza muka zauna, ɗakuna biyu ne sai muka kama ɗaya, haka duk jikin kowa yayi sanyi,ita dai zainab tashi tayi ta fice dama tun wuri, ita zainab bikinta da Abdoulmaleek sai April, watan haihuwa na kenan, yanzu kuma january muke.

Waliman kuwa yayi kyau amaryah ma tasha kyau sosai

Bayan mun dawo ne da daddare mukaje duk muka gaida Bappanun mu nida hafsy da su Aunty B da suka sauƙa a ɗaya side ɗin da Abba ya gina, kusan ɗakuna 6 ne a wannan gidan, ɗakin ummie suka buɗe a ciki suka sauƙa,mamah ma a nata ɗakin ta sauƙa tare da hafsy, hajiya ummah kuma nata ɗakin tare da Aunty Rakiya da Aunty ma'u.

********* Washe gari tun ƙarfe 9:00am bata cika ba su Abba da dukka yayuna da ummie,mamie, raliya suka iso, mota Biyu sukayi suma, yayah Muhammad ke jan su Abba da su mamie da ummie, Abba ke zaune gaba tare da yayah da yake ja, baya kuma umie ne da mamie sai raliya, ɗayan motan kuma Yayah Ahmad ne tare Da A.G a gaba, baya kuma M.G ne da heedayah sai babyn su Affan.

Babban parlon side ɗin Abbah suka sauƙa, kuma nan aka kai abin breakfast, duka yan'uwan Abba sunzi sun gaisa, maza da mata da yayayensu, nidai parlon ummie muka zauna tare da A.G, daga bayane da suka shigo muka fice domin a basu wuri suyi break, parlon mamah duk muka koma, kuma har lokacin bamu haɗu da mamie ba.

Ƙarfr 11:00am aka ɗaura auren hadiza da suraj, kuma aranan zaayi wuni, kuma akaita family house ɗinsu suraj inda yayi ginin shi, washe gari da sassafe za'a wuce da ita kaduna inda gidan ta yake.

Anyi wuni mai daƈi cike da jin daƈin ganin yʻan'uwa Abba da yʻan'uwanshi kaman bazasu rabu ba suke ji, ƙarfe biyar da kusan rabu Abba yace duk su ummie da suka zo tare yau su fito a wuce gida, har waje muka rako su, inda Abba yace ita Raliya ta zauna ta biyo mu gobe, amma fir mamie taƙi, inda take cewa gobe wai da wuri zasu fita da surkuwarta, jin haka ne yasa Abba rabuwa da su, muna tsaye a waje ga mutane dayawa ana jiran fitowan Abba, kawai saiga mamie da raliya biye a bayan Abba suma sun fito, nidai ina tsayʻe gefen headayah rungume da Affan, gefe na kuma xainab ce a tsaye.

Wani irin Salati da mamie ta zabga ne ya bani tsoro, wanda ya jawo hankalin kowa kan ta, "me nake gani tare da ayshaa kaman ciki? Yayah akayi kuma naga ciki"? Kalmar da ta fito da ƙarfi kenan a bakinta, hakan kuma ya jawo hankalin kowa zuwa gareni, nidai duk sai naji tsoro da kunya ya kamani, "ikon Allah kuwa, wanda yake bayarwa a duk lokacin da yaji ya mishi, wanda yake hanawa a duk lokacin da yaji ya mishi, shi ya bata ya kuma tsare mata shi har ya kai haka, ba dabaranta babu ikonta, sai ƙarfin mulki irin na rabbil- izzati" Aunty Rakiya ta faƈa tana karɓan Affan da yake hannuna, ko lura da irin tsoritan da nayi tayi, hala shiyasa ta karɓe yaron ko kuma mamie ta samu daman ganin abunda ke cikin ne ohoo.

"Tou ae ban taɓa zato ko tunanin ayshaa zata haihu ba, na ƈauka ita da raliya sun gado mamah ne, abun ne yaban mamaki don ba haka aka gaya mun ba" mamie ta sake faƈa cike da suɓutar baki, dariya mai sautimamah tayi sannan tace, "abu na Allah kuwa, ae shi baya shawara yake abun shi, gado kuma ae raluya ce kaƈai a gidan nan ta gado ni, nima Allah yasan dalilin daya sa bai bani ba, bawai shirkah ko tsafin mutane bane ya hanani, duk cikin rahamar shi yasa bai bani ba, kuma bana baƙin ciki, tunda yabawa mijina kuma Alhmdllh inaji kaman ni na haifah, bani da damuwa ko baƙin cikin komai, Ayshaa kuma Allah ya bata sai fatan Allah ya inganta shi ya sauƙe ta lafiya, Allah kuma ya kare mata daga sharrin ma sharranta".

Tsawa Abba ya daka musu ganin zasu fara baza hali a wurin, ga surakunen shi ga yʻan'uwa da yʻan unguwa, ga kuma ya hango hajiya ummah ta fito, mota ya nuna wa mamie akan ta shige su tafi, aiko hajiya ummah ta iso wurin hafsy a bayanta, daga gani ita ta ƙirata, mitsi - mitsi tayi da ido tana kallin Abba tana maida kallonta kan mamie kuma, "amma dai hauwa anyi mutuniyar banza anan, har yanzu usmanu bai ƈauki shawarana ya kai ki ƙasar india anmiki sabon ƈashen zuciyar ba ko? Tou aniyar ki ta biki, insha Allah khairan a gidan ayshaa babu sharran, sharran ya ƙare akanki da munafukar yʻarki da tayi saura, rashin haihuwa ba Allah yaƙi mutum bane sakarya abokiyar tafiyan shaiƈan, gaskiya kin cuci usmanu da yahaƈa zuriya da ke,

tou ta Allah ba taki ba wuce da mummunar fuskar ki aniyarki ta biki ku tafi," sannan ta maida kallonta kan A.G tace, "kai kuma ja matar ka ku tafi, ka kaita chan wurin dattijuwar kakarka kace inji ni a rubuce mata Tabara da yaseen, a ƙara da lahaula saboda sharrin bakun maƙiya, ni nan ina wurin bikin jikata ce, bazan samu zama da ita na saka a rubuce shi tsaff ba, inda hali qur'ani ma izzu sittin a rubucr mata, din sharrin matar usmanu yawa ne da shi".

Abba ne ya ƙurawa Aunty Rakiya ido ita kuma ta gane mai yake nufi, kamo hannun hajiya ummah da ta fashe da kuka tana tsinewa sharrin mamie tayi, haƙuri take bata akan su juya suje ciki, sannan tacewa A.G yayi haƙuri insha Allahu babu komai, zasu kula dani gobe da wurin za'a dawo.

Ajiyan zuciya yayi yana bina da kallo, hannu na za<nab ta riƙo muka koma gida , jama'a dai sai mamakin halin mamie kawai akeyi, haka suka tafi mu kuma muka dawo gida.

Aiko suna isa bauchi a tsorace heedayah ta labartawa mummy, jiki na rawa mummy ta sanar da Daddah da Daddy, shi kanshi Daddyn ya umurci A.G ya koma ya ɗaukoni, babu inda xan kwana sai nan, haka ko akayi muna idar da sallan ishaa sai ga call ɗinshi, waje na futa cike da mamaki, ai kuwa ganin shi nayi a mota zaune shida M.G,

Buɗe mun sit ɗin baya yayi na shiga, sannan ya ɗaga waya ya ƙira hafsy,nidai bai wani sake fuska ba shiyasa ban iya mishi magana ba, sakata yayi ta tattaru mishi duka kayana yace ta kawo mota muna jiranta.

Dariya kawai Aunty Rakiya tayi lokacin da hafsy ta gaya mata xamu tafi, ita kuma Hajiya ummah da mamah daɗi abun ya musu, sai addu'a isa lafiya kawai suke mana.

Banso ba don banyi sallama da kowa ba, hattah hadiza bamu haɗu ba, akan zamu zo gidan ta idan mun gama, don banje kai amaryah ba akan daga baya sai muje.

Haka yaja motan shiru baya kula owa, A.G dai nada dana sani ya koma mun, sai M.G ne kawai yake ɗan hira dani jifa-jifah, shima ganin nakasa nutsuwa ya saka ya rabu dani.

Fadaman mada Mukaje Gidan su A.G, har waje mummy da heedayah suka fito taryan mu, ina ankare da mummy yadda hankalinta yake tashe, fitowa tayi ta riƙo hannun na muka shige parlor, ita kuma heedayah ta karɓi kayana da yake hannun A.G.

Ɗakinta taja ni muka shige, A.G kuma suka zauna a parlor shida M.G, heedayah ta wuce kitchen kawo musu drinks.

Har bakin gado Mummy ta karasa riƙe da hannu na, zama mukayi still hannun ta rike da nawa, cike da damuwa tace, "Doug babu wani matsalah da kike ji ko? Idan akwai wani abu ki faɗa mun muje asibiti, sannan kuma a haƙura da haɗuwa da wannan ƙatuwar azzalumar, duk da dai matar mahaifinki ne amma a kiyayeta don Allah doug, don duk abunda tayi sanadi ya samu cikin nan sai nayi shari'a da ita, kuma zata gane shayi ruwa ne", ajiyan zuciya na sauƙe mai ɗan karfi kaɗan, "akwai wani abu da kike son ci ne"? ta sake tambayana a cike da tashin hankali, idona na ɗaga na kalli A.G daya shigo ya ƙura mun ido, mirmushi nayi don hankalin su dukka ya kwanta, "mummy babu komai da nakeji, kawai zanyi wanka ne sai nasha tea".

Ina gama rufe bakina naga ya juya ya fice a ɗakin, dawo da kallo na nayi kan mummy ina mai cike da kunyarta nace, "Allah da gaske mummy babu komai, kuma bana in komai", murmushi itama tayi kaɗan wanda bai ƙarasa har ciki ba, daga gani iya kan leɓe ne, tashi tayi tsaye tana tambayana, "zaki iya wankan ko kuma A.G yazo ya taimaka miki? Bana son ki ɓoye mun idan kina jin wani abu, fatana ma Allah yasa babu komai ɗin, don gsky zan ciwa matar nan mutunci yadda bata zato, Allah ya sauƙe lafiya", ta faɗa tana karasawa jikin mirrow.

Tashi nayi ina ƙoƙarin shiga toilet sai ga A.G nawa ya shigo hannun shi ɗauke da cup ɗin tea, ɗaya hannun kuma ɗauke da snacks a filet, ido na ƙura mishi, ganin har lokacin fuskan shi a ɗaure, kuma na rasa meye dalilin fushin, ajiye mun cup ɗin yayi da filet ɗin, sannan ya bani umurnin na zauna nasha tukun nayi wankan.

Mummy ficewa tayi a ɗakin ta barmu, ganin babu fuska yasa ban wani ja musu ba na zauna na ɗauki cup ɗin, idan na ɗago zan ajiye tea ɗin sai naga irin kallon da yake mun, dole yake sakani ci gaba da sha, ban ankara ba na shanye tea ɗin dukka, nine da sha amma shine kuma da ajiyan zuciya, runtse ido nayi ina jin yadda ɗumin tea ɗin yake zaga dukkan illahirin jikina, "zaki iya shiga toilet ɗin ne ko na taimaka miki"? Sautin muryan shi naji dab dani, buɗe ido nayi na zuba mishi dukka kaifin idonuna akan shi, sannan na maida kaina kalan tausayi, don fushin na shi ya dame ni, harara na yayi na wasa yace, "baki son kiyaye abu ko? Bakinki bazai buɗe kice zaki biyo mu ba ko? Idan wani abu ya sameki fah"? Ya faɗa kaman zaiyi kuka, zuwa nayi gaban shi kawai na rungumeshi, "Jarumina afuwan".

Shiru yayi bai ce uffan ba, daga baya kuma ya saka hannun shi ya rungumeni sosai, mun daɗe a haka babu wanda yayi magana, sai numfashi kawai da kowan mu yake sauƙewa, "Eeshaa na don Allah ki kula mun da kanki, ni matar nan tsoro take bani, babu imani a zuciyarta," ƙara rungumeshi nayi amma sai nai ya ɗan sassauta, ɗago fuskana yayi ya ƙura mun ido, "beauty ina jin babyn mu na motsi, ko mun matse ta ne"? Murmushi nayi na cika shi nayi hanyar toilet, nasan zai iya biyoni don ba kunyar mummy yake ba, shiyasa ina shiga nasaka key a ƙofan, har bakin ƙofan yazo yana mun faɗa, "beauty ki buɗe ƙofan mana, baki san hatsari bane ki shiga ki rufe ƙofa"?

Shiru na mishi ban kula shi ba, wanka na nayi na fito, hararana yayi dana fito sannan ya juya ya fice.

Murmushi nayi kawai na wuce nasaka kaya, ina gamawa mummy ta shigo ɗakin tare da heedayah, sallama heedayah ta mun, nidai daga zaune na mata sallama ban wani tashi rakiya ba, don yanzu muna haɗuwa da A.G zaice bana kiyayewa, daga nan ma kwanciyata nayi ina ɗan chatt dasu jammy dasu Fatima, a haka har bacci ya fara ƙoƙarin ɗauka na, tashi nayi nayi addu'a, kashe wutan nayi na kwanta a buna.

Da Asuba alerm ya tashe ni, nayi mamakin irin baccin da nayi, don tunda na kwanta ban farka ba sai da na tashi sallan asuba, gani nayi an lulluɓeni an saka mun hula akaina, nasan kuma ko A.G ne ko Mummy.

Addu'a sosai Alhaji Inuwa ya bani a rubuce a wani takadda, duk addu'a ne na neman tsari, haka muka juya Abujah lafiya bayan yan biki sun dawo.

Haihuwar Aunty B lokacin cikina ya shiga 8month, itama boy ɗin ta haifah, mudai wato gidan mu babu jika ya mace sai masu ƙaton kai, haka jiki na rawa don ɗauki mukaje gida ganin baby, don haihuwar yazo mata da sauƙi babu wani jinkiri, saboda haka a gida mukaje muka same su, shima wannan yaron kaman areef damu yake kama, nayita wa Aunty Dariyan bai ɗauko ta ba, don tasha alwashin ita zai biyu, shima wannan yaron farine kyakkyawa da shi, amma yafi ɗauko yayah umar da hafsy,

A gidan na wuni har bayan ishaa A.G nah yazo muka tafi,.

Ranan suna yaro yaci sunan Yayah Ahmad, aka mishi laƙabi da *DEEDAT* yasha gata kam kaman babu gobe, nidai wani ƙaunar yaron nakeji a zuciyata kaman me, duk da son da zanyi wa kowani yaro bazai kai irin son da nayiwa Areef ba, amma kowanne ina son shi na Areef ne daban, Deedat kuma ko don sunan yayah Ahmad ne, sai nakejin daban a zuciyata, muna tare da Fatima da su hafsy, a gida na Fatima da hafsy suka sauƙa, saboda haka da zamu tafi tare A.G yazo ɗaukan mu.

****

04/04/2023 na haihu, ansha gumurzu amma an sauƙa lafiya, labour room A.G na kan gaba kaman shi zai fitar da babyn, Yayah Ahmad, Yayah Muhammad, M.G da matansu duk suna tare da mu a asibitin, mai gayyah mai komai kuma yana ɗakin na haihu, yana rungume da kaina yana mun addu'a, dukka hannayena suna riƙe da shi, kukan babyn ne yasaka ya runtse ido yana furta, "ALHAMDULILLAH! ALHAMDULILLAH!! ALHAMDULILLAH!!! sai da yayi baki uku tukun ya buɗe idon shi ya manna mun kiss a fuskana da ya jiƙe da zufa, ɗago da babyn akayi aka nuna mun suna tambayana me na haifah?

Murmushi nayi na runtse ido na ina hamdalah a zuciyata, naji daɗi don ko babu komai nasan na farantawa A.G dayaci burin haihuwar yƴa mace, tashi yayi da sauri ya amshi babyn yana ta furta hamdalah, Gyarani sosai akayi sannan aka gyara babyn aka miƙa mishi, suka fice a ɗakin, addu'a sosai ya yiwa babyn, sannan ya dawo da kallon shi kaina, saboda jin ƙiran sunan shi da nayi a hankali " Jarumina, ina neman alfarma don Allah", na faɗa murya chan kasa a gajjiye, "beauty me kike son na miki"? Murmushi nayi na mishi alaman ya matsu, dab dani kuwa ya matso, ƙurawa babyn mukayi ni da shi muna kallonta ganin yadda taketa motsa baki kaman wanda za'a bata abinci ta karɓa, murmushi mukayi dukkan mu Idon mu akanta, wani irin ƙaunarta kaman zai fasa zuciyar mu, "jarumina sunan Mummy nake so a saka wa babyn mu mai kama da Abbinta, next year insha Allahu zamu kawo ummie, saboda jarumina Gwarzo ne", na faɗa ina kashe mishi ido, murmushi yayi ya sumbace ni, kafin yace wani abu akayi nocking ƙofan ɗakin, su yayah ne da matan su sai M.G da heedayah suka shigo, kowa ɗaukan babyn yayi ana ta santin kyaunta da girmanta, babu abunda ta bari na kama da A.G, har irin manyan idon shi ta ɗauko, lura yayi da yadda jikin heedayah yake rawan son ɗaukan babyn, sai ya karɓi yaron hannunta Affan ya bata hanya, kaman bata taɓa ganin jaririya ba sai ranan, bakinta yaƙi rufuwa don farin ciki, rungume babyn tayi tsam a jikinta tana ta smilling, da ƙyar dai ta miƙawa su Aunty J, ɗauka akai tayi 1 by 1, kowa kuma sai yayi addu'a idan ya ɗauka, M.G ne ɗaukan ƙarshe, babu tunanin komai kuwa ko shawara yayi wa jaririyar Huɗuba da sunan Mummy, Wato *RASHIDA* kaman wanda yasan abunda yake zuciyar mu kenan, ɗago da kai yayi ya ƙurawa A.G ido, chan kuma yayi murmushi yace, "sunan yƴar mu RASHIDAT wato mummy, sai anema mata nickname don sakaye sunan", lumshe ido A.G yayi ya buɗe su akaina, murmushi nayi na maida kallona kan M.G da yake miƙawa heedayah yƴar, su yayah dukkansu suka fice a ɗakin sukayi waje, sunaye kala -kala heedayah take ta ambatawa don zaɓawa yƴar ta, nidai murmushi nakeyi kawai ina kallonsu.

Babu daɗewa mummy suka ƙira waya ita dasu Hudah da su Goggo, hattah Daddah ma sai data ƙira, ummie da su hafsy duk sun ƙira, hafsy tana ta roƙon Aunty J da heedayah su mata video baby su turo mata, sai ja mata rai sukeyi.

Ana sallaman mu muka wuce gida, wanka sosai aka mun akayi wa babyn ma, inda aka saka mata pink kaya tayi kyau sosai, hattah farinta ya wani fito kamar yʻar turawa, nima kaina sha'awan yʻar naji ya cikani.

Har dare tukun heedayah ta tafi gidan ta, don su Aunty B ana magrib suka tafi, amma matar da take wurinta ta zauna mun, don gobe mai zuwa mun biƙi zata taho daga bauchi ini yayah muhammad.

Anyi haihuwar yau washegari sai ga Abba, naji daƌin ganin shi, don shima yaji daƌin ganina lpy babyn ma lpy, a wurin yayi ta tsokanan su ummie daya ƙira su awaya, yana ce musu shi yanzu ya tare a wurin sabuwar amaryan shi, dariya sosai mukayi, bayan ya tafi ne A.G ya shigo har ƌakin ya zauna bakin gadon, ƌaukan babyn yayi ya ƙura mata ido, "beauty ashe fah na fiki kyau", kallon shi nayi baki buƌe, "ta ina kafini kyau jarumina"? na tambaye shi cike da mamaki, dariya yayi yana kallon babyn yace, "dubi yʻata yadda tayi kyau saboda ta ƌauko kyauna, kinga fa ta fiki kyau sosai yarinyar nan", ya faƌa yana manna mata kiss a goshi.

Ya mutsa fuska nayi nace, "kyauna ta ƌauko, kasan sbd ta haƌa jini dani ne yasa kyaun nata bayyana sosai, da watace ta haifeta kyaun baxai kai haka ba", na faƌa ina jan zip ƌin rigana da yake zuge.

Murmushi yayi yace, "wani suna zamu ƙira mummy da shi"? Kallon shi nayi da yʻar a hannun shi nace, *NASREEN* murmushi yayi ya sumbaci babyn yace, "Allah ya raya mun mumsy nah, Allah ya mata albarka flower gidan aljannah, Allah ya haskaka rayuwarta", da Ameen na amsa mishi, muryan shigowan heedayah da mukaji ne ya saka shi ajiyeta ya fice.

Yʻan bauchi sunzo sosai, daga gefe na da gefe A.G duk an zo, ranan suna kuwa babyn tacu sunan *RASHIDAT AMINU GARBA, (NASREEN)*

Munsha gata sosai nida baby na, daga mahaifinta har yʻan'uwana da kakanun ta sun mata gata, anyi suna da 2dys ummie da mummy suka zo ganin Nasreen, ranan naga ƙauna na zahiri a wurin mummy, don gaba ƌaya ƙaunar A.G da takeyi duk ya koma kan Nasreen.

Nasreen watan ta uku wani tsautsayi ya hau kaina, don zazzaɓi sosai nayi, ga wani ulcer daya sakoni gaba, muna zuwa asibiti kawai sai ga ciki, nayi kuka kaman zuciyata zatayi bindiga, na birkicewa A.G akan sai na zubar da cikin, munyi rikici sosai da shi sosai a lokacin, amma daga baya yafi ƙarfina na haƙura, domin fita hidimana yayi gaba ɗaya, baya kulani baya cin abinci na, idan na gaishe shi baxai amsa ba, sai dai kawai ya shigo ya ɗauki Nasreen yayi mata wasa, idan ya dawo ma ya ɗauke ta ya wuce ɗakin shi da ita, baya fito da ita har sai idan tayi kuka, wani lokacin har suyi bacci tare.

Abun ya taɓa zuciyata sosai, ballantana wani rana da yayi tafiya bai sanar mun ba, ya shigo da safe ina toilet, ina jin shi yayi ta mata wasa, fitowa na kuma ya tafi, tashin fitan motan shi kawai naji, sai da yammah da heedayah ta shigo ne naji wai yaje jos kuma asthman shi ya tashi, Daddy ya tura driver ya ɗauke shi, mummy duk hankalinta ya tashi, sbd ko awa guda baiyi da shiga jos ɗin ba ya tashi, cikinane naji yayi wani sauti kaman ana buga ganka, sai dai naƙi nuna mata ban san da tafiyan ba, sai dai na nuna ban san ciwon ba, har ima vewa ko shiyasana ƙira bai ɗauka ba, nan dai tace tou kada na faɗa ita ta gaya mun, domin yayah zaici ubanta, gaskiya na shiga tashin hankali, kuma alokacin nayi wa kaina faɗa,bazan zubar da cikin ba, zan kuma neme sulhu.

Da dare na ƙira wayan shi lokacin yana tare da mummy, bai ɗauka ba mummyn ce ta ɗauka tace mun, "doug yayah kuke"? Amsa mata nayi da muna lafiya, bayan mun gaisa take cemun gashinan bacci yakeyi, amma gobe insha Allahu zai biyo jirgi ya dawo Abujah,idan ya tashi zai ƙira, godiya na mata daga baya take tambayana mai sunanta.

Wurin 9:00am M.G ya ɗauko shi daga airpot, gida suka taho tare, sun dawo ina kitchen, jin sautin muryan M.G ne ya fito dani ina kallon A.G daya wuce bedroom ɗin shi, bayan mun gaisa da M.G ne ya mun sallama ya wuce ya fita, barin abinda nakeyi nayi na wuce side ɗinshi Nasreen goye a bayana tana ta bin ko ina da kallo, ga ajiyar zuciyar da ta ke tayi, domin yau rikici ta tashi da shi tun asuba, taƙi kwanciya ita kaɗai sai dana goyata tukun tayi shiru.

Ina shiga naji shi a toilet ɗinshi, zama nayi bakin gadon ina kunce nasreen da take shirin cika 4month, don kwanaki ne ya saura ta cika, ɗago ido nayi na ƙura mishi ganin ya fito, kallo ɗaya ya mun ya ma yar da kallon shi kan nasreen, wuce mu yayi ya zauna a bakin gadon shi, ganin irin shareni da yayi ya saka na kwantar da nasreen akan gadon.

Tashi nayi naje har gaban shi na tsuguna a gaban shi ina kallon fuskar shi daya matsar da shi ya bar kallona, hannu na nasaka na riƙo nashi hannun duka biyu, ina ganin alaman zai ƙwace hannun shi nayi sauri na rungume shi na fashe da kuka, shiru yayi yabar ƙoƙarin tureni a jikin shin, kuka sosai nake mishi ina ƙara rungumeshi ajikina, kaman nasreen ta san fushi Abbinta yakeyi dani sai ita ma ta fashe da kuka, da sauri ya ɗagoni ya matsa ya ɗauko ta ya rungume yana rarrashi, ganin ya miƙe da ita tsaye yana jijjigata nima na miƙe naje na rungumesu shi da ita ina mishi nawa kukan itama tanayi, "Jarumina na kawo ƙaran kaina wurinka, don Allah ka mun hukunci da bulala bada kanka ba, ina buƙatan ka sosai nida ummie nah dake manne a cikina, baby nah ina kewan ka sosai don Allah ka yafe mun, ko kuma ka hukunta ni da dorina amma bada ƙaurace mun ba Gwarzo na, na gajji bazan iya ba", na faɗa ina ƙara sautin kuka na, ita ma nasreen sai ƙara nata kukan takeyi, ganin duk mun rikita shi sai ya kamo hannu na muka zauna a bakin gadon, ɗaura mun ita yayi akan cinya na yace, "ki rarrasheta sai naji da ke tukun", kallon fuskan shi nayi cike da tausayawa, ganin har lokacin yana fusgan numfashin ne da ƙyar, nono na saka matata ɗan fara sha kaɗan yana shafah mata kanta a hankali, tayi shiru tana sha tana kallon fuskana, idona mayar kan shi, shima kallona yakeyi cike da alaman jin jiki.

Bacci ta koma bayan tasha nonon, ganin ta sake nonon ya sa ya karɓeta ya ɗaura ta a kafaɗan shi, chan bayan tayi gyatsa ya maida ta kan gadon ya kwantar, sannan ya miƙo mun hannun shi, da sauri na ƙarasa jikin shi ya rungume ni.

"Beauty bana son rikici kinji, idan kin zubar mun da ciki ae baki sonane kuma baki godewa Allah daya baki ba ko?"

Jijjiga kai nayi bance komai ba sai kukan daya zo mun na ba shiri, murmushi mai sauti yayi, "kayi fushi dani jarumina, gaba ɗaya bana jin farin ciki, bazan ƙara ba, ko yanzu ma ka ƙara wani cikin akan wannan ina so".

Wannan karon sautin dariyan shi ne ya fito, "Beautyn A.G wannan ma dana baki ajiya kinyi mun tawaye inaga na ƙara wani akai kuma fah? ae sai ki gudu ki barni, ki saka nayi ƙaramin hauka", ya faɗa yana sunsuna wuyana yana dariyan kukan da na sake baki ina yi.

Ganin kukan yaƙi ƙare ya saka shi rarrashi na dole, ni ma na bashi haƙuri sosai na nemi gafaran rikicin dana mishi, "beauty tun ranan na yafe miki, ban taɓa kwana dake a zuciyata batare dana yafe miki ba, nidai fatah na da buri na ki riƙe mun ɣayɣana da amana, ki kula dasu da tarbiyan su, ki sani bayan Mummuy duk duniya

babu abunds nake so irinki da yayana," ya juyar da kanshi ya dubi nasreen da take bacci, sannan ya dawo da kanshi kaina, "Eeshan A.G" ya faɗa idon shi na kaina,

"Beautyn A.G" ya sake faɗa yana lumshe ido yana kallo na,

"Babyn nah ki kula mun da Nasreen duk duniya bani da sama da ita, ki kula mun da abunda yake cikin ki ina mata wani so na musamman, kaman ina mata son da duk wani mahaifi ba zai taɓa yiwa yar shi haka ba," kallon shi yadda yake shafa cikin, "idan kuma namijine fah"? Naji bakina ya tambaye shi, murmushi yayi ya sumbuce ni.

"*NANAH KHADIJAH CE* insha Allahu, amma idan Allah yayi ikon shi yazama namiji ne tou masoyinane ".

"Daddy" na tambaye shi, murmushi ya kuma yi yace, "Daddy mahaifinane, M.G masoyina ne, ina son shi, ke kaɗai ne a duniya kika ture wannan gwamnatin shi a zuciyana, har nafi jin daɗin zama da ke akan shi", ya faɗa yana wani turo bakin shi gaba irin na sakalcin nan da yakeyi idan yana tare da Mummy, buge bakin nayi da wasa nace, "Babyn mummy kawai", dariya yayi ya rungumeni a jikin shi gam, yana kuma jan numfashi babu daɗi.

"A.G na ko za'aje asibiti ne?" na tambaye shi, ƙara rungumeni yayi yace, "kawai ki gaisa da GITANDRA muna gaisawa zan ware," murmushi nayi nace bari na kawo maka tea mai ɗan zafi kasha tukun, rungumeni ya sakeyi yana ƙara maida kanshi wuyana.

Wani abu daya bani mamaki a wannan ranan guda biyu ne, shine irin baccin da Nasreen tayi har zuwa azahar bata tashi ba, da kuma A.G daya kasa barina har zuwa azahar abu ɗaya yakeyi,A.G baida yawan takuri, idan yaga bakida buƙata yana ɗaga ƙafa, amma yau na gajji har sai da nayi kuka lokacin da ya dawo mun ana uku wurin azahar, ina fara kuka shima yafara mun kuka, "Eesha kada ki guje ni, Eeshaa ina sonki! Eesha kina mun daɗi! Eesha Allah ya kare mun ke da yayana", jin surutan shi yasa na haƙura da ƙyar, ana fara ƙiran azahar na zame jikina ana shi, toilet na shige na sakarwa kaina ruwan zafi a chan, lokacin kuma Nasreen sai ta tashi, wurinta ya koma yana rarrashi.

Dana fito a toilet kitchen na wuce na bar shi tare da Nasreen, bansan yyh yayi da ita ba tayi shiru, don nidai abinci na ɗaura, achan kitchen ɗin ya tarar dani yana rungume da nasreen da har lokacin ƙananun rikici takeyi, "Eesha sai ina ji kaman yarinyar nan bata da lafiya ne, ga rikicin ta yaƙi ƙarewa ga kuma yanzu naji jikin da ɗan ɗumi, sai mura kuma".

Juyowa nayi na dube shi yadda naji yana ɗan jan numfashin shi yasa na ajiye abunda nakeyi na ƙarasa dab da shi, "A.G da ruwan sanyi kayi wankan ne? Naji kaman numfashin yana maka wuyan ja"? Hannu na miƙa na karɓi nasreen, amma

sai ta maida kanta kafaɗan shi ta kwanta, wuyanta na taɓa naji da ɗumi, maida kallona nayi kanshi yadda yayi mun kyau sosai cikin white three quater da white armless da ya saka, sai ƙamshi mai ɗan sanyin daɗi yake yi, "A.G na kaida doug ka gaba ɗaya baku jin daɗi, ko na ƙira M.G ne kuje asibiti? Bana jin daɗin ganin haka", na faɗa ina ƙoƙarin ɗaukan wayana, amma sai naji ya saka hannun shi ya karɓe wayan, gefe ya aiye ya matso ya haɗani da nasreen ɗin duk ya rungume mu.

"Eesha ki bar maganan asibitin nan, yanzu sai hankalin mummy ya tashi, babu wani abu ae na shaƙi inhela yanzu kafin na fito, kawai kiji damu nida yɗata", ya faɗa yana ƙara manna ni sosai a jikin shi, "tou bari na mana ɗan abinda zamu ci sharp-sharp", girgiza kai yayi alaman a'a na bari.

"Baby tou me zamu ci"?

Lumshe ido yayi yana ƙara mannuwa da jikina yace, "ki ƙira heedayah kice tayi abinci dake, nidai kizo ki kula damu, bamu da lafiya", ajiyan zuciya na sauƙe mai ɗan ƙarfi, "kai bazak ci abincin bane"?

Ɗago kai yayi ya kalleni, "kice ta mun peppesoup kawai ya isa", riƙo hannun shi nayi muka fito daga kitchen ɗin, bayan mun zauna aparlon ne na ƙira Heedayah nace tayi mun peppesoup ta soya mun irish, muna gama wayan na sake miƙa hannu zan karɓi nasreen amma taƙi ta sake lafewa a jikin Abbeen ta, ido na ɗan ya mutsa na tura baki gaba, da ido ya mun alaman tambaya, "ta takurani ta hanani kwanciya a ƙirjin mijina, ni ka ajiyeta na kwanta a jikinka", murmushi yayi ya miƙa mun hannu, jawoni yayi jikin shi, dai-dai kunne na yace, "mumcy baby ce amata uzuri plz, yau ɗaya taji ɗumin jikin Abbeen ta kaɗan".

Marairaice fuska nayi ina kallon yadda ta manne sosai a jikinshi, ina kalon su wayan hafsy ya shigo wayana, bayan na ɗauka mun gaisa ne take bani labarin yau Abbah yayiwa mamie kacha -kacha akan rashin kunyar da tazo har ɗaki tayiwa Ummie, kuma ya mata kyakkyawan warning akan cewa da tayi wai ta shiryah taryan baƙin ciki akan rayuwar aure na dana hafsy da ba a riga da anyi ba, yace duk abunda ya samu yaranshi itace, ina jin maganan ya fara tsayi na miƙe na wuce bedroom ɗina, sannan kuma yayah umar ya mata rantsuwa wallahi ta sake kai ƙafanta koda parlon ummie ne bada zaman lafiya ba sai ya harbeta, sai dai Abba ya sallama shi, yanzu haka ta fita tun safe a gidan ita da sister ta da tazo bayan abun ya faru.

Ajiyan zuciya na sauƙe, "tou ummien yayah ta ke? Fatan dai bata wani ɗaga hankalinta da surutun banzan matar nan ba ko"? Na tambayi hafsy.

"eh tou ba sosai ba, da hankalinta ya tashi amma dai Su Yayah sun ƙirata sun lallaɓeta sun bata baki, sunce ta ƙara ƙarfin addu'an ta akanmu, insha Allahu babu abinda ta isa tayi wanda Allah bai nufa xai faru ba, ni wallahi Adda Ayshaa narasa

meye ummie tayiwa matar nan da ta sakata a gaba? Naga dai ita tazo ta aure mata miji, ta sameta a gidan, kuma ga mamah kaman tafi ƙin ummie da mu".

Murmushi nayi idona yana kan A.G daya shigo ya kwanta shida yʼar shi da ta fara bacci a gefe na, ido na yana kan shi yadda naga yana ɗan jan numfashin shi a hankali, daga dukkan alamu yana jin jiki.

"Tou ke banda abunki Hafsy dole ae ummie ta tsole ata ido, zaratan sojoji har uku ta dire a gidan, ga kyawawan folawowi guda biyu da ta dire a gidan, ba dole tayi kishi da ummie ba, kuma duk da yarintar ta miji hankalin shi yana kan ladan noman shi, kedai kawai addu'a shi zai raba mu da kowa, da sharrin kowa, amma insha Allahu babu abunda zai sake faruwa damu,munfi ƙarfinta taji da damuwarta kawai".

Dariya hafsy tayi sannan ta tambayeni "ina A.Gn ki da Nasreen Ɗiyata"?

Murmishi nayi na saka hannu ina shafa fuskan A.G nace, "ga A.G na kwance agefe na, ga Yʼarki Nasreen kwance a gefe na ta hanani sakat da mijina, da tayi six month ma turo miki ita zanyi na huta tare da mijina", dariya ta kwashe da shi tana kashe wayan don jin nace ga A.G na kwance a gefe nah, shi kuma harara na yayi yace, "kada ki fara cire mun yʼa a nono beauty, ki bar wannan mafarin, mumcy nah sai tasha ta ƙoshi a cireta".

Dariya nayi na kwanta a jikin shi, ina shafa fuskan shi nace, "ae Jarumina kun makara da shan nono har wai kusha ko ƙoshi, ae sai dai kuga wasu suna sha amma banda ku, tunda kun cika gaggawa sai kuyi haƙuri idan kunyi 10month" na faɗa ina jan kunnen shi, tayi yayi zaune ya ɗago ni sosai muna fuskantar juna.

"Eesha kada ki cire mun mamana a nono na roƙi alfarmanki, tasha nono har sai kin haihu tukun a cireta, idan bazaki damu bama su sha a tare, shima likitoci sun yadda da hakan, amma idan kinga zaki takura tou sai ita ki cireta idan kin haihu, don Allah beauty abi yadda nace", ya faɗa da wani kalan tausayi, wanda har sai da naji kaman hawaye zai taho mun, rungumeshi nayi sosai a jikina, "baby duk yadda kace haka za'ayi, insha Allah mumcy zata sha nono har ranan da yʼar'uwarta ko ɗan'uwanta zai zo duniya, na maka wannan alƙawarin indai ina raye".

Rungumeni yayi sosai a jikin shi yace,

"insha Allahu ma kina raye, don jikina yana bani zaki rayu da yʼayʼana, zaki musu tarbiya irin wanda ni nake fata da burin ganin su da shi, don kema yʼar gidan tarbiyane mai tarbiya, sbd haka bani da damuwa da hakan, sai fatan Allah ya ƙara

miki haƙuri da juriya akan tarbiyansu, don iyaye mata dayawa rashin haƙuri da juriya ne yake saka su kasa bada tarbiya wa yaɣansu, amma ke kam bani da haufi akanki, shiyasa kullum nake ƙara godewa Allah daya mun ni'ima da samun salihar mace irinki, roƙo na da fata na Allah yasa mu kasance har aljannah a tare, Allah ya bani ke har a aljannah", ya faɗa yana ƙara matseni a jikin shi, "Eesha ina sonki wani irin son da inaga ko uwa batayiwa abunda ta haifah, wani irin sone da Allah ne kaɗai yasan irin shi, don ko ni ban isa nace ga irinshi ba, ki kula dani ki kula da yaɣana, kiyi haƙuri ki basu kulawa wanda zasu zama abun sha'awa a ko'ina, ina so su rayu tare da mu, bana fatan su tashi a hannun wani ba hanun mu ba ni da ke, ina roƙon Allah ya musi albarka, ya baki juriya beauty nah".

Shiru mukayi daga ni har shi muna rungume gam da juna babu wanda ya sake magana, sai numfashin shi da yake mishi babu daɗi, sai kuma ɗan yari kaɗan da yake yi lokaci-lokaci.

Muna haka har aka ƙira sallan la'asaar, tashi yayi ya fice masallaci ya barni, nima sallan nayi daga nan na ƙara gyara ɗakin ma fice parlor ina ɗauke da Nasreen ɗayan hannun kuma ina manne da wayana muna waya da ummie nah, muna ta labarin hali irin na mamie da raliya, wai don ɗazu Raliya ta ƙira hafsy sunyi kacha-kacha wa junan su, inda itama hafsyn bata barta ba don dama kar ne tasan kar, sunyi wa junan su fatafata yau, don sai da Abba ya ƙira raliyan ya mata babu daɗi, nidai haƙuri nayita bawa ummie, inda nake kuma sanar mata A.G nah baijin daɗi, "subhanallahi asthman shinne ya tashi? Idan ya shigo ki haɗa ni da shi, Allah ya bashi lafiya, ina kuma nasara take"? Cewar ummie dariya nayi don jin yadda ummie ke jan jikar nata, don kirarin da take mata kenan, Nasreen nasaran mata, bayan munyi sallama ne kaɗan sai ga heedayah ta shigo ɗauke da basket mai ɗan girma, kan dinning ta wuce bayan ta goye da Affan wanda ya kusa cika 1yr, idon shi biyu yana ta mun dariya, nia dariyan nake mishi har ta ƙarasa kan dinning ɗin ta ajiye ta juyo, hannu na miƙa mishi, ai kuwa ƙoƙarin ɓalle goyon yake yi, dole ta sunce shi ta miƙo mun shi, ina karɓan shi ita kuma ta ɗauki nasreen, ɗan ya mutsa fuska tayi ta juyo tana kallona, "Aunty yayah kamar yata tana ɗan zazzaɓi"? Lumshe ido nayi na buɗe akan Affan daya ke tsallen sun sauƙa ƙasa daga cinya na yana wasan shi, "wallahi kuwa heedayah, harda mura ma", na faɗa ina kallon idon Nasreen ɗin, "an bata magani ne? Inaga kaman haƙori ne, don ga bakinta yana ƙarni", cewar heedayah, "da wuri zata fara laulayin haƙori kenan ", na tambayi heedayah, zama tayi gefe na rungume da Nasreen a hannunta, ido na ƙura musu sai naga kaman ita ta haifeta tsabar kamanin da sukayi, sannan na maida kaina kan Affan daya ke ta zaga parlon da, tafiyan shi wanda baigama ƙwari ba yanayi yana faɗuwa, sai dariya yakeyi don jin daɗin su na yarah, dawo da kaina nayi kan heedayah nace, "nabata maganin mura da zazzaɓi, ni na ɗauka shi yake damuta ae, ni duk asthman Abbeenta ne yake damuna wallahi, idan naji sautin numfashin shi hankalina tashi yakeyi da yadda yake fita, bana jin nutsuwa wallahi", na faɗa ina miƙawa Affan hannu daya zo kusa dani yana mun gwalantun yarah.

"Allah sarki yayah A.G wallahi asthman nan yana matsa mishi sosai, kuma idan ya tashi fah sai ya bawa mutane tsoro, amma ae da sauƙi tunda ya fita mosque nagani," cewar heedayah, haka dai mukaita hira, nan take gaya mun ta haɗu mana da alale, jin akwai alale yasa na miƙe naje dinning ɗin, alalen na zuba da peppesoup ɗin, sai kunun gyaɗa mai zafi shima na zuba a cup, wuri na gyara na fara ci, ina kallonta jefi-jefi tana wasa da su Affan, Nasreen na lafe a jikinta.

Sai da akayi salan magrin A.G suka shigo tare da Yayah Ahmad da M.G, ɗaukan Affan yayi suka zauna a kan kujera, Yayah kuma ya ɗauki Nasreen, dayake bata ƙiwuya sai ta karɓe shi ta wani ƙura mishi ido kaman ta san waye, har sai da yayi dariya yace, "Ayshaa yar nan zatayi wayo sosai kamam hafsy", dariya dukkan mu mukayi, heedayah kamar muna fika ta musu sallama ta wuce gida, anan ta bar Affan, nima ɗaki na wuce ɗauke da Nasreen domin sun wuce dinning don cin abincin, sai da aka ƙira ishaa A.G ya mun magana nazo yaya zai tafi, sallama mukayi yace ya haɗa Ummie da A.G sun gaisa, godiya sosai na mishi, har waje na rakasu, bayan ya wuce ne na dawo na barsu tsaye shida M.G, kowa yana rungume da nashi ɗan, inda naji M.G na zolaya na wai A.G yace ya haɗa auren Nasreen da Affan, saboda haka gobe zasu musu baiko, dariya nayi na wuce ciki na barsu.

Dinning ɗin naje na tattare, duk sun cinye alalen, kunun kaɗai suka rage kaɗan sai peppesoup ɗin ma kaɗan, gyara parlon nayi naje kitchen nayi wanke-wanke, indomie na dafa da wani kifina da yake friedge, parlon na dawo naci, har nagama naje na wanke basu rabu ba, daga baya ne ma ya ƙirani na karɓi nasreen akan na bata magani tana so tayi rikici, ciki muka shiga, goge mata jiki kawai nayi da towel, nasaka mata kaya masu ɗan kauri,na bata magani sannan na saka mata nono tana sha, ido duka zube akanta inaga tsantsan kamanta da A.G, wani wurin kuma sai naga kaman Mummy, inaga da mummy take kama farinne na A.G, domin mummy kam baƙa ce, murmushi nayi na ƙura mata ido ina jin daɗin yau gani ina shayar da yar A.G, Allah sarki ashe fararen nan miji nane? Shiyasa tun ranan da na fara ganin su suka tsaya mun a raina, ashe dogon ciki wanda bai kai ɗayan haske ba rabo nane, dariya nayi ni kaɗai, sannan na cire mata nonon a baki ganin tayi bacci, kwantar da ita nayi na ɗan lulluɓata.

Toilet na shige nayi wanka na, ina fitowa nayi ɗan gyare gyare na, nasaka rigan bacci milk colour wani gajeren wando da riga armless, silk ne kayan A.G yasha gaya mun yana son wannan kayan baccin, shafa humrah nayi sosai a jikina, bayan na

gama shiryawa ne na ɗauki wayana, Data na buɗe na shiga group ɗinmu, ai kuwa hira na samu sunayi gashi full house dama ni ake jira, hira sosai mukeyi ana shan chafter, Fatima tace ta sama mana wani haɗin daka mai gigita mai gida, hadiza sai wani zaƙewa takeyi don Allah a aiko mana, nima dai cewa nayi Fati kada amanta da Eashann A.G please, muna cikin haka ne naga ya buɗe ƙofa bakin shi ɗauke da sallama ya shigo, yayi wanka ya saka wata farar jallabiys yayi kyau yayi wani haske sosai, amma kuma ciwon kwana ɗaya ko biyu har ya ramar da shi, ido na zuba mishi a zuciyata nace, "akwai matar da tayi dace da haɗaɗɗen miji irin nawa kuwa? Gsky A.G na Duniya ne".

Lumshe ido yayi ya ɗan kanne munsu, murmushi nayo na cigaba da yaba kyaunshi azuciyata, ɗaukan nasreen yayi ya gyara mata kwanciya bayan ya matsar da ita, hannu yasaka ya jawo ni yana kwantar da ni a jikin shi, kashe wutan ɗakin yayi yana cewa, "zoki gaya mun murmushin me kikeyi dana shigo ɗakin,"? sautin murmushi nane ya sake fitowa, rungumeshi nayi sosai a jikina nace, "Baby nayi dace da miji, babu wata mace a faɗin duniya da tayi dace da miji irina, daɗi nakeji idan naga wai A.G na miji nane".

Murmushi yayo yana ƙara rungumeni jikin shi sosai yace, "a hakan ma mijinki ke kaɗai insha Allahu duniya da lahira".

Rungumeshi nayi ina dariya nace "Allahu yasa ni kaɗai ce matarka A.G nah, don ranan da zaka Ƙara auren wata mutuwa zanyi nasani", "insha Allahu ma A Gn naki ne ke kaɗai, Allah ma kada ya nuna mun ranan da zan haɗaki da wata yɑ mace a duniya, don wuta xan tafi direct, bazan iya adalci a tsakanin ku ba, Allah na roƙeka kasa Eeshaa ce kawai rabona a mata", rungumeshi nayi ina jin son shi kaman zai zautar dani, murya a ɗage nace, "Ameen! Ameen!! Ameen!!! A.G nah, nagode Allah ya bar mu tare."

Ɗago ni yayi ya kunna hasken wayan shi yana kallona fuskan shi ɗauke da wani murmushi da ya mun kyaun gaske, "akwai wano namiji da zako so a duniya na bayan ni"? Ya mutsa fuska nayi ina hararan shi nace, "ae musulunci ma ya haramta mun wani ɗa namiji ballantana har ta kai dana so shi", na faɗa ina murguɗa mishi baki.

Lumshe ido yayi yana murmushi, "misali idan bana raye zaki so wani sama da yadda kika soni"?

Wani irin mummunan faɗuwar gaba naji, har sai da naji wani ɗumi a tafin hannuna dana ƙafana kamanmai zazzaɓi, fuska a ɗaure nace, "bana son sake jin irin wannan furucin jarumina, bana son irin wannan tunanin da kakeyi, nida kai insha Allahu har sai mun tsufah tare, zamu rayu da yaya anmu mu aurar da su muyi jikoki yadda su mummy suka ga jikokin su insha Allahu".

Lumshe ido yayi yana jawoni jikin shi, wani irin sex yayi dani a wannan rana da wannan lokacin wanda zance bai taɓa yin irin shi ba, don wuraren ƙarfe ɗaya kuka mai ƙarfin gaske ya saka mun, "Eeshaa kin gajji ni ka bansan me yake faruwa ba nakasa gajjiya Eesha ta, ina sonki Eesha, ina sonki Beauty nah", rungumeni yayi sosai yana kuka, "Eesha ki kula mun da yaranah, baby yarah nah, mummy nah", rungume shi nayi ina rarrashin shi, don ji nake kaman gabana xai buɗe cikin ya zubo, dauriya kawai nakeyi har nasamu yayi shiru.

Wankana tashi na shiga, bayan na fito na same shi rungume da nasreen a jikin shi ya fara bacci, tashin shi nayi a hankali nace yaje yayi wanka, Buɗe ido yayi da ƙyar yana kallona, chan kaman zai koma baccin sai kuma ya miƙe, kiss ya yiwa nasreen a goshinta sannan ya wuce toilet, baifi mintuna kaɗan ba naga ya fito, bakin gaɗon yazo ya zauna ni kuma ina kan dressing Mirrow ina busar da gashi na, tari yakeyi sosai yana jan numfashi da ƙyar, ajiye dryer nayi na zo wuron shi zama nayi a gefen shi ina shafa kanshi ina mishi sannu, "ru...wa..a," ya faɗa aɗan fusge, da sauri na koma jikin mirrow na ɗauko bottle na ruwa na kawo mishi, kaɗan yasha ya miƙo mun, sannan ya mun alama na bashi jallabiya, ɗauko wannan jalabiyan nayi na miƙa mishi, taimaka mishi nayi yasaka, ae kuwa kaman jira yakeyi agama sakawa sai numfashi yafara gardama, ga tari mai zafin gaske, nidai jikina duk rawa yakeyi na rungumeshi ina kuka.

Wayan shi ya nuna mun nayi sauri na ɗauko na miƙa mishi, murya a fusge yace, "mu..m..my" zaro ido nayi ina nuna moshi time, wurin ƙarfe biyu saura ne fah, amma sai ya ɗaga mun kai alaman na ƙira mishi ita, banyi nawa ba na danna mata ƙira nasaka a handsfree, ae kuwa kaman wanda take zaman jira kuwa naji charaf ta ɗauka, "A.G nah jikin ne? Nakasa bacci wallahi inata tunanin jikinka", naji muryan mummy, nine nayi saurin amsa mata da "mummy wallahi jikin ne, shine yace na ƙira ki", na faɗa ina kuka, "subhanallahi A.G nah kajina" muryan Daddy ne naji, bayan najiyo muryan mummy tana kuka a gefe.

Lumshe idon shi yayi ya buɗe yana ɗaga kai alaman yanaji, da ƙyar kuma yasake cewa, "mu..mmy ki..zo, mat.....aa nah, ya.....ata, mummy ki...zo".

Muryan Daddy naji yana cewa, "Ayshaa kashe wayan ki ƙira M.G ku wuce asibiti", jiki na rawa na kashe wayan, ƙiran M.G na fara amma sai naji shi number busy, ashe ina kashe wayan Daddy kuma sai ya hau ƙiran shi, ae watsi nayi da wayan na fice a ɗakin da gudu, buɗe ƙofan parlon nayi kawai na kama hanyar side ɗin su M.G ina kuka ina tafiya gudu-gudu, ban ƙarasa ba naga ya buɗe ƙofan parlon su yana fitowa hannun shi riƙe da jallabiya yana sakawa, bayan shi kuma heedayah ce riƙe da key ɗin motan shi, ganin suna tahowa sai kuma na juya gidan mu da gudu.

Har ɗakina suka shigo dukkan su inda A.G yake yashe a ƙasa yana ta kokuwa da numfashi, duk fuskan shin nan yayi wani ja sosai, kuka na sake fashewa da shi na durƙusa ina ƙoƙarin riƙo shi, gefe ɗaya kuma nasreen ta fashe da kuka, ɗaukan ta heedayah tayi tana rarrashi, M.G kuma na taimaka mishi muka ɗaga A.G, rungume shi yayi mukayi mota da shi, daga chan heedayah ta fito mun da dogon hijabi nasaka don na manta ma wannan kayan baccin ne kawai a jikina, baya na shige na rungume kan A.G a jikina ina kuka, heedayah M.G yace ta rufe gidan mu ta wuce da Nasreen gidan su, taso bin mu amma ya hana, haka mukaja muka tafi da gudu zuwa asibitin.

Muna shiga suka wuce emergency da A.G nah, nidai kuka kawai nake ta zabgawa, muna shiga wayan daddy ya sake shigowa wayan M.G, ɗauka yayi sukayi magana da Daddy, daga nan ya miƙo mun wayan yace na riƙe, bayan wani lokaci aka maida shi wani ɗaki, sakawa A.G oxygen aka yi, da ƙyar numfashina yake tafiya daidai, ganin yadda A.G yake shan wahala, sai naƙara tsorita da ciwon asthma, ido na yana kanshi har zuwa ƙarfe huɗu saura, lokacin sai na fara jin ƙaran sautin Oxygen ɗin yana fita da ban, da sauri wasu nurses guda biyu suka zo kanshi, M.G kuma yayi waje ya ƙira Dr, tare suka shigo yana mishi magana suna tahowa tare, nidai sanyi naji yana rufe ni sai na fita a ɗakin, na neme kujera na zauna.

Huɗu yana cika dai-dai kaman wanda aka tsabureni na miƙe tsaye n shige ɗakin da aka kwantar da A.G, ina shiga naga nurses ɗin nan suna rirriƙe M.G dayake shirin faɗawa kan A.G, zuciyana ne naji ya tsinke, ɗago da kaina nayi na ƙurawa A.G ido danaga an cire mishi oxygen yana bacci, azuciyata nayi hamdala nace ya samu bacci, sannanna maida kallona kan M.G dayake wani irin kukan fitan hankali, muryana yana ɗan rawa nace, "Yasamu bacci ne? Numfashin ya ɗan lafa ko"? Na tambayi Dr da yake tsaye akan A.G, ɗaga mun kai yayi alaman hakane, sannan na maida kaina kan M.G nace, "Yayah M.G kayi shiru mana tunda kaga ae da sauƙi tunda har ya samu bacci", na faɗa ina shigowa ɗakin, amma lokaci ɗaya naja na tsaya bakina a buɗe jin abinda M.G yake faɗa muryan shi a sama kaman muryan shi zai cika ɗakin ya fasa, "Ayshaa Ɗan'uwana yayi baccin da babu farkawa ne, A.G nah ya tafi ya barni da ƙalubalen duniya, A.G na ya rasu ya barni alaokacin danake tsananin buƙatanshi".

Ido na mayar an A.G domin na gasganta abunda M.G yake faɗa, amma sai banga alaman ya rasu ba, domin ni dai naga kaman numfashi yake a nutse, sai kuma wayan shi da yake ringing a hannu na na kallah, DADDYna gani akan screen ɗin, ban wani ja ba na ɗaga wayan, har lokacin kukan Mummy nakeji, muryan Daddy cike da damuwa yace, "M.G yyh jikin A.G ɗin, an samu numfashin ya lafa? Ga mamanku ta ɗaga mun hankali akan mu taho a daren nan, amma yanzu inaga zamu taho kawai", yana gama faɗin haka na ji bakina ya buɗe da ƙarfi nace, "Daddy A.G nah ya rasu inji M.G, mijina wai ya rasu inji M.G," kaman kuma an zabure ni sai na kashe wayan bayan naji sautin salatin Daddy da ihunn mummy, ido na yana kullewa don azaban zafi haka nasaka number yayah Ahmad nayi dialing, yana ɗauka naji yace, "M.G yyh dai, meya faru"? "Yayah mijinane wai ya rasu inji M.G, A.G nane a kwance wai ya rasu inji M.G", shima salatin daya sakane na yi sauri na kashe wayan ina zare ido kaman kuncacciya, layin ummie na kawai nasaka, amma har ya gama ringing ba'a ɗauka ba, chan sai nasaka na hafsy na ƙira, yana farawa kuwa ta ɗauka, sallama a bakinta amma ban barta ta gama ba, "ummie na A.G ya rasu inji M.G, ummie kizo mijina ya rasu inji M.G" salati hafsy ta saka tana ƙwalawa ummie ƙira da take toilet, kashe wayan nayi kaman sukuwa, lokacin kuma ƙiran Daddy da yake shigowa ya sake shiga, Miƙawa M.G wayan nayi ina nufan kan Gawan Mijina, "wai da gaske ne mijina ya rasu"? Iya ƙarfina nayi wannan tambayan Aunty nice, wani tambaya mai ciwo wanda amsan shi yafi komai ciwo a zuciyata da rayuwata.

A lokacin hajiya Ayshaa tsayawa tayi da bani labarin,domin wani irin ciwon rashin A.G daya zo mata alokacin, wanda muka haɗu mukayi kukan da muke yawan yi idan mun tuna mazajen mu da rasuwar su, wanda shine ƙarfin tarayyah da ita, nayi kuka a ranan na tuna nawa mijin.

Wannan shafin na sadaukar wa duk wacce ta rasa mijinta ko ɗanta daya rasu da ciwon asthma, na sadaukar wa duk matar da ta rasa mijinta a shekarunsu kaɗan na rayuwar aure 😭😭😭😭😭😭Irin wannan mutuwa yana da ciwo yana da taɓa zuciya, tabbas naji mutuwar A.G kwatankwacin yadda naji mutuwar nawa mijin 😭😭😭

Allah ka haskaka kabarin A.G, ka haskaka kabarin Nuhu, karaya mana abunda suka bari cikin amincinka □□□□□□□□😭😭😭😭

Allah kajiƙan yan'uwana da suka rasu ɗauke da ciwon asthma

Kassim Jama'are

Musa yawale

😭😭

NABEELAH ARABI

NUHU ARABI (Bappah)

KHADIJA AMINU GARBA (MAMAH)

ALLAH YA MUKU ALBARKA

Tabbas wannan rana munyi kuka, munyi kukan rashin Gwarzayen mazajen mu, mazajen da suka nuna mana ƙauna sama da kansu, nayi kukan tausayin kaina, nayi kukan tausayin Ayshaa,.....shin da gaske akwai wata mace a duniya data saura kamar ni da Ayshaa da kewar mijinta? Idan akwaita please ta nemi ni ta wannan number 08036181881, a zuciyata da tunani na kaman babu sai ni, amma dana haɗu da ayshaa sai naji akwai dai ɗaya kam bayan ni, Allah ya jiƙan mazajen mu Allah ya musu rahma,.... Da ƙyar muka rarrashi kanmu da kanmu, sannan na nemi ayshaa da mu bar wannan hiran a wannan ranan, amma sai tayi murmushi tace, "Aunty nice yanzu ma zamu fara kuma mu gama, kinfi kowa sanin duk yadda muka haɗu mukayi hira akan su sai mun koka, ballantana na yau akwai banbanci", hawayen ta ya sake biyo kan kuncinta, ganin haka ya saka na sunkuyar da kaina na bar kallon ta, shiru kaman babu mai sake tankawa a tsakanin mu, chan kuma sai na tsinkayi muryanta da yake rawa wanda yake ƙara raunana mun nawa zuciyar ta cigaba da bani labarin.

"Jikin gadon da gawan A.G na yake na ƙarasa, ido na ƙura a cikin shi don ganin ko yana numfashi, amma sai naga shiru, hannun shi da yake ɗaura akan cikin shi na ɗaga sama, sai kuma na mayar na ajiye, still dai A.G na bai motsa ba, murmushin da bai kai ciki ba nayi wanda har yau ban san dalilin hakan ba ko yin hakan, ido na mayar kan kyakkyawar fuskar shi da tayi wani fari sol, skin ɗin shi kaman idan an zuba ruwa bazai zauna ba tsabar santsi da sheƙin da naga yanayi, dab da fuskar shi nakai nawa fuskan, a hankali kaman wanda nakejin tsoron wani yaji ni nace, "A.G nah" naji shiru bai amsa ba, "mijina ka buɗe idonka kacewa kowa kana da rai, bacci ne kawai kakeyi," sai na kai hannu na kan cikina nace, "wannan babyn tana ciki, idan tazo duniya zatayi kuka batagan ka ba, zatayi kuka baka ɗauke ta ba, bazan iya bata haƙuri ba" sai na juyar da kaina gefe kaman ina neman wani abu, "Nasreen

zatayi kuka baka ɗauke ta ba, waye mummy zata gani idan baka nan? Gidan mu kake so na koma na zauna A.G? No bazan koma gida ba, gidan ka zan zauna, zan maka komai, zan ƙara addu'a Allah ya baka lafiya ka daina asthman nan bana son shi," sannan na kai hannu na kan fuskan shi ina shafawa, dai dai lokacin naji an dafa kafaɗa na, da sauri na ɗago kaina na kalli yayah da hawaye yake bin fuskan shi gefe ɗaya kuma yayah muhammad ne ya sunkuyar da kan shi ƙasa, nuna musu gawan A.G nayi nace, "mijina" juyawa yayah muhammad yayi ya bar ɗakin, matsowa dab dani yayah Ahmad yayi ya riƙo ni jikin shi, amma sai na turje na sake nuna mishi gawan A.G nace, "mijina yayi bacci, amma M.G ya rikice yace wai ya rasu, matso ka duba fuskan shi kataɓa ganin wanda ya rasu mai kyau? Yayah mijina bai rasu ba bacci yakeyi, ina son mijina, ina son ya tashi yanzu ku gani, kada a yadda da maganan M.G aje a bunne shi na shiga uku", kuka sosai Yayah Ahmad yake a lokacin, amma ni ko tarfin hawaye babu a ido na.

"innalillahi wa'innah ilaihir raji'un, dana san zanji ciwo da tashin hankali da ban rubuta book ɗinnan ba, wannan page yana bani wuyan rubutawa 😭😭😭😭😭 Ina jin ciwo sosai a zuciyata, how i wish kun san ciwo da zafin da nakeji a yanzu da nake rubuta wannan page ɗin? Nasani ba kowa bane yasani, kuma nayi imani da Allah ba kowacce mace bace da mijinta ya rasu tasan zafin irin yadda nakeji, don kowa da irin rayuwar shi, kowa da irin ƙaunar da aka mishi, kowa da irin ƙalubalen rayuwar da ya shiga bayan mutuwar mijinshi 😭😭😭😭😭 Kana kuka ne sbd ciwon mutuwar, da kuma rayuwar bayan mutuwan 😭😭😭

Riƙo hannu na Yayah Ahmad yayi yana rarrashina da mu fita waje Dr zasu sake dubawa suga ko yana raye, don ba lallai bane ma ya rasun, kaɗa kaina nayi alaman hakan ne, sai na maida kaina kan Dr da yake tsaye ya ƙura mun ido, gefen shi wani Dr ne daban da ban san lokacin da ya shigo ba, sai nurses guda biyu da suke tsaye, "Dr kuzo ku duba mun mijina, hala ma dogon suma yayi, don nasan yana sona, bazai rasu ba yanzu bayan ban haihu ba", ina faɗa suna ɗaga mun kai alaman zasu zo su duba shi, haka na fita nabi bayan yayah Ahmad muka bar ɗakin.

Muna fita muka samu su Yayah muhammaɗ suna zazzaune, M.G kanshi ɗaure akan kafaɗan wani abokin su ɗan bauchi yana ta rarrashin shi, gefe ɗaya kuma Yayah muhammad ne rungume da Aunty B da taketa kuka yana rarrashinta, Aunty J kuma ta kife kanta akan kujera tana tsugune a ƙasa tana kuka, hannun ta ɗaya rungume da babyn ta, matsuwa nayi kusa da su ina cewa, "bai rasu ba dai, yanzu Dr yazo da wani Dr zasu sake duba shi, haba A.G nah ne zai rasu, suma yayi, yanzu zasu farkar da shi mu tafi gida, yana tashi ma ni bauchi zamu tafi tsoron Abujan ma

nakeyi, zan gayawa su Daddy zamu gudu bauchi mu ɓuya, Abujah kam mutuwa akeyi", ganin surutu na ɗin ya fara yawa sai Yayah muhammad ya sake Aunty B yazo ya rungumeni, "Ayshaa tou muje gida ki shiryah kayanki kawai mu wuce Bauchi da zaran A.G ya farka, inaga hakan yafi kamata" murmushi nayi na riƙo hannun shi nace, "mutafi kam bana son ganin asibiti ma, kawai mutafi" sannan na juya na dubi Yayah Ahmad da ya kasa daurewa ya kifa kanshi a jikin bangon wurin yana kuka kaman ran shi zai fita, murmushi nayi nace, "yayah barrister kadaina kuka zafa mu gudu mu bar Abujan nan, kuma ku tattaro kayanku kubar garin, kajira Drs ɗin su gama duba shi mu kam zamu wuce gida," ae kuwa kaman na tsokano M.G sai yafara wani irin kuka kaman zai sandare a wurin har yasa naji jikina yayi sanyi, amma sai yayah Muhammad ya riƙoni su Aunty suka bimu a baya muka fita, gaban mota na shiga su kuma suna baya, daga shi har su hawaye sukeyi amma ni kam ko gezau, sai zare ido kawai nake ina kallon hanya, muna dab da zamu shiga unguwar mu sai ga ƙiran ummie na ya shigo wayan yayah muhammad, akan idona ƙiran ya shigo, saboda haka ganin bazai ɗaga ba yasaka na ɗauki wayan na ɗaga, kuka naji tana yi tana tambayan yayah, wai yayah nake fatan ɗai babu abunda ya sameni? Murya na da yake asama na kasa daidaita shi nace, "ummie ae ba rasuwa yayi ba, yanzu ma zamu gudu mu bar Abujan ne kada ace kuma ya rasu, kinga idan mun gudo bauchi ae zaku ɓoye mu keda mummy ko? A.G nah yana kwance shiru baya motsi, shine M.G daya rikice yace wai ya rasu ne, ae na ƙiraki nagaya miki yace ya rasu sai hafsy ta ɗauka, ae bai rasu ba, yayah ma yagani ae", ina faɗa na juya ina kallon yayah da yake tuƙi hawaye yana zuba mishi, "yayah ae kaga mijina bai rasu ba ko?" ɗaga kai yayi alaman hakane, dariya nayi na cigaba, "ummie yayah ma ae yace bai rasuba, bakiga yadda yayi kyau ba, kinsan mijina mai kyau ne fari, ina ae bai rasu ba".....kuka sosai ummie ta fashe da shi, sai kuma naji muryan mamah a gefe tanata salati, Abba ne ya karɓi wayan daga baya yace, "Ayshaa tah" jin muryan shi yasa naji wani hawaye mai ɗan ɗumi ya taho mun a kan kunci na, "Abba mijina bai rasu ba, kawai M.G ne ya gigice da ciwon yace wai ya rasu"..... Hawayen ne suka ƙara zubo mun, a hankali Abba ya sake ƙiran sunana yace, "Aysha ki ringa faɗin Innalillahi wa'innah ilaihir raji'un" ɗaga kai nayi kaman yana gani na, amma bance komai ba, ganin mun shiga gate ɗin gidan mu yasaka na miƙawa yayah wayan shi, saboda hango heedayah da nayi ta fito hannun ta ɗauke da nasreen da taketa kuka, da ƙyar na jira yayah ya buɗe ƙofan na fita, wurinta naje ina kallon yadda duk ta wani fige ta birkice, "Aunty yayah jikin Yayah A.G"? Murmushi nayi nace, "yayi bacci ae, shine mijinki ya burkice yana ta ihu yana kuka wai mijina ya rasu, ta yayah ma zai rasu kowa mijinta yana nan"? Miƙa hannu nayi na karɓi nasreen muƙa shige parlour mu, har ɗakina muka shige da su Aunty muka bar yayah a parlour yana waya da su Abbah.

Bakin gado na zauna ina bawa nasreen nono, da ƙyar ta kama tana ta sauƙe ajiyan zuciya, kallon su nayi suna haɗa mana kaya suna kuka, heedayah kuma sai

tambayan su takeyi wai meya faru ne? Meyasa suke haɗa mana kaya? Da taga bazasu bata amsan da takeso ba ne yasa ta dawo kusa da ni, "Aunty ina zakuje da kaya mai yawa haka? Yyh jikin yayah na yake"?

Murmushi nayi nace, "kema kije ki haɗa kayan ki bauchi zamu koma Abujan nan gaba ɗaya babu alkhairi a zaman shi, yanzu Drs ɗin zasu farfaɗo da shi sai a wuce, kowa ma ya amince", na faɗa ina kallon su Aunty da suka gama haɗa kayan.

Kuka heedayah takeyi sosai ta fara ƙiran wayan Mummy, daga nan ta biyoni parlour inda muka samu yayah zaune yana ta kuka, dafa ƙirji heedayah tayi tace, "yayah meya faru ne kam kowa bai ce mun komai ba, M.G kuma yaƙi ƙirana", kallonta yayi sannan yayi dauriyan ce mata itqma ta haɗa kaya bauchi za'a mayar da A.G, idan ya samu sauƙi sai a dawo, hankalin Mummy zaifi kwanciya, ɗaga kai tayi alaman hakane, sannan ta wuce side ɗinta ta haɗa kayan M.G da nata da kuma na Affan.

Duk yadda naso su bari na haɗa kayan A.G sai yayah yace na bari akwai kaya a bauchi ae, haka na haƙura muka zauna a parlour, shi kuma ya fice waje yana ta amsa waya.

A wannan baƙin daren ne kafin six na asuba Abba da Daddy har Alhaji Inuwa sunyi arranging tahowar mu bauchi ta jirgi, an tsayar 8:00am zam shigo bauchi, zuwa 10:00am za'a kai A.G nah gidan shi na gaskiya, ni kuma gefe ɗaya burkitan kai yakasa sawa na gane hakan sai surutai nakeyi, gashi babu wani babba a wurin da zai sakani nutsuwa, suma su Auntyn duk ba sanin abunda ya kamata suyi mun ba sukeyi, duk suma sun burkice iya irin nasu, yayau na kuma tsantsan tausaya mun yasaka suka kasa taɓuka komai.

Duk yadda aka so bamu shiga bauchi ba sai 9:00am, kuma babu wanda ya nuna alaman da na fahimci gawan A.G yana jirgin, muna isa kuma mu aka fara gaba damu kafin fitar da gawan, direct gidan su A.G da yake fadaman mada muka wuce, jama'a kaman an haɗa garin bauchi ne a ƙofar gidan ya saka na fara jin yankewar zuciya, ido nafara zarewa ina kallon mutan.

Gate ɗin gidan a buɗe haka muka shiga cikin gidan har inda ake packing motocin gida muka tsaya, jikinane naji ya ɗauki rawa lokaci ɗaya, juyawa nayi na kalli Aunty B da ta rufe idonta da hijabin ta tana kuka, dawo da kaina nayi gefen Aunty J na ƙura mata ido, ita ma kwantar da kanta tayi jikin murfin ƙofan tana kuka, chan naji muryan heedaya a rikice tana tambayan driver, "Malam Ali waye ya rasu a gidan mu mukazo? Alhaji ne ya rasu"? Hankali na yana kan driver naji me zaice amma sai kawai ya kifar da kanshi kan stearing motan ya fashe da kuka, ae buɗe motan tayi da gudu-gudu ta fice, a wurin ma ta ajiye Affan tana ƙwala ƙiran sunan Mummy tayi cikin gidan.

Buɗewa mukayi dukkan mu muka fito, hannu Aunty J tasaka ta karɓi nasreen a hannu na, ban ƙiba na bata ta haɗa da nata muka shige ciki, bin mutane kawai nakeyi da kallo suna ta kuka, barin ma da suka ganmu mum shigo, nidai banyi kuka ba har lokacin sai zare ido ina kallon mutane, parlour mummy muka shige dukkan mu, inda daga wurin nake jiwo muryan Heedayah tana kuka tana tambayan waye ne ya rasu a gaya mata, ban bi takanta ba na ƙurawa ummie da ke rungume da hafsy, kuka hafsy takeyi gefe ɗaya kuma ga yan gidan mu, gasu Gogho ƙanwar ummie maman zainab, ga zainab, sai kuma maryam a gefenta, hajiya ummah, mamah, mamie, ga kuma dangin Abba dana ummie cike a parlour, cinyar ummie Aunty B da Aunty J suka saka kansu suna kuka, Goggo kuma ta amshi nasreen daga hannun Aunty J, nidai kasa ɗaga ƙafa na nayi daga inda nake, dukkan illahirin jikina rawa yakeyi.

A shigowar mu na hango Daddy a waje, tou mummy ce data ji jikin A.G ta rasu? Sai kuma tunani na ya tsaya daidai lokacin da mummy ta fito daga bedroom ɗin ta Huda na biye da ita a baya, kasa rufe bakina nayi wanda nake shirin tambayan waye ya rasu?

Rungumeni naji tayi ta fashe da wani irin kuka mai taɓa zuciya, "Ayshaa an mana mutuwa ni da ke, tabbas rasuwar A.G ni da ke akayiwa, innalillahi wa'innah ilaihir raji'un", naji ta faɗa tana ƙara rungume ni, Huda ma ta rungume mu tana kuka, ɗaga kaina nayi na dubi ummie na da ta ƙura mun ido tana share hawayenta, wani ƙararrawa mai ƙaran gaske naji yana kaɗawa a ƙwaƙwalwata, wani abu mai zafi da ƙarfi kuma ya taho tun daga tsakar kaina har ɗan yatsan ƙafa na, ido na namayar kan yatsan ƙafa na ɗin don ganin menene, amma banga komai ba, maida kaina nayi kan mummy nasaka duka hannaye na na ɗago ta, "A.G nane ya rasu"? Na tambayeta, kuka ta fashe bata ce komai ba, ido na mayar kan Hida na sake tambayanta, "mijinane ya rasu muna hanya"? Nan ma kuka takeyi ta ƙara rungume ni.

Juyawa nayi na kalli ummie, daga inda nake na biɗe bakina da ƙarfi nace, "Ummie!!!" na ƙirata da ƙarfi, sannan nace, "ke kaɗai zaki iya gayamun hankalina da tunani na su fahimta", ido na ƙura mata.

Tashi tayi daga inda take tazo har gabana, hannunta ta saka ta riƙo hannu na, inda take zaune ta kaini da nufin na zauna, girgiza kai nayi sannan nace, "bazan iya zama ba ummie,"

Kujera aka nuna mata kusa da hajiya ummah akan na zauna, har wurin ta kaini na zauna ita kuma ta zauna a gefena hannun kujeran, dafani tayi a hankali tace, "ki ringa furta innalillahi wa'innah ilaihir raji'un", kallonta nayi alaman ita nake jira, hawayenta ta share tacigaba, "kiyi haƙuri Aysha nah, Allah daya fimu son Aminu shi ya karɓi abun shi tun daren jiya, bawai kuna hanya bane ya rasu tun jiya Aminu ya amsa ƙiran ubangiji, kiyi haƙuri ki rungumi irin naki ƙaddaran, kiyi haƙuri da juriya irin yadda addinin mu ya koyar da mu, ki dubi Mummy wacce ta haife shima ta karɓi ƙaddaran ta, kiyi haƙuri Aminu yanzu addu'ar ku ita yake buƙata".

Kallon ummie nayi na tsawon lokaci mai tsawon gaske, daba don ita ta haifeni ba, kuma nasan dattijan takarta da gaskiyarta, yau dana ce ko dai ummie ta samu rauni ne a ƙwaƙwalwarta, amma sanin dattakunta da girmanta gareni nasan bazata mun ƙaryah ba, kenan dai tabbas A.G na ya barni, A.G na ya barni bari na har abada, A.G na bazan ƙara ganin shi ba, bazan ƙara taɓa jikin shi ba, baxan ƙara jin muryan shi ba, mutuwar na dai da akeyi itace yau A.G na yayi, da sauri na ɗaga kai na kalli jama'ar da suke parlour suna kuka, bance komai ba banyi kukan ba, ido kawai na ƙurawa nasreen da take rungume a hannun Mamah da ta karɓa a hannun Goggo, na daɗe ina kallonta ban san tunanin me nakeyi ba, chan na mayar da kallona kan hafsy da take rungume jikin su Aunty B suna kuka, maida kaina nayi kan Mummy da gaba ɗaya ta firgice, Huda ma kuka takeyi tana rungume da Mummy.

Kallon kyakkyawar fuskar ummie na nayi na tsawon lokaci, babu abunda na iya cewa, sai kallon su kawai nakeyi suna kuka, idan na kalli wannan sai na kalli wannan, ina ma zan iya jin kukan yazo mun, amma abu ya gagara.

Tsawon lokaci muka fara jin hayani a waje alamar an taho da gawar A.G gidan kenan, kuka ne ya sake tashi a parlour, Mummy ta miƙe da sauri zata fice, amma wata yakombonta ta bada umurnin a riƙeta tukun, kuka sosai sukeyi amma banda ni.

Daga baya Hassan mijin Huda ne ya shigo, yace mummy wai tazo inji Alhaji, Goggo ce da sai a lokacin na ganta ta kamo hannun mummy suka fice, daga baya akazo akace muzo parlour Abba dasu Huda da Heedayah, Ummie a lokacin ta riƙo hannu na ta miƙawa mamah akan muje tare, haka na bi bayan Mamah muka fice zalam zalam ina binta, babu uhm babu ah'ah, A gefen dinning ɗin Daddy na hango gawan A.G na kwance akan tabarma, an mishi wanka an saka mishi kayan gado, Gefen shi Alhaji ne sai Dadda, ga Daddy da Mummy duk a wurin, alama dai addu'a suke mishi, wurin ƙafafuwan shi kuma M.G ne yashe a wurin ya kifa kanshi daidai ƙafan A.G, juyawa nayi gefe sai naga Abba na dasu yaya a zaune a cikin parlour, kasa yin gaba nayi na ƙurawa Abba na ido, a hankali naga ya taso ya taho har inda nake tsaye, hannun shi duka ya riƙo ni ya wuce dani har inda gawan A.G yake kwance, yayah muhammad yana mara mana baya, gefe ɗaya kuma yayah Ahmad ya kwantar da kanshi yana kuka anata bashi haƙuri.

Tsugunawa nayi a gaban gawan mijina, Abba yana riƙe da hannu nah, ɗago ido Daddy yayi muka haɗa ido, idon shi duk sun kumbura yayi kuka kaman ba namiji ba, "sannu baiwar Allah, sannu Ayshaa, matso kiyiwa mijinki addu'ar ban kwana", muryan Alhaji inuwa naji yana mun magana, kallon shi nayi na sake maida kallona kan A.G, buɗe fuskan shi sukayi bayan an yaye mayafin da yake rufe da shi.

Kuka Mummy tafara tana jera mishi addu'o'i, "nayafeka Aminu nah, nayafe maka duniya da lahira, dama ni baka taɓa mun komai ba Muhammad Aminullah, idan ka mun ma na yafe maka, Allah ya karβi baƙuncinka Aminu na, Allah yasa kayi ƙarshe mai kyau, Allah yasa ƙarshen wahalar kane Aminu nah, nikan na yafe maka, Allah ya kula da bayanka, Allah ya raya abunda ka tafi ka bari cikin aminci, Aminu na maka alƙawarin kula da abunda Allah ya bar maka har ƙarshen numfashi na, zan sota tamkar yadda na soka ɗana, innalillahi wa'inna ilaihir raji'un" mummy ta furta da ƙarfi tana kwanciya a jikin shi, duk dauriya irin na Alhaji inuwa sai da ya share hawaye, rungumeta Daddy yayi, Huda da heedaya ma addu'a suka mishi, amma dai huda ce ƙarfin yin, heedayah kam kukanta kawai takeyi.

Hannu na na ɗaura akan fuskan A.G, na ƙura mishi ido ina jin wasu daga kalaman shi suna dawo mun cikin kaina, bakina nake son buɗewa amma sai naji wani abu yana tokare mun bakin, muryan Daddy na ji yana cewa "ki mishi addu'a Ayshaa za'a fita da shi ne."

Ɗago kai nayi da sauri nace, "mijina ɗin za'a tafi da shi?" sun kuyar da kai Daddy yayi yana share hawaye, sai Abba ne ya mun magana a hankali yace "addu'a zaki mishi magana Ayshaa ta"

Dawo da kaina nayi kan fuskar Abba, sannan naji wani nutsuwa yazo mun lokacin da Abba ya ɗaga mun kai alaman nayi addu'an.

Bakina ne ya buɗe maji na furta, "Innalillahi wa'innah ilaihir raji'un, Allahummah inna (Muhammad Aminu) fee thimmatika, wa habli jiwaarika, faqihi min fitnatil - qabei, wa 'athaabin - naari, wa 'anta 'ahlul - wafaa'i wal haqqi - ghafoorur - raheem.

Allahummaghfur lahu warhamhu, wa 'aafihi, wa'fu 'anhu wa'akrim nuzulahu, wa wassi mudkhalahu, waghsilhi bil maa'i waththalji walbaradi, wa naqqihi minal-khataayaa kamaa naqqaytath-thawbal -abyadha minal - danasi, wa'abdihu, daaran khayran min daarihi, wa ahlan khayran min 'ahlihi, wazawjan khairan min zawjihi, wa'adkhilhul jannataa, wa 'a'ithhu min 'athaabil qabri wa athabin -naar.

Allah ya baka ikon amsa tambayar kabari.

Allah ya haɗaka da mala'ikun rahma mijina, Allah yasa ka huta", kafin nagama mishi addu'a hawayena sun cika gaban riga na, zuba sukeyi kaman ruwan pampo, rungume ni mummy tayi kawai dukkan mu muka fashe da kuka, lokacin kuma ake riƙe M.G don a ɗaga shi za'a ɗauki gawan A.G

Mutuwa rigar kowa, wannan book bawai soyayyah bace ta ja hankalina ga rubuta shi, gaskiya babu wani abu sai darasin ciki, book ne daya taɓa zuciyana kuma nayi imanin ya taɓa zuciyar mutane da dama, misali irin mugunta da asirin da akayi wa Goggo wurin rayuwar aurenta a gidan su M.G, anshiga hakkin uba da ɗa, an rabaƘaunar su an hana su zama tare, kuma duk macece sila,

Rayuwar gidan su Ayshaa shima ƙalu bale ne akan mu mata, mamie ta cutar da Ayshaa tun farkon labarin, ta rabata da wanda ya sota ta haɗa auren da yaarta, abun ɗubawan bawai rashin auren Aliyu bane damuwa, a'a raba tsakinin habiba da ayshaa shine muguntar da tayi, wanda habiba ba mai tsawon rayuwa bace, na uku muguntar da tayi a tsakanin rayuwar auren A.G da Ayshaa, ta cutar da su ta hana musu jin daɗin zaman su, wanda a ƙarshe tana shirin jifan su da mummunan abu, sai kuma Allah yayi ikon shi ya ɗauki rayuwar A.G, duk fah sharrin na mace ne, mata me muke nema a duniya da babu wani buri a zuciyar mu illah mugunta.

Mu raba mata da miji

Mu raba ɗa da mahaifi

Mu raba ɗan'uwa da ɗan 'uwa

Mu raba uwa da ɗa

Mu nemi da ƙusar da rayuwar ɗan'uwan mu wai duk a matsayin kishi, tou ƙaryah ne ba kishi bane mugunta ne da kuma hassada, da kuma rashin tsorom Allah

Ya Allah ina roƙonka kasaka wannan littafi yaje har wurin mamie ko yʻarta Raliya. Ya Allah kasa ɗaya daga cikin su ta karanta, ko wata nasu ta karanta, yadda tabbas zata san duniya ta san me take ciki, Allah yasa ka mu fi ƙarfin zukatan mu, inda muke kuskure Allah ka shiryar damu □□😭😭

ALLAH KA KAI HASKE DA RAHMA KABARIN MIJINA DA MIJIN AYSHAA, ALLAH KAYI WA RAYUWAR YARANMU ALBARKA, ALLAH YADDA KA NUNAWA AYSHAA AUREN YʻARTA CIKIN LUMANA NIMA KABAWA TAWA YʻAR AURE NA MUTUNCI NA ALKHAIRI, ALLAH KABAWA NUHU NA LAFIYA DA DUKKAN MAI CUTAR SICKLER DA ASTHMA, ALLAH KABAWA KO WACCE MACE DA TA RASA MIJINTA HAKʻURI DA JURIYA □□□□□□□□😭😭😭😭

****

INA UWARGIDAYEN SUKE? NACE INA UWARGIDAYE MASU CAPACITY SUKE, IDAN BAKI YI MATSA GA MASU AUTHOURITY, NACE TSAYA IDAN BAKIYI GA AMARE MASU AUTHOURITY, IDAN KIN SHIRYAH GWANGWAJE SHINFIƊAR MAIGIDA, TOU KI KʻYALE YʻAN LOCALLITY KI MATSO KI SAYI NAKI, BEDSHEETS YʻAN GASKE, KU MATSO KU YAKʻI PORVERTY DAGA TASKAR HALIMA YISUF GWARZO, INA MAI TABBATAR MIKI IDAN KIN SHIMFIƊA ZAKI ZAMA MAI CAPACITY MAI AUTHOURITY, DOMIN KI WANKE ZUCIYAR MAIGIDA YA HASKAKA, MUNA AIKAWA DA SHI KO'INA A FAƊIN KʻASAR NAN.

DOMIN SAYEN ƊAYA KO SARI, KU TUNTUƁE NI TA WANNAN LAMBAR

08064586559

****

Masu Buƙatar Siyan Atamfa ɗaiɗai ko sari a farashi na rangwame, da masu order na anko kama daga dangin atamfa zuwa laces da Adire, ku garzaya zuwa ga shafin Halima.hz Collection (gidan Atamfa) a instgram ko ku tuntuɓe su direct ta whatsapp 07018098175.